IGIYAR ZATO.....□_

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(SABON TAKU)

[1:1] بسم الله الرحمن الرحيم

In the name of Allah, the Gracious, the Merciful.□

_*SHAFI NA DAYA_*

ZARIA

2004

Zaune nake a ‘dan tsukukun gefan kofar dakin mu. Gaba na kuwa wani tsohon kwano ne dake ‘dauke da sandararren tuwon dawa da miyar kuka koriya shar da

ita, ina ci ina korawa da ruwan bunu marar sukari, can gefe na kuwa su Alawiyya ne da Hinde sun barbaje suna afka lomar taliya yar mirji data sha manja sun yayyan ka tumatir da albasa a akai. Kuka na na hadiye ina ko’karin ‘karasa cin tuwon gaba na don sauri nake yi zan kai wa yayan mu abinci dake can tsallaken gaban gidan mu can yake bakanikan ci. Fitowar babar su Alawiyya ne yasanya ni hanzarin mikewa, Na dauke kwanon gaba na, Ai kuwa muna hada idanu ta zabga min harara wadda tazame mata jiki kullum sai ta min.

“Mayya! Aniyar ki ta biki. Kurwar mu kur wallahi, anyi gado awajen uwa. Da shegen idanu kamar na ungulu..”

Nai shigewa ta d’aki, Na baro Babar su Alawiyya wacce ake kira da Bintalo tana zuba min kwandon zagi. Na danne bacin rai na na dubi Innar mu dake tsintar hatsi a tire nace,

“Innaar mu bari naje na kai wa yaya abincin sa..”

Na karasa magana, hade da d’aukar wata fashasshiyar kular abincin mu wadda itace me kyau acikin kwanukan mu da ake zubawa yayanmu abinci. Innar mu tayi murmushi tana gyarawa autar mu kwanciya dake baccin ta hankali kwance, gefan zaninta ta sunce ta ciro naira hamsin wadda itace dama a kullin zanin duk ta kanannade ta mikomin,

“Ungo ki taho da man gyadan ashirin sai yajin goma, ki biya ta gurin ladiyo mai koko ki sayo koko da kosai na ashirin.”

Rissinawa nayi hannu biyu na karb’i kudin, idanuwa na suka kawo ruwa cikin tsantsar tausayi nace,

“Innar mu to ke mezaki ci? Kinbar mana tuwon ni da yaya Najib, koko da kosan kuma na Aminatu ne.”

“Banasan sakarci sanda naci abincin idanuwan ki biyu?”

Girgiza kai nayi alamun a’a. Kafin na janyo kodadden koren hijabi na daya zama tamkar na gado na zura shi cike da tausayin innar mu, Uwa kenan gwara muci ita ta zauna da yunwa har sai mun gama sanwar rana. Sallama nayi mata na fito kai na a kasa na wuce ta gaban bintalo ai kuwa ban gama maganar ta a zuci ba ta zubamin rankwashi ji kake .’kwas’.

Su Alawiyya da Hindatu suka tuntsire da dariya suna gasamin magana, share hawaye na nayi, domin inda sabo na saba da irin rayuwar gidan mu. Dakyar na karasa sauka daga benen gidan mu mune a saman karshe mu dasu Bintalo da Usaiba maman su Larai, wato dakuna na uku acikin d’akuna tara dake gidan. Domin kaf layinmu da unguwoyin gaban mu babu wanda bai san gidan mu ba, wanda akewa laqabi da ‘Gidan Mata Tara’.

HAYIN RIGASA MECHANICS

Ina tafe a hanya ina bitar haddar Suratul Yasin da za’a karba anjima a islamiyyar mu. Sauri nake yi na ‘karasa na kai wa yaya abincin sa. Cikin nutsuwa na ‘karasa wurin aikin su. Na gaggayshe da abokanan aikin su kafin na wuce wajen daya ke zama. Can ‘karkashin wata mota na hango shi yana gyara notinan taya. Yayi dumu dumu da bakin man fetur. Cike da murmushi na ‘karasa wajen sa. Cikin nutsuwa da girmamawa na dan durkusar da kaina yadda zai iya jiwo murya ta nace,

“Yayan mu! Sannu da aiki. Ga abincin ka.”

“Na’am Batoul! Sannun mu! Ya innar mu da auta?”

“Lapia lou Yayan mu. Bari naje nayo cefane.”

Ina gama fada na mike daga tsugunnan da nake, Yaya ya zura hannu a aljihu yana lalibo kudi. Nera sittin ya ciro duk sun dunkule da junan ya miko min naira arba’in ya maida ashirin din cikin aljihun sa. Na danne kukan daya tahomin ina kokarin mayar da kai na gefe dan kada Yayanmu ya gano yanayi na.

“Yayanmu ALLAH ya kara bud’i. Me zan siyo aciki?”

“Jia kin tambayeni kudin Omo ko? To kiciri goma ki sayo omon. Naira talatin din sai ki sayo abunda babu a gidan.”

Gyad’a kai nayi, Ina tunanin abunda babu,

“Shikenan zan sayo maggi mai tauraro na goma sai albasa da tumatir na sauran ashirin din. Nagode Allah ya saka da alkhairi ya ‘kara bud’i. Na tafi Yaya sai ka dawo.”

Sallama mukai dashi alokacin yana kokarin bude kular ‘dumamen tuwon jia dana kawo masa. Allah sarki Yayan mu bai ci komai ba ya fita daga gida tun asubah. Hanyar ‘karamar kasuwar sayar da kayan masarufin unguwar mu na nufa. Nan na hadu da Fadila babbar ‘kawata tana sauri itama da alama cefanon zata yo. Dan ‘daga murya nai yadda zata iya jiyo ni na shiga rafka mata kira ina hadawa da sassarfa don cinmata,

“Fadilah! Fadila!..!”

Juyowa tayi da sauri tana kallo na, fuskar ta dauke da murmushi. K’arasawa nayi ina haki. Ta dan dafa ni tana bubbuga bayana,

“Sannu tawaje na, daga ina kike?”

“Wallahi daga gida amman na biya na kaiwa Yayan mu abincin sa.”

Murmushi tayi hade da sakalo hannuwan ta ta wuyana muka ci gaba da tafiya a haka, Har muka karasa wajen Falalu mai kayan miya. Mutum hudu ne a gaban mu.

Dan haka muka koma daga gefe muna hira. Fadila ta sauke nannauyar ajiyar zucia tana yar carafke da duwatsun hannun ta,

“Tawaje na nakasa cire Yaya Najib a rai na”

Na muskuta kusa da ita ina mai kallon kwayar idanun ta dake fitar da hawaye, Na kasa gane wane irin so takeyiwa Yayan mu, gashi a gidan su an hanata kula shi ko nace Umman su ta hane ta da kula Yayan mu saboda su sunada rufin asiri mu kuma talakawa ne wanda bamuda tabbacin cin yau ko na gobe. Mahaifiyar ta irin iyayen nanne masu son ‘yayan su su shiga babban gidah. Gashi Yayan namu a babban ajin sakandire na biyu yake ko ‘karewa bai yi ba, ya dena zuwa ya koma sana’ar kanikanci (mechanics) ta haka yake d’auke mana wasu hidindimun na gidah dana makaranta duk kuwa da ta gwamnati muke yi. Ajiyar zuciar nima na sauke, cikin bata baki da kwantar mata da hankali nace,

“K’awata kenan, dan Allah ki ‘kara hak’uri ki fawwalawa ALLAH lamurran ki, na rantse maki da ALLAH idan har Yayan mu mijin ki ne to babu shakka sai anyi auren ku. Sannan ki sani Yayan mu fa har yanzu kinga ba gama makaranta yayi ba ko ince ya dakatar da zuwa makaranta saboda muna cikin halin rashi. Muma kuma duka duka yanzu muke a karamin aji na biyu. Kinga kuwa akwai sauran lokaci, Saura aji hudu mu gama makaranta muma. Kuma ma ai shekarun mu bana zamu cika sha hurhudu fa (14). Dan dai ma kece kawai kina son sa ne amman naga shekaru hudu fa ya bamu...”

Nagama fada Ina murmushi, Fadila ta rafka min hararar wasa tana tsuke baki hade da sakin tsaki,

“Wai an gaya miki kowa irin ak’idarsa ce da ke? Ke wannan yadama amman ni gaskia inason Yaya Najib kuma zan iya salwantar da komai don zama mallakin sa.”

Tabe baki nayi ina sake cuno shi gaba, narasa meyasa take son Yaya Najib, ko yaushe tasan so oho? Kuma ma dai ni abokan Yayan mu wallahi kallon yara nake musu. Ina cikin zancen zuci ashe har layi yazo kanmu. Fadila ta mike ta sayo kayan miyan sai gani nai ta miko min bakar leda cike da kayan miya, Na bita da kallon ‘karin bayani. Duk kuwa da nasan hakan ba farau bane awajen mu. Amman gaskia

ni kunya nake ji duk sanda tayi haka duk kuwa da nasan tasan mu ba masu hali bane.

“Dalla tashi mu tafi, kin ‘kuramin idanuwan ki irin na Ashwariyya rai!”

Daria nayi, domin duk sanda ta tanka idona da irin na Ashwariyya abun daria yake bani. Domin nasan ni dai ba jinsin indiyawa bace amman sosai mutane kemin kallon ruwa biyu ce ni. Saboda kyau da tsarin halitta da ALLAH yayoni dashi, wanda kwata kwata nafi yan gidan mu da yan d’akin mu kyau. A takai ce dai kamanni na daban. Na kan sha kuka na a duk sanda Bintalo ko sauran matan gidan mu suka tasani a gaba suna zagi na da aibata ni, koda yake wasunsu a gurin mazajen su suke jin cewar wai ni ba ‘yar baban mu bace, Ni shegiya ce. Nima nakan zauna wani sa’in na tambayi kai na ya akai na fita zakka a gidan mu? Amma kuma me? Ai ALLAH shine mamallakin kowa da komai, a haka ya yoni badan ya tsane ni ba. Cikin tafiya tunanin da nai fatata tai wani mugun radadi sakamon zazzafan mintsilin da Fadila ta sakarmin a dantsen hannu na na dama.

Hararar wasa na jefa mata hade da mika mata hannu na ta ja ni na tashi tsaye. Shagon Habulele store muka je na siyo maggi da da mai da omon da zan wanke uniform dina. Ganin harda rarar canji da na samu sakamakon kayan miyan da Fadila ta siya mana, hakan yasanya na tsaya na sai mana kifin talatin bayan na siyo koko da ‘kosan autar mu. Dadi kashe ni yau zamu ci dadi. A hanya naita yiwa Fadila godiar alkairin da take mana, Saboda kayan miyan yau data siya mana zai yi na nera dari, wanda idan har mun cancana shi zai mana sati munashan lagwada. Har k’ofar gidah Fadila ta rakani saboda gidan su na gaba da namu. Shigewa nai cikin gida fuska ta dauke da murmushi. Banbi takan surutan su Bintalo ba nai hayewa ta sama, dakin mu na shige baki na dauke da sallama.

Autar mu ce kawai xaune akan shamilalliyar katifar mu wadda kallo d’aya zakai mata kasan tayi shekaru a haka. Sai kwanukan mu a gefe nacin abinci. Gefe d’aya kuma kullin kayan mu ne a daddaure kamar kayan wanki. Tamkar dai a kurkin kaji. Domin kwata kwata dakin mu bai fi girman taku hudu na auni ba. Gashi mune a karshe, babu wundo kullum kamar dafamu akeyi Idan lokacin kwanciya yayi. Labulen dakin mu a jeme yake shima, Tun kafin a haifi autar mu makociyar mu inda Innar mu ke wankau a gidan itace ta baiwa Innar mu lokacin banfi shekaru takwas a duniya ba. Kallon Autar mu na sake yi ganin yadda ta dukunku ne tana sharbar kuka da jan majina, kusa da ita na je na janyo ta jiki na ina bubbuga bayan ta,

“Autar mu menene?”

Cikin rawar murya hade da jan majina tace dani,

“Yaya! Kashi ne ya matse ni naje bandaki don kasayar dashi. Ashe wai Kawu ila ya shigar da ruwan wankan sa, shine yai ta mun masifa na fito ko yashigo yaci ubana. Lokacin kuma ciki na ne yake ciwo. Koda na fito sai ya shiga ya dakko bokitin ya juye min ruwan a kai na. Sannan ya ‘kwallama innar mu kira kan ta biyashi ruwan sa tunda na ‘bata ruwan da warin kashi na, Kuma wallahi Yaya ni ko hanyar ruwan banyi ba, Wai lallai sai tabi layin tuk’a tuk’a (borehole) ta debo masa bazai yi amfani da ruwan rijiyar gidan nan ba, Kuma yaita zagin ta yana runkwashi na akai...”

Ta k’afarsa fada hade da fashewa da kuka. Nima kukan na shiga rerawa ina mai yin addua a zucia ta kan ALLAH ya yaye mana wannan ‘kuncin rayuwar da muke fama da ita shekara da shekaru,

“Yanzu ina Innar mu?”

“Ta tafi gangare debo masa ruwan.”

Hawayen dake yar tsere a fuska ta na goge, Sannan na mik’e na fice ina jaddadawa autar mu da taci koko da kosan dana siyo mata kafin mu dawo. Ficewa nayi cikin sauri nayi gangare inda tuk’a tuk’ar (borehole) yake. Can na hango Innar mu a layi, ta dan tsugunna tana duban wasu yara dake wasan yar gala-gala a gefe. Da sauri na nufi wajen ta,

“Innar mu.”

Juyowa tayi ta dube ni fuskar ta dauke da murmushi, dan sam bata ‘bata ranta a duk lokacin dasu Baba Ilah suka sauke mata kwandon rashin mutunci, Saboda batason ‘kimar su ta rage a idanun mu, Saboda ‘kannen uba da yayyun sa suma iyaye ne agare mu.

“Batoul..”

“Na’am Innar mu, Kije gidah zan taho da ruwan.”

Kad’a kai tayi, Sannan ta mike tana nunamin bokitin baba ilan. Tana tafe tana hada hanya saboda yunwa ga masifar su Baba ila da kullum da ita muke tashi. Mutum uku ne a gabana da haka da haka har layi yazo kai na. Na debo taf sannan na tafi gidah. Har cikin band’aki na kai masa, Sannan na haye sama abu na. Autar mu na gefe tana cin koko da kosan ta, Innar mu kuma tana yayyanka tumatir da albasa. Zama nai a bakin kofa ina bubbuga ‘kugu na sakamakon ciwon dayake min,

“Wash Allah Na!”

“Sannu Batoul.”

“Sannun mu Innar mu, Yawwa kayan miyan Fadila ce ta siya mana, nayi karambani na sayo kifi da kudin da Yaya ya bani.”

“Babu komai Batoul. Allah sarki Fadila angode mata Allah ya saka mata da alkhairi.”

“Ameen Innar mu”

Ba adau lokaci ba Innar mu ta gama abincin ranar mu, aka zubawa Yayan mu a roba autar mu takai masa. Mu kuma muka hadu muka ci namu a babban tire, domin haka muke cin abincin mu a tare ko Yayan mu yananan dashi ake haduwa aci. Na tattare dakin na share na kintsa komai sannan na debi uniform dina na makaranta da na autar mu nai kasa, na wanke tas banbi takan ba’ka’ken maganganun dasu Alawiyya ke gasamin ba.

Nasan mai karatu zai yi mamakin irin halin rayuwar da muke ciki a gidan mu, tamkar gidan haya dake tattare da yaruka kala kala. Toh zan baku takaitaccen tarihin mu.

ASALIN MU

(TAK’AITACCEN TARIHIN MU)

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😈□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□ *_IGIYAR ZATO_.....□_*

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(SABON TAKU)

_*SHAFI NA BIYU_*

ASALIN MU

(TAK’AITACCEN TARIHIN MU)

GWANI IDRIS NAJIBULLAH

Marigayi Gwani Idris Najibullah shine sunan mahaifin baban mu, Tare da matar sa Malama Halimatu Alkali. Ya kasance Malami a garin na kaduna, matar sa wato mahaifiyar su baban mu ita kadai ce mai dakin sa, ALLAH ya albarkace su da ya’ya shida: Kawu Ishaq, Kawu Dawood, Gwaggo Aminatu, Kawu Khamis, Sai mahaifin mu Salis, Sai Kawu ilyas wanda ake kira da baba ila shine karamin cikin su. Dukkanin yan dakin nasu a Zaria suke gidan mu d’aya, Banda Gwaggo Aminatu wadda ke aure a Kaduna. Gidan da muke ciki a Zaria gida ne na gado, wanda iyayen mu suka hada karfi da k’arfe suka siya. Dakuna tara ne acikin sa, kowanne guda d’aya d’aya ne ba ciki da parlor, Sai dakin baba ila dake ‘kasa shine mai ciki da parlor. Dukkanin yan uwan mahaifin mu a gidan suke da zama da matan su. Gidah ne mai hawa biyu, mune a saman karshe dake dakuna uku ne: Muna cikin d’aya, sauran biyun kuma Bintalo da y’ay’an ta na d’aya. Sai Usaiba mahaifiyar su Larai da Talatuwa, Usaiba matar Kawu Ishaq ta farko, sai amaryar sa Rabi’atu ita takansace juya ce bata haihuwa, sannan a dakin k’asa take, Dakuna uku na ‘kasan mu kuma, Kawu Dawood ne da matar sa Hafsatu sai yan biyun su Fareed da Fareedah. Sai Kawu Khamis da matar sa Innatuwa da Yayan su maza biyu ‘kanana wato Yusha’u da Bala. Sai dakin karshen saman nasu wanda Rabi’atu take ciki wato matar Kawu Ishaq ta biyu. Sai Kawu ila wanda ke dakunan ‘kasan karshe shi da matan sa Ummita da Hajara, dakin farko mai ciki da parlor Ummitan ce aciki wato matar sa tafarko Ita da tawagar yayanta su biyar dake yawan haihuwa take yi akub’i akubi. Sai d’aki dayan karshe na amaryar sa Hajara wadda ya aure ta bayan rasuwar mahaifin mu. Takasance tanada tsohon ciki wadda zata iya haife shi a kowanne lokaci saboda ya tsufa.

Marigayi Malam Salis Idris Najibullah shine mahaifin mu, Malama Kaltume Rabiu shine sunan mahaifiyar mu. Mahaifin mu kafin rasuwar sa ya kasance yanada mata biyu, Innar mu Kaltume sai Baba Zara'u wacce ake kira da Bintalo. Mahaifin mu dan asalin cikin garin Kaduna ne, almajiran ta takawo su shida yan uwan sa Zaria. Anan kuma ALLAH yayi zasuyi aure su hayayyafa. Mahaifin mu lokacin da suka fara sana'ar tashi zuwa garin katsina anan Allah yayo zai gamu da mahaifiyar mu a kauyen Shema. Mahaifiya ta irin fulanin nanne na jaub'awa, Mahaifin mu kuwa bahaushe ne gaba da baya. Domin kakan su ma kafin Allah yayi mai rasuwa ance a garin kano yake. Baba Bintalo y'ar uwar mahaifin mu ce, da kakanta da mahaifin baban mu uwa suka hada uba kuma kowanne da nasa. Auren nasu ma auren had'i ne ko nace auren zumunci ne, mahaifiyar mu kuwa itace matar sa ta ladan noma wato auren saurayi da budurwa. Mu bakwai ne awajen mahaifin mu, dakin mu mu uku ne, Yaya Najibulla wanda yaci sunan kakan baban mu ana kiran sa da Najib. Sai ni Fadimatuz-Zahra'u, wadda ake kira na da Batoul. Naci sunan mahaifiyar maman mu wadda ALLAH yayiwa rasuwa tun ina yar 'kankanuwa. Sai autar mu Aminatu. Wadda taci sunan Yayar mahaifin mu dake garin Kaduna. Sai 'ya'yan Bintalo guda hud'u, Yaya Zabba'u wacce ke aure a kauyen kod'e dake lahadin makole a Kano. Sai Alawiyyah da Hindatu wacce muke kira da Hinde, Sai autar su Hauwa.

Nasan mai karatu zai yi mamakin yawan gidan mu da kuma ahalin dake cikin sa, Toh kamar yadda kuka gani a baya, 'Gidan Mata Tara' gida ne mai dakuna guda tara. Sannan gidah ne wanda mahaifin mu da yan uwan sa su hudu suka hadu suka siya tun kafin a haife mu.

Mahaifin mu marigayi Malam Salis ya rasu ne shekaru bakwai da suka wuce lokacin autar mu Aminatu na jaririya, ya rasu ne akan hanyar sa ta zuwa gidah sakamakon hatsarin mota daya rutsa dasu, wata jibgegiyar gingimari ce tabi takan mashin din da yake kai alokacin yayo cefanen sunan kanwar mu Aminatu. Tundaga lokacin rayuwar mu ta canza zuwa halin rashi da kuma 'kunci.

Ashe haka 'kanne da yayyun uba suke? Tabbas mun shiga garari na rayuwa domin duk juya mana baya su kayi, abincin da za'a ci da rasuwar ma sai makwabta ne suke temakawa su bayar, sai da Gwaggo Aminatu tazo daga kaduna ne ta fuskanci halin da muke ciki, ta bamu hakuri sannan ta bayar akayo mana cefanen kayan abinci. Hakika Gwaggo Aminatu ita kadai ce mai kirki acikin yan uwan mahaifi mu, itace keyin mai yiwuwa don ganin ta tallafa mana ta tsaya har aka raba mana gado, mahaifin mu bashi da wata kadara fyace gidan da suka hada kudi suka saya shi da yan uwan sa, inda mahaifiyar mu da Bintalo kowanne ya kasance yanada rabo biyu biyu, tanada mata hudu mu kuma namiji daya mata biyu wato biyu kenan muma. Kowanne b'angare daga cikin mu ya tashi da daki d'aya d'aya. Sai da'ki d'aya

wanda Rabi’atu take ciki wato matar Kawu Ishaq ta biyu, shine ya zamto a tuminin takabar su Innar mu. Nasan zakuyi mamakin toh a'ina Yaya Najib yake kwana ko? Toh Yayanmu yana d'aura net a tsukukun kofar dakin mu ya kwanta a kan yar tabarmar sa, wani lokacin kuma yakan kwana a langa langar makarantar almajiran dake kallon kofar gidan mu.

Tunda mahaifin mu ya rasu mu kai sallama da farin ciki, Innar mu ta kanyi wankau a gidajen masu hannu da shuni saboda rufin asirin mu. Yaya Najib kuma ya kasance yana kanikanci don samo mana abunda zamu afa a baka. Ni da autar mu kuma mu kadai ne keyin makaranta, itama ta gwamnati, wanda Yaya Najib da yanayi ya dakatar saboda bamuda halin da duk kanin mu zamu dinga zuwa makaranta, duk kuwa da ta gwamnati ce, Amman akwai tsarabe tsaraben kudin fom nera talatin duk wata, ga kudin littafi da fensir. Hakan yasanya Yayanmu dakatar da zuwa makaranta ya fara sana’ar kanikanci dan kare mana mutuncin mu, sannan muna zuwa Islamiyya duk wata naira hamsin itama yayan mu ne ke biya mana kudin. Duk kuncin rayuwar nan muka d’ai ne muka shige ta banda Bintalo da ‘Yayan ta domin ita su Baba ila suna taimaka mata. Hakan yasanya na qudri niyyar tsayawa tsayin daka don yin karatu sosai, Saboda inaso nayi amfani da damata na cika mana burikan mu. Hakika ALLAH ya yoni da saurin ‘daukar karatu da kaifin basira, komai yawan karatu cikin sauk’i nake gane shi na kuma hadde shi, Shiysa haddar AlQur’ani da muke baya min wahala, cikin kankanin lokaci nake haddace ta akai na.

Tabbas ALLAH ya yoni da zatin halitta da kyakkyawar sura, Idan ka kalle ni dole ne ka sake kallo na duk kuwa da kankancin shekaru na amman halittar jiki na a tsare take, ko’ina ya cika, sannan na kasance mai wata irin kalar fata ni ba fara can ba ba kuma baka chakulet ba. Na kasance tsaka tsaki wadda turawa ke kira da ‘brown skin’. Inada tsawo sosai TubarkAllah. Idanuwana farare ne tas da su kamar ruwan madara, kwayar idanu na kuwa burawun ce sosai, sai yalwar gashin gira domin saura ka’dan su hade da juna, baki na dan mitsi-tsi ne jawur dashi kai kace jambaki na shafa, hanci na dogo ne sosai, ga kuma tawadar ALLAH a gefan hancin wanda ya kara kyawun fuska ta, Inada yalwataccen gashin kai tubarkAllah tamkar ni na kera abuna, har gadon bayana yake zuwa. Shekaru na goma sha hudu a dunia, inada sa’oina sosai a gidan mu, Wanda suke kula-kulen samari kamar tinkiyoyi. Idan kaga layin da ake a kofar gidan mu za kwi mamaki. Na kasance ina da dinbin samari, Sai dai basa kulani saboda rashin ganin fuskar hakan. Sannan Yayan mu ya hanani kula kowanne daga cikin su. Hakan ba damu na yayi ba domin nima banida ra’ayin kula samari yanxu. Nafison sai nayi karatu sosai, kuma inada burin auren wanda ya girmemi ni sosai domin agani na sunfi hankali da nutsuwa.

Duk abokanan Yaya Najib kallon yara nake musu, har a sujjada nake rok’on ALLAH karya sa na auri wanda ya girme mini da shekaru biyar, nafuson na auri wanda ya bani shekaru goma da yan kai saboda wasu dalilai na dana barwa zucia ta. A karamin aji na biyu nake a jiniya sakandire, wadda ake kira da gwanmen gels jiniya sakandire sukul, shekaru na sha hudu a duniya, banida burin da nake so na karanta irin karantar bangaren zallar ingilishi. Kuma har farfesa nake so na zama a fannin.

Gidan mu ya kasance mai dakuma tara aciki, kuma Idan ka lissafa matan auren dake ciki su tara ne, Hakan shi yasanya yan layin mu dama unguwoyin gaban mu, yiwa laqabi da gidan mu 'Gidan Mata Tara'

Wannan shine takaitaccen tarihin gidan mu dama nawa a tak’aice.

WASHE-GARI

Tun asubar fari dana tashi ban koma ba, bandaki nai hanzarin shiga nayo wanka na, saboda ban’daki d’aya ne kawai a gidan mu, kuma har layi ake yi akan sa. Ina gama wanka na na tado autar mu itama na sab’e mata jikin ta. Innar mu ma tayo nata bayan mun gama kintsawa. Uniform dinmu na zaro mana a karkashin kwallar da muke ajiye kwanukan abincin mu. Domin anan nake mana ninkin guga sai na zura su a leda na dora kwallar akai sai kuga kuma sun ninku tamkar an goge shi. Rogowar dumamen shinkafar jia muka ci, na koma gefe ina azkhar, Innar mu kuma tagama nata tuni, ta kunna yar rediyon ta tana jin labaran jamus. Autar mu kuma ta kishingid’e tana bacci, daria taba ni yadda ta kanannade tana baccin ta da yar ledar littattafan ta a hannu. Gyara mata kwanciyar nai yadda zata ji dad’in baccin ta. Haka dai nai ta jira har rediyon hannun Innar mu suka sanar da ‘karfe bakwai da ‘kwata’. Mikewa nayi na dan diga turaren ‘dan duwalar da shi kadai ne turaren mu na shafe jikina dashi. Tashin autar mu nayi ta kara wanko bakin ta da fuskar ta. Innar mu dake gefe ta mik’o min naira talatin,

“Ungo ki dau ashirin din ki barwa auta goman, ALLAH ya bada sa’ar karatu mai amfani.”

Rissinawa nayi na karba cike da girmamawa,

“Mungode Innar mu ALLAH ya ‘kara bud’i.”

“Innar mu mungode..”

Autar mu tafada tana rufe bakin ta sakamon hammar data taho mata, da alama baccin bai gama sakin ta ba.

Haka dai na tasa keyar ta muka fara sauka a bene, a lokacin su Alawiyya ke wanka, kamshin soyayyan kwai sai tashi yake daga dakin su. Da alama dashi zasu tafi makaranta. Nida autar mu ne kawai ke yin makarantar gwamnati. Su Alawiyya firabet suke zuwa duk tam dubu d’aya da dari biyar. Makarantar su d’aya da Fadila babbar k’awata. Ina ta jan hannun autar mu muka tafi makaranta, har ajin su na kaita sannan na wuce namu ajin. Koda aka fito birek awara da wainar fulawa na siya mana ni da autar mu. Goman ta kuma muka sai ruwan biyar da alawa. Ana tashin mu muka dauki hanyar gidah, Muna tafe a hanya ina bitar haddar Ashmawin da za’a karba an jima a islamiyya. Tun a kofar zauren kofar gidan mu muke jiyo hayaniyya, kai na na dafe da hannun dama ina girgiza shi, shin yau ko da suwa ake dambatuwa oho? Muna shiga na jiyo muryar usaibatu maman su Larai tana lailayo ashar tana durawa Bintalo. Nan dai suka hau gumirzin fada, Baba ila dake tsakar gidah ya janyo bokitin karfe ya zauna akai yana duban su da kallo. Sunne kai nayi a ‘kasa na fara hawa bene, muryar Baba ila na jiyo yana doka wa suna na kira,

“Batoul, Ke Batoul...”

Gaba na ya fadi jikake ‘ras, Shin menayi ni kuma?! Cikin rawar baki da jiki na fara komawa kasa ina nanata,

“Na’am Kawu...Gani!”

_____

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😈□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/Zyl7_eSgXuo

IGZ

SHAFI NA: UKU

•••

“Zo nan dan uban ki.”

Wani abu ya tokare min a wuya na, Na rasa mai yasa ala dole sai sun zagi Abban mu aduk lokacin da zasu mana fad’a. Jiki ba ‘karfi na ‘karasa kusa dashi na tsugunna tamkar mai neman gafara.

“Gani Kawu.”

Da alama bai masan meyasa ya kira ni ba, Domin sai cixan lebe yake alamun tunani. Babu abinda nayi masa wallahi, Kawai dai neman yadda zai dake ni yake yi ko tozarta Innar mu.

“Ruwan tuk’a tuk’a zaki ebo mani, kwarankwatsa idan kika da’de baki kawo ba sai na lahira yafi ki jin dadi.”

Na ‘kara kasa da kai na ina kukan zuci, duk ga yara nan ciki harda almajiran gidan amman babu wanda zai ebo masa ruwan sai ni? Ga yunwa dake addabar ciki na sai kukan agaji yake. Rankwashi ya sakar min a kai na nai saurin dafe wajen,

“Toh kawu a me zan ebo maka?”

“Tambaya ta kike? Lalle figegiyar mahaifiyar ku ta kara lalata ku.”

Mik’ewa yayi daga kan bokitin da yake zaune ya shiga zundumawa Innar mu kira ba ‘kakkautawa,

“Ke Kaltume, Kaltume, kina ina ne? Zaki fito ko sai na raunata shegiyar yar nan taki?”

Innar mu dake sallar nafila tai hanzarin sallamewa, cikin sauri tafi to tana dafe kirji,

“Kawun su, ya akai? Lefi ta maka? Dan Allah kayi mata hak’uri.”

A dai dai lokacin Usaiba tai kukan kura ta cakumi Bintalo tana yage dankwalin kanta, Tun d’axu suke fada.

“Shegiya mai kan ‘kwakwido.”

Cewar Usaiba ta fadawa Bintalo tana tsurtar da yawu a gefan Bintalo, Bintalo ta kece da daria tana nuna Usaiba da hannu,

“Shegiya wada, tamkar a kife ki da kwando, da ido aciki munafuka.”

Baba ila yaja tsaki yana nuna su da hannu,

“Ku fitar min a hanya, ko nai sanadin barin mutum anan gidan.”

Innar mu dake saukowa daga bene tafara girgiza kanta tana mai cewa da baba ila,

“Kayi musu hak’uri sharrin shed’an ne.”

Kawu ila ya kece da daria, hade da tafa hannaye kamar mace, Cikin kasakantaccen kallo ya dubi Innar mu,

“Toh munafuka algunguma, Sa’idinawa ana ruwa kuna irgawa masu bacci da ido d’aya.”

Innar mu tayi shiru kanta a ‘kasa, Bintalo ta buga zanin ta tana sakin gud’a,

“Kuji min annamimiya, Ke har kina da bakin magana? Dangin mayu uwar shegiya, acike nake da ke wallahi kika kuskura wata kalma tafito daga bakin ki sai na daka shegiyar yar ki.”

Innar mu tayi shiru kanta a ‘kasa, na goge hawayen da ya fara tsere a fuska ta. Wai shin yaushe zamu dandani farin ciki ne? Wannan wacce irin musibace ace yan uwan mahaifin ka na jini su dinga kyamatar ka suna la’antar ka.?

‘Ya ALLAH ka nuna min ranar da zan mai dawa su Kawu ila martani, domin nagaji da rashin ‘kauna da tozarcin da suke mana shekara da shekaru. Ameen ya hayyu ya qayyum.’

Na fa’da a zuciata ina mikewa tsaye.

Bokitin da ya mike akan sa na d’auka na fice cikin sauri, Usaiba dake gefe ta ja tsaki tai hayewar ta sama tana mai jifan su da munanan kalamai. Har naje tuk’a tuk’a na dawo ina jiyo muryar kawu ila yana zuba magana da alama da Innar mu yake domin ina jiyo ta tana bashi hak’uri, A soro na tsaya ina mai baje kunnuwana don jiyo zancen su,

“Ki jawa shegiyar ‘yar ki kunne, dan billahil azim idan ta sake nanata hali irin na yau sai nayi maganin ta. Kina jina ko?”

Innar mu tai hanzarin ka’da kanta alamar Eh kafin tace,

“Toh Kawun su! Insha Allahu ba zata kara ba, ayi mata uzuri.”

Hawaye na na goge, ina takaicin banyi komai ba, amman kusan kullum sai an laqaba min sharri kawai don Innar mu ta kaskantar da kanta taba su hak’uri, shi

yasa duk wata bolar su akan mu suke zuba ta. Shin a haka zamu dawwama cikin bakin ciki? Cikin zucia ta na shiga nanata,

‘Ya Raheem sa’adneey min kullu amr!’

Har bandaki na kai masa ruwan, sannan na koma bakin kofar dakin sa,

“Kawu! Ga ruwan na kawo”

“Annamimiya! ‘Bace min daga bakin kofa.”

Jiki ba kwari na mike nai hayewa ta saman mu. Cin karo nayi da Alawiyya ta yab’a jambaki a baki tana kwarkwasa, Bintalo dake gefen ta tana gyara mata mayafi tai bake bake a matattakalar benen da zan wuce. Na tsaya ina jiran ta wuce,

“Meye kike bin ta da kallo? Zaki ‘kasa da idanun ki ko sai na zuba miki mari?”

Matsawa nayi nesa dasu kai na a ‘kasa, Kawu Dawood ya fito daga dakin su yana aswaki, shi gaskia ba shida hayaniya irin tasu Kawu ila, Kawai dai shi matar sa ce zata nemo abinci ko da kuwa bara za tayo, babu inda zashi kullum yana kwance a daki tunda aka kore shi daga wajen aikin sa, cikin tab’e baki ya dubi Bintalo,

“Hayaniyar menene haka kuke yi?”

“Hayaniyar da akai ai da yawa, wacce daga ciki?”

Ya tofar da yawu ya cigaba da kuskure bakin sa kafin yace,

“Hayaniyar yanzu, Meyasa waccen yarinyar ke rakub’e a gefen ku? Ki bata hanya ta wuce mana.”

“Oh shegiyar can? Take Alawiyya tai a kafa ta kuma nemi ta bangaje ni kan naki matsa mata ta wuce..”

Ware idanuwa nayi jin sharrin da Bintalo ta hadamun. Cikin rawar murya nace,

“Kawu Dawood wallahi ban aikata ko d’aya daga ci...”

“Wuce ki tafi.”

Ya fadamin batare da yaji karashen magana ta ba, rabawa nayi ta gefan su na wuce dakin mu. Ina shiga na tarar da Innar mu tana lazimi, autar mu kuma tana aikin da aka basu a makaranta. Kayan makaranta na nacire na d’aura zani, wanka kawai nakeso nayi idan naci abinci. Kwanon gabanta Innar mu ta matso dashi kusa dani, budewa nayi ina murmushi, garin kwaki ne da mai da yaji. Na wanko hannu na a tukunyar bayan mu sannan na fara handama shi a baka bayan nayi bismillah. Ina gama cinyewa nai hamdala, nacaccen hijabi na na zura na dauki robar sosan wankan mu da sabulu irin ‘danyaka ‘dinnan na naira ashirin. Na hada da bokiti na sauka kasa don yin wanka. Da mutum acikin band’akin, hakan ya sanya na zauna a dandamalin kitchen din ‘kasa wanda matan Kawu ila ke amfani dashi. Bude kofar bandakin akai, na daga kai na don ganin wanda zai fito. Innatuwa ce tafuto wato matar Kawu Khamis, sai baje hanci take yi da alamun kashi tagama kasayarwa.

Shiga nayi bayan nayi adduar shiga bandaki, Wanka nayo nima na dan karkace na sau kashi na wanda dakyar yake fitowa sakamakon garin da naci, saman mu na haye, na shafa mai hade da sanya kayana dake karkashin kwallar mu, hijabin islamiyya na zura na dau yan littafan da muke yi, nayiwa Innar mu sallama kan sai na dawo, Tare da yiwa autar mu kashedin kar tayi latti. Saboda manya mu karfe uku muke tafiya yara kuma sai karfe hudu.

Ta gidan su Fadila na biya, a bakin gate din su muka hadu da ita tana sanya hijabi, Tana gani na ta dashare hakora, nayi murmushi ina tsaye a bakin kofa,

“Tawan..”

Fadila ta fadamin tana mikomin jakar ta, karfa nayi na rik’e ina jujjuya littafan hannu na,

“bestie ya kike? Kice yau baki makara ba kenan.”

Daria tayi tana harara ta,

“Dalla na dinga makarar kenan? Yauwa na taho miki da lessons din da akai mana yau, Idan aka fita free period sai na koya miki..”

“Nagode bestie! Allah ya bar zumuncin mu har gaban abadan.”

“Ameeen!”

A tare muka tafi, hannuwan mu saqale dana juna, Idan ka ganmu dole ne mu birge ka saboda yadda muke ba amintar mu hakkin ta, hakika Fadila ta xarce aminiya ta zama hamimiya kuma yar uwata ta jini mai son cigaba na, duk karatun da ake musu a makarantar su sai ta koya min, sannan tanada lesson teacher dake zuwa har gidah ya koya mata karatu ranar asabar da lahadi, shima dik sai ta koya min, B’angaren Islamia ma duk abunda bata gane ba ina koya mata, kasancewar ni ce monitan ajin mu sannan nafi kowa kokari da hazaka ba yabon kai ba. Idan kayan dadi suka yi a gidan su sai ta kawomin nata rabon, bama b’oyewa junan mu komai, mun kasance muna bawa junan mu shawara duk sanda hakan ya kama.

Akan hanya muka hadu da Haysam, wato d’aya daga cikin samarin dake nacin so na, Ina ganin sa na bata fuska na shiga zame hannu na daga na Fadila saboda nasan dole sai ta tsaya tasa munyi magana dashi ala dole. Haysam matashi ne mai jini a jika, dan shekaru goma sha tara, yanada kyau da kamala, sannan ‘da ne ga Alhaji kabeer wafa, wato manajan chanjin kud’i na b’angaren Zaria. Banason

Haysam saboda ‘dan masu ku’di ne ni kuma yar talakawa ce, bayaga haka ma banason kula kulen samari ga kuma sharadin Yayan mu daya hanani kula kowannen su. Saboda na tsaya na fuskan ci karatu na sosai. Tundaga nesa Haysam ya tsuramin ido yana bin kallo na tundaga kan yan yatsun kafata zuwa kirji na da fuska ta,

“Dan iska..”

Na fada ina cuno baki na gaba ina sake k’ok’arin kwace hannu na daga na Fadila ganin yadda take masa murmushi alamin ya matso kusa ga ni. Kin sakin hannu na tayi, Hakan yasanya Haysam tunkaro mu yana taune leben sa na kasa.

“Batoul!”

Yakira sunana yana sakin murmushi, na kauda kai na gefe ina sake hade fuska ta, Ganin hakan ya sanya shi mai da kallon sa ga Fadila,

“Aminiyar mu, ya kike?”

“Lapia lou saurayin mu. Ya gidah?”

“Alhamdulillah fa! Islamiyya zaku ne?”

Ya tambayeta yana mai sake maida kallon sa fuska ta.

“Eh wallahi can zamu.”

“Nazo nayi rakiya?”

“Meze hana? Bismillah!”

Jerawa mukai dashi muna tafiya, Fadila na tsakiyar mu suna hira, lokaci zuwa lokaci yakan sako sunana ko zanyi magana, Ni kuwa shiru nayi naki tankawa har muka k’arasa makaranta. Sallama su kai da Fadila ya tafi gidah mu kuma muka shjga ciki.

“Ki dena abunda kike Allah! Menene makusar Haysam? Meyasa bakya son sa? Akan wane dalilin zaki dinga garashi tamkar taya? Haba Batoul! Ki dena yiwa samarin ki haka Allah. Wasu ma ido rufe suke neman masoyan ke kuwa kin samu damar ki a hannu kina neman ta kubce miki, kiyi tunani tawan.”

“Bestie kenan, Duka-duka shekarun mu nawa? Sannan ko ajin farko na siniya sukul bamu shiga ba, bayaga haka Haysam dan masu hannu da shuni ne, Banason hada kai na da wanda suka fini a komai, har a addinan ce a har kullum so ake ka kalli na ‘kasa da kai ba wanda yake saman ka ba ya kere ka. Sannan sahibin ki ma wato Yayan mu ya hana ni kula samari.”

Fadila ta fad’ad’a murmushin ta jin na ambaci masoyin ta.

“Hakane kuma. Toh Allah ya zaba mana mafificin alkhairin sa Ameen.”

“Ameen”

Aji muka shige, aka fara tilawar karatu kafin Ya Sayyadi ya shigo. Haka dai mukai ta tilawa sannan aka kada kararrawar sallar la’asar. Sallah muka fita muka yo sannan muka koma aji, Malam yabi daliban ajin mu d’aya bayan d’aya ya karbi haddar suratul Yasin da Ashmawi. Ya fita sai Malamin dake mana Bulughul Maram da Buhgayatul Muslimeen ya kara mana, daga ‘karshe mukai Sira da kuma Usulul Thalatha.

•••••. ••••. •••••. ••••.

Haka dai rayuwa ta cigaba da garawa, Safiya ta zama rana, Rana ta zama yammaci, Yammaci ya zama dare. Lalle Allah qadirun ne ala manyasha'u. Yau da dadi gobe babu, A haka dai akai mana hutun karshen aji, a daddafe muka je Shema k'auyen su Innar mu ni da autar mu mu kai hutu. Ana'i sauran kwana ki biyu za'a koma makaranta muka dawo. Dan kudin da muka samo a Shema dasu Innar mu ta yanka mana sabon inifom aka dinka mana, ta sai mana takalma na makaranta da safa yar gwanjo. Takuma yi mana dan tsince tsincen kayan abinci, Ciki har da rabin buhun gawayi da taliya yar aune, dari ukun kai kuma ta auno kananzir da manja, nera darin kai kuma ta bani kan na ajiye mana kudin birek ne na makaranta ni da autar mu har tsawon kwana ki uku. Dama gashi ni na shiga babba aji na uku na jiniya sakandire, Autar mu kuma ta shiga ajin firamare na uku. Haka dai muka shiga rufawa juna asiri don ciyar da kan mu.

Ranar wata asabar muka tashi da tashin hankali, Domin ogan su Yayan mu wato mai wurin kanikancin su ya sayar da wajen ga wani mutumi inda za'a mayar da wajen filin yin biki na kudi dake 'katon waje ne. Gefe kuma wajen wanke mota. Yayan mu yaci kuka ko ince munci kuka duk kanin mu, Innar mu kuwa muryar ta har dashe wa tayi tsabar kuka. Kasa zuwa makaranta muka yi ni da autar mu. Yayan mu mai share mana kukan mu yanzu shima abun a taimaka masa ne. Tsawon kwana ki uku muka dauka bama zuwa makaranta. Islamiyya kuwa munma ajiye babinta a gefe, domin bamu da tabbacin samun kudin biyan islamiyyar na wata wata. Yayan mu ya buga ko'ina amma babu aikin yi, domin duk inda yaje nema sai ace sai ya kawo takardar kammala sakandire tukun.

Da dare tare muka hadu muka ci kwadin tafasa da Innar mu ta samo a gidan da take wankau. Sannan muka dora da taliya da mai da yaji, Innar mu ne gefe tana jin rediyo, Mu kuma mu da Yayan mu muna hirar mu. Har lokacin bacci yayi, Yaya ya dauki yar taburmar sa da net ya daura a tsukukun kofar dakin mu ya kwanta lokaci d'aya bacci yai awun gaba dashi, Cikin dare fitsari ya ishe ni na mike daga kwancen da nake daure da zani na zira hijabi na dauki cocilan mu na shiga haska gabana dashi, a hankali na tsalle Yayan mu na sauka bandakin 'kasa na shiga zurara fitsari na ahankali ina rufe bakina sakamakon bahaguwar hammar da naketa saki wadda kallo d'aya zaka min kasan bacci ne a idanu na. Ina gamawa nai tsarki na fito daga bandakin baki na dauke da addua. Ina hawa bene mu kai kicibus da Islaha kanwar Bintalo wadda tazo daga kauyen su, Ta kasance tana mutuwar son Yayan mu. Gashi Yayan namu ko kallon ta bayayi idan suka hada idanu ya zabga mata harara. Hango Yayan mu nai ya tattare kayan kwanciyar sa zai fita waje, Da alamun takura masa tashiga yi. Ni dai daki nai shigewa. A hankali a hankali nake jiyo nacin da Islaha ke yiwa Yayan mu,

“Sakarmin hannu dalla malama”

Da sauri na fito daga daki ina kallon yadda Islaha ta rike hannun Yayan mu dumu-dumu acikin nata. Sai zabga mata harara yake yi yana kokarin kwace hannun sa taki sakin sa. A dai dai lokacin Bintalo tafito daga daki kallo d’aya tayi musu ta daura hannuwan ta akai, cikin sakin wata irin shegiyar ‘kara tace,

“ihuuuuuu Gardiiiiiiiiii”

Ai bata rufe baki ba mutan gidan mu suka fara firfitowa daga dakunan su, kankace me? Anyi cincirondo kowa yana kallon su Yayan mu, Islaha daure da zani ba dankwali a kanta, Shi kuma Yayan mu sanye yake da wando dogo babu riga ajikin sa, sakamakon zazzafan zafin da ake zubawa yasa tun da zai kwanta ya cire yashiga cikin net.

“Innalillahi wa’inna ilaihir raji’un..!”

Itace kalmar da Yayan mu yake ta furtawa, lokaci d’aya hawaye suka shiga yar tsere a fuskar sa. Nima na goge nawa hawayen tare da tsugunnawa, sakamakon rawar da kafafuna suka shiga yi sun kasa daukar gangar jiki na tsabar tashin hankali. Na dubi Bintalo dake sakin wani makirin murmushi tana tafa hannuwa,

“Shege wan shegiya ‘dan shegiya! An tsotsa a mama ai dole a nuna hali, Toh ‘karshen tuka-tuka tik, Allah ya kama ka. Tun ranar da yarinyar nan tazo gidan nan kake bibiyar t...”

Bata karasa ba Innar mu tayi hanzarin shiga tsakanin su, Ta kwace hannun Yayan mu daga na Islaha, cikin rawar baki da jiki tace.....

——

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😻□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA HUDU_*

•••

“Ya ishe ki Bintalo, Banason tashin hankali shiya sa bana biyewa ayi dani idan hayaniya ta kaure a tsakani. Saboda haka kada ki ‘kara sheganta min yara, ‘ya’yana yan halak ne. Allah ya isar mana idan har kika kara aibata su. Banda bina da ‘yayana da sharri ba abinda kika iya, Allah ya tsare mu daga miyagun halayen ki...”

Tunda Innar mu tafara magana har ta gama gaba d’aya kowanne acikin yan gidan mu mamaki ne dankare a zukatan mu, idanuwa muka zuba mata ni kam harda ‘kyak’kyaftawa ko mafarki nake, domin tunda nake bantaba ganin Innar mu ta maida wa wani martani ba fyace yau. Da alamun an kaita mukura, dadi ne ya mamaye ni ganin tafara samawa kanta ‘yanci. Na dubi Bintalo yadda ta daskare a wajen tana kikkifta idanuwa, da alamun maganganun da Innar mu tayi sun shammace ta. Cikin tunanin dana tafi na sake jiyo Innar mu tana yiwa Yayan mu magana,

“Wannan yaron (Saboda ‘dan fari ne) Inaso ka gayawa kowa yadda ku kai da yarinyar nan data bika da sharri.”

“Innar mu wallahi kawai ina kwance a cikin net na jiyo ana kiran sunana, Sai kawai na mike tsaye ina kallon gabana ganin mai kiran nawa, Ashe ita ce. Tasa hannu kenan zata bude min net din na mike tsaye gaba d’aya na tattare tabamar tawa da net din zan koma langalangar almajirai, Toh a lokacin ma na hango Batoul ta dawo daga kasa da alamun bandaki taje. Bayan shigar Batoul daki ke da wuya kawai naji ta rik’o min hannu, nai nai ta sake ni ta’ki, Nasa d’ayan hannu na kenan zan fincike sai Bintalo tafito daga dakin ta tana kurma ihun gardi, Wallahil azim hakan akayi. Daman tasha tara ta a koina ne tana gayamin kalaman so. Gata nan a tsaye idan ‘karya nai mata.”

Bintalo tayi kukan kura tana girgiza jiki agaban kowa,

“Sittin ta Ubangiji karya kake yi, Waya san sau nawa kake lalata ‘ya...”

“Karya kike yi Bintalo, wallahi tallahi wannan yaron baya kula wata ya mace ma ballanta na har yakai ga lalata. Allah ya isa wallahi. Kin kai ni karshe Bintalo..”

Innar mu ta karasa fada tana sharce hawayen bakin ciki. Kawu ila dake jingine da kafar bene ya ja tsaki yana komawa dakin sa. Kawu Dawood ne yai kokarin cewar,

“Toh ita yarinyar tafada da bakin ta abunda ya faru. Sai musan hukuncin da zamu dauka ko kuwa?”

Su Kawu Khamis suka daga kai alamun ‘Eh hakan yayi’. Kawu Dawood ya sake maida kansa ga Islaha da kanta ke a ‘kasa tana lankwasa yan yatsun ta yace,

“Ke gaya mana gaskiyar lamari, shin abunda yace shine gaskiya ko kuwa karyane shi ya kira ki?”

Bintalo tasa kafa ta take ta Islaha alamun tace Eh shine ya kirata. A hankali Islaha ta goge hawayen dake kwarara a idanun ta, cikin rawar baki tace,

“Eh Kawu! Hak’ik’a Yaya Najib shine ya kira ni, Tun ba yau ba yakeson yai la.l..lalata da ni.”

Bintalo ta saki wata uwar guda, kai kace amarya aka kawo. Cikin buga zanin ta hade da tafa hannuwa tace,

“Alhamdulillah yanzu naji zance. Daman na gaya muku shine ya neme ta.”

Yayan mu ya saki wani marayan kuka mai k’ona zucia, wanda kowa ya saurara sai ya tausaya masa. Cike da rawar baki ya tsugunna a gaban Islaha yana duban idanun ta, Wadda tai saurin kauda kai gefe.

“Is..Isl.Islaha ki dubi girman Allah ki sanar da su gaskiyar lamari, zamu mutu zamu koma ga Allah. Allah yana kallon ki, shin ni na kira ki ko kuwa kece kika neme ni?”

Islaha tayi shiru tana goge hawayen nadama, Yayan mu ya sake tambayar ta har sau uku nan ma dai amsar d’aya dince dai tabashi. Kawu Dawood yai gyaran murya kafin yace,

“Toh shikenan yanzu dai a barwa wayewar gari komai, Ke Islaha kiyi hak’uri hakan ba zata sake faruwa ba. Kai kuma Najibulla kaje langa langar ka kwana zuwa safiya zamu yanke maka hukunci. Allah ya kyauta”

Wani kukane ya kufce min jin abunda Kawu Dawood yace, Na dubi Islaha jiki na rawa nace,

“Kiji tsoran Allah Islaha, karki ga kwarjinin Bintalo, ki fad’i gaskiyar lamari.”

“Dakata shegiya, waya ce ki tsoma bakin ki? Zatai muku karya ne? Zaki matsa ko sai na sharara miki mari. Ai wallahi Idan naji hukuncin da aka dauka masa bai min ba wallahi zakuji sammaci a kotu.”

Cewar Bintalo. Ta karasa fada tana jan hannun Islaha, Innar mu dake gefe ta sharce hawayen fuskar ta, Sannan ta dubi Yayan mu cikin sakin murmushin dayafi kuka ciwo tace dashi,

“Kayi hak’uri wannan yaron. Kai dai ka cigaba da fawwalawa Allah lamurran ka, zamu tayaka da addua. Wallahi komai nisan dare gari zai waye, Allah zai bayyana mai gaskiya.”

Tana gama fada ta shige daki, Nabi bayanta ina fashewa da kuka, Tsabar bakin ciki Yayan mu ko kayan shimfidar sa bai dauka ba ya fice daga gidan. Daganan kowa ya watse. Ana jiran safiya tayi aji hukuncin da zasu yanke wa Yayan mu.

WAYEWAR GARI

Taliyar jia na shekawa ruwan zafi muka ci. A roba na zubawa Yayan mu na tafi kai masa. Yana zaune a bakin kofar langa-langar kansa a kife.

“Yayan mu!”

Na fada ina mai ajiye robar abincin a gaban sa, dago kansa yai. Na tsorata kwarai matuka da ganin yanayin sa. Jijiyoyin kansa sun fito sunyi rud’u-rud’u dasu, idanuwan sa sun kada sunyi jajir dasu, lokaci d’aya ya zabge ya jeme tamkar wanda yayi shekararren ciwo. Murmushi ya ka’karo yana mai kokarin danne damuwar sa,

“Na’am Batoul.”

“Barka da safiya Yayan mu.”

“Barkan mu. Yasu Innar mu?!”

“Lapia lou Alhamdulillah.”

“Ga abinci nan Yaya ka daure kaci”

“Wallahi cikina a cushe yake. Amman zan ci.”

“Yauwa Yayan mu. Allah ya maka sakayya, Ya fidda kai daga sharrin su”

“Ameen ya Allah.”

Mik’ewa nai na barshi yana kokarin bude filet din da aka rufe robar dashi. Ina shiga gidah na kwaso kayan wanke wanke na sauko kasa na wanke tas. Na koma na hada gawayi na dora ruwan zafi. Tsabar munafunci ko makaranta babu wanda yaje acikin yaran gidan mu, kowanne jira yake yaji hukuncin da za’a yanke wa Yayan mu. Ta sama na hango Kawunnin mu suna ta shiga parlorn Kawu ila d’aya bayan d’aya. Anan duk suka hallara. Kasancewar nanne kadai mai parlor kuma wadatacce wanda zai dauke su. Kawu Ishaq, Kawu Dawood, Kawu Khamis, Sai shi Kawu ila din. Daki na ruga na zauna hade da janyo carbin Innar mu na shiga yin lazimin Allah ya dora Yayan mu akan su. Allah yasa su yanke masa hukunci sassauk’a.

Can parlorn Kawu ila kuwa hallara su kai, Sai da sukai yar caftar su wanda dole ne idan suka hadu sai sunyi fada. Tukun sannan daga baya Kawu Ishaq kasancewar shine babban su hakan yasanya yayi gyaran murya kafin yace,

“Toh kamar yadda kuka sani abunda ya taramu anan yau hukunci ne wanda zamu yankewa Najibulla. Shin tayaya kuke ganin za’a warware bakin zaren. Wane irin mataki ko hukunci zamu yankewa yaron nan. Kun san dai sarai Bintalo ba yadda zatai ba idan taji abunda muka yanke bai yi mata ba?.”

Kawu Dawood dake sakace hakoran sa da tsinke ya ajiye a gefe kafin ya sauke nannauyar ajiyar zucia.

“A yanke masa hukunci dai dai da laifin sa akuma yi masa sassauka. A nawa fahimtar wannan matsala da aka samu a tsakanin su abune wanda ke a b’oye wanda babu wanda yasan tabbacin gaskiyar yadda komai yake.”

Ya karasa fada yana maida kallon sa ga Kawu Khamis. Kawu Khamis ya sau siririn tsaki.

“Hakane amma ni ina ganin kawai daga shi har ita su bar gidan nan. Hakane kawai zai kawo karshen matsalar nan. Amman muddin yana nan suna zaune tare a wuri d’aya to dole sai an sake maimaita rana irin ta jiya. Amma ya kuke gani.”

Kawu ila dake kishingid’e tun d’axu yana kallon su sunata magana sai a lokacin ya dan gyara zaman sa, cikin cigaba da fifita da mificin dake hannun sa yace,

“Bangane ba Khamis, Su je ina kenan?”

Kawu Khamis ya bude baki kenan zai yi magana Kawu Ishaq ya tari numfashin sa,

“Idan na gane abunda kake nufi kana nufin ita ta tafi k’auyen su shi kuma ya koma wani wajen da zama? Ma’ana kenan yabar nan Zaria ko?”

Kawu Khamis ya jaddada kai. Baba ila ya gyara zaman sa da alamun sun tabo masa inda yake masa ‘kai’kayi.

“Wannan shine dai-dai, Tun ba yau ba nakeson shegen yaron can ya bar gidan nan. Domin naga alamun shi ke tsayawa uwar sa take yiwa mutane gani-gani, A yau ba sai gobe ba dan tselen uwa zai bar gidan nan.”

Ya karasa fada sauran na ‘babbaka daria banda Kawu Dawood. Domin shi Kawu ila yafi su rufin asiri, Don har shagon kayan masarufi yake dashi a gangare, Sannan mahaifin matar sa yanada kudi babu laipi. Kunsan yaro da kudi abokin manya, ko kaine kafu kowa kudi a dangin ku dakayi magana d’aya ta zauna kenan babu mai musawa. Shi yasa kowanne hukunci ya zartar da shi suke amfani, Kawu Dawood ne kawai baya shiga harkar sa sakamakon rashin jituwa da basa yi. Mik’ewa Kawu Dawood yai, Yayi hayewar sa sama. Nan yabar su Kawu ila dasu Kawu Khamis suna zantawa.

K’arfe sha d’aya saura kwata na ‘karasa tuwon dawar da Innar mu tasani, Ina kwashe wa na dora ruwan miya, gaba d’aya zucia ta babu dadi nake jinta, domin idan ka cire mahaifin mu daya rasu, da kuma Innar mu toh duk duniya babu wanda nake so irin Yayan mu da autar mu. Hakik’a ALLAH ne kawai gatan mu, Amma Yayan mu yana iyakar kokarin sa ganin muna cikin farin ciki ya zamto mana makara ‘dau duka. Hawaye ne na goge hade da saurin mikewa tsaye jin muryar Kawu ila yana dokawa sunana kira.

“Na’am Kawu gani nan.”

Na fada ina mai zura hijabi na. Ko takalmi ban tsaya sawa ba sanin masifar Kawu ila, Ai kuwa ina sauka kasan ya zabga min harara yana nuna ni da dan yatsan hannun sa guda d’aya na hannun dama,

“Wato tsabar raini ina kiran ki tun d’axu kina jina shine sai yanzu zaki sakko?”

“Kayi hak’uri Kawu wallahi banji ba sai yanzu.”

“Okay wato karya na shirga miki kenan? Zo nan dan uban ki. Shegiya mai idanuwa irin na jemagu.”

“TubarkAllah!”

Na fada a zuciya ta, Ina mai k’arasawa kusa dashi a tsorace. Tuni hawaye suka fara wanke min fuska. Kyakkyawan rankwashi ya sakarmin a ‘kwanyar kai. Cikin rad’ad’i na shiga sosa kai na ina hawaye, yaran dake wajen suka shiga babbaka daria cike harda Hinde dake wanke wanke. Na goge hawaye na , baki na na rawa nace dashi.

“Kayi hak’uri Kawu”

“Hakurin uban ki. Shashasha! Fita ki kira dan iskan wanki a waje kice yazo ya ji hukuncin sa yanzu ba sai anjima ba.”

“Toh!”

Shine kawai abunda baki na ya iya furtawa, naja k’afafuwa na na fita waje, cikin sa’a kuwa na hango Yayan mu shida wasu almajirai suna hira. Karasawa nai daga dan gefe nace,

“Yaya. Wai kazo inji su Kawu ila.”

Daga kai yayi, ya biyo ni a baya. Kowannen mu da abinda zuciar sa ke ayyana masa. Ni na fara shiga sai shi daga baya na. Bakin mu dauke da sallama, Kawu ila ya janyo nacaccen bokitin karfen sa daya maida shi na zaman tsakar gidah ya zauna, yana nunawa Yayan mu gefan sa daga kasa. Babu musu kuwa Yayan mu yaje ya zauna. Hinde dake hawa bene da kwanukan data wanke Kawu ila ya callarawa kira. Juyawa tayi tana zumburar baki.

“Yar hindodo mai farin jini, yarinyar gwal mai sa’ar rayuwa. Kira min babar ku da Islaha. Kice suzo yanzu suji hukuncin da aka yanke.”

Daga kai kawai tayi batare da ta amsa shi ba, tacigaba da hawa benen. Da ni ce kuwa nayi masa haka ya dinga tulata kenan kamar dabba. Amma saboda su ‘yayan da ake so ne ko fada ba ayi musu. Benen na fara hawa nima ya doka min kira cike da isa, jiki na rawa na juya,

“Na’am Kawu”

“Kira uwar ki taji yadda ake yan kewa danta hukunci.”

“Toh”

Kawai na fada na ‘karasa hawa. Daki na shiga da sallama zan fadawa Innar mu sak’on Kawu ta dakatar dani, da alamun ta jiyo shi. Cikin dan murmushin gefen baki wanda kallo d’aya za kai mata kasan tana cikin tashin hankali tace.

“Na jiyo shi Batoul. Gani nan sakkowa ‘kasan.”

Kada kai nayi alamun ‘Toh’. Sannan na juya na koma ‘kasan.

“Tace gata nan Kawu.”

Wani dogon tsaki yaja yana zabga min harara sai kace ni nayi lefin, fada ya hau yi shi kadai kamar wani mahaukacin kare ta inda yake shiga batanan yake fita ba, ya shiga dokawa Innar mu kira yana balbaleta da fada, Ni da Yayan mu dake gefe mukai shiru, idanuwan Yayan mu suka sake yin ja alamun ransa yakai kololuwar baci, Ni kuwa tsugunnawa nayi ina hawaye, domin duk sanda muke cikin tashin hankali k’afafuwa na basa iya daukar gangar jiki na. Shi kuwa Kawu ila sai ‘kara rafka mata kira yake yanata faman ihu,

“Ke kaltume, Kaltume! Ba zaki sakko ba? Ko sai na lallasa shegun dake gabana a zaune?”

—-

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😻□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□

[9/16, 11:28 AM] Maryam Jumare: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA BIYAR_*

•••

Gaba d’aya manya da yaran gidan mu duk sun hallara a tsakar gida, Wasu a ‘kafar bene, wasu suna lek’e daga sama, wasu ta ‘d’akunan su. Kowanne ya baza hanci da idanu yana jiran jin hukuncin da aka yankewa Yayan mu. Cikin nutsuwa Innar mu ke sakkowa daga bene hannun ta d’auke da carbi tana ja harta ‘karaso inda nake tsugunne ta tsaya. A lokacin Bintalo da Islaha suka sakko suma, Bintalo na cin cingom tana fasa ‘kwan, Islaha kuma kan ta a ‘kasa tana matsa yatsun ta, kallo

d’aya za kai mata kasan akwai alamun rashin gaskia a tattare da ita. Kawu ila ya janyo bokitin zaman sa na gado ya zauna yana bin kowannen mu da kallo, sai da ya mula yasha iska tukun sannan ya nuna Innar mu da yatsa,

“Ke kaltume wato saboda kin gama raina mu shine tun d’axu za’a aiko a kiraki sai yanzu kika ga damar sakkowa nace sai yanzu?”

“ilyasu kenan, Sai na katse sallar da nake na taho kiran ku? Agaban ALLAH fa nake, ai yafi gaban komai.”

Wani dogon tsaki yaja yana zabga mata harara, cikin ‘daga muryar sa ya fara magana yana mai mai da duban sa ga Yayan mu.

“Toh kamar yadda kuka sani daren jia Najibu ya nemi ya keta haddin Islaha, Saboda haka mun yake musu hukunci dai dai da laifin su.”

Innar mu dake gefe tai murmushin yake tana mai girgixa kai cike da tausayi, cikin wata irin murya tace,

“Ilyasu keta haddi fa kace? Kenan kun yadda wannan yaron ya aikata hakan?”

“Kwarai kuwa, domin rikakken namiji ne mai jini a jika, yana tashen samartakar sa, yanzu ne yake jinsa namiji sab...”

Da sauri Yayanmu ya riko kafar kawu ila yana hawaye gwanin ban tausayi, Gaba d’aya ilahirin jikin sa rawa yake yi,

“Kawu na rantse da Allah ban aikata abun da ake zargin na aikata ba, wallahi ALLAH gatanan a tsaye ko yatsun hannun ta ban taba kamawa ba, hasalima ni ba shiga harkar ta nake ba.”

Kawu ila yasa ‘kafar sa ya shure hannun Yayan mu, cikin tab’e baki yace,

“Mun rigada mun yanke muku hukunci kai da ita.”

Bintalo tayi kukan kura ta dira agaban Kawu ila. Cikin d’aga hannuwa ta shjga kwaso rantsuwa tana direwa,

“Sittin ta Ubangiji bazan yadda ba, ya nemi yai lalata da ita kuma sannan ace za’a hada a yanke hukuncin harda ita? Kaga ilyasu kasan sarai ba yadda zanyi ba, Rufa rufar da akai kad’ai a shekarun baya ta isa, kowa yasan shegun yaran nan gada su kai awajen mahaifiyar su, kalle su mana kowanne kamar sa daban, kowannen su da baban sa kenan. Shegiyar can kuwa inaga a yan gudun hijra aka samu ubanta domin kowa yasan ba...”

Bintalo bata ‘karasa ba Innar mu ta sha gabanta, hawaye suka shiga tsere a fuskar ta, Nima dake gefe na goge nawa jin sharrin shegentamu da akeyi,

“Karki kara shegenta min yara, domin kuwa kamar kowa suma nan gidan su ne, auren sunna mu kai da mahaifin su aka same su, Banda jahilcin ki ba ALLAH ne ke halittar mutum ba a yadda yaso a kuma sanda yaso? Bari kiji Bintalo tun kafin a san za’a auro ki muke tare da salis, Shin me kika sani game damu? Idan baki san nasani ba to inasan ki saurare ni da kyau, Nasan ta yadda aka auro ki, domin abun kunya ki kai, aka temaka aka hada auren ku dake ‘yar uwar su ce ke. Ko ba rufa asirin yan uwa kukai ba ya temaka ya auro ki?”

Kowa ya mai da kallon sa ga Bintalo, Ai kuwa ta zube a ‘kasa tana rusa kukan makirci,

“Wayyo nashiga uku, Yanzu Kaltume ‘k’aryar da zaki sharara a kaina kenan?”

Kawu ila dake gefe ya fara bata hak’uri yana rafkawa Innar mu harara,

“Kiyi hak’uri Bintalo, wannan zance nata ‘kage ne kawai, kowa yasan kece son ran Salisu. Ita kuwa agumi suka hada da iyayen ta ta mallaki Salis ta dole. Yara kuwa badan Aminatu tayi kanai-kanai acikin maganar gado ba ai da badasu za’a raba ba wallahi. Ki share hawayen ki Bintalo, Kowa yasan gaskia.”

Bintalo ta saki gud’a tana buga gaban zanin ta, Kawu ila yai murmushin da jajayen hokoran sa suka bayyana wanda suka rine su kai jajir saboda cin goro, Ya dubi Yayan mu dake gefan sa a tsugunne kamar kayan wanki,

“Kai Najibu, Bude kunnuwan ka ka saurare ni dakyau kaji hukuncin da aka yanke.”

Yayan mu ya daga kai, Ni dake gefe nasan ya hannu na asaman kai na na dafe ina mai zirarar da hawayen bakin ciki,

“Toh hukuncin da aka yanke shine kai Najibu zaka harhada naka ya naka ka bar garin nan, kada ka sake waiwayo gidah fyace sai mun neme ka. Ke kuma Islaha kema ki koma gidan ku, kya iya dawowa idan komai ya lafa.”

Na fashe da wani irin kuka mai tsuma zuciyar duk wanda ya saurara, Na dubi Yayan mu da ya kasa kuka gaba d’aya sai jajir da idanun sa su kai, jijiyoyin kansa sunyi rad’au-rad’au kallo d’aya za kai masa kasan yana cikin tsananin tashin hankali. Innar mu tayi murmushin da yafi kuka ciwo kafin ta dubi Kawu ila ta na mai cigaba da jan carbin hannun ta,

“Ilyasu na iya tafiya?”

“Eh kya iya komawa”

Sannan ya dubi Yayan mu yana mai nuna shi da yatsa,

“Minti talatin na baka kayi sallama da mahaifiyar ka da yan uwan ka da abokanan ka. Tashi ka je.”

Yayan mu ya mike dakyar yana hada hanya yabi bayan Innar mu dake hawa sama, Nima binsu nayi ina goge hawayen dake yar tsere a idanu na. Ina jiyo gud’ar da Bintalo ke saki tana tafa hannayen ta alamun duniya tayi mata dadi. Tuni gidan mu ya kacame da hayaniya kowa yana tofa albarkacin bakin sa, wasu sunji dadin hukuncin da aka yanke wasu basu ji ba. Koda muka shiga d’aki Yayanmu zubewa yayi akan katifar mu ya shiga rafka kuka, Autar mu sai hak’uri take bashi itama tana tayashi kukan. Innar mu zama tayi akan dadduma tana addu’oin ta. Duk kuwa da kallo d’aya zaka mata kasan itama tana cikin tashin hankali.

Sai da tayi addu’oin ta sosai sannan ta mike ta shiga duba cikin langunan da take ajiye kudaden wankin ta. Harhado su tayi duk sun manne da junan su. Ta shiga mik’ar dasu tana jera su d’aya kan d’aya. Yayan mu dake gefe sai ajiyar zuciya yake sauke wa yayi kukan har ya gaji. Innar mu kuwa bayan tagama hada yan kudaden ta kuma babban kad’a inda kayan mu suke taciro sauran kudin ajiyarta ta Sannan tadawo kusa da autar mu ta zauna. Cikin nutsuwa ta dubi Yayan mu da kalamai masu kwantar da zuciya ta shiga yi masa nasiha mai ratsa jiki tana yi yana hawaye, Ta k’ark’are da.

“Ka ‘kara hak’uri wannan yaron. Allah yana tare da masu hak’uri. Kuma komai na duniya rubutacce ne daga gare shi, Kasani komai nisan dare gari zai waye, Hakika ALLAH zai bayyana mai gaskiya tsakanin mu da su. Kacigaba da addua. Addu’ar wanda aka zalunta wallahi batada hijabi da ALLAH. Yana can a madakata zai yi sakayyar sa ko anan ko acan (Lahira). Allah yasa barin ka nan din shine mafificin alkhairi, ALLAH ya kare ka ya tsare ka aduk inda kake. Allah ya shiga lamurran ka, Yasa albarka a duk abunda kasa gaba. Allah ya maka albarka kai da yan uwan ka baki d’aya. Ameen”

“Aameen! Ya Hayyu Ya Qayyum.”

Muka amsa baki d’aya, autar mu kuwa har da shafawa a fuskar ta. Yayan mu ya goge fuskar sa sannan ya mike yana gyara zaman rigar jikin sa, cikin wata irin murya ya dubi Innar mu,

“Toh Inna zan tafi, Amma ina kike ganin zance kenan?”

“Toh wannan yaron ni dai tun dare nake adduoi kawo wa safiyar yau. Kuma zuwan ka Shema yafi kwanta min arai, Nasan su acan zasu zamar maka madogara, Tunda ‘ya’yan Baffa Ardo na zuwa tashi Kano, sai ku tafi tare. Kano cibiyar kasuwanci ce.”

Haka dai Inna da Yayan mu su kai ta magana, daga karshe ya amince da zuwa Shema. Na tattaro yan kayan sa na dakin mu na zuba a leda na rik’e masa. Inna ta bashi kudin ya duka hannu biyu ya karba yana godia. A d’aki ta masa adduar ALLAH ya kiyaye hanya da samun nasara, Muka amsa baki d’aya. Kafin nida autar mu mubi bayan sa, har titi muka rakashi muna yar hirar mu, duk kuwa da zukatan mu ba a nutsuwa suke ba. Cikin yan gidan mu kuwa babu wanda yayiwa yayan mu fatan ALLAH ya kiyaye hanya, Face Kawu Dawood da har naira talatin ya mika wa Yayan mu wai yasha ruwa a hanya. Babur Yayan mu ya tarar suka fara cinikin zuwa tasha. Muna daga gefe muna jin su. Sai da suka kammala sannan Yayan mu ya dawo kusa damu. Naira dari biyar ya ciro ya miko min,

“Ki Bawa Innar mu tayi cefa nen kayan azumi da za’a fara. Wannan kuma ki dau talatiin ki bawa auta ashirin. Allah ya muku albarka ya tsare ku.”

Ya karasa fada yana sake miko min naira hamsin. Na karba ina rissinawa idanuwana na fitar da ambaliyar hawaye. Hakama autar mu dake gefe.

“Mungode Yayan mu ALLAH ya saka da alkhairi. Allah ya tsare ka ya kare ka daga sharrin masu sharri. Allah kuma ya baka sa’a a komai na rayuwar ka Ameen.”

“Ameen Batoul! Ku ri’ke karatun ku duk wuya duk runtsi karku ce xaku dena. In sha Allah nima idan Allah ya buda min zan dinga aiko muku da wani alherin. Banda kula kulen samarin da zasu hanaki karatu, Banda bin wayayyun kawaye kina jina?”

“Eh Yaya”

“Yauwa! “ALLAH ya baku sa’ar karatu da nasarar rayuwa. Kuyita kauda kai dan Allah. Duk abunda zai had’a ku da yan gidan nan kada ku biye musu. Mu cigaba da hak’uri. Allah yana tare da masu hak’uri..”

Haka dai Yayan mu yaita bamu shawarwari. Ni kadai ke sauraron sa. Dan kuwa autar mu ta baje a ‘kasa tana yar carafke da duwarwatsun dake kwance akan ‘kasa. Kamar kada mu rabu haka naji. Yana hawaye muna yi. Haka dan mashin yaja shi, Muma muka kama hanyar gidah hannu na saqale dana autar mu.

.••••. .••••. .••••.

Bayan tafiyar Yayan mu abubuwa da dama sun faru, ciki kuwa harda sana’ar sangas na kudi dana fara. Tanan muke samu mu rufawa junan mu asiri. Ga wankau da Innar mu keyi. Autar mu ma ba’a barta a baya ba domin tana yin kafutsire ta kukkulla d’aurin biyar biyar ta siyar. Abun dai sai hamdala domin kuwa mun dan samu saukin wahalhalun rayuwa. Hakan kuwa ba k’aramin rashin dadi yaiwa Bintalo dasu kawu ila ba. Domin har gaban abadan sunfi son su ganmu a tsiyace ba cigaba. A satinne kuma Innar mu ta samu aikatau a gidan Alhaji Kabeer Mai Wafa wato mahaifin Haysam wanda ke so na. Haka dai rayuwa tacigaba da garawa, Lalle ALLAH qadirun ne Ala Manyasha’u.

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA SHIDA_*

ZARIA

BAYAN WASU SHEKARU

2008

GGSS ZARIA

(GOVERNMENT GIRLS SENIOR SECONDARY SCHOOL ZARIA)

Gaba d’aya farfajiyar makarantar mu acike take dankam da dalibai, Kallo d’aya zaka mana kasan muna cikin tsantsar farin ciki da annushuwa. Gaba d’aya uniform dinmu mun zane shi da rubutun maka da biro. Wake wake kawai muke rairaya wa cike da jin dadin kammala makarantar sakandire da mu kai, A yau ranar Alhamis biyu ga watan afrilu shekara ta dubu biyu da takwas.

Shantu ‘kwarya dadi, kai mu karkada shantu yan uwa ai ko badan komai ba sai dan Al’adun hausa. Ya Allahu muna rokan ka, Ya Allahu muna rokan ka daka sa muci SSCE ai ko badan komai ba sai dan mu burge iyaye. Principal ma tafada, vice principal ma tafada, Allah yasa mu ci SSCE ai ko badan komai ba sai dan mu burge iyaye.

Haka dai mu kai ta bushe bushe na usur da wakokin candy. Abun gwanin birgewa. Kiran sunayen masu muk’ami principal ta shiga yi. Turyan turyan har akazo kai na wato ni shugabar daliban makarantar baki d’aya. Yara sai ihu suke yi na murnar kiran sunana. Murmushi fad’ade akan fuskata. Kai dagani kasan ina cikin farin ciki. Haka malamai suka hadamun kyauta himili guda. Har sai dana zubda hawayen farin ciki. Nasamu yabo daga bakunan malamai da dama. Alhamdulillah Allah shine abun godia. Hamdala kawai nake a zuciata har muka fito daga harabar makarantar ni da yan ajin mu. Autar mu ta tayani rikon kyaututtukan da aka babba ni. Sunana na tsinkayo Malamin Literature din mu na dokamin. Amsawa nayi ina tafiya don amsa kiran sa. Ko bai fada ba nasan Malam Tasiu yana min son son fisabilillahi bai dai fada ba. Amman na gano tuni a irin yadda yake rawar jiki a kai na. Yana tafe shima yana sosa k’eya haka muka tsaya nesa da juna kadan. Cikin sunkuyar da kai na kasa nace,

“Malam gani...”

“Sannu Malama Batoul... Yau an kammala makaranta, Shikenan za’a mance damu ko?”

Murmushi nayi, Wanda kumatu na ya lotsa, Yar wushirya ta ta bayyana. Cikin kasa da murya nace,

“A’ah Malam ai ban isa ba.”

“Hmm! Haka dai kike gani, Amman kin isa har kinyi yawa a zucia ta.”

Yak’arasa fada yana gyara tsaiwar sa, Sauran Malamai dake nesa sai kallon mu suke, Da alamun muhawara ake akan mu. Shiru nayi ban amsa shi ba. Shima bai sake magana ba sai zaro wata zungureriyar wasika da yayi a aljihun sa ya mik’o min. Na ki karba ina matsawa baya,

“Karbi mana batoul. Dan Allah karki ki karbar kokon barata. Wannan wasikar zata shaida miki duk abunda ke zuciata..”

Sunan ALLAH daya had’ani dashi yasanya bazan ki amsar takardar ba, Na sa hannu biyu na karba ina dan rissinawa. Sallama nai masa na koma cikin k’awaye na muka cigaba da tafiyar mu.

BATOUL

Nasan mai karatu zai yi mamakin girma na. Toh dai a lokacin shekaru na 17/18. Na kasance mai wata irin sihirtacciyar kalar fata, Domin da agidan hutu nake ma da tuni kala ta ta kara turuwa. Inada yalwar gashin kai dana gira. Baki na dan mitsitsi ne kamar na jarirai jajaye dasu. Hanci na tsaye yake a mike kamar ni na zana kaya na. Ina da tsawo TubarkAllah domin dole ka sani a jerin dogaye. Jikina a murmure kirar zatin halitta ta ta zauna daram. Duk namiji mai jini a jika ya hange ni ni Batoul dole yai sha’awar kasancewa ta matar sa. Lalle dik dan adam tare yake bai cika

goma ba, Amma ni Batoul na cika tara na cif cif Alhamdulillah! lamarin sai godiyar uhangiji kawai. Yau ne ranar da na kammala makarantar sakandire inda na karanci fannin Art. Hakika ina da ‘kwazo da basira fiye da tunanin mai tunani.

GIDAN MATA TARA

Shigar mu gidah kenan ni da Autar mu muka hangi su Usaiba da Rabi’atu matan Kawu Ishaq su na dambatuwa a tsakar gidan mu. Gaba d’aya ahalin gidan mu sun firfito ciki harda ‘yayan ma’kota. Yadda kukansa gidan kallon kwallo haka akataru ana kallon dambatuwar da suke yi. Kawu ila na Zaune akan bokitin sa na gado yana sakace hakora. Innar mu ce kawai bata tsakiyar gidan.

“Ci uban ta Rabi”

Bintalo tacewa Rabi’atu da suke kokawa da Usaiba. Girgixa kai nayi na haura sama abuna. Ina jiyo kukan Rabi’atu. Wadda usaiba ta daga ta maka a ‘kasa. Tsakar gidan suka kece da daria. Dakin mu na shige baki na dauke da sallama.

“Wa’alaykm Salam.!”

Innar mu ta amsa tana kokarin tace taliya a mataci. Zama nayi hade da ajiye kyaututtukan da aka bani akan yar katifar mu. Dubawa nayi ganin banga sauran ba. Na shiga duddubawa ina babbanka dasu. Tunawa nayi suna hannun autar mu. Kishingidawa nayi akan katifa. Cikin gajiyar dana kwaso nace wa Innar mu,

“Innar mu sannu da aiki..”

“Yauwa Batoul. An dawo. Ina auta kuma?”

“Tana can kallon wasan kwaikwayo a kasa.”

Dakuwa Innar mu tayi min tana mai juye taliyar data tace a cikin dan foodflask din mu. Muskutawa nayi na debo kyaututtukan na ajiye a gaban ta.

“Innar mu yau mun ‘kare makaranta. Munyi candy. Alhamdulillah! Kinga kyaututtukan da aka babbani wasu ma suna hannun autar mu.”

Albarka Innar mu tasa ka min akan karatun. Tana mai duddu ba kayan cike da farinciki. Mikewa nayi domin kiran autar mu. Ina lekawa ta saman na shiga k’walla mata kira. A guje ta taho tana juyawa tana cigaba da kallon fa’dan da akeyi. Inda sabo mun saba sai afi awa ana kwasar fada a gidan mu. A kwanta washegari a tashi a dora daga inda aka tsaya kamar wasan kwaikwayo. I m

“Ke zo nan.”

Kawu ila ya kira autar mu yana mai zare mata idanuwa. Komawa tayi wajen sa jikin ta sai rawa yake yi. Yatsa yasa yana mai nuni da kayan hannun ta.

“Meye wannan?!”

“Ka..kak. Kayan Yaya Batoul ne.”

Dago kansa yayi muka hada idanu. Ya maida duban sa ga autar mu.

“Ajiye kayan ki tafi. Ke kuma zonan dan uban ki.”

Ya sallami autar mu. Ni kuma ya kira ni. Yana mai babbankada kayan kyautar da aka bani. Autar mu ta shige daki a guje ni kuma na karasa sauka kasan na tsugunna daga gefe.

“Gani Kawu..”

“Dan uban ki a’ina kika samu wannan kayan? “

“Kawu kayan kyauta ne da aka babbani a matsayi na na shugabar dalibai.”

Tab’e baki yayi, hade da zazzage ledojin. Ta farko littafai ne aciki da math-set. Leda ta biyu kuma kifin gwangwani ne guda biyar da lemon roba shima biyar. Babban dansa mai suna Yazeedu ya kwallawa kira, Da sauri yaron yazo ya tsugunna a gefe na,

“Gani Baba.”

Ledar farko mai dauke da littafan da math-set ya mika masa, Kai na kawai na girgiza ina mai jin wani abu ya tokare min wuya na tabbata na b’acin rai ne. Ina jiyo shi yana ce masa,

“Rik’e nan. Ka dau guda biyar kabawa su Mariya sauran. Maset din kuma ka dauka.”

Karfin hali. Allah kayi mana sakayya cikin gaggawa. Allah kana ganin yadda wannan bawa naka yai mana. Allah ka saka min. Haka nai ta nanatawa a xuciata domin nasan wallahi adduar wanda aka zalunta batada hijabi da ALLAH.

Cikin adduar da nake kwararawa a zucia ta na jiyo muryar sa,

“Ungo rike , Tashi ki bani waje.”

Kifin gwangwani d’aya ya mi’ko min guda d’aya da lemo d’aya, sauran kuma ya nannade a leda ya zura akan bokitin sa dayake zaune. Kifi d’aya kacal yabani acikin guda biyar da lemo d’aya shima acikin guda biyar. Abu biyu dai kacal ya bani acikin guda goma, Ban dama sauran littafan. Hawayen daya tahomin na goge wallahi

badan nasan autar mu zatai kwadayin ci ba da bazan karba ba. Yahada ya cinye ya biyani a lahira. Sama na haye ina jiyo Bintalo tana dariyar mugun ta. Ina shiga daki na mikawa autar mu lemon da kifin,

“Ku raba keda Innar mu. Ya debe sauran. Innar mu har littafan da aka bani da math set ya dauke duka. Agabana ya kira Yazeedu ya mika masa wai shi dasu Mariya. Hakama kifin da lemon d’ai d’aya ya bani ya boye sauran. Shin wannan wacce irin rayuwa ce Innar mu? Narantse da Allah bazan taba yafe musu ba. Innar mu hak’uri na ya....”

Innar mu ce tai hanzarin katse ni, Ta hanyar cewa,

“Ya isa Batoul. Kar ki manta dai iyayen ki ne. Komai sukai dai dai ne. Ki dena cewa sun zalunce ki. Kina jina?”

Daga kai kawai nayi, Na juya bayana ina kuka ahankali marar sauti. Ban dena kuka ba har sai da aka fara kiraye kirayen sallar azahar sannan na mike na dauki bokitin wankan mu da soso da sabulu nai kasa. Ruwa na diba a rijiya zan shiga band’akin Bintalo ta bangaje ni ta saka bokitin ta aciki.

“Duka na zaki yi? Nace dake ni mana. Sai in san kin zama rikakkiyar mara kunya..”

Kawu ila ne ya fito daga dakin sa yana shan lemon roba ta daya kwace na d’axu.

“Menene Bintalo?”

“Sittin ta ubangiji yarinyar nan ce ta mangaje ni kawai dan zan shiga band’aki.”

Ido na zaro ganin irin rantsuwar da tai akan karya bayan ban aikata hakan ba. Ya sake kurbar lemon hannun sa sannan ya saki wata uwar gyatsa kafin yace,

“Ita da ni ne, shiyasa zata kare rashin kunyar akan ki. Ki shigewar ki zanyi maganin ta.”

“Wallahi Kawu b..”

Saurin dakatar da ni yayi yana mai nuna ni da yatsa.

“Rufemin baki. Almura da idanuwa tsuru tsuru sai kace na mayya. Zaki matsa daga nan ko sai na take kan shegiya.”

Komawa nayi baya. Kan dan simintin kusa da rijiya na zauna ina mai mamakin irin rayuwar gidan mu. Sai kace gidan haya mai dauke da yaruka kala kala. Haka nai ta tunanin kuncin rayuwar mu har Bintalo ta futo daga bandakin. Tana fitowa don neman tsokana ta karkade ruwan soson ta a fuska ta kafin ta wuce sama. Bandakin na shige nai wanka na hade da rage nauyin ciki na. Ina gamawa na haye sama. Alokacin su Alawiyya suka dawo daga makarantar su. Suma sun kammala makaranta yau. Ina jiyo Kawu ila yana sanyawa abunda suka karanta albarka. Ina idar da sallah na ciro kayan da na saka a karkashin kwallar mu. Atamfar sallar mu ce ta bara wadda gwaggo Aminatu tayi mana. Na saka ta hade da mayafin da balkisa yar kanwar Innar mu dake Shema ta bani kunce. Banyi kwalliya ba amma sosai nayi kyau. Sai kallon kai na nake ta madubi. Turaren mu dan duwala na shafa. Hade da d’aukar letar da Malam yabani.

“Innar mu zanje gidan su Fadilah na mata Allah yasanya alkhairi.”

“Madallah! Kya gaida maman tasu. Kar kiyi yamma dai.”

“In Sha Allah bazan dade ba.”

“Nima yanzu dana gama shirina zan le’ka gidan su Haysam. Ko akwai aikin da zan taya Haj Husnah.”

Ajiyar zuciya na sauke. Har ga Allah na tsani zuwa yawan aikatau da Innar mu keyi. Shiyasa na quduri niyyar yin karatu mai zurfi domin nima na samu wani mukamin ko aiki mai tsoka a gwamnati domin tallafawa Innar mu dama yan uwan mu marassa shi gaba d’aya. Sannan banason tana aiki agidan su Haysam. Duk kuwa da ba son shi nake yi ba. Amman banason tana aiki acan. A sanyaye nace,

“Toh Innar mu. Allah ya dawo dake lapia. Sai na dawo.”

Hannun autar mu na rike muka tafi gidan su Fadilah wato babbar kawata...

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

NA HANSATU XOXO□□

_*SHAFI NA BAKWAI_*

•. •. •

Muna shiga gidan su Fadila muka tarar da baban su zai fitar da motar sa waje. Yana ganin mu yayi murmushi. Saboda yasan amintar mu ni da Fadila, Har k'asa muka dur'kusa muna gaishe shi ni da autar mu. Ya amsa fuskar sa fad'ad'e da murmushi.

"Lapia lou Batoul. Yau an kare makaranta ko?"

Kai na a kasa cike da girmamawa nace,

"Eh Baffa!"

"Toh Allah ya zaba maku abunda yafi alkhairi a rayuwar ku. Ki shiga tana ciki. Bata jima da dawowa daga makaranta ba itama."

“Ameen Ya Rabbi Baffa.”

Mikewa mu kai daga dur’kushen da muke, Mu ka shiga ciki, Shi kuma ya ja motar sa ya fita. Aunty Nanah mahaifiyar su Fadila na zaune a tsakar gidan tana sawa Hauwa’u y’ar autar ta kunshi a yatsun hannu. Gaishe ta mu kai ta amsa ciki-ciki. Domin ita sam batason huldar mu baki d’aya da Fadila. Tafison Fadilan tayi kawance da ‘yayan masu kudi irin su. Shi yasa shekarun baya lokacin da Fadilan ke mayatar san Yayan mu. Hanata kawancen mu tayi. Sai a b’oye muke haduwa muyi hira. Fadila na jin murya ta ta futo d’aga dakin ta. Cike da murnar gani na ta washe hak’ora tana murmushi,

“Shigo Aminiyas.”

Murmushi nayi nima muka shiga cikin d’akin. Muka kafa dandalin hirar candy, kowannen mu yana bawa dan uwan sa yadda ranar yau takasance. Autar mu ta bingere a lallausar katifar Fadila, Tuni bacci barawo yayi awun gaba da ita. Fadila tayi rau-rau da idanu. Cikin ‘kasa-kasa da murya kar maman su ta jiyo ta tace dani,

“Wai ya labarin Yaya Najibu? Shiru wai ba xai dawo bane?!”

Nannauyar ajiyar zuciya na sauke,

“Yana Kano! Muma mun kwan biyu bami magana dashi ba. Y’ar wayar da Innar mu ke amfani da ita ta ‘bata rannan. Mun rasa waye ya sace ta wallahi.”

Na k’arasa fada muryata na rawa. Fadila ta sake sakin wata ajiyar zuciyar. Kafin cikin damuwa tace,

“Da kaman kince min yana Shema garin su Innar mu.”

“Eh da acan yake. Toh daga baya kuma shi da ‘yayan wan maman mu suka tafi Kano neman ku’di. Kinsan ALLAH ya sanyawa Kano albarkar kasuwanci. Mutane anata zuwa neman kudi.”

“Oh okay! Allah yasanya albarka a kasuwancin nasu Ameen!”

“Ameen Tawan.”

Haka dai mu kai ta ‘yan hirarrakin mu, Har zancen samari ya shigo ciki. Fadila ta dinga tsokana ta kamar ko yaushe.

“Amiyas matar tsofi. Har yanzu kina nan akan bakan ki ko kuwa?”

Nayi murmushi kawai, Kafin cikin gaskiya ta nace.

“Fad’i ki kara, In Sha Allahu kuwa. Yo me zan yi da wanda suka bani Shekaru biyar ko ‘kasa? Wallahi basu isa aure ba. Ke ni ko wanda yabani shekaru bakwai bana fatan aura.”

Fadila ta shiga ‘babbaka daria harda rik’e ciki. Tana yi tana share hawaye tsabar dariar tayi yawa. Sai da tai mai isarta kafin tace,

“Lalle Aminyas. Ki ce kin sake ‘karo wulakan ci. Yanzu kenan wanda ya baki shekaru bakwai ma bakyasan aura? Lalle k’awata. Allah ki dena fadar haka. Hmm kilama Haysam ne mijin. Kuma kinga shekara biyar ya baki. Wai Aminiyas meyasa bakyason Haysam? Matashi dashi yaje yayo digiri d’insa a kasar waje. Shakaran jia dana had’u dashi wallahi yaketa min maganar ki Allah. Wai zai koma yayo digiri na biyu (master). A kasar Cyprus. Kuma so yake wai kafin ya tafi ya kai ku’din auren ki.”

Gwalalo idanuwa nayi ina ‘kik’kifta su cike da mamakin jin kalaman ta na karshe,

“Kai kudin aure fa kika ce? Saurayi na ne shi da zai kawo kudin aure na ko kuwa auren dole za’a min? Shi fa ya cika rigima. Dududu shekarar sa nawa?.”

Fadila ta sake kwashewa da daria kafin cikin dariyar tace,

“Shekarun sa ashirin da uku. Ai ya isa aure, Kuma in banda ke da abun ki ca yai auren fa sai ya gama masters tukun.”

Tsaki naja cike da takaici, Jin karfin hali irin na Haysam. Wai aure? Yaron da ko rabin hamsin bai kai ba (25). Cikin tunanin da nake a zuciata. Na jiyo Fadila na sake soko wani zancen.

“Allah Haysam na son ki Aminiyas. Wallahi bakiji yadda yake yabon ki ba. Wani irin son so yake miki mai wuyar bayyanawa. Na rokeki ki dena ganin ‘kankantar shekarun sa. Shi fa namiji baya kadan. Wallahi sai kiga anyi auren kakki mamaki satin farko ki ganki da ciki. Daganan zaki rena tunanin ki.”

Saurin rufe bakin ta nayi, Ina mai nuna mata Aunty da ido. Cire hannu na tayi daga kan bakin ta,

“Yo meye? Ai gaskia ne. Ke yanzu fa mun gama sakandire. Shafin sabuwar rayuwa muka buda. Kefa Aminiyas wallahi ki nada matsala. Duk samarin ki kin kore su bakya kula su. Idan an miki magana Ki ce du yarane ko kuma ke kinyi kankanta da zance. Dan Allah Aminiyas ki canza. Sai adinga miki kallon marar samari bayan kinadasu tirela tirela. Karki wasa da damar da ALLAH ya baki pls. Kinji tawaje na?”

“Naji Tawan! Yadda kika ce ai haka za’ai.”

Na bata amsa. Muka ha’da hannu muka tafa. Cikin so ta mance da dayar maganar nace,

“Ya babin karatu? Candy to aure zaki yi ko candy to ‘karo karatu?”

Yamutsa fuska Fadila tayi, Ta daga kai tana tunani kafin tace,

“Ke ni Yaya Najibu zan jira. In Sha Allah! Shine uban ‘ya’yana.”

Ajiyar zucia na sauke. Tabbas Fadila na kaunar Yayan mu. Matsalar mahaifiyar ta ba yadda zata yi ba. Kuma babu kyau tsallake maganar iyaye. Cikin son nunar da Fadila gaskia nace,

“Tawan ki tsaya ki saurare ni, ki auna maganar da zan miki a mizanin basira.”

Gyad’a kai Fadila tayi kafin tace,

“Ina jin ki.”

“Tawan kiyi hak’uri da batin jiran Yayan mu. Ki sani komai na duniya muqarrabi ne daga Allah. In dai ALLAH yayi zaki auri Yayan mu wlh ko me zai faru sai anyi. Idan kuma ALLAH yayi ba zaki aure shi ba w...”

Dakatar dani tayi ta hanyar rufemin baki. Hawaye suka fara yar tsere a kyakkyawar fuskar ta. Cikin rawar baki tace,

“D..Da..Dan ALLAH karki min fatan rashin auren Yaya. Wallahi ina son sa. Zan iya rasa farin ciki na idan har aka rabani dashi. Ya zanyi?”

“Kiyi hak’uri tawan. Ki kuma cigaba da addua. Allah zai zaba maki abunda yafi alkhairi a rayuwar ki. Zan so ki karanta wani littafi na wata writer mai suna miss

xoxo. Sunan littafin SON RAI KO ZABIN IYAYE. Firdausin makarantar mu ce ta karanta mana a makaranta lokacin free period. Dake tanada waya . Kada kibi son ranki ki tawan. Kibi zab'in iyayen ki. Allah zai baki lada ya kuma sa farin ciki a rayuwar ki. Bazan mantaba a littafin yarima Aliyu yaso bijirewa iyayen sa akan ance ya auri yar uwar sa. Yak'i ya auri son ransa. Sai gashi ta zame masa masifa. Ata'kaice dai zabin iyayen da suka zabar masa Meenah sai gashi itace ta zamto wani haske acikin rayuwar su baki d'aya. Dan Allah tawan kakki bijirewa su Aunty. Allah ya zaba miki abunda yafi alkhairi a rayuwar ki, Ameen."

Jiki a sanyaye tace,

"Ameen Ya Hayyu Ya Qayyum."

Tunowa nai da wasikar da Malam Tasiu ya bani, Ciro ta nai na mika mata ina murmushi,

"Kawata karanto mana muji mai ta 'kunsa. Malamin Literature dinnan namu ne ya bani. Wai naje gidah na karanta."

Na karasa fada ina daria, Fadila ta karba da sauri tana warwareta, Zaro ido tayi, Hakan yasa nace,

"Karanto mana muji, Wai meyace ne? Naga kina zare idanu?"

Fadila tai murmushi kafin cikin dan daga murya tafara karanto abinda wasikar ta 'kunsa:

ZUWA GA MAMALLAKIYAR ZUCIA TA

FATIMATA! ZAHRA'U NAH, BATOUL! NOORAL QALB.

ASSALAMU ALAIKI YA HABIBATY!

Nasan zaki yi mamakin wannan wasika tawa dama abunda ta ‘kunsa. Dan Allah kada kiyi mamaki. Domin wannan wasika zata bayyanar miki da tarin shekararren soyayya ta a gare ki. Ina fatan farin ciki zai wanzu a zuciar ki farawar karanta wannan wasika zuwa karshen ta.

Hakika son ki ya mamaye min zucia. Son ki yayi tsamo tsamo acikin kogin rai na. Ya Habibateey ki tallafamin ki karance wasikar soyayyar nan duka.

Na dade ina kallon taurarin samaniya yayin da naga wacce tafi kowacce haske,

_Sai naga bakowa bace na ke gani ba sai ke masoyiyata! So gamon jinine, haqiqa sonki ya zamo jinin jikina! _

Kinfita daban a cikin mata, duk lokacin da na kallleki, sai naga kamar babu kyakykyawar mace sai ke! Ki kwantar da hankalinki masoyiyata babu wata a zuciyata sai ke kadai!

Yarda da amincewarki gareni sune zasu tabbatar da soyayyarki tagaskiya a gareni! Dan Allah ki tallafawa zucia ta ki karbi kokon barar soyayya ta.

_Farin ciki baya dorewa a rayuwa sai tare da bakin ciki, dan haka kowane hali nake bazan ta6a mantawa dake ba masoyiyata! Nakan raba dare ina mai roqon Allah don neman biyan buqata, _

Yanayin sanyi kan sa mutum ya takura, Tare da lullu6a da qaton mayafi amma ni duk sanyin da ake idan na tunaki sai naji tamkar yanayin zafi! Kamar yadda kowacce bishiya kanyi rassa a sama, kuma tayi saiwa a qasa, haka sonki ya mamaye dukkan jikina, idan na kalleki sai nayi farin ciki, idan naji tattausan muryarki, sai nishadi da walwala tare da annashuwa gami da farin ciki su mamaye zuciyata!

DAGA ‘KARSHE

Ko kinsan kece abu na farko da nake

roqon samu? Wallahi ko iyalina basu kai matsayin ki a zucia ta ba. Wallahi nafi son ki akan matata. Bata min halacci. Bata kula dani, Abinci ma sai taga damar dafawa. Ki temakamin ki aure ni ki maye gurbin soyayyar da nake miki a zuciata.

NI NE NAKI:

TASI’U BALA

Tana gama karantowa ta shiga babbaka daria, Naja tsaki ina cigaba da firfita da d’ankwalin hannu na. Cikin b’acin rai nace,

“Allah ya sawwake masa, Duk namijin da baya yabon matarsa wallahi bashida hali, Sannan makaryaci ne, domin kai ma haka zai kai mata zancen ka, Wannan ai rashin adalci ne. Fisabilillah ya zaiyi da ni? Gani yake yi fa da wannan kalaman zai mallake ni ko?”

Fadila ta kad’a kai tana daria. Sai da tai mai isar ta kafin tace,

“Gaskia bai kyauta ba. Ni ya ban haushi ma. Misali ace tana yi masa hakan ma, Sirrin su ne menene dalilin sa na gaya miki?”

“Oho masa. Idan ma yana kai sunana wajen Allah In Sha ALLAH bazan zama mallakin sa ba. Allah kuma ya sakawa matar sa karyar da yake yi mata.”

“Toh Ameen dai.”

Haka dai muka cigaba da hirarra kin da suka shafe mu. Mun jima muna tattaunawa kafin na mike hade da tashin autar mu. Tayi fitsari ta wanko bakin ta da idanun ta,

muka tafi gidah bayan Fadila tamana rakiya ta koma. Daga nesa na hangi Innar mu tana dawowa, Haysam a bayanta rike da leda a hannun sa. Nayi saurin juyawa kar ya hango ni.’ Amma autar mu da bata shiru ta tsalawa Innar mu kira. Hakan ya karkato da hankalin sa ya ganni. Ai kuwa ya biyo baya na. Ina gaba yana biye da ni. Nagaji na tsaya ina kauda fuska ta gefe. Nacin Haysam yayi yawa wallahi. Zuciyar sa kamar kare ya cinye, Sam baya boye soyayyar daya kemin ko a idanun waye. Ina jin sa yana wani furta sunana cikin soyayya a hankali acikin wata irin siga. Cikin turo baki gaba na amsa ciki ciki ina gaishe shi, tunawa da nai da dokar da Innar mu ta kafamin ta dole sai na dinga gaishe shi ai ba sa’ana bane.

•••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□[9/16, 11:28 AM] □: *_IGIYAR ZATO_.....□_*

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(SABON TAKU)

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

•. •. •.

_*SHAFI NA TAKWAS_*

Ido cikin ido ya ‘kuramin idanu yana min wani irin kallo, Kasa jure wa nayi na fara matsawa dan guduwa. Saurin rik’o ‘kasan mayafi na yayi yana wani marairaice fuska sai kace karamin yaro,

“Batoul! Dan Allah ki tsaya ki saurare ni.”

Allah daya hadani dashi yasa na tsaya ina ‘kwace kasan mayafi na hade da doka masa harara. Cike da bacin rai nace masa,

“Kada ka kuskura ka ‘kara tab’a min mayafi.”

“Kiyi hak’uri ki tsaya ki saurare ni dan ALLAH.”

“Ina jin ka..”

Na fada a gatsine, Domin teburin Haladu mai shayi dankare yake da samarin unguwar mu. Sai lek’owa suke suna hangen mu ciki harda mazan gidan mu, Wato su Yazeedu da Shafi’u ‘yayan Kawu ila. Nasan kuma sai sun kai masa rahoto.

“Ashe yau kun gama makaranta ko?”

“Eh”

Na bashi amsa ina lankwasa yatsun hannu na na dama. Hannun sa d’aya yasa yana shafa gemun sa. Nai murmushi kawai gemu ba gemu ba sai wani iyayi yake yi kamar wani babba. Cikin maganganu na da nake a zuci na jiyo shi yana magana,

“Allah ya sanya albarka a karatun naki. Yanzu zaki bude wata chapta din rayuwar ki. Zaki cigaba da karatu ne ko...?”

Bai karasa ba yasa hannun sa yana sosa keyar sa, Sa rai nasan kunya yake ji ya furta ko aure zanyi? Cikin nutsuwa nace dashi,

“Duk abunda ALLAH ya zabar min shi zanyi.”

“Masha Allah! Kinyi magana mai kyau Mine..”

Wai Mine sai kace wata mallakin sa, Na fada a zuci ina murmushi, Yaron nan ya gama rai na min wayo.

“Pls Batoul ki bani dama na fara zuwa zance wajen ki...”

Wata uwar harara na dankara masa ina kyakkyafta idanuwa,

“Kace me?”

“Nace ki bani dama na fara zuwa tadi wajen ki..”

“Tab Ya Haysam kenan! Ai ban isa zance ba.”

Ware idanuwa yai yana sake motsawa kusa dani. Nai baya kadan. Cikin rawar baki ya dube ni,

“Mine! Please ki tausaya min.. Wallahi na matsu.”

“Tame fa?”

Na tambaye shi ina neman ‘karin bayani.

“Ta fara zuwa zance wajen ki.. Wallahi inda akwai gaban matsuwa nayi.”

Ajiyar zuciya nai, Domin narasa ta yadda zan fito ‘karara na nuna masa ni bana ra’ayin sa. Gashi ya tsare ni da mayen kallon sa, Sai bin ilahirin jiki na yake da kallo kamar wata mutum-mutumi.

“Ya Haysam zanje gidah sauri nake yi.”

Na karasa fada ina nuna gidan mu. Murmushi yai wanda hushiryarsa ta bayyana. Ya shafa kansa kafin yace,

“Toh yaushe zanzo kenan? Saboda zan koma Cyprus ‘karo karatu, kuma..b..Banason na tafi ba tare da ‘kwakkwaran magana a tsakanin mu ba.”

Nayi murmushi kawai, Lalle zancen Fadilah dagske ne. Dak’yar na iya daga kai na dube shi kafin cikin nutsuwa nace dashi,

“Duk yadda ake ciki zaka ji abakin Fadila”

“Meyasa ba zanji a bakin ki ba uhm.. ?Batoul..!”

Ya karasa fada yana jan k’arshen kalaman sa.

“Ya Haysam bari na tafi gidah. Innar mu na jira na.”

Ina gama magana na shige gidah na barshi a tsaye batare dana bashi amsar tambayar da yai mun ba. Domin narasa ma mai zance masa. Ina leken sa ta zaure naga ya mike yayi titi hannayen sa zube acikin aljihun wandon sa na jins. Girgiza kai kawai nayi na ‘karasa shiga gidah na haye sama.

GIDAN MATA TARA

Usaiba matar Kawu Ishaq da Hansatu matar Kawu Dawud sune a tsakar gidan mu suna hira, Gefe kuma Innatuwa ce matar Kawu Khamis da Hajara amaryar Kawu ila wadda ke baje akan tabarma tana afka kalba a baka. Cikin ta yafuto sosai, Zata iya haife shi a kowanne lokaci. Wato haihuwa ta biyu bayan ta Basmah babbar ‘yarta. Wadda ta haifa shekaru hudu baya.

Tunda na shiga da’kinmu na kafa kofin ruwan randar mu a baki ban cire ba sai da na shanye ruwan tas. Domin ‘kishiruwa nake ji sosai. Gefe na zauna ina ajiyar zucia,

“Innar mu sannu da dawowa..”

“Sannun mu Batoul. Ya Auntyn su Fadilan?”

“Lapia lou Innar mu.”

“Haysam din ya tafi? Yaron kirki tunda ga gidan su ya dakko min ledar nan ya rako ni wallahi, Akwai hankali da nutsuwa.”

Shiru nayi ina ninke mayafi na.

“Ko baki ji mena ce ba?”

“Angode masa. Ya tafi, Yace wai zai koma ‘karatu.”

“Eh haka hajiyan su ke fada wai zai yi digiri na biyu a ‘kasar waje.”

“Eh haka yace. Muma ALLAH yabamu ikon cigaba da karatu Innar mu. Ilimi da dadi yake . Ina so naga ina koyarwa a jami’a ace na zama wata nima, Ana damawa dani a fannin ilimi.”

“Allah ya tabbar da alkhairi uwata.. Allah ya baku nasara a rayuwar ku Ameen.”

“Ameen Innar mu..”

Muka hada baki muka fada gaba d’aya harda autar mu dake zanen gidah a littafin ta.

“Innar mu mai zan dafa?”

“Ai inaga ba sai anyi abincin daren nan ba. Kinga hajiyar su Haysam ta zuba min abinci ishashshe. Har Haysam din ya riko min. Yake tambayar ki. Nace kingama makaranta yau.”

Na dubi ledar da take nuna min. Baka ce an kulle saman ta. Yanzu duk aikin da take musu ba zasu iya zuba mata ko a kwano bane sai leda? Allah ya yaye mana wannan ‘kuncin rayuwar. Allah ya kawo mana haske a cikin lamurran mu. Ameen! Yak’e nayi na zauna kusa da ita ina matsa mata kafafunta.

“Sannu Innar mu.. ALLAH dai ya nuna mana lokacin da zamu ji dadi a rayuwar mu. Allah har abun matsa kafafu zan siya miki. In sha ALLAH!”

“Ameen Uwata Ameen”

Dake wani lokacin haka take kirana saboda sunan mahaifiyar ta naci wadda ake kiranta da Fadimatu_Zahrau. Yan kwanukan wanke-wanken mu na sauka dasu. Ina wankewa autar mu na ‘dauraye wa. Cikin haka su Alawiyya da Hinde suka shigo, kowacce da ledoji a hannun ta. Sai Hauwa a bayan su tana biye dasu da wata ledar.

Bintalo ta sakko a guje daga sama. Daga ita sai ‘d’aurin zani, Kanta ba dankwali, ‘kuda-kudar kwanyar diddigaggen gashin ta duk ta fito. Kawu ila ma ya fito daga dakin sa hannun sa ri’ke da bokitin da yake zama akai. Washe baki yayi yana kallon ledojin hannun su Alawiyyah. Saboda tsabagen gulma da annamimancin sa. Da kuma son cin zarafin mu a kullum shi yasa ya dena zuwa shagon sa yana zama. Sai yaro ya samu mai zama masa. Shi kuma kullum yana gida yana neman magana.

“Sannu ‘yayan albarka. Masu farin jini da dimbin alkhairi. Yau kuma me muka samu? Nan duk kayan murnar kare makarantar ne?”

Cewar Kawu ila, yana tafa hannaye sai kace mace. Bintalo sai raye raye take tana murna. Hinde ce kadai ta daga masa kai alamun Eh, Alawiyya kuwa fasa ‘kwan cingom tayi hade da zama a gefan Hansatu matar Kawu Dawood.

Gud’a Bintalo ta hauyi tana buga zanin ta. Ummita matar Kawu ila dake gefe ta karbi ledar hannun Alawiyya tana zazzage wa akan taburma. Bota ce guda d’aya sai biredi mai yanka yanka leda biyu da kwamfulas sachat babba guda d’aya. Ledar hannun Hindatu kuma kek ne na Oasis guda uku da lemon roba guda biyar. Sai ledar hannun Hauwa kuma lemon ‘bawo ne da ayaba. Yadda kukasan duniya aka kawo haka Bintalo ta dinga shewa tana goranta mana,

“Ahayye nanaye! Kaga masu farin jinin yan gida d’aya. Ga kaya nan na motsa baki na dubunnai, wasu kuwa sai dai su ciji yatsa babu masu kawowa, A hayye nanaye..”

‘Chassss’ suka hada hannaye suka tafa da Ummita matar Kawu ila domin itace aminiyar gulmar ta itada mijin ta Kawu ila.

“Tab! Gaskia sun kashe kudi, Nera tayi kuka anan yasin. Kalli kek dinnan sai gidan yan gayu ake samu.”

Kawu ila ya karasa fada yana jujjuya kek din hannun sa. Hada kayan wanke wanken mu mu kai muka fara hawa bene dasu,

“Zo nan mai idon jemagu..”

Kawu ila ya kirawo ni, kin juyawa nai domin harga Allah natsani yadda yake tankamin halitta ta.

“Zaki zo ko sai na zo na damki wuyan shegiya?”

Juyawa nai na fara sauka autar mu kuma ta haye sama harda tuntub’e. Nesa dashi na tsaya ina kallon ‘kasa.

“Bak’in ciki kike yi musu ne?”

Kamar daga sama na jiyo muryar sa, Wai bak’in ciki? Na nanata a zuciya ta. Toh mezan yi wa bakin ciki? Kayan da samarin su suka fita dasu suka siya musu ko kuma samarin nasu wanda yan gidah d’aya ne zan yi bakin ciki? Nama rasa wanne irin bakin ciki yake nufi ina yi musu. Domin gaba d’aya banga abunda zan musu bakin ciki akai ba. Sau nawa ana kawomin fiye dasu ina mayarwa wanda suka bani. Saboda ni abun hannun samari ba damu na yayi ba. Cikin maganganun da nake a zuci na sake tsinkayo muryar sa yana cemin,

“Ko dan naki samarin hannun su irin na yan dambe ne? Kullum basa miki ungo? ‘Kan’kamin na ‘kamora masu hannu kamar na yan dambe.”

Gaba d’aya yan tsakar gidan suka bushe da dariya. Nayi murmushi kawai ina girgiza kai na, Ina mamakin irin ahalin gidan mu. Domin tabbas yaci sunan da yan unguwa ke gaya masa,

‘Gidan Mata Tara: Gidan guntsi fetsi, Ba babba ba yaro, Gidan da rashin daraja ke arha, Barbadaddu, Tsigalallu. Gidan su Ila baban Yusha’u, Su Alawiyya yayan gwal din karyar gulai Bintalo, Gidan Dan Dawooda malalaci mai macacciyar zucia. Mai kwanan daki matar Hafsatu mai neman na kai. Mace mai kamar maza kwari ne babu, Nasu Aminatu kanwar Batoulu mai kyau...’

•••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA: TARA_*

••••

Rankwashi Kawu ila ya sakarmin a ‘kwanyar kai na. Na dafe wajen ina runtse idanu na saboda azabar rad’adin da yake min. Allah ka sakamin. Na fada a zuciata ina sake sadda kai na ‘kasa.

“Je ki. Kyallukazar kaya.!”

Na wuce sama hade da kwasar ‘yan kwanukan da muka wanke. Ina jiyo su suna gulmata hade da shewa. Ina shiga da’ki na ajiye kwanukan a ma’ajiyar su. Sannan na zauna ina zabga tagumi, Innar mu dake gefe tana zazzage abincin gidan su Haysam a filate din abincin mu ta dube ni, fuskar ta dauke da alamun tambaya,

“Ke kuma menene hakan? Ban hanaku tagumi ba?”

Cire tagumin nayi na dan muskata kusa da ita ina matsa mata k’afafuwan ta.

“Babu komai Innar mu. Su Kawu ila ne a kasa ya rankwashe ni akan su Alawiyya.”

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta dube ni,

“Ko mai ya miki dan ya isa ne. Kakki manta mahaifin ku ne shima. Sai ki kokari ki dena yin abunda zai rankwashe kin.”

Daman nasan abunda zata ce kenan. Domin sai dana ayyana abunda zata fada a zucia ta. Bata taba fad’an lefin su, kullum Sai dai tace ai iyayen mu ne mu rabu

dasu lapia albarkar su ta bi mu. Amman su basa ganin hakan, Rashin mutunci sala-sala suke yanka mana. Murmushi kawai nayi,

“Toh Innar mu zan dena..”

Na fada domin kawo karshen maganar tasu. Mik’ewa nai na shiga duba lungu da sako na dakin mu.

“Yaya Batoul me mike nema ne?!”

Autar mu ta tambaye ni tana bina da kallo Itada Innar mu ganin yadda na hautsina dakin gaba d’aya. Gumin daya zubo min na sharce ina daria,

“Wai ko ALLAH zai sa na gano wayar Innar mu. Wallahi zuwa akai aka dauke ta.”

“Ai kuwa dai na gayawa Innar mu nagan ta a hannun Yusha’u d’axu tace ba ita bace.”

“Wohoho biri yayi kama da mutum, Domin Yusha’u dazu dana hange shi a majalisar su dauke kai yayi yana sosa keya. Innar mu dan Allah ki kyaleni naje na karbo miki wannan wacce irin sata ce. ?“

“Uhm uhm dai! Da kika fada me nace miki Auta?”

“Ca ki kai ba taki bace ai ba kekadai kamfanin wayar su kayiwa ba.”

“Yauwa banason neman rigima. Idan shi ya d’auka ma yaje na bashi. Da nasan zan samu ne?”

Girgiza kai nayi ina kwafa. Na rasa wacce irin zucia ce da Innar mu. Sam bata bari wata ‘baraka ta shiga tsakanin mu da yan gidan mu. Koda kuwa hakan zai janyo mana bacin rai su ya faranta musu. Ita kullun dai burin ta bai wuce taga zumunci ya wanzu a tsakani ba sam batasan husuma ko kadan. Jiki a sanyaye na koma na zauna a gefan randar mu. Har cikin dakin mu ya shigo ya sace wayar Innar mu. Shi yasa nake so ALLAH ya hore min na sai mana kwado muma mu dinga kulle k’ofar mu. Ina cikin zancen zuci na jiyo Innar mu nace min,

“Wanko hannun ki kuci abincin Uwata.”

“Toh Innar mu.”

Na fada ina wanke hannu na a gefan tukunyar kusa da randar mu. Shinkafa da miya ne da kafafun kaza guda biyu da kai d’aya. Sai kamshin tafarnuwa ne tashi a miyar, Kallo d’aya za kai mata kasan miyar gidan yan gayu ce. Bismillah mu kayi sannan muka fara ci. Har wani lumshe idanuwa autar mu keyi tana kada hannayen ta cikin dadi. Rabon mu da irin cimar nan har mun manta. Domin sai sallah ko kuma gidan biki ko idan mun kai ziyara kaduna gidan Gwaggo Aminatu. Kan kace me? Har mun tashi da abincin nan. Innar mu ta bar mana kai da kafafuwan. K’afa d’aya na dauka na taune na barwa autar mu sauran,

“Alhamdulillah!”

Na fada ina shafa ciki na, Innar mu tayi murmushi tana tattare shinkafar data zubar a gaban ta. Harhada kwanukan da suka ba’ci nai na sauka kasa dasu. Wanke su nai tas na koma sama abuna. Lokaci zuwa lokaci mu kan taba hira da Innar mu. Domin kullum cikin lazumi take. Wani littafin hausa mai suna duk kyan takalmi na dauka na fara karantawa, Littafin kwarai yayi dadi. Inason yadda rayuwar Aisha-Farida take itada Dr Shureim. Dake ba sallah nake ba haka na wuni ina karantawa har bayan magrib.

Cikin daga murya na jiyo wasu yara na magana suna ambaton suna na. Ta sama na leka ina kallon yaran. Su uku ne kowanne hannun sa dauke da ledoji shake da kaya a ciki. Daki na koma ina sanarawa Innar mu,

“Innar mu kinji an aiko wasu yara guri na.”

“Toh je ki ji menene? Allah yasa alkhairi ne.”

“Ameen!”

Na fada ina zura hijabi na. K’asan na sauka, dandazon yan gidan mu kowa ya fito ciki harda Bintalo da ta tasa yaran agaba tana tanbayar su,

“Anya kun tabbata wajen ta aka aiko ku? Ko dai ca akace muku Alawiyyah ko Hinde?”

Yaran suka ka’da kai alamun a’a. Na biyun wanda ya fisu dan tasawa yace,

“Aa mu dai ca akai mana mu bawa Batoul din Innar mu.”

Bintalo tasa hannu a kirji tana zare idanuwa. Kawu ila yafuto daga bandaki yana baje idanuwa,

“Kai su waye wannan?”

“Toh ga su dai wani ne ya aiko su, A k’aryar su dai sunce wajen shegiyar yarinyar nan ne.”

“Kai waye ya aiko ku?!”

“Ca yai muce gashi inji Haysam.”

“Waye haysam?”

Kawu ila ya fada yana dora hannayen sa a kugu. Bokitin zaman sa na gefan sa. Bintalo taja k’wafa tana girgiza kai,

“Haysam dan gidan Alhaji Kabeer Wafa, Sittin ta ubangiji akwai wani abu a kasa, Domin acan Kaltume ke aikatau.”

Usaiba matar Kawu Ishaq dake sama ta sakko tana tafa hannaye harda rawa, Domin tasu ba tazo d’aya da Bintalo ba. Ledojin ta karba daga hannun yaran tana taka rawa,

“Kuce masa angode ALLAH yayi albarka.”

Ta karasa fada tana mika musu nera ashirin data ciro a gefan zanin ta. Bintalo taja tsaki tana matsawa gefe, Kawu ila kuma ya shiga daga wuya yana zare idanuwa dan hango abubuwan da aka kawo min. Ni dai na tsakure a gefe na zabga tagumi. Rayuwar gidan mu na bani mamaki wallahi, Na rasa a wane hali nake ciki, shin fari ne ko baki oho?. D’aya daga cikin yaran da aka aiko ne ya dawo da sauri,

“Wai ana sallama da Batoul..”

“Aiyiriririrururuuuuu! A hayye Nanaye! Masu abu da abunsu! Kaga wa’enda su kai gadon abun arziki, Kaga wa’enda kuttin farin jini ya fashewa, Kaga wa’enda ake zuwa har gidah a aiko musu da cimar ‘yayan manya. Kaga masu daraja, Kai Kai Kai shagali! A hayye sama ruwa kasa ruwa.. Kaje kace gatanan zuwa yanzu.”

Cewar Usaiba, Tana fada tana rausaya wa, Duk dan saboda Bintalo. Rai na a turnube na fita ina jan hijabi na ya rufe min hanci. Har ga Allah banso baba Usaiba ta karbi kayan can ba. Domin bana karbar abun hannun saurayi, saurayin ma Haysam wanda rai na yafi tsana aciki. Ciki ciki na gaishe shi ina juyar da fuska ta. Muna tsaye ne a zauren gidan mu. Ina kallon yaran gidan mu na leken mu, Zasu Kai wa iyayen su tsegumi.

Sanye yake cikin shadda kalar sararin samaniya, Ta sha turarren aiki kalar kayan, Yasa takalmi da hula duk kalar aikin jikin rigar sa, Kamshi sai tashi yake a jikin sa. Hasken wutar injin teburin Haladu Mai Shayi ne ya haskaka shi, Mu kai ido biyu dashi, Gaba d'aya ya tattara hankalin sa da nutsuwar sa a kai na yana karemin kallo. Mayen kallon sa ne ya karasawa na tsane shi. Na tsani yawan kallo a rayuwata. Domin babu kyau ko a musulunci. Baki na tabe ganin bai amsa gaisuwar sa ba, Ko bai jiba oho? Na sake cuno baki gaba,

"Ina yini?"

"Alhamdulillah Mine! Kina lapia?"

"Gashi kuwa ka ganni."

Dan murmushi yai mai sauti yana shafa sajen sa, Na saci kallon sa ta gefan ido, Sai wani bokarewa yake yi kamar wani babba. Cikin wani irin salo ya amsa ni,

"Naji dadin kasancewa ta dake yau dinnan. Batoul! Pls ki jiyo ki saurare ni."

"Kunne ke ji, Ina jin ka."

"Ya batun d'axu? Shin kin aminta na fara zuwa zancen?"

Ajiyar zucia na sauke, Na dan ja hijabi na kasa ina wasa da yatsun hannu na. A tsaye muke yana kallon gabas ina kallon yamma, Amman lokaci zuwa lokaci na kan dan juya na saci kallon sa.

"Kayi hak'uri Ya Haysam. Gaskia yanzu dai bazan fara zance ba, Kaga yau ne fa na gama makaranta. Ina bukatar tunanin me zanyi a gaba."

Shima ajiyar zuciar ya sauke. Duk kuwa da nasan tasa ta damuwa ce. Cikin marairaicewar murya kamar zai yi kuka yace,

“Dan Allah ki sasssauta min Mine! Ki bari manyan ki su san da ni. Kar kiyi *ZATON* da shiririta nazo, Ni wallahi da aure nake neman ki Mine. Dan Allah ki dai duba.”

“Shikenan duk yadda ake ciki dai zaka ji daga bakin Fadilah In Sha Allah.”

“Meyasa sai a bakin Fadilah? Uhm! Mine? Meyasa?”

Murmushi nai, Yaron nan yana bani daria, Sai wani lankwashe murya yake yi. Shi fa ganin sa yake matashi mai jini a jika ko? Kofa rabin hamsin beyi ba (25) Dududu fa shekarun sa 23 kila ma bai cika ba. Amma wai neman aure na yazo yi. Na tabe baki ina sake ‘kurawa bango ido. Domin juyawa nai bangon gaba d’aya saboda nagaji da nacin kallon sa. Dan iska. Na fada ina zura hannu na na daga hijabi na daga saman kirji na dan karya kwanta ya kalle min na ALLAH ya isa. Sake jiyo shi nai yana narkar da murya,

“Mine! Pls kiyi magana ko zucia ta zata samu sassauci.”

“Dankari!”

Na fada a hankali, Dan satar kallon sa nai, Hannun sa rike da mukullin motar sa,

“Ya Haysam kayi hak’uri zakaji daga bakin ta, Sannan dan Allah ka dakata na dakko kayan can daka bayar aka kawo min.”

“Wai meyasa bakya karbar abun hannu na? Tsanar har ta kai haka?”

Saurin girgiza kai nayi,

“Aa wallahi! Ba haka bane. Kawai dai bana amsar abun hannun samari ne”

“Toh ki fara a kai na, Ai ni yayan ki ne. Ki dauka tamkar Najibu ne ya baki. Kyauta ce na murnar kammala karatun ki. Na roke ki da ALLAH kar ki mai do da hannun kyauta baya kinji ko?”

“Shikenan Nagode! Amma kayan sunyi yawa ne bandai duba ba, amman naga ledoji da yawa.”

“Kai haba! Tarkace ne kawai. Amma akwai yar karamar waya wadda nake so mu dinga magana. Nasa layi da komai. Dan Allah dan Allah kar ki ce bakyaso. Dan Allah”

“Shikenan! Ka rigada ka hadani da ALLAH kaga bazan ki ba. Nagode Allah ya kara bud’i. Allah ya saka da alkhairi.”

“Ameen! Allah kuma ya bani ke a matsayin matata. Ameen”

‘Ba Ameen ba In Sha Allah’

Na fada a zuciata ina yak’e a fili. Agogon sa ya kalla kafin ya dube ni.

“Toh zan gudu Mine! Congratulations once again. Allah yabada nasara a rayuwa.”

“Ameen Ya Hayyu Ya Qayyum! Nagode sosai Ya Haysam.”

Sallama mu kai ya fice ni kuma na shige gidah. ‘Yayan gidan mu dake labe suka shige da sauri nai murmushi kawai ina tuno d’aya daga cikin kirarin gidan mu. Gidan Mata Tara: Gidan guntsu fetsi. Ba babba ba yaro. Gidan da daraja ke arha, Tarbiyya tai karanci.

******

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

Mucigaba da shakatawa da wannan, KAFIN A FARA KAFTA WASAN□□❤□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA GOMA_*

Ina shiga na tarar Usaiba tayi ‘dai-dai da kayan ledojin tana fadar sunayen wa’enda tasani. Himilin yan gidan mu kuwa kowa ya zuro kayuwa yana kalla, Wasu ta d’akunan su, wasu ta sama wasu kuma ‘yayan su suka aiko. Wucewa nai zan hanye sama Usaiba ta janyo ni tadawo dani kusa da ita,

“Tsaya ki kallon kayan ki ‘yarnan. Anci uban nera yasin. Yayi gwarzon kokari wannan saurayi naki. Kutsin uban chan kayya kai. Dubi kaya ahayyye.”

Ni de murmushi nai ina mai da kai na gefe. Usaiba kuwa ta shiga daga kayan nan tana fadan sunan kowanne yadda kukasan kayan lefe. Bintalo na gefe hannunta a baki tana ciza. Su Alawiyya kuwa sai cika suke suna batsewa.

“Ledar farko mayukan shafawa ne da turaruka masu kamshi da tsada. Leda ta biyu kiret din kwai ne guda biyar. Leda ta uku chakulats ne masu tsada gasu nan kuna gani. Leda ta hudu atamfofi ne guda uku da mayafi d’aya. Leda ta biyar kuwa lemukan kwali ne gasunan da biskit masu tsada suma a kwalin su. Ledar karshe kuma kaji ne masu tashin kamshi. Kutsin uban can kayya kai harda wayar tarho ta salula... Ayirrrruruuuuu.’

Usaiba ta karasa fada tana sakin guda. Gaba d’aya gidan mu ya kacame da magana. Harda yayan makota da suka shigo gulma. Usaiba ta shiga sakin guda a karo na ba adadi. Sai da tayi mai isarta tukun sannan ta janyo hannu na tana mikamin ledojin,

“Rike yarinyar arziki, Mai farin jinin samarin gidan manya. An buga dake anbar ki ya zasuyi dake. Dole aganki kuma a bar ki yarnan. Ledoji shida rigis aka kawo miki ‘yar nan. Kowanne yaro hannun sa leda biyu ya dakko, Idan aka hada da ta yar karamar wayar ki ma ta kama bakwai kenan. A hayyyye kayya kai..”

Murmushi nai, Baba Usaiba na bani daria kwarai duk sanda ta fadi kalaman ta na kullum wai kutsin uban can kayya kai. Mik’ewa nayi ni dai na haye sama abuna. Ai kuwa tatas ta tattare ledojin ta hayo min dasu itada ‘yayanta Larai da Talatuwa. Uffan ba wanda yace domin kowa shakkarta yake. Ciki harda Kawu ila bata raga masa. Kayan suka kai gaban Innar mu dake kara rediyo a kunnen ta tanaji, Sakamakon batirin da yai sanyi bata kara, Allah ka horemin na siyawa Innar mu sabbin batiran rediyo da kwadon kulle kofa. Na fada a zucia ta ina sauke ajiyar zuciya.

“Kaltume, Ajiye rediyo ki kallon kayan abun arziki...”

Innar mu ta ajiye rediyon tana murmushi,

“ALLAH yasa muga alkhairi.”

“Alkhairin ne kuwa, Kalli abun arziki, Manemin Batoul ne ya aiko aka kawo.”

“Kai du kayan nan?”

Innar mu ta tambayi Usaiba tana bin ledojin da kallo cike da mamaki domin tun d’axu rediyo take ji, Ga kullum gidan mu cikin hayaniya yake baka bambamce fada da hira, Abun farin ciki ko na baki.

“Eh fa! Gasu nan acan acan. Hashimu ne ya bayar aka kawon ta.”

Daria na fashe da ita jin yadda baba usaiba ta fad’i sunan wai Hashimu,

“Haysam ake cewa Baba.”

Cewar Autar mu. Kada kai Baba Usaiba tayi alamun tagane, Sannan ta shiga matsar da ledojin gaban Innar mu,

“Gasu fa kaltume.”

Lekawa Innar mu tayi tana jaddada kai. Hade da rike haba.

“Anya usaiba kayan nan basuyi yawa ba? A mayar masa ko?”

Usaiba ta kece dariya tana sosa kanta.

“Kutsin ubancan kayya kai. Yasin baza’a mayar ba.”

“Innar mu wallahi nima sai dana ce masa nide bazan karba ba, Yai ta hada ni da ALLAH. Ba yadda zanyi ne da wallahi bazan karba ba. Kuma danma ya rigada ya bayar an ka...”

“Jar ubanki nace! Kaji min yar jakar uba, Yo ba dole a ansa ba. Kinfison kullum sai dai ayita cewa bakida masoya, Ko kuwa ace tarin marowata ne.?”

Usaiba ta cemin tana min dakuwa. Murmushi nai kawai na maida kai na gefe. Sake maida kallon ta tai ga Innar mu.

“Kaltume ga fa kayan.”

“Usaiba ni wallahi bani da tacewa, Ke da Batoul din dai kwa san yadda zakuyi dasu.”

“Baba Usaiba ki raba kawai. Allah badan keba kinsan kayan nan Kawu ila kwace su zai yi.”

Su Talatuwa suka kece da daria. Usaiba ta gwaggwafe ta fara raba kayan.

Mayukan shafawar da turarukan miko min su duka itada dasu atamfofin da kwalin wayar. Ta kuma bawa autar mu kiret din kwai uku ta kawo gabana. Sanan ta raba chakulet din gida uku tabani rabo biyu. Lemukan kwalin ma da biskin ta kawo rabi gaba na, Sannan ta zazzage kajin akan filet, Guda biyar ne gasassu. Guda uku ta zuba min akan wani filet ta turo shi gabana. Murmushi nai ina tunanin da Kawu ila ne yai rabon nan da kilan fukafuki zan samu. Mik’ewa tai ita dasu Larai dake tayata rikon wasu kayan.

“Nagode baba usaiba.”

“Mune da godia yar nan. Yau zamu washe bakin mu da kayan Hashimu au Hesan.”

“Haysam ne fa baba..”

Autar mu ta kara gyara mata tana daria. Dariar baba usaiba itama tayi tana sude hannayen ta,

“Ba kuma muje kasa ayi rabon wannan. Nasan anacan an kafa dandalin gulmata. Na gurji bakin shege da shegiya wallahi.”

“Sai da safe usaiba. Angode”

Innar mu ta fada mata, Tana k’ok’arin sake kunna yar rediyon ta. Matsawa nai kusa da Innar mu,

“Innar mu ga kayan fa.”

Ajiye yar rediyon tai tana kallon kayan. Cike da damuwa tace,

“Wallahi kayan sunyi yawa uwata. Nide da zaki ji ta tawa. Wayar nan da atamfofin ki bar su kar ki amfani dasu. Da safe in sha Allahu idan naje aiki sai na mayar masa ko kuwa?”

Tak’arasa fada cike da damuwa. Ni kai na kayan gaskiya yawan su sun tsorata ni. Gashi ba son sa nake ba. Kar nan gaba yace na yaudare shi abun hannun sa nake kwadayi. Amman ya zanyi ya rigada ya hadani da ALLAH ?

“Innar mu ya riga ya kashemin jiki, Ya hadani da ALLAH kada na mayar da hannun kyauta baya, Wai na dauka tamkar Yayan mu ne yabani.”

Ajiyar zuciya Innar mu ta sauke.

“Toh ai shikenan! Allah yasa hakan shine yafi alkhairi! Ameen.”

“Ameen..”

Muka amsa baki d’aya harda autar mu. Wadda tadawo kusa da ni tana jiran abata kason ta. Dak’yar na shawo kan Innar mu ta raba mana, Da catai sai dai muci ita ta k’oshi. Muna ci kunnuwan mu na matsowa. Rabon da muci dadi irin haka wallahi harna manta. Domin inde ba gidan su Fadilah ba. To sai kaduna idan munje gidan Gwaggo Aminatu.

Usaiba tun daga kafar bene ta fara shewa muna jiyo ta,

“Toh ahalin ‘Gidan Mata Tara’ ku marmatso kusa ku dandali abun arziki. Wasu sai dai su shige ‘daka su cinye su da ‘yayan su. Ahayye kayya kai.”

Tana zuwa ta baje akan taburma tana karkasa kayan motsa bakin kashi-kashi. Kashi biyar ta raba kowanne kayan, cikin sude hannu ta shiga kiran sunayen kowanne daki kamar a makaranta ana kiran rajista.

“Ke Hinde ungo naku da uwar ku.”

Bintalo dake tsaye ta buga zani tana sakin tsaki ta haye sama. Usaiba ta kece da dariya,

“Yo ai kin banza. Mutum yace baya so ba zai ci ba mana. Jar uba kayya kai.”

Ta maidawa Bintalo martani tana gu’da. Sai da tayi mai isarta kafin ta cigaba da rabawa,

“Ke Fareedah ungo naku ku da gyatumar ku Hansai, Bala rike kai da Yusha’u ne da Innatuwa. Idris ungo nan rike kai da tawagar yan dakin ku. Ungo nan Larai namu ne, Wannan na Hajara ne da Rabi ki kai musu, Rike da kyau.”

Tas tagama rabe shi, Kawu ila dake kan bokitin sa ya sake gyara zaman sa. Bokitin ma duk ya tsufa yayi tsatsa. Dake bokitin karfe ne ga alamun an kai yan walda an walde shi, Sai kace bokitin sihiri. Yaran mokota dake tsaye suka zubawa Baba Usaiba kallo suna jiran nasu kason. Burbidin ta kasa ta daddanka musu a hannu,

“Toh kuje ‘yayan sa’idunawa. Da safe kwazo ku dora daga inda kuka tsaya.”

Ta k’arashe maganar tana tsaki. Uffan ba wanda ya tanka mata domin shakkarta ake. Zagin ta kadai idan ta lailayo su ta dura maka sai kayi ciwon kai, Ba sirke haka

take zagin ta. Mutinci awajen Baba Usaiba daman babu tuni su kai hannun riga. Hayewa sama tayi tana kurbar lemon ta tana wake wake da karfi,

“Kai tsakanin ‘dan Adam da kudi! Tsakanin dan adam da kudi..”

Kawu ila ya zabga mata harara ta baya, Ya duka ya dau bokitin zaman sa ya kai daki, Ya fice shagon sa ransa a matukar b’ace.

Mun jima muna dandalar kayan dadin nan a daki. Wayyo Allah kamar sallah. Tas na cinye nama na, Na tauna kashin na tsotse bargon na taune duddugar na had’iye. Na kafa kwalin lemon don simon da aka rubuta ajikin lemon, Na dinga tuttulawa ciki na. Ga sanyi ga dadi. Ina gama sha, Na bude ledar chakulet din. A dunkule take alawar. Na dashare hakora ina nunawa Innar mu,

“Innar mu kalli. Yasin kamar daddawa ko? Kinga yadda chakulet din take. Wayyo Allah dadi..”

Innar mu dake kurbar lemon ta tai murmushi tana juya tata chakulet din a hannu,

“Ai kuwa wallahi. Kai wannan yaro ALLAH ya saka masa da alkhairi an motsa baki sosai Allah ya bud’a masa.”

“Ameeen..”

Na amsa ta ina sake tura chakulets din a baki na mai suna ‘Maltesers. Wata bahaguwar gyatsa autar mu ta saki tana shafa cikin ta,

“Alhamdulillah! Yasin kamar a gidan yan gayu.”

Muka bushe da dariya. Mik’ewa nai Ina mika, Na d’au kofi zan debi ruwa a randa naji wayam. Babu ruwan ya ‘kare. Na dubi Innar mu dake nannade ragowar naman a takarda,

“Innar mu ruwa ya kare karfe nawa?”

Rediyon ta ta kunna ta danyi shiru tana sauraron su. Da alama so take ta gano shirin da lokacin sa , Domin ta rike komai.

“Takwas saura kwata.. Yanzu zasu yi shirin ‘Duniyar Mu A Yau.”

“Ai dare beyi ba. Bari naje na ebo mana ruwan famfo. Na randar ya kare.”

Autar mu tai hanzarin mik’ewa tana gyara zaman hijabin ta.

“Yaya zan ebo.”

“A’a ki zaman ki. Dare yayi. Innar mu bari na ebo mana ruwa.”

“Zan raka ki Yaya.”

“A’a na hutasshe ki.”

Na karasa fada ina zura hijabi na, Na dau bokitin ebo ruwan shan mu na fice. Domin idan na bari autar mu ta min rakiya toh zamu dade bamu dawowa. Domin ta dinga yimun tambayoyi kenan kala kala na duk abunda tagani akan hanya ko sunayen jikin shago...

Can gangaren famfo na nufa. Inda famfon unguwar mu yake. Akan hanya naci karo da Fareedah yar gidan Kawu Dawood ta karshe da kuma Basma yar autar Kawu ila. Ma’ana yarinyar da Hajara amaryar sa ta haifa shekaru hudu da suka wuce. Tsaki naja! Allah ya kyauta. ‘Kananan yara a dinga barin su wasarere su kadai suna yawo. Kayi magana a zage baban ka dake kabari. Har nayi gaba na dawo wajen su suna tafe hannuwan su a sarqe ko ina zasu a daren nan? oho. Na dubi Basma daga ita sai yar shimi ba ko wando a jikin ta. Fareeda kuma da riga iya gwiwa ba dankwali. Itace babba ma akan Basmah. Ita Basma shekarun ta hudu. Fareedan kuma batafi 6 ba.

“Ina zaku?”

“Atana damu ciyo.”

“Wai Ashana.”

Fareedah ta fada tana dariyar tsamin bakin Basma. Na dubi shagon ‘Galin naga akwai wuta har zasu siyo su dawo. Ko na jira su ne? Na fada a zuciata. Cikin haka na hango Kawu ila yana tafe yana watsa hannu baya yana magana shi kadai.

“Shikenan ma kuje ga Kawu can.”

Na sauke ajiyar zuciya ganin kila ya jira su siyo tunda yana wajen shagon. Tafiya sukai nima na kama hanyar debo ruwan. Basma na ganin Kawu ila ta rungume shi tana masa oyoyo.

“Maza kuje ku dawo.”

Yace dasu yai wucewar sa gidah. Suna zuwa shagon Gali ya dashare hakora, Lungu da sako ya kalla babu kowa. Ya yafuto su da hannu suka je,

“Ashana za’a bamu.”

Gyada kai kawai yai yana janyo Fareedah jikin sa. Shafa kanta ya shiga yi yana dage rigar ta sama. A hankali ya shiga rad'a mata,

"Karki fad'a a gida. Kiyi shiru zan baku kayan dadi. Me kike so?"

"Alawa da biskit da cizi da madara da lemo."

"Tam zan baki harda karin biredi ma kinji?"

Daga kai tayi. Yayi murmushi yana tande harshe. Kofar shagon ya dan rufe yadda za'ai zaton baya nan. Ya koma ya janyo Fareeda da Basmah yana shafa bayan su kawai. Hade da lumshe idanu. Sai da ya gaji dan kansa sannan yadakko ya basu. Ya kuma dadd'akko duk abunda Fareeda tace tanaso ya zuba musu a leda yabasu. Yace suce abokin Kawu ne ya siya musu. Cike da dadi suka karba suna murna. Ya sake nana ta musu,

"Kuce abokin Kawu ne ya siya muku, Kungan shi can ya tafi. Karki fadi abunda na muku. Idan kika fada bazan kara baku kayan dadi ba. Gobe ma kuzo na kara muku na kuma baku kayan dadin..Kunji?"

Cike da murna Fareedah tace,

"Toh.."

INA zuwa na tari ruwan a famfo. Sai dana kafa kai na na sha mai isa ta sannan na cika bokiti nai hanyar gidah. Nan na kara haduwa dasu Basmah. Kai wannan yara sun cika yawo. Na fada a zuciata ina girgiza kai. Na dubi ledar hannun Fareedah cike da su biskit sai tsalle suke,

"Waya baku kayan dadi?"

“Abokin Kawu ne. Gashi can ya tafi.”

Gyada kai nayi, Domin na hango wulgin wani mutum ya wuce. Cikin gidah muka shige. Nai hayewa ta sama. Na shiga daki bakina dauke da sallama.

“Wa’alaykm Salam”

Juye ruwan nayi a randar mu. Sannan na haye kan yar katifar mu ina ko’karin bude sabon kwalin waya ta da Haysam yabani. Starcoms ce babba mai k.yau bak’a. (Kada ku manta alokacin muna shekarar 2008) Na nunawa Innar mu da autar mu sosai suka tayani murna. Cike da farin ciki da annushuwa haka muka kwanta. Ina Allah-Allah safiya tayi na kai wajen chaji. Domin bamu da wuta a dakin mu. Masifar yan gidan mu sun sa an yanke wayar dake bamu wuta.

Koda su Fareedah suka nunawa iyayen su abunda Gali yabasu. Basu dau mataki ko neman tambayar wanene ya siya musu ba. Hasalima dasu aka hadu aka cinye.

Tsit kake ji ko’ina sai munshari ne ke tashi agidan mu. Kowa yayi bacci banda dakin Bintalo da iyalan ta.. Shin ko meyasa? Oho. Lokaci zuwa lokaci Bintalo ke jera tsaki a karo na ba adadi. Hannayen ta dumu dumu a habarta ta zabga uban tagumi. Su Alawiyya sun tasa ta a gaba suna zumburar baki. Wani shegen tsaki ta sake ja. Cikin zabura ta buga hannun ta a jikin bango da karfi ta shiga nana ta,

“Kan babban bala’i. Sittin ta ubangiji ba zai yiwu ba……”

Shin ko meye ba ze yiwuba? Oho dai. Mu barwa safiya□□

•••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA SHA 'DAYA_*

*•**•*•**

“Kan babban balai! Sittin ta ubangiji ba zai yiwu ba.”

Bintalo tafada tana mai buga hannun ta a bangon dakin da suke jingine. Zaune suke ita dasu Alawiyyah. Sun yi jungum-jungum tamkar wa’enda ke zaman makoki. Timemiyar katifa ce taci ta koshi a dakin. Sai fankar tsaye tana ta basu iska. Kwan fitilar dakin ja ne ya haskaka dakin. Sun jeru tamkar makarantar allo. Hauwa ce kawai ke bacci tana ta jan munshari kamar bijimin sa. Lokaci zuwa lokaci Alawiyya ke sakin tsaki. Bintalo ta cire tagumin data zabga tana watsa hannu baya, Cike da kwakwazo tace,

“Anya akwai wata a kasa. Shin taya dan gidan Alhaji Kabeeru zai so shegiyar yarinyar can? Uwar ta fa agidan su take aikatau.”

Alawiyyah ta ja ajiyar zuciya ta sauke,

“Gaskia da walakin goro cikin miya.”

“Gaskia dai Baba kisan nayi. Domin ba zata sabu’ba bindiga a ruwa.”

Hinde tafada tana tura d’aurin ta gaba. Jelar gashin dokin data kara a kanta ta bayyana. Bintalo ta mike a fusace tana huci, Zata fita Alawiyya ta ri’ko ta,

“Baba ina zaki a daren nan?”

“Haba ya za’ai a kawowa shegiyar can kayan da yafi naku? Ki duba fa ki gani sai data ga naku ba dad’ewa sannan tasan yadda tai aka kawo mata. Hmm sittin ta ubangiji akwai ‘kullalliya a kasa”

“Ki bari safiya tayi Baba, Gaskia Kawu ila yasamo mana mafita kawai.”

Ta karasa fada tana janyo hannun Bintalo suka xauna akan katifa.

“Zan same shi da safe muyi maganar. Shegiya da ido ‘kwalakwala irin na mayu.”

Haka dai su kai ta maganar Batoul da kayan da aka kawo mata. Sun raba dare suna zancen da yadda xasu samo mafita. Ranar dai su Alawiyya baccin bakin ciki su kayi. Bintalo kuwa bata runtsa ba, Tana ta saqawa da warewar yadda zata lalubo bakin zaren.

WASHE-GARI

Da safe na tashi ina mik’a. Baki na dauke da sunan ALLAH. Na so makara ma saboda ba sallah zanyi ba. Autar mu na kasa tana wanke-wanke Innar mu kuma tana tafasa ruwan bunu. Burushi na na dakko na tatsa makilin dinmu ‘dan nera ishirin ‘dinnan na leda. ‘Kasa na sauka na wanko baki na, Daki na shiga na rataye hijabi na a saman kofar mu. Rissinawa nayi ina gaida Innar mu,

“Innar mu ina kwana?!”

“Lapia Alhamdulillah uwata. Yanzu aka tashi kenan?”

Innar mu ta fada tana tsokana ta. Murmushi nai,

“Wallahi dake jiya bamu kwanta da wuri ba. Inna akwai abunda zan taya ki dashi?”

“A’a! Kinga ruwan shayi na dora. Ga biredi nan nasa auta tasiyo a shagon Kamalu. Ga sauran naman jia nan na ‘dumama shi.”

Motsa baki nai ina kada kai. Cike da jin dadi nace,

“Tab yau za muci dabge kenan.”

Daria Innar mu tayi. A lokacin autar mu ta shigo hannuwan ta dauke da dan kwandon wanke-wanken mu. Ta wanko su tas. Ajiye su tayi ta zauna a kusa dani,

“Yaya ina kwana?”

“Gashi nan a kwanon gaban ki.”

Daria mukai baki d’aya kafin na mike na janyo kwalin wayar jiya. Jujjuya ta na shiga yi,

“Dama ace muna da wuta sai na jona kawai anan.”

Na fada ina ‘kasa da kai na, Rai na yana sake tafarfasa. Idan har natuno wai kaf gidan mu dakin mu ne kawai babu wutar lantar ki. Haka kawai akan abu kalilan su Kawu ila suka cuzgune mana wayar dake kawo mana wutar a daki. Ajiyar zuciya naja na sauke, Da alamun na dade ina tunani. Domin Innar mu magana tai tamin ganin yadda autar mu ke jijjiga kafata tana kallon Innar mu.

“Lapiar ki kuwa?”

“Ina tunani ne Innar mu.”

“kankanuwar ki dake? Ki dena kinji?”

“Toh Innar mu..”

“Toh ku matso kusa muci abinci.”

Matsowa mu kai kusa da Innar mu muka fara karin kumallo. Wai yau ni Batoul dasu Innar mu muke karyawar safe da biredi da kaza? Ga ruwan bunu da sukari. Kai wayyo dadi. Muna ci muna lumshe idanu, Yaushe rabon da mu gana da biredi ga kuma kaza? Tab dadi kan dadi. Ga ruwan shayi da sukari. Kai garin dadi na nesa! Ko da muka gama cin abincin tashi nai na shiga kaude-kaude, Na gyara ko’ina tsaf. Dan zanin gadon mu na karkade na shimfide shamilalliyar katifar mu dashi. Na share ko’ina sannan na kunna dan turaren tsinke mai kamshi. Tuni dakin yai ‘das dashi yana kyalli. Innar mu ta mike ta dau kwandon soson wankan mu ta sauka kasa yin wanka, Tana ta sauri zata tafi gidan da take aikatau, Wato gidan su Haysam.

Zabga tagumi nai ina tunanin abunda zamu dafa. Mun tashi ba ko kwandala a gidan. Ajiyar zuciya naja na sauke a hankali nake furta,

“Ya ALLAH kai ka iya kai zakai ya Allah, Kai ne mamallakin kowa da komai. Allah kasa mu futa daga kuncin wannan sarqaqiyar rayuwar. Shin meyasa yan uwan mahaifin mu na jini suka tsane mu? Meyasa suke kyamatar mu kamar ba tsatson dan uwansu ba? Ya ALLAH ka kawo karshen wannan sarqaqiyar. Ameeeen!”

Na karasa Ina mai shafawa a fuska ta. A dai-dai lokacin Innar mu ta shigo tanata sauri. Ta ajiye kwandon sosan wankan mu, Mi’kewa nai don bata wuri ta shirya. Tsakar gidan mu na leka. Can karshen bango na hango Kawu Dawood yana bacci, Matar sa kuma ta gama shiryawa ta fice nemo musu dan abunda zasu afa a baka. Girgiza kai nayi ‘kowa da abunda ya da me shi.’ Na furta ina komawa dakin mu. Innar mu ta gama kintsawa tsaf tana shafa dan turaren mu dake kan kwalla. Mace mai kamar maza kenan. Allah ya azurta mu, Na fada a zuciata.

“Innar mu har kin gama kintsawa?”

“Na gama uwata. Sai tafiya kawai, ALLAH yabamu albarkacin dake cikin wannan rana mai albarka Ameen.”

“Ameen.”

Na amsa mata ina janyo kwalin waya ta,

“Na kai chaji ko Innar mu?”

“Ya kunna injinne dan haru?”

“Gaskia kilan sai anjima.”

Na fada ina zaro ta a kwalin ta. Addua na tofe wayar da ita ina murmushi. Kamar wasa ina gwada kunnawa ta kunnu. Da chajin ta a cike sannan akwai layi aciki, Da fara’a na daga kai ina dubar Innar mu dake gyara zaman hijabin ta ajikin ta,

“Kinga Innar mu acike take ma sannan akwai layi aciki.”

“Ah Masha Allah! Toh a tsofe lapia uwata. Allah yasa rai aka yiwa.”

“Ameen! Innar mu ko na kira Yayan mu? don naga akwai kudin kira aciki.”

Sa hannun ta tai akan leben ta tanamin alamun nai shiru. Saurin daga kai nayi alamun ‘nagane’. Tunawa da nai da babu wanda yasan muna magana da shi a boye. Wayar Innar mu ma da aka sace shi yabamu muka bata, Lokacin munje hutu shema shekaru biyu baya nida autar mu . Yanzu kuwa yana kano neman kudi da karatu. Ko ya kammala yanzu oho? Sanda mu kai magana dashi ta waya karshe yace yafara karatu a sa’adatu rimi kwalejin ilimi dake kano. Dake dama sanda yana nan a babban aji biyu ya dena zuwa. Suna zuwa kano kuwa yayi SSCE ya cike

kwaleji ya fara zuwa. Ko me yake karanta oho? Nasan dai suna yar buga buga da sana’ar dinkin huluna samfurin zanna-bukar su siyarwa attajirai, Sannan suna kiwon shanun Baffa Ardo, Suna kuma yin leburanci a kasuwar singa dake kano duk karshen sati.

“Me za’a dafa ne Innar mu?”

Na tanbayeta ina kauda wancen zancen. Kullin zanin ta naga ta sunce ta ciro naira dari da goma, Su kenan da ita duk sun dunkule ta mikomin,

“Ki bawa auta ta siyo kananzir na goma, Gawayin hamsin. Sittin kenan ko?”

Gyada kai nayi, Na saka hannu biyu na karbi kudin.

“Yauwa sai ta had’o da manjan talatin. Tumatir da albasan ashirin. Naga akwai tsaki, Sai ki ruda kiyi danmalele. Da daddare In Sha ALLAHU ba zamu rasa abunda zamu ci ba.”

“In Sha Allah! Toh Innar mu. Kila nima na biya na yiwa matar soja sangas dan abunda na samo sai a hada asai wani abun.”

“Toh! Allah ya rufa asiri. Bari na.....”

Bata k’arasaba sakamakon bubbuga kofar dakin mu da Kawu ila ya shiga yi ba kakkautawa. Kofar har ta ballo dama ba kwari ne da ita ba. Innar mu ta sa hannu biyu ta dafe kirjin ta. Nima na zuba ido ina bin su da kallon karin bayani shi da Bintalo dake bayan sa tana taunar cingom tamkar tsohuwar karuwa. Da alamun koma meye sun gama shirya shi. Cincirundon yan gidan mu duk sun firfito suna leken ganin yadda zata kaya,

“Zo nan ku! Ku maimata abinda idanuwan ku suka gane muku jia.”

Yusha’u da Bala suka futo daga bayan Bintalo ni banma lura suna bayan ta ba sai yanzu. Ina ganin su na tuno sun ga sanda Haysam ya riko kasan mayafi na. Yusha’u ya dashe jajayen hakoran sa wanda suka rine saboda rashin tsafta sai hamamin wari suke,

“Yasin shine nan ya riko hannun ta da mayafin ta..”

“Bangane ba?!”

Innar mu tafada cikin tsantsar tashin hankali. Kafafuwana da suka kasa rike gangar jiki na naja na zauna akan tukunya. Ina dafe kai na. Bala ya matso gaba cikin murya mai sauti ya shiga kwararo karya da gaskiya,

“Yasin atare su ke da Kaltume da Yaran gidan Alhaji Kabiru ya riko wata leda a hannun sa ya bawa kaltume ya bi bayan Batoul dake baya can, Sai...”

“Kuji tsoron ALLAH Bala.”

Na fad’awa su Bala da Yusha’u ina dafe kai na saboda ciwon daya faramin yana barazanar fadowa. Kawu ila ya dankara min harara. Bala ya cigaba da cewa,

“Toh shine sai ya riko hannun ta da mayafin ta..”

Ya karasa fada yana jujjuya idanuwa alamun hadin zancen karya. Bintalo ta saki guda,

“Ah toh sittin ta ubangiji daman nace akwai wata a kasa. Ashe lalubar ta yake.”

Innar mu ta kasa motsi tana binsu da kallo. Domin ita kanta tasan sharri akai min. Murmushin yake tayi ta gyara zaman hijabin ta,

“Sharri dai dan aike ne Bintalo, Batoul kuma ‘yar ku ce. Idan kunga dama ku yanka ta. Matsa na wuce.”

Matsawa Kawu ila yayi Innar mu ta wuce tana girgiza kai. Kawu ila ya ajiye bokitin sa daya taho dashi daga kasa ya zauna a kai yana sakutar baki, ya dube ni kamar kashi,

“Dan uban ki jikin sa kike bashi yake muku hidima?”

Girgiza kai na shiga yi, Idanuwana na fitar da ambaliyar hawaye,

“Kawu ila wallahi karya suke min. Na rantse da ALLAH bai taba min hannu ba.”

“Shegiya! Ki gayamin gaskia. Kafin na tashi na ci uban ki.”

“Kawu wallahi bai rik’emin hannu ba. Kawai dai ya riko kasan ma..”

Ban k’arasa ba Kawu ila ya sharara min mari. Tuni naga gilmawar wuta saboda tsabar zafi. Na kifa akan katifa, Kuka na shiga yi mai sauti wanda ka tsuma zuciyar duk wanda ya saurara, Innar mu dake sauka kasan bene tayi murmushi cikin daga murya yadda Kawu ila zai iya jiyo ta tace,

“Alhaki kwikwiyo me shi yaka biye, Muje zuwa.”

Tana gama fad’a ta karasa sauka tai ficewar ta. Kawu ila ya shiga zubamin fada ta inda yake shiga batanan yake fita ba,

“Y’ar iska shegiyar yarinya. Wato abun kunya kike so ki janyo mana kenan? An samo ku ta hanyar haka shine kema zaki jajibo mana? Zaki dena rusgar kukan nan ko sai na lakada miki na jaki?”

A hankali na rage sautin kuka na, Ina jan majina saboda murar data kamani lokaci daya, hannu na nasa na shiga goge hawaye na ina nanata,

“Innalillahi wa’inna ilaihir raji’un!”

“Dan ubanki ina wayar daya baki?”

Cikin kuka na cusa wayar acikin rigata. Ganin zai ‘kwace ta,

“Gatacan Innar mu ta tafi mayar masa.”

Kad’a kai yayi yana kwafa. Bintalo ta shiga sakin gud’a a karo na ba adadi. Cikin shewa tace,

“A hayye! Dama da walakin wallahi. Sittin ta ubangiji da ganin yawan kayan nan kasan ba banza ba. Ashe sai da ya rabe ki sannan ya baki. Y’ar iska.”

“Allah ka sakamin. Allah kana gani. Allah kamana sakayya da wa’innan bayin naka azzalumai.”

Na shiga fada a hankali ina goge hawayen fuska ta, Kawu ila ya mike tsaye yana karkada hannuwa,

“Karki bari na sake jin ko ganin haka ta faru. Sannan karya kara tako kafar sa yazo gidan nan dan wallahi zan mugun sab’a miki. Shashasha, Sakarai. Daga ganin su Alawiyya sunzo da kayan dadi shine zaki bada jikin ki don a baki? Kaga karamar y’ar iskar yarinya. Ina ke Ina tsatson gidan Alhaji Kabeeru Mai Wafa? Ki cigaba dasa ido ko bakin ciki akan abunda aka basu. Wallahi zaki nadamar sani na a rayuwar ki. Da ido tsuru-tsuru kamar na mayu.”

Yana gama fad’a ya sauka kasa, sauran na biye dashi. Bintalo kuma ta shiga yada magana tana zunden Usaiba dake yiwa Talatuwa kitso. Ci kanki batace mata ba. Da alamun tama ta take yi. Mikewa nai na debi ruwa na shafa a fuska ta. Inda ya mare ni harya kumbura da shatin hannun sa. Autar mu dake rakub’e a gefe ta rungume ni tana bani hak’uri. Murmushi nai kawai ina goge mata hawayen dake zuba a idanun ta,

“Ungo rik’e ki siyo kananzir na goma, Gawayin hamsin. Sai manjan talatin da tumatir da albasa na ashirin. Kiyi sauri ki dawo karki zauna wasa.”

Gyada ka tayi ta karb’a da gudu ta fice. Murhun mu na gyara yadda data kawo zan dora komai. Na d’akko tsakin ina tsince shi, Zuciata cunkushe da bakin cikin rayuwar gidan mu. IN SHA ALLAH zan tambayi Innar mu ko da akwai dalilin da yasanya aka tsane mu haka. Ba jimawa autar mu ta kawo komai. Cikin kankanin lokaci na kammala mana. Na zuba na Innar mu a yar kular abincin mu. Mu kuma na sa mana a filet muka ci. Ina gamawa na fuce makwabtan mu can gidan matar soja don yi mata sangas (some gaps) Mun jima ana mata dake ‘kanana ne. Sai bayan magriba na koma gidah, Lokacin Innar mu harta dawo. Na mata sannu da zuwa hade da ciro dari biyun kud’in sangas na mika mata,

“Gashi Innar mu.”

“Toh uwata! Angode Allah yayi albarka. Sai asiyo wani abun aci ko?”

“Eh mai sauk’in dafawa ba.”

“Toh taliya za’a siyo kenan? Amma fa ba mai sai dan kad’an Innar mu.”

Innar mu ta dafe habar ta tana tunanin abinda za’a siyo. Taja ajiyar zucia ta sauke,

“Yanzu idan akace a siyo taliya ma kudin man a zaune yake da kayan miya. Gaushin ma ya kare ko?”

“Eh Innar mu”

Na bata amsa ina matse hawayen dake neman zubo min.

“Dan Allah ayi y’ar kanannidaddiya (Indomie)kawai.”

Autar mu tafada tana murna. Innar mu tai murmushi,

“Abincin yara zaki ce. Toh ita nawa take?”

“Nera ashirin ce Innar mu.”

Autar mu ta fada cike da jin da’di. Innar mu ta mikomin dari biyun. Na karb’a ina zura hijabi na. Autar mu harta fice tana murna.

“Ta nawa zamu siyo ne?”

“Asiyo ta dari ko? Da safe sauran darin ayi karin kumallo da ita.”

“Toh Innar mu sai mun dawo.”

“Allah ya dawo daku lapia.”

“Amin..”

Ficewa mu kai ni da autar mu. Shagon Gali muka je, Yana tsaye yana kulla gishiri a leda. Yana ganin mu ya dashare baki, Hade rai nai saboda banason raini. Muna aji biyar a firamare ya rubuto min leta wai so na yake. Ni da shi bansan wanda ya girmi wani ba. Amma tsabar cika ido wai ni yake so.

“Bamu Indomie guda biyar..”

Dakkowa yai ya zuba a leda yana mikomin,

“Gashi aunty na.”

Karba nayi ina cuno baki na domin nasan da biyu ya fa’di haka. Biskit ya debo yana mik’awa Autar mu. Girgiza kai tayi tak’i k’arba domin Innar mu ta hana ta kar’bar abun hannun mutane. Hannun sa yasa zai riko nata nai saurin janye ta ina zabga masa harara,

“Akan wane dalilin zaka bata biskit ba d’aya ba ba biyu ba.?”

Ina karasa fada na zabga masa harara. Ina jan hannun Autar mu muka fice ganin yadda yake kallon ta yana murmushi yana wani tande baki. Tsaki naja na sauke..Mtscew’

“Dan iska, Sai kace maye.”

“Yaya menene?”

“Babu komai! Kar ki kara zuwa shagon Gali siyo abu. Ko ya kiraki karki je ke bama shi kadai ba da sauran mutane. Kina jina?”

“Eh Yaya.”

Gida muka shige. Innar mu na kishingid’e tana jin rediyo. Sannu da zuwa tai mana ta cigaba da sauraron shirin da take. Gaushin na fifita dake da dan sauron wutar tuni ruwan kai ya tafasa na zuba indomien. Cikin kankanin lokaci na gama na juye mana a tire. Hannuwa muka wanke muka fara ci. Tas muka cinye, Autar mu kuwa hadda sude tiren. Na tattare kwanukan na sauka na wanko su tas. Na tashi autar mu data fara gyan-gyadi na kai ta tayo fitsari. Muna dawowa kuwa ta bingere tafara bacci. Matsawa kusa da Innar mu nayi ina matsa mata kafafu a hankali kai na na kasa,

“Innar mu...”

“Na’am Uwa ta.”

“Innar mu kiyi hak’uri dan ALLAH. Shin akwai dalilin da yasan ya aka tsane mu a gidan nan? Cin kashin da ake mana yayi yawa Innar mu. Na rokeki ki, Dan ALLAH Innar mu... Nagaji ne, Zuciya ta tana *ZATON* wani boyayyen lamari. Dan ALLAH Innar mu ki gayamin akwai dalilin da yasa basa son mu ?A matsayin mu na yayan dan uwan su na jini?”

Ajiyar zuciya Innar mu ta sauke. A sanyaye ta dago daga kishingid’en data ke. Cikin wata irin murya mai wahalar fasaltawa ta fara magana,

“Toh uwata kinyi magana. Wadda dama nasan komai daren da ‘dewa wannan ranar zata zo. Kamar yadda wannan yaron (Najibu) shima ya nemi sanin haka a shekarun baya. Itama kuma auta da Lokaci yayi idan har ina raye zan sanar mata. Idan kuma rai yayi halin sa toh na rokeku daku sanar da ita. Idan kuma komai ya dedeta kafin lokacin hakan falillahil hamdu. Haka akeso dama, Kina jina ko?”

D’aga kai nayi ina sharce hawayen dake y’ar tsere a fuska ta. Innar mu ta kara nisawa kafin ta cigaba,

MAFARIN KOMAI:

___

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA SHA BIYU_*

*•**•*•**

MAFARIN KOMAI

“Kamar yadda kuka taso kuka ji sunan mahaifina Malam Rabi’u Shema. Ya kasance yana da mata biyu. Mahaifiyar mu kinsan sunan ta kika ci, Muna kiran ta da Inno. Itace kuma matar mahaifin mu ta farko. Sai matar sa ta biyu Iyalluwa. Mu bakwai ne duka ‘yayan baban mu. A b’angaren mahaifiyar mu mu hudu ne. Yayan mu Abdullahi shine ‘dan fari kaf gidan mu, Sai Yayar mu Halimatu. Sai ni dake mabiyar ta, Sai dan autan mu Baffajo wanda yaci sunan Baffa Ardo kawun mu. Iyalluwa kuma nada ‘yaya uku: Bello, Yafendo da kuma Usmanu,

“Mahaifin mu kafin rasuwar sa ya kasance manomi ne, Kuma shine mai bada shawarar Mai gari. Mai garin yankin namu kuma yayan mahaifin mu ne. Uba suka hada, Uwa kuma Kowa da tasa. Shi mahaifin mu d’akin su d’aya dasu Baffa Ardo. Mahaifiyata wadda kikaci sunan ta kafin rasuwar ta, Ta kasance tana sana’ar saye da sayar wa tana kuma yin kosai da koko, Babu lefi gidan mu ana zaman lapia da kaunar juna. Kowannen mu yana bin nagaba dashi. Akwai biyayya gaskia,

“Asalin kakannin kakannin mu fulani ne na jaub’awa. Kuma ance Sheman ma zuwa kakannin mu su kai, Ma’ana tsatson mu daga wani yanki suka taso sukazo Shema suka kafa ahalin su. Mahaifin ku kafin rasuwar sa ya had’u da ni ne abisa tashi da suke yi shida yan uwan sa. Ma’ana suje wannan gari su kafa kasuwancin su idan rani tayi su koma wani garin su kara yin wani kasuwancin. Lokacin da suka zo Shema a wajen mai gari suka sauka kafin mahaifin mu ya nema musu wajen da zasu zauna. Anan shak’uwa mai k’arfi ta shiga tsakanin mahaifina da naku. Saboda

yafi sauran yan uwan sa sauk’in kai da son jama’a. Hakan yasanya yan gidan mu ke son sa. Aka dauke shi tamkar ‘da. Har sai da takai ta kawo an ajiye masa kwanon abinci a gidan mu. Safe, rana, dare sau uku cass ake bashi abinci. Har yakai ya janyo abokan kasuwancin su suna zuwa suyi ma inno d’inmu cinikin koko da kosan da take na siyarwa,

“kafin a baka auren d’aya daga cikin tsatson mu sai an gudanar da wasu al’adu kafin a yadda a baka ‘dayan mu. Mahaifin ku ALLAH ya dasa masa soyayya ta a zuciar sa. Tun ina d’aukar sa a matsayin yaya na har na dawo nima na fara son sa. Muka fara soyayya cikin so da shakuwar juna. Bazan manta ba a lokacin yan uwan sa sun kyamaci ne a matsayin wacce yake so. Ganin daga k’auye nake kuma mu ba masu rufin asiri bane. Al'adar Shadi na daga cikin al'adun mu da suka shahara. A duk shekara muna taruwa domin gudanar da gagarumar gasar a kowanne rassa na arewacin Nijeriya. Mun kulla soyayya dashi har ta kai yaje wa da mahaifin mu zancen. Saboda kaunar da mahaifin mu ke yi masa shida Baffa Ardo da Baffa mai gari. Hakan yasanya kawai aka bashi ni batare da ya gudanar da al’adun da muke yi ba, Mai gari yayi shela kan ya bada aure na ga wani da yayiwa alqawari shekarun baya. Ba ajima ba kuwa aka kawo goron aure na aka sanya rana. Babu dogon zance akayi biki. Alokacin mahaifin ku sun sayi wannan gidan da muke ciki,

“A shekara d’aya akai bikin mu da sauran ‘yayan baffanin mu. Zagayowar wata shekarar duk suka hayayyafa ni kuwa ban taba batan wata ba. Mun zaga ko’ina ance lapia ta lau haka ma shi mahaifin ku, Haihuwar ce dai ALLAH be kawo ba. Daga baya mahaifiyar mahaifin ku ALLAH yai mata rasuwa dama tuni mahaifin su ya rasu shima. Tun daga lokacin yan uwan mahaifin ku wutar ki na tak’ara ruruwa a zukatan su. Sun tsane ni tsana mai tsanani idan muka cire Aminatu da Dawooda shi dama bai cika magana ba. Dangin mahaifin ku su kai ta kananan maganganu kan ni juya ce bana haihuwa ga matan yan uwan sa nan da aka samu a lalle tare sun hayayyafa. Wato Usaiba matar Ishaq da ummita marar ilyasu. A tare suka haihu d’aya da rana d’aya da yamma. Larai da safe Usaiba ta haife ta, Mariya kuma da Yamma aka haife ta. Makirci da manakisa babu wanda ba a shiryamun a gidan nan Allah ne kawai yake kare ni. Har ta kai an hadamun wani tuggu wanda hakan yai sanadiyyar komawata gidah. Sabuwar shekarar da muka shiga aka tafka mana rasuwa, Baffan mu ya rasu da wata biyu inno dinmu ta rasu itama bayan wata biyar kuma iyalluwa ta rasu. Hak’ik’a mun shiga matsatsi da kuncin rayuwa, wa zan kai wa kukana? Wadanda zasu sharemun hawaye na duk Allah ya karbi rayukan su. Ban koma gidah ba sai bayan watanni biyar, Na koma najj wani sabon lamarin kuma,

“Mahaifin ku an bashi auren yar kanwar kakan sa dake kauyen kode ta jihar kano kauyen lahadin makole. Naci kuka kwarai har sai da yayar mahaifin ku tazo daga

kaduna gidan aurenta ta kwantar mun da hankali kan cewar bawai dan bana haihuwa bane zai auro ta. A’a kawai dai rufa mata asiri zai yi ita wadda zai auren ya kuma kara karfin zumuncin su. Shi da ita sun bani baki sosai haka dai na hakura ya karo auren. Tazo ta tare, kullum burin ta shine had’ani rigima da mahaifin ku, Tsegumi, Gulma da hassada ciki harda makirci babu wanda bata yi mun. Shekarar farko ta haihu ta samu diya mace wato yayar ku zabbau dake aure a kod’e. Na sha bakaken maganganu daga kawunnin ku. Na rufe kunnuwa na cigaba da zaman aure na. Sai bayan shekaru biyu zama yaki da’di, Baffa Ardo yasa bello ya d’akko ni ya kai ni gidah cikin ikon Allah ina komawa gidah da wata d’aya da rabi na fara wani irin ciwon ciki komai na ci sai na amayar ana min gwaji akace ciki ne. Da akai aike aka fadawa mahaifin ku kwarai yayi murna a daren yataho Shema. Amma yan uwan sa kawunnin ku kenan sukace basu yadda ba lalle ba cikin sa bane. Dakyar dai da yardar ALLAH na dawo gidan nan. Ai kuwa ni da wannan yaron munsha muzgunawar rayuwa, Akai ta shegan ta shi ana aibata mu suna ware shi acikin yara ana kyamatar sa,

“Allah ne ka’dai ya raya shi da kuma kwanan sa agaba. Ba don haka ba kala kalar muguntar da aka yiyyi masa da mai karar kwanane da yara su….”

Innar mu na kaiwa nan tayi jimm tana jinjina kanta, Siraren hawaye suka shiga reto a kyakkyawar fuskar ta. Cikin muryar rarrashi na shiga bata hak’uri,

“Kiyi hak’uri Innar mu. In sha Allah komai ya kusa zuwa karshe, ALLAH zai inganta rayuwar mu muma da yardar Allah.”

“Ameen.”

Innar mu tafada tana sharce majinar da ke tsiyaya a hancin ta. Saboda tsabar kukan da take yi tuni mura ta kamata. Ajiyar zuciya taja ta sauke tacigaba da cewa,

“Tun bayar haihuwar wannan yaron ban sake wata haihuwar ba har Bintalo ta sake haihuwa inda ta haifi Alawiyya, Nan ma dangin mahaifin ku su ka kara yo min caa. Daga baya cikin ikon ubangiji bayan haihuwar Alawiyya da shekaru biyu da wata d’aya lokacin mahaifin ku sunje tashi Bintalo ta sake haihuwa inda ta haifi Hinde. Ni kuma cikin ikon ALLAH na je Shema bikin Atuwa yar Baffa Ardo, A cikin watan shekarar ala fara fadan musulmi da arna dinnan. Ashe da shigar ciki, Ni kuma haka

Allah ya qaddara min samun ku. Har ciki ya tsufa ba hanyar sanarwa da yan uwan mahaifin ku. Nan Allah ya albarkace ni da samun ki, Baffa Ardo shi yayi miki huduba yasanya miki sunan mahaifiyar mu. Uwata in k'ark'are miki zance dai sai aka sake sheganta min ke akaro na biyu bayan na wannan yaron. Mahaifin ku yayi mai yiwuwa don tabbatar mu su kudin jinin sa ne, Fafur sun ki yadda. Ban kara wata haihuwar ba sai bayan shekaru bakwai. Cikin Aminatu auta ne kawai na haife shi anan gidan. Ita dinma ca su kai basu yadda da shi ba. Mahaifin ku da Aminatu sune kadai su kai mai yiwuwa don ganin sun nusar dasu cewar kuma 'ya'ya ne kamar kowa amma hakan yaci tura. Har ALLAH ya karbi ran mahaifin ku a har kullum addu'ar sa da cikar burin sa baya wuce yaga ya cire mummunan *ZATON* da suke akan ku ba. Ni kuma banason na kwashe ku na tafi da ku Shema, Kinga zanbar baya da k'ura kenan, Domin har gaban abadan mutan garin nan zasu yadda da *ZATON* da ake muku. Fatana a har kullum shine ALLAH ya ganar da ahalin gidan nan su sakko dagga *IGIYAR ZATON* da suke muku. Ai dole dai idan muna tare dasu su maye muku gurbin mahaifin ku. Amma da na tafi daku, duniya zata fara yamadidi da kiran ku 'ya'yan mace. Allah dai ya samu dace duniya da lahira. Ameen!"

"Ameen Innar mu.. Hak'ik'a labarin nan ya dimauta ni, kuma an sha gwagwarmaya dake kin tsaya tsayin daka akan mu. Allah ya warware wannan sarqaqiyar yasa su gane turbar gaskiya. Ameen."

Haka dai mu kai ta zantuttuka da Innar mu, Sai da dare yaja sosai tukun sannan muka kwanta, Zuciata cike take fal da labarin mu da Innar mu ta bani.

WASHE GARI

Washe gari da asuba da kyar na farka, saboda dad'ewar da mukayi da Innar mu akan tarihinsu da take bani. Ina mutstsike idanuwa tare da murzasu da hannayena guda biyu saboda kaykyayin da suke min, a haka na mike tsaye, wata irin hamma na saki kai kace yanzu nake shirin kwanciya baccin, amma ba komai bane sai irin na yarda jikina yayi wani irin tsami. Bokiti na d'auka da ragowar ruwa a ciki saboda naje na tsarkake jikina, dan naji duk na b'aci daga kasa na, kasan cewar bana amfani da pad sai d'an tsimma saboda rashin kud'in siyan kunzugun. Innar mu na kalla wacce ke zaune tana lazimi akan tabarma tana gyangyad'i, na saki d'an murmushi tare da girgiza kai ina jin kaunar mahaifiyar tamu har cikin zuciya ta.

Fitowa nayi ina kallon lungu da sako na saman benan ko zanga wani, ganin babu kowa yasa na dan lek'a k'asan benan. Da sauri na k'arasa sauka k'asan saboda hango usaiba na zuba ruwa a buta, wanda da alama ban d'akin take son zuwa itama, zan iya barinta ta shiga, sai dai wannan karon nima sauri nake yi domin idan na bari ta shiga sai randa hali yayi saboda dad'ewar da take yi a ban d'aki idan ta shiga. Ina jiyo ta tana mita daga bakin k'ofar, ni dai ban ce komai ba har na gamana fito sannan ita kuma ta shiga.

Sai dana gama shiryawa tsab, sannan na tashi na d'ebi wankin mu duka, K’asa na sauka da sabulun wanki na shiga dirje mana kayan ina sab'ewa a ruwan d'auraya, k'ugu na sai radad’i yake min amman haka na karasa wankin dakyar. A inda zan shanya su na fara tunani ga masifar 'yan gidan da suke yinta babu gaira babu dalili. Shanya su nai a k'afar bene da jikin bangon benen tsakiya, na nufi sama da bokitan da nayi amfani dasu. Ina shiga d'aki, na tarar da Innar mu da autar mu sun cure guri guda Autar mu tayi bacci akan taburmar da tai sallah Innar mu kuma ta kudundine da hijabin ta. Idanun ta sun kad’a sunyi jawur. Da alamun zazza’bi ne ya rufeta daren jiya..

“Innar mu ina kwana?! Subhanallahi! Innar mu jikin ne? Sannu ya jikin naki?”

“Lapia Alhamdulillah uwata.. Na tashi ai naga bakyanan ina kikaje ne?”

“Wanki nai Innar mu. Naga kayan sun taru da yawa. Zazzabin ne?”

Na karasa fada ina taba kafafunta dake rawar sanyi. Jikin yai ‘kau. Ya dau zafi sosai. Daurewa tai ina hankalce da ita. Ta rik’e hab’a tana jinjina kai,

“Du wannan wankin ke kadai? Ca nai fa ki bari zamu yi tare. Ai yayi miki yawa ke kadai.”

“Babu komai Innar mu. Na kammala ma harna shanya su.”

“Masha Allah! Toh angode ALLAH yayi miki albarka.”

“Ameen Innar mu! Allah ya azurta mu muma mu dinga bayarwa ana wanko mana. Ko mu sai injin wanki irin na gidan matar soja.”

Dan murmushi Innar mu tayi. Tana rintse idanu cikin ciwo.

Gabaki d'aya jikinta ya sanyaya daka ganta kasan cewar akwai abinda yake damunta, wanda ba wai a iya fuskarta yake ba, a'ah har can cikin zuciyarta take jin ciwon. Bata iya kallo na ba, muryarta a sanyaye tace dani.

“Babu wani abun da zaku iya sarrafawa kuci yanzu, kuyi hakuri ku daure har naje gidan aiki naga ko ALLAH zai sa na samo muku koda k'anzo ne kuci.”

Na kalleta da mamaki a fuskata jin tana ambatar fita, bayan jikinta kamar garwashin wuta yake. Duk da cewar wankin da nayi ya kuma sanya min wata azababbiyar yunwa, hakan hakan bai zai sa na bar mahaifiyata da take halin rashin lafiya ta fita aikin wahala ba. Na sanyaya murya dan na kwantar mata da hankalinta ina cewa.

“A'ah Innar mu kiyi kwanciyarki, keda baki da lafiya ya za'ai kije aiki.”

“Dole ne naje na nemo muku abinda zakuci uwata, idan ban fita na nemo ba, waye zai kula ku dan bakuci ba a cikin gidan nan?”

“Innar mu ki kwanta, bari naje gidan ruwa naga ko ALLAH zai sa na samu wacce zan yiwa kitso, abinda na samo sai muyi amfani dashi”

Na gama fad'a ina sake kai hannuna jikin k'afar Innar mu ina sake jin yanayin jikin nata, gidan ruwan da nake fad'a zanje can ne bayan gidan su Haysam, inda ake buga musu ruwan leda wato (pure water) na bada sari, a jiki akwai wani gidan mai d'auke da mata uku, nan naso zuwa ko ALLAH zai sanya suce ayi musu kitson, amman Innar mu tace.

“Uwata kiyi zamanki, hurumin samar mana da abinci baya wuyanki yana wuyana. Ki zauna gurin 'yar uwarki zanje na dawo yanzu, ai zan iya zuwa.”

Babu yadda na iya dole na rabu da ita, ina ji ina gani ta mik'e da kyar tana rintsa ido alamun kanta yana tsananin bugawa. Tashi nayi na d'akko mata hijabi ta karba tasa sannan ta yi min sallama ta fita daga cikin d'akin namu. Ina jiyo lokacin da kawu ila yake ce mata.

“Toh garin ya waye za'a tafi yawan ta zubar ko? AlLLAH ya kiyaye ba uwar ba 'ya'yan tur da irinku.”

Banji muryar Innar mu ba, hakan ne ya tabbatar min da cewar bata kulashi ba, saboda idan da sabo wannan kalaman sun riga sun zauna a zuciyar Innar mu. Na mik'e tare da fara gyara d'akin namu, ina gamawa na koma na kwanta tare da zaro wayar da Haysam ya bani sai faman kallonta nake yi.

“Ke Batoul! Batoul.!”

Na jiyo muryar Bintalo daga kasan bene tana ta kwad'a min kira kamar wacce na karbarwa bashi. Kamar karnaje saboda nasan yanzu kasan cike yake da 'yan gidan, kuma idan har na sauka duk wani wulak'anci a gabansu za'a yi min shi.

“Ko bazaki zo bane ni na zo?”

Na sake jiyo muryar Bintalo, ko yaranta bata iya yiwa wannan kiran da take yi min. Na juya tare da maida wayar inda nake b'oyewa na aje, sannan na fito ina mistsike ido kamar a lokacin ne na tashi daga bacci. Da hannunta take mun alamun na sakko, na kalli mutanen dake gurin kowa na harkar gabansa, sannan na sauka kamar wacce babu kashi a jikin ta.

“Kaga sarauniyar mata, ana tafiya kamar yar gidan wani sarkin.”

Cewar Bintalo tana tsaye ta rik'e kugu jira kawai take na gama sakkowa, cikin rai na nayi murmushi domin ba zan bari wata kalma tasu ta bata min rai ba a yau.

“Kawu Dawood ina kwana?”

Na gaida shi kasan cewar yana zaune ne a kafar bene yana asuwaki, ya amsa min ba tare da ya kalleni ba, don shi bai fiye yin doguwar magana ba sai dai duk abinda ake yi yana ji tankawa ne da kuma kallo ba zai yiwa abin ba. Na gaida duk wad'an da suka cancanci gaisuwa a gurin, wasu sun amsa min yayin da wasu suka share ni tamkar ba dasu nake ba, saboda kawai basu dauke ni a bakin komai ba.

“Kitso nake son kiyi min mai kyau, zanje biki da anjima.”

Wani irin bakin ciki ya tokare a wuya na jin abinda take son nayi mata, babu wani lallami ko daddad'ar kalma, a'a cikin gadara da bada umarni haka take min kai kace itace tayi nakuda ta. Shirun da taji nayi mata ne ya sake bata damar yin magana a karo na uku cewar.

“Ko ta hana ki yi mana ne iye?!”

Nasan Innar mu take nufi, dan haka nayi saurin girgiza kai alamar bata hana ba, sai dai fuskata a cunkushe take saboda na tsani yiwa matan gidanu kitso domin kana yi kana shan takura gashi ba godiya bare a kaiga bani kudi. Na kalli kawu ila dake can gefe yana cin dumamen tuwo, kai da kaganshi kasan ci kawai yake amman nutsuwarshi da sauraronshi suna kan duk wani wanda yake magana a tsakar gidan. Na had'iye wani bakin yawu saboda tsabar fargabar abinda zance.

“Kai na ne yake sara min tun kafin na gama wanki, ko zaki bari anjima kafin ki tafi din sai na lallab'e miki?”

“Iyeeee! Batoul ni zaki yiwa kiwa? Nace miki anjima zanje bikin shine zaki ce dani sai anjimar zaki lallab'e min? Toh yanzu nake so wallahi, kodan mu kin raina mu, shine bakya son yi mana kitso? amman ai kan gaytumarki ai kullum cikin yi mata kike yi, idan kuma ba zaki yi ba sanar min.”

“Zan yi miki mana Babah, a kawo kibiyar da kum d'in.”

Dariya ta saki tare da sakin gud'a Ayirrrrrrr tana bugun cinyarta, cikin wata irin shewa taja hannuna muka nufi k'ofar d'akin na zauna akan kujera 'yar tsuguno. Alawiyya ce ta fito tare da cillo min kum din tana cewa.

“Kiyi mata da wannan banga kibiyar ba.”

D'auka nayi bance komai ba, har Bintalo ta zauna a gabana, tana cire dankwalin naga gashin kan nan a harhad'e kamar gashin biri, gashi jawur babu ko d'igon baki a jiki. Yi mata na farayi duk kuwa da irin gajiyar nayi ga bakar yunwar da take sake ciwo ni. Muna farawa naga Innar mu ta dawo jikinta ya kuma saki, tana yin sallama ta haye sama na bita da idanuwa.

“Babah bari naje gurin Innar mu na dawo.”

Na fada ina saurin karasa mata wanda na kusa kaiwa dan naje na gano Innar mu, ta kuwa buka kasa da tafin hannunta tana yatsina fuska tace.

“Bafa zaki bar kujerar nan ba Batoul, har sai kin gama min kitson nan, eh salon ki tashi ku shiga d'aki kuyi kuskus d'insu har lokacin tafiya ta yayi ki barni da rabin kai ko?”

Naji hawaye na shirin zubowa daga cikin idanuna, nayi ta kifta idanu har kwallar ta koma, na d'aga kai sama na hangi Autar mu tana kallo na, da alama ni take son kira amman tana tsoran jarabar Babah Bintalo. Ban tashi ba sai da na kammala mata, tun kafin ma na mike tsaye ita ta riga ni, na tabe baki nima naja kafafuwa na nayi sama, ALLAH ya temake ni har na bar wajan kawu ila bai kulani ba. A kwance na

tarar da ita ta lullub'e jikinta da hijabi fuskarta a ciki sai sauke ajiyar zuciya take. Nayi azamar karasawa inda take ina k'ok'arin bud'e fuskarta amman ta hanani.

“Innar mu har kin dawo?''”

Kai kawai ta iya d'aga min.

“Kinyi aikin ne?''

Ta girgiza min kai alamun a'a

“Sannu Innar mu, hajiyar su Haysam d'in ce tace ki dawo?”

Nan fa Innar mu tayi shiru, kafin daga bisani naji sautin kukanta yana fitowa. Hankali na ya sake tashi, na kuma kai hannu zan bud'e fuskarta ta sake hanawa.

“Kyale ni uwata, kuyi hakuri nasan dai kuna jin yunwa zuwa yanzu. Amman yau kam ban iya samo komai ba, kuyi hakuri.. Kuyi hakuri.”

Bansan menene yasa Innar mu kuka ba, amman zuciyata na raya min cewar anyi mata abinda ya tab'a ranta ba wai rashin abinda zamuci ne kadai yasa ta wannan kukan ba. Tsam na mike Na zari hijabi na ba tare da na sanar da ita ba Na fice, Autar mu na kallo na sai dai itama yau duk iya tambayarta bata tambayi inda zanje ba. Kasa na sauka da sauri nayi waje ina ta bankama sauri kai kace bashi aka ce naje na karbo.

Gidan Alhaji Kabeer Wafa na nufa, wato gidan su Haysam inda Innar mu take aiki. A harabar adana motoci na tsaya ina karewa gidan kallo wanda yaji shuke-shuke kamshi sai tashi yake yi. Ba wannan ne ya kawo ni ba, hakan yasa na nufi hanyar da zata sadani da ainahin cikin gida, naci karo da Rabi matar da take yi musu girki.

Gaida ita nayi kasan cewar ta sanni sanadin zuwan da muke yi da Innar mu kafin matar gidan ta hana zuwa damu nace da ita.

“Inna Rabi mai ya faru naga Innar mu ta koma gida da wuri? Ko Hajiya ta yafe mata aikin ne ganin bata da lafiya?”

Sai naga Inna Rabi ta fara waige-waige kafin daga bisani taja hannuna muka shige wani d'an korido, tana kallo na tace.

“Ahirr d'inki Batoul da zuwa jin abinda ya faru da mahaifiyar ki gidan nan, abinda nake son kiyi kawai shine, kije kice da Hajiyar kinzo kiyi aikin a madadin mahaifiyarki.”

Baki na a bud'e nake kallon ta, bata ce komai ba sai jinjina min kai da take yi alamun naje nayi abinda ta ce, ban kawo komai cikin zuciya ta ba, hakan yasa na shiga gidan baki na d'auke da sallama. A hakimce a parlour na tarar da mahaifiyar Haysam dashi kanshi a gefenta yana breakfast, kwanuka ne birjik a gaban shi da cup d'in tea a hannunsa alamun sha yake yi suna hira. Na had'iyi wani kakkauran yawu kafin na durkusa kasa ina gaida Hajiyar. Ta amsa min tana had'e rai bayan kuma lokacin da na shigo tararwa nayi tana ta dariya, shi kuwa ko bi takansa banyi ba na fara jeru bayani.

“Hajiya daman zuwa nayi amadadin Innar mu, zanyi mata aikin.”

Baki da hanci Haysam ya bud'e jin abinda yake tafe dani, ina kallansa ta gefen idanuna, najiyo muryar Hajiya tana cewa.....

••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😈□□😎😎😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SHAFI NA SHA UKU_*

•••

“Daga ina kenan? Wacece Innar ku?.”

Mamaki ne ya mamaye fuska ta, Jin tambayar da take min. Tana nufin batasan Innar mu ba kenan ko kuwa wulakanci ne nasu na masu kudi? Gaba d’aya baki na sai yayi nauyi, Na kasa furta mata kalma d’aya. Haysam dake kusa da ita duk ya dubibi ce da alamun shima ya rasa yadda zai yi. Cigaba da cin abincin ta tayi, Kallo na na mayar kan abincin da suke ci. Sai hadiyar yawu na dinga yi. Rai na ya biya ba kadan ba gashi yunwa sai addabar ciki na take yi. Cikina sai kukan yunwa yake. Nasa hannu na na dafe shamilallen ciki na da babu komai cikin sa tun abincin daren jia. Dagowa tayi ta dube ni tana karkada kafafu, Hannun ta rike da fok dauke da dankalin turawa da kwai, ‘Mak’ot’ na hadiye yawun daya tsayamin a makogaro. Da cokalin ta shiga nuna ni tana yamutsa fuska,

“Ko kece wadda ku kazo da mai wankin mu kwanaki?”

Jiki a sanyaye, Idanuwa na kawo ruwan hawaye na dube ta,

“Eh ni ce!”

“Ni fa gaskia nagaji da halin uwar ki. Yo tazo fa duk tayi yaushi a jeme kamar zata fa’di. Nace mata mu munsamu mai yi mana wanki da guga tun daga kauye aka dakko shi. Nace taje na sallame ta, Kudin aikin ta kuma zan bayar akawo mata, Amman shine ta turo ki?”

Ajiyar zucia naja na sauke, Ina mamakin yadda masu shi suke daukar kansu. Bayan duk takai ta kare dai a rami Iri d’aya za’a sa mu. Shin meye na takamar dan Allah ya azurta ta ka dinga wulak’anta na kasa da kai.? Na duba na hango yanxu idan nai fushi na tafi ba inda zan samo mana abincin da zamu ci. K’asa nai da kai na ganin yadda Haysam ya zubamin na mujiya,

“Kiyi hak’uri Hajja! Yau Innar mu tatashi ne babu lapia shi yasa. Idan da akwai abunda za’a miki yanzun sai nayi.”

“Masu aikin yanzu sai da tsaro, Yanzu mutum zai yi shekararriyar ajiya, Amman rana d’aya yan aiki sai su sace shi.”

Shiru nayi kai na a kasa ina mamakin maganar ta. Sai data dau lokaci kafin ta dube ni,

“Akwai kayan ciki na(undies) dina a daki ki wanke mun su, Sannan kar dai kiyi min ‘dan hali (sata) Domin ba zan lamunta ba. Biyo ni”

Mikewa tai ta fara hawa benen sama na bita a baya, Haysam sai ya zama tamkar mutum-mutumi domin tun sanda nazo ya tsaya da cin abinci yana kallo na. Wani tankamemen daki muka shiga, Tsayawa na fada muku tsaruwar sama bata lokaci ne. Komai yaji babu k’arya. Durowar dake shake da kaya ta bude, Sai da idanuwa na suka kusa fad’owa saboda ganin yadda take a hargitse. Kayan ta duk a dukunkune wasu akan wasu. Kasan durowar ta janyo, Kayan ciki ne kawai a ciki fal. Wando panties, Siket gajere, bireziyoyi fal sun nadi datti. Wandunan har da wanda jinin al’ada ya ‘bata duk akwai su. Da ‘kafa ta turo min su gabana tana nuna min bandakin dake cikin dakin da hannu,

“Ga bandakin nan, Akwai ruwa da komai aciki, Ki wanke su sosai su wanku yanzu.”

“Toh hajia”

Na fada ina durkusawa hade da dibar kayan a kasa, Ita kuma ta sauka tana wake-wake. Ciki na sai ‘karar yunwa yake yi. K’irjina kuwa har wani zafi yake yi min. Da alamun olsa tace zata tashi domin dukkanin mu muna da ita sakamakon rashin samun ishasshen abinci da bama yi.

Bandakin na shiga, Dankari makari! Babu ce kawai babu. Gaba d’aya kai na sai ya juye, Domin ko na gwaggo Aminatu da nake ganin ya hadu bai kai rabin kwatan wannan ba. Kwamin wankan da wajen wanke hannun ma kadai abun kallo ne. Na dubi wajen kunna famfon na rasa. Na shiga kokarin bude shi na kasa. Gudun kar na lalata musu yasa na juya na sauka domin tambayar ta yadda ake yi, Haysam na kan kujera mai kallon matattakalar bene ya zuba ido, Hajian su kuma tana zaune akan kujera mai kallon tasa, Sake sunkuyar da kansa yai yana kallo na ‘kasa-k’asa. Kayan takaici! Na fada a zuciata ina ‘k’arasawa daga nesa na tsaya, Wani banzan kallo ta watsamin na ya haka? Cikin inda-inda na shiga nuna benen,

“Uhm wannan”

“Wannan me? Ya haka? Me kika aikatamin a daki?”

“Ba-ba komai! Dama famfon ne ban iya kunnawa ba.”

Dogon tsaki taja ta sauke tana yamutsa fuska. Da sauri Haysam ya mike yana sosa k’eya, kallon sa hajian tayi tana murmushi,

“Ina kuma zaka auta na?!”

“Umma sama zani na dan kwanta.”

“Toh dan kunnawa bagidajiyar nan famfon bata iya ba. Ko meye abun wahala oho?”

Kamar zai yi kuka haka yai rau-rau da idanu, Da alamun beji dad’in yadda ta kira ni ba. Haye saman benen yai cikin sauri, Nabi bayan sa a hankali ina nanata kalmar data kirani da ita. Ina shiga dakin na ganshi a tsaye ya harde hannuwa, Ya narkar da idanuwansa a kaina yana min wani shegen kallo. ‘Dan iska! na fada ina zura hannuwa na na dago hijabi na don karya kallemin na ALLAH ya isa. Cikin band’akin na shige bakina d’auke da addu’a’. Shigowa yayi yana murmushi.

“Ya zan kunna?”

Na tambaye shi, Domin so nake ya fice na karasa aikin gaba na. Matsowa yai kusa dani na ja baya.

“Matsoraciya!”

Ya fa’da yana kunnamin famfon. So nake ya fita amma yaki fita yaja baya yana harde hannuwan sa,

“Ba gaisuwa?”

Ya tambaye ni yana murmushi, Wani kallo na watsa masa na cigaba da tara ruwan wankin da zanyi a bokiti.

“Na zo na taya ki?”

Ya sake fada a karo na biyu yana matsowa wajen da zanyi wankin, cikin sauri na girgiza kai na.

“A’a Ya Haysam! Nagode.”

“Saura gaisuwa. Tunda sai da na roka.”

“Ina kwana?!”

“Alhamdulillah Mine! Lokaci yana ta tafiya fa baki gayamin matsayina ba. Ko kawai na fara zuwa.?”

“A’a Ya Haysam! Kawu nama yace na dakatar da kai tukun.”

Ware idanu yai yana kallo na cike da tsantsar mamaki,

“Meyasa? Shin nayi wani laifin?”

“A’ah!”

Na fada a sanyaye ina saka bireziyoyin a ruwa dan fara wanke su saboda yawanci farare ne kuma sunyi dauda. Kamar yayi kuka haka yayi rau-rau da idanu cikin rawar murya ya dube ni,

“Meyasa? Uhm? Mine? Kiyi magana dan Allah?”

Bansan meyasa ba kawai sai naji ya bani tausayi, Ina ya me son ka? Ajiyar zucia naja na sauke,

“Babu komai, Kawai dai yace sai nan gaba kadan.”

Na fadi hakan ina sharce gumin da nake yi. Jiki a sanyaye ya fice yana rufomin k’ofar. Sai da nayi wa kayan wankin nan wanki biyar biyar dauraya biyar biyar. Domin sun nad’i datti ga tsami dake tashi daga cikin su. Yar wayata dake mak’ale a zanina na zaro ina duba lokaci sha biyu saura kwata. Har yanzu bamu ci abincin safe ba. Lokaci d’aya innar mu da autar mu suka fadomin a rai. Ko awane yanayi suke.? Innar mu ba lapia ga autar mu zata tashi taga babu abinci. Duk da ba yau farau ba amman kwanakin nan muna samu mu ci mu sha babu laifi.

A bokiti na zuba su, Sun yi ‘kal dasu suna sheki. Fita nayi ina neman inda zan shanya su. Zaune Haysam yake hannun sa na dama yasa ya dafe kansa. Wata k’ofa na hango da alamun baranda ce dauke da abun shanya da dan abunda ake sawa yake rik’e su kada su fado. Shanya su nai bayan na karkade su. Kamar wadda kwai ya fashewa aciki haka na sauka kasan banbi takan mayen kallon da Haysam ke bina dashi ba. Hajia Husna na hakimce a doguwar kujera tana danna waya, durk’usa wa nayi daga nesa,

“Na gama Hajia.”

“Kin tabbata sun wanku?!”

“Eh na wanke sosai..”

“Toh shikenan zaki iya tafiya.”

Kasa mikewa nai. Domin idan na tafi na koma hannu biyu gidah me zamu ci? Ga Innar mu ba lapia zazzabi ya rufe ta. Kallo na tayi tana tabe baki,

“Akwai wani abunne?”

“Eh.. Abinci!”

“Ni zan baki abincin?”

Ta fada tana watsamin wani wulakantaccen kallo. Kada kai na nayi alamun a’a,

“Zan kai wa Innar mune na baro ta ba lapia.”

Siririn tsaki taja. Cikin dan daga murya ta shiga kwararo sunan Inna Rabi. Da azama inna rabin ta shigo ta dur’kusa cikin azama.

“Gani hajia.”

“Bawa yarinyar nan abincin nan.”

“Toh Hajia.”

“Mungode Allah ya kara bud’i.”

Bata ce uffan ba sai ma nuni da tayi min da hannu alamar naje kawai. Ina jiyo takun Haysam daga kafar bene yana sakkowa,

“Sai ina kuma auta?”

“Zan rage gashin kai na ne.”

“Adawo lapia. An gama maka soup din fa. Ba yanzun zaka ci ba?”

“Eh Ummah sai na dawo.”

Ficewa nayi nabi bayan Inna Rabi shi kuma ya fita daga gidan. Kitchen muka shiga. Sai kamshin tafashen nama yake, Ina rakube ni dai a gefen kofa. Ina kallon Inna Rabi tana kalle kalle, Kafin ta juye wani abinci acikin leda baka ta mikomin, Hannu biyu nasa na karba ina rissinawa,

“Kiyi hak’uri ‘yar nan. Abincin da tace abaki kenan. Kinsan nama da hakki, Gashi yanzu idan na dauka na baki zata gane domin ta gama irgasu kafin a dafa. Kiyi hak’uri kinsan shi nama hakk’i ne dashi..”

“La babu komai Inna Rabi. Ni abincin yafiye min, Domin zamu ci mu koshi. Allah ya saka da alkhairi.”

“Ameen ALLAH ya azurta mu ‘yar nan. Ki gayar da Innar taku. Kiyi mata ya jiki.”

“Ameen. Zata ji In Sha ALLAH!”

Ficewa nayi da sauri daga gidan. Fatana na karasa gidah kawai Innar mu da autar mu suci abinci ganin rana ta hudo. Ta shagon Chibuzor me kyamis na tsaya ina tunanin na bashi wayar hannu na ya bani maganin zazza’bi na kai wa Innar mu. Kyamis din na shiga na jira har layi yazo kai na.

“Chibuzor ya gidah?”

“Laffia batoulu! Kene ba laffia?”

“Lapia lou! Dan Allah temako na zaka yi.”

“Ina jin ki”

“Dan Allah maganin zazzabi na manya zaka hada min dana mura. Amma...”

“Ehen ya akai?”

“Amma zan bada jinginar waya ta. Idan na samu kudin sai na kawo ka bani wayar.”

Dan jim yayi kafin ya mik’o hannun sa alamun na bashi wayar, Domin yasan halin kuncin rayuwar da muke yi agidan mu. Mika masa nayi ya karb’a yana jujjuya ta. Zura ta yai a aljihun sa. Ya daddakko min magungunan ya mikomin, Bayan ya rubuta kowanne adadin da za’a sha. Cike da murna na karba nayi hanyar gidah. Fatana Innar mu tasha ta warke, Cikin sauri na isa layin mu. Ina zuwa kofar gidah zan shige naji yo ana kiran sunana cikin muryar da ko a mafarki aka kira ni zan gane ta waye. Juyawa nai, Tabbas shine! Kamar sa da zatin k’irar sa kai har ma da sautin muryar sa ba zasu taba gushewa a kwakwalwata ba.....

—

Ba yawa ma hade gobe IN SHA ALLAH😍❤

—

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

*_ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN_*

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😈□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

BATOUL WA HAYSAM

NA

HANSAI MAI AWARA

_*14*

•••

Jiki na har rawa yake, Da sauri na koma inda yake a tsaye yana sallamar mai mashin daya sauke shi. Bansan sanda na kai masa runguma ba.

“Yayan mu...”

“Batoul din mu.”

Ya amsa ni yana murmushi. Gaba d’aya ya canza yayi haske. Jikin sa ya murmure yayi kalau dashi, Gaba d’aya tamkar an ‘kara masa cikar halitta. Bacco din jaka ce a hannun sa shudiya, Dayan hannun kuma ledojin viva ne shake da kaya.

“Yayan mu barka da dawowa.”

Na karasa fada ina daukar ledojin gefan sa, Ya riko bacco din a hannun hagun sa, Kafadar hannun daman sa kuma jaka ce yar goyo, Ya goya ta ta gefe. Muna tafe muna yar hira haka muka shiga zauren gidan mu bakunan mu dauke da sallama.

GIDAN MATA TARA

Da Bintalo muka fara cin karo taci kwaliyya kamar bazawar akuya. Bakin nan yasha jambaki wanda ake cewa ‘gyatuma rad’au.’ Tana ganin mu mun taho muna

murmushi muna magana ta hau buga salati. Yadda kukasan ance wani ya rasu haka ta rafka ihu tana sallallami. Tuni yan gidan mu suka firfito yadda kuka san ana kada ‘kararrawar sanarwa haka manya da yara suka fito, Kowa ya hangi yayan mu sai kaga sun koma gefe suna magana ‘kasa ‘kasa. Usaiba na ganin mu ta taho a guje tana taka rawa,

“Kutsin uban can kayya kai, Yau wacce rana ce? Laraba ce tabawa ranar samu. Ranar albarka mai kawo alheri. Najibu ashe kai ne zaka iso? Shi yasa naji yanayin gaba ki d’aya ya can za. A hayye kayya kai..”

Ta karasa fada tana sakin gud’a: ayyiriririririrrururueurue. Bintalo ta ja tsaki ta sauke tana susar diddigaggen kanta. Ni da Yayan mu kawai sai muka zubawa sarautar Allah idanu. Musanman ni da ke da ayyana tarin tambayoyi kala kala a zucia ta. Shin sun bashi damar ya dawo ne ko kuwa gamon kansa yabi ya dawo? Ina cikin tunani naji an bugo kofar bandaki. Kawu ila ne ya fito yana baje hannuwa yana mammatse idanu. Da alamun kashi yayi. Domin sai baje kofofin hancin sa yake yana wani bubbuda wa irin ‘kauran nan. Bintalo ta sake sakin salati tana yiwa Kawu ila signa na ya jiyo fa ga Yayan mu. Shi kuwa ila shigewa yayi dakin sa yana dafe ciki da alamun katsa masa yake yi. Kilan ko ganin mu beyi ba. Da sauri kuma ya sa kai ya fice a hargitse. Gaggayshe su Yayan mu yayi, Wasun su suka amsa wasu suka share shi. Muka haura sama abin mu, Domin inda sabo mun saba da rayuwar gidan mu. Wadda ake yinta tamkar gidan haya mai dauke da yaruka kala-kala. Dakin mu muka shiga dauke da sallama. Innar mu ta cukwikwiye cikin hijabin ta, Autar mu kuma ta tasa tukunyar jia agaba tana cin ‘kanzon ciki domin tun jia bamu saka komai a bakin mu ba. Tana ganin Yayan mu ta ‘dane jikin sa tana murna,

“Yayan mu...”

Shima rungumeta yayi yana daria.

“Autar mu! Haka kika kara girma? Iyye yanzu ajin ki nawa?”

“Firamare fayib.”

“Masha Allah! Allah yasanya albarka a karatun ki.”

Innar mu ta dan daga hijabin ta tana duban mu. Idanun ta sun sake rinewa sunyi jajir. Jijiyoyin kanta sunyi rad’au rad’au dasu. Dak’yar ta mike tana dafe kanta. Da sauri Yayan mu ya durk’usa daga gefan ta,

“Sannu Innar mu! Baki da lapia dama?!”

“Eh wallahi zazzabi ya rufe ta. Innar mu sannu! Ga abincin na samo, Aminatu wanko tiren can ki kawo a juye”

Na karasa fada ina sunce kullin ledar abincin da Hajian Haysam tace Inna Rabi ta bani. Da gudu autar mu ta dauki tiren tayi kasa ta wanko shi.

“Sannu Innar mu! Allah ubangiji ya baki lapia yasa kaffara ne. Allah ya tashi kafadun ki Innar mu.”

“Amin wannan yaron.”

Tafada tana jingina da bango hade da rintse idanu cikin ciwo. Magungunan dana karb’o mata awajen chibuzor na dakko. Hade da ebo ruwa a kofin kan randar mu.

“Inna ga magungunan. Kici abinci sai ki sha.”

Karbar ledar magungunan tayi tana bina da kallon karin bayani.

“Aina kika samo su Uwata?”

“Innar mu awajen chibuzor me kyamis na karba. Na bashi jinginar wayata. Duk sanda Allah yasa muka samu sai na kai masa.”

Murmushi tayi cikin ciwo tana dafe kanta,

“Toh Allah ya kawo yadda za’ai. Amman da kinsani baki karbo ba. Na fa warke.”

Murmushi kawai nayi. Innar mu kenan. Kullum Idan tana rashin Lapia haka take cewa ta warke don kada ta daga mana hankali mu shiga cikin damuwa.

“Nawa ne magungunan? Ga chanji ki kai masa ki karb’o wayar taki”

Yayan mu ya fada yana ciro dari biyar a aljihun gaban rigar sa. Karba nayi hannu biyu cike da murna,

“Angode Yayan mu! Allah ya kara bud’i.”

“Ameeen.”

“Tab Yaya kaga yadda ka dawo kuwa, ALLAH ka zama dan gayu Yaya. Kano ta karb’e ka.”

Murmushi yayi yana shafa ‘k’eyar sa. Innar mu sai kallon sa take a sace. Domin bata iya hada idanu dashi saboda kunyar ‘dan fari da take yi.

“Haba? Ni kuwa ku nagani kun kara girma TubarkAllah! Innar mu cema naga ta dan rame kodan saboda bata da lapia ne.”

“Allah dai ya bata lapia.”

“Ameen Ya Rabbi.”

Autar mu ta kawo tiren sai rawa jikin ta yake saboda tsabar yunwa. Juye abincin nayi gaba dayan sa. Kwananniyar jalof ce sai tashin tsami take yi. Gaban Innar mu na kai ta. Yayan mu sai kallon mu yake cikin so da k’auna ta yan uwantaka. Caccakuna Innar mu tayi ta bar mana. Mu kuwa nida autar mu handamar abar mu muka shiga yi muna korawa da ruwa. Saboda yunwar da take addabar cikin mu, Cikin kankanin lokaci muka lakume taliyar nan tatas. Muka lallashe hannayen mu. Babbalowa Innar mu magungunan Yayan mu yayi ta hahhadiya da ruwa. Cikin kankanin lokaci bacci ya dauke ta. Ganin haka yasanya na kwashi tukunyar da autar mu ta kankare kanzo da tiren da muka ci abinci yanzu nayi kasa dashi dan wankewa. Ina sauka kasa nai kichibus da Bintalo da Kawu ila sun shigo daga waje. Da alamun nemo shi taje tayi ta kira shi. Ba zancen zuwa biki tuni ta ajiye shi agefe. Tayi wuri-wuri da ita gaba d’aya alamun rashin gaskia sun bayyana a tattare da ita. Wanke kayan na shiga yi ina kara sunkuyar da idanu na. Domin muddin idanuna ya hadu da nasu yanzu zasu fara aibata min shi suna tanka halitta ta. Bokitin zaman sa ya dakko a daki ya fito dashi tsakar gidan ya ajiye. Ya shiga zundumawa sauran kawunnin mu kira,

“Ishaq, Khamis, Dawood kuna ina? Ku sakko ‘kasa akwai magana.”

Haka yaita kwalla musu kira, Yana kuma sake tura yaran su su kira su. Ina gama wanke wanke na na dora a ka ina sharce ruwan jikin buhun sosan wanke wanken mu. Domin dashi muke wanke wa. Har na kai mattalakar bene na uku Kawu ila ya callara wa sunana kira,

“Ke Batoul kira min shegen Yaron nan mai kunnan ‘kashi wanda ya raina na gaba dashi. Kice yazo nan dan uban uban sa.”

Gyada kai nayi hade da doriyar,

“Toh Kawu.”

Ina karasa hawa na ga yayan mu na zura takalman sa a kafafun sa. Babu alamun fargaba ko ‘dar a zuciyar sa. Da alamun ma ya jiyo shi. Shi yasa ya fito daga daki don amsa kiran sa. Cikin mintina kalilan su Kawu Ishaq sun hallara a tsakar gidah ciki harda Kawu Dawood dake jera hamma ba ‘kakkautawa, Da alamun Hansatu matar sa bata samo musu abun karin kumallo ba a yawan neman abincin data tafi tun farar safiya. Ta sama nake hango su ni da sauran magulmatan gidan mu. Wasun su kuwa tuni sun sassauka kasan sun yiwa kansu wuri tun d’axu. Innar mu kuwa na kwance tana baccin ta. Da alamun acikin magungunan akwai me kashe jiki. Dadi naji data samu bacci domin da tuni idanun ta biyu za’ai wannan tashin hankalin, Abu biyu su hade mata a rai.

Daga gefe Yayan mu ya zauna akan dan dandamalin kusa da rijiya. Cike da girmamawa ya dan rissinar da kansa yana gayshe da wa’enda d’axu basa gidan lokacin da ya dawo. Wato Kawu Khamis da Kawu Ilyasu.

“Kawu Ina wunin ku?”

“La..”

Kawu Khamis bai karasa ba Kawu ila ya tari numfashin sa,

“Da bamu wuni ba zaka ganmu a haka ne? Dan uban ka. Kaga ja’irin yaro wanda ya rena na gaba dashi.”

Shiru Yayan mu yayi kansa a kasa bai tanka musu ba. Kawu ila ya ja tsaki ya sauke,

“Wato ga mahaukaci ina magana kana shiru ko?”

“Allah ya baku hak’uri Kawu.”

“Ha’kurin uban ka? Kai uban waye ma ya baka damar tako shegun kafafun ka kazo nan gidan. Ba munce ka dakata ba sai sanda muka neme ka? Wato kai kana jin kanka ka zama wani abu shine za ka tsallake maganar mu?”

“Allah yabaku hak’uri Kawu”

Yayan mu ya sake basu hak’uri a karo na biyu yana yak’e. Kawu ila ya taso zai mareshi Kawu Khamis ya dakatar dashi ta hanyar rike masa riga.

“Da hak’uri yai gabas yamma nayi dan uban ka. ‘Dan tasha ka zama ne? Dan uban ka ana magana kana washare hak’ora kana bada hak’uri. Na hada ka da ha’kurin na gunguri uban ku.”

“Sittin ta ubangiji duk mana’kisar uwar su ce. Tana ‘daka tana ji ai.”

Bintalo tafada tana watsa hannu baya. A tsaye take kamar ta hadiyi muciya a kusa da Kawu ila yadda kukasan zata koma cikin sa. Gaba d’aya a hargitse take ranta idan ya kai miliyan a b’ace yake. Yadda kukasan ta fasa kuka dan tsabar bakin cikin dawowar Yayan mu.

“Ke Karimatu! Karimatu!”

Kawu ila ya shiga dokawa Innar mu kira.

“Bata jin dadi Kawu! Tayi bacci sakamakon maganin zazzabin data sha.”

“A gidan uban ka? Matar da sassafe ta fita yawon ta zubar kace wani bata da lapia.”

“Kayi hak’uri Kawu wallahi batada lapia.”

Yayan mu ya fada yana hada hannayen sa biyu alamun ban haku’ri. Tsaki Kawu ila yaja yana sake dafe cikin sa.

“Bara na shiga bandaki na fito. Zaka fada mana dalilin daya sa ka ketare maganar mu ka dawo dan uban uban ka.”

Yana gama fad’a ya shige bandaki.

“Algungumai..!”

Bintalo tafada tana zama akan bokitin Kawu ila. Duk sauran kawunnin mu su kai shiru, Kawu Dawood kuwa na gefe yana aikin sakin hamma. Duk jiran Kawu ila ake ya fito daga bandaki aji ta bakin sa. Shi Kawu ila nacan bandaki yana katse gumi. Sakin gudawa kawai yake tsiiii. Muna jiyo sautin zubar ta har sama. Ya dau lokaci kafin ya fito yana dafe da cikin sa. Bintalo ta sauka daga kan bokitin shi kuma ya zauna yana dafe cikin sa hade da rintse idanun sa da alamun katsa masa yake yi. Cikin dauriya kamar dole ya sake duban Yayan mu,

“Dan uban ka! Akan wane dalilin za kai fatali da umarnin mu k.....”

Bai ‘karasa ba cikin sa ya sake katsawa tuni iska ta kufce masa ya shiga jera sakin wata irin tusa mai wahalar rubutawa. Sai tsami da hamamin gudawa. Ji kake,

‘Siiiit...’birr.. ‘but’but.. dadar...’

Ba shiri Bintalo taja baya tana rufe hancin ta da d’ankwalin rigar ta. Ba ita kadai ba duk sauran wa’enda ke wajen sai da suka rufe hancin su. Kawu Dawood ya kasa rike dariyar sa. Ya shiga darawa yana rufe hancin sa. Kawu ila tamkar ‘kasa ta tsage haka yaji. A kunyace ya mike yana rike wandon jikin sa ta baya. Da alamun ta fara zuba a zaunen da yake. Bandaki ya shige yan rufo kofar da karfi. Sautin futar

gudawar sa ce kawai ke zuba ji kake ‘kurusss bul’bul’bul. Amman dan masifa yana cikin bandakin ma bai fasa magana ba,

“Bara na fito dan uban ka, Ka gaya min hujjar da yasa kayi fatali da uzurin mu. Kai kuma Dawood zaka gayamin abunda ya baka dariya. Zan fito duk zaku yi bayani kai da shi. Domin naga alamun kai ne ka tsayawa shegun yaran nan suke yadda suka ga dama a gidan nan.....”

Babu wanda ya tanka masa, Shi dai Kawu Dawood sai da yai dariyar sa ishasshiya tukun sannan ya cigaba da jera hammar sa tamkar zai hadiye yan gidan baki d’aya. Cikin tafiyar yan kaciya haka Kawu ila ya fito daga bandaki daga shi sai rigar sa iya gwiwa, Wandon rigar a hannu yai saurin shigewa daki. Bai wani jima ba ya fito sanye cikin wasu kayan yana ‘bata rai, Ya goggoge sinadarin zuciar sa. Ma'ana bokitin karfen sa na zama. Wanda ya zama tamkar na gado ko na wani sihirin. Domin tun ina karama nasan bokitin gashi har girmana yana nan sai dai yasha walda awajen yan walda. Ya tsufa kwarai matuka. Amman ya kasa rabuwa dashi. Ni kuwa dana dube shi sai sautin tusoshin daya dinga saka d’axu nake tunawa. Zama yayi akan bokitin yana batsewa. Ya ja majina kafin yace,

“Toh zamu ‘dora daga inda muka tsaya....”

•••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IGIYAR ZATO...□

_*15_*

Kowa ya zura masa idanu. Ana jiran abunda zai ce. Waya ga ‘karamin su babban su. Yatsa yasa yana mai nuni da Yayan mu yana karkada masa shi,

“Kai ga saurayi mai jini a jika ko? Da har xamu gindaya maka sharad’i akan kada kazo sai mun neme ka, Shi ne za ka sa kafa kai shuri da zancen mu? Wato kai ‘kwankwararren marar kunya. Shin meya sa ka ‘ketare umarnin ka dawo?”

Yayan mu yai murmushi kafin ya dubi Kawu ila. Cikin gaskiyar sa yace,

“Ba ‘ketare umarnin ku nayi ba Kawu. Kawai dai nayi kewar gidah ne, Shekaru hudu ban ga mahaifiyata ba. Batasan a wane hali nake ba, Ni ma kuma zucia ta na ayyanamin abubuwa kala kala. Na kasa nutsuwa ne Kawu! Shekaru hudu na dauka bangan ku ba Kawu..”

Kawu ila yaja tsaki yana yamutsa fuska,

“Kaji makaryaci, baka ga mahaifiyar ka ba dai da yan uwan ka. Toh ka bude kunnuwan ka dakyau kaji. Kana saurare na ko?”

“Eh Kawu!”

“Toh yadda kazo haka zaka koma yanzu ba sai anjima ba.”

“Kayi hak’uri Kawu. Saboda ko gaisawa ba muyi ba da Innar mu, Tana kwance ba lapia.”

“Tabdijan! Ni kake cewa ba zaka tafi ba. Kaci uban uban ka.”

“Kayi hak’uri Kawu. Ba kin bin maganar ka nayi ba. Afuwan!”

Kawu ila yaja tsaki ya sauke, Kawu Khamis dake gefe yana aswaki ya dubi yayan mu,

“Kai Najibu tukun nama awane garin kake ne. Daka bar nan ina ka tafi? Sannan wacce sana’ar kake yi ko karatu kake yi?”

Yayan mu ya girgiza kai cikin girmamawa yace dashi,

“Dana bar nan Shema naje, Daga can kuma bayan wani lokaci sai na koma kano.”

“Me kakeyi a kanon? Sana’a ko karatu?”

Sai da Yayan mu yayi shiru na dan wani lokaci tukun sannan yace da Kawu Khamis,

“Almajiran ta na.,”

Bai karasa ba Bintalo ta shiga babbaka daria tana tafa hannaye. Gyara xaman d’ankwalin kanta tayi tana murmushin jin dadi,

“Almajiran ta. Ashe mun samu babban ‘kolo agidan? Dole a taho neman wahidin sadakayiya, Iya almajiri bara Iya. Iya ko gari ne ba suga. A hayye nanaye...”

‘Ayiririririrurururiii” Ta karasa magana tana sakin gud’a. Hade da gyara zaman gyalen ta, ficewa tayi tana nanata,

“Toh sai anjiman ku na tafi biki. ‘Dan Malam Au ‘kolon gidan mata tara idan Xaka tafi na baka na ‘dan sukari. Almajiran ta ba dadi. A hayye nanaye”

Duk sai gidan kuma ya hautsine da maganar almajirantar Yayan mu. Na dubi Yayan mu yadda yayi tsaf dashi yayi kyan gani, Idan ma almajirin ne shi menene? Ba karatu bane ba na neman duniya da lahira? Alhamdulillah da ya zama dan tasha ai gwara almajirantar.

“Almajiran kace ko? Toh awacce makarantar allon kake a kanon?”

Kawu Ishaq ya tambayi Yayan mu, Yayan mu ya sake daidaita zaman sa kafin yace,

“Makarantar allon Gwani Bukar dake unguwar bachirawa.”

Kada kai Kawu Ishaq yayi alamun gamsuwa. Kafin ya sake tambayar sa a karo na biyu,

“Naga dazu ka wuce da kaya nik’i-niki kayan menene?”

“Kawu kayana ne dana tafi dasu. Sakamakon can din ana sace mana idan mutum bai da gidan aiki.”

Kawu ila ya kece da daria har yana buga ‘kafafun sa a kasa, Sai da yau mai isar sa tukun sannan ya dubi Yayan mu,

“Waya baka kudin zuwa nan din?”

“Uwar daki na dake can ce tabani.”

“Toh kwana biyu na baka jal kayi ka koma almajirantar ka. Waya ga almajiri na’am! Zo ka karba.”

Kawu ila ya karasa fada yana kecewa da dariya, Da alamun almajirantar da Yayan mu yace yanayi ba karamin dadi suka ji ba. Domin har gaban abadan sunfi son su ganmu cikin kaskantacciyar rayuwar da babu jin dadi a tattare da ita sai wahala, kullum jiya i yau babu cigaba. A hankali ya mike tsaye ya nufi sama, ganin ya taho yasa na koma d'aki ina jiran ya shigo. Kamar wani marar lafiya haka ya samu waje ya zauna, kallo na yayi yana murmushin yak'e, alamun maganar da zai min ba mai dad'i bace. Ya kira suna na yana kallon Innar dake ta bacci.

“Batoul..”

“Na'am Yayan mu.”

“Yau zan juya zuwa kano, zama na a gidan nan hatsari ne. Inna bata da lafiya, tana bukata ta a kusa da ita, amman hakan ba zai yiwu ba, saboda zamana zai sake sanya mata wani ciwon da irin kalaman da su Kawu zasu dinga jifa na dashi. Batoul nasan kuna da hakuri, toh ina son ku kara akan wanda kuke dashi, zan koma kano yau saboda ko na amince zan zauna anan bani da wajan kwana, Allah yana tare daku, kuci gaba da hakuri wata rana sai labari.”

Yana kaiwa nan yasa hannunsa ya rik'o k'afar Innar mu, idanunsa a lumshe da alama kuka ne yake neman kwace masa amman ya hanashi fitowa. Ni kuwa tuni na fara kuka domin munga samu munga rashi, ko Yayan mu bazai d'auke mana komai na rayuwa ba, ganinsa ma kadai jin dad'i ne a rayuwar mu. Amman yanzu munaji muna gani zai koma inda ya fito saboda tsangwamar 'yan gidan mu.

“Yayan mu dan Allah ka zauna karka biye musu, munji dad'in ganinka yaya, ka daure kayi mana kwanaki biyun da suka baka dan Allah”

Cikin matsanancin kuka na karasa maganar, ya tashi tare da rik'o hannuna yana so ya sanya idanunsa cikin nawa amman naki yarda.

“Batoul rufin asirinku da nawa nake son karewa, tunda kika ga sun nuna rashin amincewar su na dawowar nan da nayi, toh lallai akwai wani makircin da zasu sake kullamin, wanda zai sa nayi nadama idan ban tafi ba. Kuyi hakuri Batoul ku zauna Allah yana tare daku, gashi banda wasu kud'in da zan iya bar muku, nima sai na fita zan samu wani abun nayi wanda zai sa na samu kud'in zuwa kano. Amman ga wasu 'yan kaya na sabulun wanka dana wanki, sai sukari da makaroni leda uku taliya guda biyu da shinkafa rabin kwano, da d'an wani wake baifi gwangwani biyu ba, nasan zaku kwana biyu kuna amfani dasu, akwai wata riga 'yan gwanjo ne guda biyu babba da karama ki dauki d'aya kiba Auta d'aya, Allah ya bawa Innar mu lafiya yasa kaffara ne, na tafi Batoul bana son ki nunawa kowa har sai na bar gidan nan.”

Wannan shine bankwanan da muka yi da yayan mu, yasa hannunsa ya share min hawayen da suke ta reto a fuskata, sannan ya juya zuwa wajan da ya ajiye jakarsa, ya rataya ya kalli Innar mu sosai kamar yau ya fara ganinta, kafin ya wuce da sauri ya fita, ina kyautata tsammanin kuka yake yi shima. Da gudu nabi bayansa amman abin mamaki har yakai kasa ya fice tamkar walkiya.

Da gudu na koma d'aki tare da zubewa a k'asa ina rera kuka, na rasa wace irin rayuwa muke yi a cikin gidan mu, kowa yana tare da 'ya'yansa a gabansa, amman mu sai neman tarwatsa mu ake yi, shin menene dalilin? Rashin uba ne ko kuwa rashin kudi? Duk na kasa ware wane ne a ciki yasa muka shiga cikin wannan azababbiyar rayuwar.

“Mai sunan uwa.”

Naji Innar mu na kirana a hankali, wacce da alama sautin kukan da nake yi ne yasa ta farkawa. K'ok'arin goge hawayen nake amman yaki tsayawa hakan ne yasa na kasa juyawa na kalleta har sai da ta kuma kiran sunana sannan ne na juya ba tare da na kalleta ba.

“Ya aka yi kike kuka? Menene?”

Na kasa magana sai wasu hawayen ne da suka sake b'allowa, ta fara k'okarin tashi zaune nayi saurin matsawa kusa da ita ina girgiza mata kai.

“Bakya hanani zama ba mai sunan uwa, barni na tashi naji matsalarki, shin ina Yayan ku?”

Ai kamar ta dokeni bansan lokacin da na bud'e baki ina shesshekar kuka ba, ALLAH sarki tuni ta fara shinshino akwai matsala, ta cije lebenta na sama tare da cewa.

“Yana ina?”

“Ya koma kano Innar mu, wallahi Inna su Kawu ila basa kaunar mu. Shin yanzu da suka hanashi zama ina suko son yaje a karb'e shi? Nan fa a k'a'ida gadon sa ne yana da iko da gidan nan amma kiri-kiri sun hanashi zama Inna, sam kawu ila ba zaiji koda k'amshin aljanna ba bare ya shig....”

“Ya isa haka, Iliyasu mahaifine a gareku dole kuyi masa biyayya. Karna sake jin kin aibata kowa a cikin zuri'arku kina jina?”

Ban amsa ba, saboda kokawar da na tsaya yi da numfashi na jin yana barazanar d'aukewa. Ta kuma kallo na tare da gyara zama tace.

“Ko bakiji ba ne?”

“Naji Innar mu”

Na fad'a dakyar kamar zan had'iye rai na. Haka muka zauna mu biyu babu mai cewa komai, kowa da abinda zuciyarsa take sak'a masa tsawon lokaci. Daga baya ne na mike na fara firfito da kayan da Yayan mu ya kawo mana, ALLAH sarki ko yanzu ya samu na motar 'oho' ALLAH kadai masani, cikin zuciyata na dinga yi masa fatan alkairi har na kammala gyara inda zan ajiye komai, daga bisani na dora mana abincin dare, duk da Innar mu har yanzu bata ce komai ba amman daka ganta kasan cewa akwai tsantsar damuwa a tare da ita.

Da daddare ana kiran sallar isha'i ina kasa ina alwala kasan cewar ko bani da tsarki ina zama da alwala, muryar Fadila ce ta katse min tunanin da na shiga ina cikin wanke k'afa. Da murna na amsa sallamar da tayi na mike ina gyara zaman hijabi na.

“K'awas kece da daddare haka?”

“Nice Aminiyar, wani labari naji shine nazo dan naji tabbaci, wai da gaske Yaya Najibu ya dawo?”

Naja dogon numfashi tare da kallon mutanan dake shawagi a tsakar gidan mu, yanayin fuskata ya canza, na ce mata.

“Kawas yazo, amman kuma ya koma tun d'azu.”

“SubhanAllah! Da sauri haka?”

“Ai kuwa dai, a can wajan da yake d'an aiki ne suka yi masa kiran gaggawa shi yasa ya koma”

“Kai amman naso ganin shi wallahi, nasan zuwa yanzu ya kuma zama babba ko?”

Murmushi nayi mai sauti ina k'ok'arin jan hannunta dan mu hau sama, sai tayi saurin dakatar dani ta hanyar rik'oni tana cewa.

“A'a daga nan ma ya isa, sauri nake yi, ki gaishe da Inna idan kin shiga daki.”

Na rausayar da kai, ganin ta juya yasa na rakata har zaure, A nan ne na tarar dasu Basma da Farida zasu fita, nayi saurin dakatar dasu ina cewa.

“Ku kuma ina zuwa da daddaren nan?”

“Shagon Gali zamuje.”

Farida ta fad'a tana cuno baki.

“Aiken ku aka yi?”

“Eh alawa zamu siyo.'”

Cewar Basma tana jan hannun Farida. Tsaki naja ganin akwai manyan yara a dakunan su, amman a rasa wanda zaije siyo musu alawa sai su dan tsabar rashin kulawa. Na kuma kallansu duk kansu vest ce da d'an pant a jikin su, nace.

“Ku kawo kud'in naje na siyo muku.”

Ai kamar na maresu, gabaki d'aya suka fashe da kuka, nayi saurin waigawa ko wani ya taho ace nice na musu wani abun, ganin babu kowa yasa nayi saurin shiga na haye sama ina mamakin sharrin yaran nan. Daki na shiga, Innar mu na zaune akan tabarmar da ta idar da sallah, autar mu kuma tana cin macaroni fara da mai da yaji wacce na dafa d'azu. Guri na samu na zauna ina jin tamkar na gaya mata, sai dai nasan gwaleni zata yi sai nayi shiru kawai ban ce komai ba.

“Innar mu na zuba miki abincin?”

“A'a mai sunan uwa, kedai ki zuba kici ni sai anjima saboda ina son gobe na tashi da Azumi”

“Innar mu baki da lafiya zaki azumi?'”

Na tambayeta ina rausayar da kai na gefe.

“Ai naji sauki sosai.”

Ban yadda ba nasan zata yi ne kawai saboda abinda ake yi mana a cikin gidan mu, za tayi ne saboda ALLAH ya shigo cikin lamarin mu. Sai naji nima dama ina da tsarki sai muyi tare amman ba dama. Zubawa nayi naci na dauki kwanukan na sauka kasa zan wanke, Kawu ila dake rike da karfen bene wanda da alama hawowa zai yi sai kuma ya dakata, ya kalle ni yana tambayata.

“Ke, ina wannan yaron mai kunnan kashi?”

“Baya nan kawu.”

Na fad'a cike da jin haushin sa, shi kuma ya sake gwaggwafewa a gurin naji kamar na koma sai dai na daure.

“Ina yaje har yanzu bai dawo ba?”

Haushi ya sake kamani, katon namiji yake cewa wai bai dawo ba har wannan lokacin karfe takwas da rabi da mintuna uku, bayan kuma mazan gidan sai sukai sha biyu ma basu dawo ba. Wata uwar tsawa da ya daka min itace ta dawo dani hayyacina, ya sake cewa.

“Idan ya shigo daga yawon nashi, ki turo min shi.”

“Kawu ya koma ai.'”

“Waye ya koma? Ina aka koma?”

Na yatsina fuska ba tare da na bari ya gani ba nace.

“Kano, yace ba zai kwana ba saboda yaga ranku duk bai so hakan ba”

“Munafuki..! Kaji wani makirci, oho dan kar ya bamu na siyan goro shine ya sulale ya tafi bayan ya cika ku da abubuwan arzik'i ko? Toh koma ciki kice da tsohuwar ku ta bada nawa ya kawo min.”

Kafin nayi kwakkwaran motsi muka jiyo hayaniya daga k'ofar gida, nan da nan Kawu ila ya juya saboda an jiyo sabuwar gulma ya fita, ni kuma na sauka kasa ina Allah wadarai da halayensa saboda kakaf babu na d'auka a ciki. Ina durkushe a wajan rijiya na jiyo muryar Yusha'u yana babbanka ashariya yana cewa.

“Ance daga wajan shagon Gali aka gansu, to wane d'an iskan ne ya lalata musu rayuwa har su biyu dan tsabar shaid'anci? Wallahi tallahi sai munyi shari'a da duk d'an iskan da aka kama ya yiwa Farida da Basma fyad'e.”

___

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IGIYAR ZATO...□

_*16_*

Yusha'u na kaiwa nan, a lokacin Kawu ila yakai inda suke, nan na jiyo wani gundumeman ashar daga cikin bakin kawu ila yana buga rigarsa da hannun hagu.

“Nace wane d'an gidan shed'aniyar ne ya lalata min yarinya?”

Ya karasa maganar yana karb'ar Basma da ake miko masa ita wacce ko motsi bata yi tuni ta dad'e da sumewa. Jikinsa yana kyarma ya fara shirin komawa cikin gida domin dai yaje ya kara tabbatarwa dan zuciyarsa sam bata yarda da abinda kunnuwansa sukaji ba.

“Ga wannan kud'in a hannunta muka gansu.”

Cewar wani matashi wanda shine ya kinkimo Basma daga inda Gali mai shago ya zubar dasu bayan ya biya buk'atar sa. Aikuwa Kawu ila ya waiga tare da sanya kafarsa ya naushi cikin matashin tare da fara zazzaga masa ruwan mafisa.

“Naci kaza-kazan ubanka, ni zaka kawowa iskanci da wulak'anci? d'ari biyun banza d'ari biyun wofi. Ni idan na kama wanda ya lalata min rayuwar yara na wallahi tallahi ko hukuma bazan sanarwa ba zan ci uban mutum.”

Yana kaiwa nan ya shige cikin gida, ni kuwa da nake bakin k'ofa ina jiyo abinda yake faruwa, jin motsin shigowar Kawu yasa na koma ciki da gudu dan kar ya ganni. A tsakar gida ya tsaya yana kiran matarsa, amman jin irin yadda yake bude murya yasa kowa ya fito daga d'aki, Yusha'u yana rik'e da Farida wacce take ta faman kuka tana rik'e gabanta.

“Me yake faru haka?”

Usaiba ta tambaya tana karasawa wajan Kawu ila.

“Wallahi wani mugun ne yayi musu fayd'e daga fitar su yanzu.”

“Lailaha'illAllahu Muhammadu rasulillahi S.A.W, fya me?”

Duk mutanan wajan suka had'a baki wajan maganar, a dai-dai lokacin na kusa shigewa d'aki naji hakan yasa ni juyowa da sauri ina kallon su ta sama. Kawu ila ya mik'awa Usaiba Basma yana faman nad'e kafar wando kamar wanda zai yi dambe, Gida kuwa ya dauki hayaniya kowa da abinda yake cewa.

“Karku zargi kowa, ni nasan wanda ya yiwa yaran nan wannan wulak'ancin, kuma billahillazi sai ya gane shayi ruwa ne. Ke Kaltume kisan yadda kikai kika fito da Najibu idan ba haka ba na lahira sai yafi ku jin dad'i a gidan nan.”

Gabana ya buga jin Kawu ila yana k'ok'arin yiwa Yayan mu mugun sharri wanda baiji ba bai gani ba, wanda ya tafi yana kuka saboda tsoran irin sharrin da za'ai masa idan ya zauna a gidan. Ashe zai tafi ne yabar mana baya da k'ura. Ashe har gwara ya zauna aci masa mutuncin da duk aka ga dama akan wannan sharrin da ake son goga masa karo na biyu.

“Kana nufin kace shine ya lalata wad'annan yaran?”

Kawu Khamis ya tambaya wanda da baiyi niyar fitowa daga cikin daki ba, har sai da yaji ance fayde akai sannan ya zabaro takalma yayo tsakar gidan.

“Kwarai kuwa, Domin maganar da nayi masa d'azu na cewar waya tambaya da har ya dawo gidan nan, toh ashe tayi masa zafi, shine ya tattare kayansa yace musu komawa zai yi can kano, kunga ni gashi nan kafin ya bar garin ya tsaya d'aukar fansa akan yaran da idan a kauye yake tuni yayi aure ya ajiye irin su. Toh na rantse da abinda raina yake hannunsa sai na wulak'anta Najibu, sai ya san wanene ilyasu, sai ya gane kuranshi yabar ganin ya fara tara gemu, wallahi k'asa-k'asa zanyi da shi.”

Yana ta surfa masifa, su kuwa iyayen yaran banda koke-koke babu abinda suke yi, suna ta faman cewa sun shiga uku sun lalace ga Bintalo ta hana aje asibiti, a cewar ta idan suka je kotu za'a kai maganar kuma daga nan shige nan an lalata musu suna, gara a bari har Najibullah din ya dawo sai a dauki fansa. Da wannan shawarar sukaki kai yara asibiti sai ruwan dumi da suka sanya su aka basu magunguna Basma kuwa tamkar ba zata yi rai ba saboda an yi mata kaca-kaca abun babu kyan gani.

Ni kuwa d'aki na shige tare da zama jikina banda rawa babu abinda yake yi, na kalli Innar mu wacce idanunta ke kafe waje guda, tsoro ya kamani duk a tunani na bata numfashi saboda banga wani gurin numfashi a jikinta yana bugawa ba. Na rarrafa tare da kai hannu na tabo kafadunta, sai naga ta kalleni ba tare da tayi motsi ba. Autar mu ta shigo da gudu kasan cewar itama tana k'asa, tazo ta fad'a jikin Innar mu tana kuka, duk muka koma kanta muna tambayarta abinda yake faru da ita.

“Innar mu jini a jikin Farida, Inna kuka fa take yi tana cewa zafi, wayyo Inna Basma zata mutu tana ta yin wani abubuwa”

Magana take yi, amman jikinta sai rawa yake daga ganinta kasan bata da nutsuwa. Inna ta sake janta jikinta tana shafar bayanta, cikin dauriya da k'okarin kai zuciyarta nesa tace mata.

“Ya isa haka, ba zasu mutu ba kinji ko? Amman kema ki dena sauka kasa da daddare kinji ko? Saboda kar kema abinda ya same su ya sameki kinji Auta na?”

Ta dinga d'aga kai tana sauke ajiyar zuciya, ni kuma na koma gefe tare da sanya hannu a hab'ata ina hawaye, cikin rai na ina hango lokacin da zasu tafi siyan alawa. Kamar na gayawa Innar mu abinda suka min d'azu da nace su kawo na siyo musu, sai dai nayi shiru saboda nasan haka zata ce min karta sake jin na yi maganar cewa naga fitar su, musamman ma da yanzu suka sake dora zargi akan Yayan mu.

A ranar dai bamu samu isasshen bacci ba, saboda tashin hankali ana ta fama da Basma wacce ke suma tana dawowa. Shi kuma Kawu ila ya addabi mutane da ashariyar da yake ta dannawa Yayan mu da besan ana yi ba. Tun daga wannan abun da ya faru, sai tsana da tsangwama suka sake yi mana yawa, jikin Innar mu kuwa ya sake tsananta amman babu wanda yayi yunkurin cewar zai kaita koda chemist ne bare a kaiga asibiti. Kullum nice nake zuwa gidan su Haysam a matsayin Innar mu, ina yin aiki na dawo na gyara dakin mu nayi girki domin yanzu ko ragowar abincin ma Hajiya Husnah tace a dena bani.

BAYAN WATANNI TAKWAS

Bayan watanni shida jarabawar kare sakandiren mu ta fito, cikin hukuncin ALLAH takarduna duk sunyi kyau muna ta murna nida su Innar mu, sai dai babu halin ci gaba da makaranta duk da cewar ina son haka. Samari kuwa sai dai nace sambarka domin zuwa suke yi waje na neman aure amman da Kawu ila yaga saurayin yana da abin hannu sai yaje yayi min sharri, daga ranar ba zan sake ganin kowa ba. Kullum addu'a ta shine ALLAH ya bani abinda yake alkairi, Gashi duk wad'anda suke zuwa d'in irin shekarun d'in da zan iya aure ne, amman Kawu ila sai dai nace Allah ya shiga tsakanina dashi, domin duk korarsu yake cikin hikima ba tare da mutum yasan sharri yake min ba.

Kamar kullum kasan cewar tunda na fara aiki a gidan su Haysam sai Inna ta dena zuwa sai dai ni naje. Yau kam ina kare aiki na nazo zan tafi gida naga Haysam a tsaye jikin motar Abban su. Ina kallonsa amman saboda karya tsaida ni sai nayi saurin wuce shi, amman taku uku zuwa hud'u ya tare gabana yana sakin murmushi.

“Gaskiya mine, kina bani wahala duk da cewar ance abinda zaka samu baka samun shi ta sauki. Duk wannan saurin na menene?”

Na kauda kaina gefe domin kallonsa yawa yake min, sai naji duk na tsargu idan ya kafeni da idanunsa.

“Mine ki gaya min yanzu me zaki yi tunda kin karbo takardunki, Aure ko karatu?”

Nayi shiru domin bansan me zanyi ba, babu kudin tafiya jami’a, mijin auran kuma suna zuwa ana b'atani a gurin su, to mai zance dashi? Sai naji ya sake min magana.

“Kinga dai ni tafiya zanyi k'asar cyprus saboda Hajiya ta matsa kan cewar ba anan zanyi karatuna ba, wallahi mine bana son na rasaki shi yasa nake son jin menene ra'ayinki a yanzu?”

Kallansa nayi muka had'a ido nayi saurin kawar da nawa gefe. Yatsuna biyu nasa ina jan karan hancina kafin daga bisani na gyara tsayuwa nace dashi.

“Duk biyun ina so, sai dai a yanzu babu abinda zance dakai, saboda ban san abinda Allah zai shirya min ba”

“Toh mine ki tafi kiyi karatu mana? Nasan har lokacin na dawo sai kawai muyi aure ko?”

Nayi wani guntun murmushi mai cike da takaici, toh da ina da ikon komawa makaranta zan tsaya bata lokaci ne, amman dan ya raina min hankali shi zai tafi k'asar waje karatu, ni anan din ma karatun neman gagagarata yake amman yake min wannan maganar. Cikin son katse hirar domin na gaji so nake naje na huta nace masa.

“Toh zanyi.”

Na fada cikin gatse, amman abin mamaki sai naji yace.

“Good girl! Toh yanzu zansa a nemar miki inda zaki yi Jamb, insha Allahu duk inda kika samu gurbin karatu zan dauki nauyin ganin komai ya tafi da ikon ALLAH, mine karki zato ko wani tunani akan wannan abin da zanyi miki. A'a nayi miki ne fisabillahi, badan na dage sai na aure ki ba. Kije ki fara shiri zanzo muje kiyi registration din Jamb din idan an fara.”

Bansan tun lokacin da na bud'e hakora nake faman farin ciki da murna dajin wannan kalaman na Haysam ba, sai naji kaso d'ari cikin kin da nake masa ya ragu sosai, a yanzu ji nake tamkar na rungumesa dan murna. Cikin jin dadi na dinga zuba masa godiya har sai da dakan shi ya gudu cikin gida, sannan na juya da sauri nima nayi gidan mu dan zuwa sanarwa da Innar su. Koda naje na bata labari itama tayi murna da farin ciki, ta dinga sanyawa Haysam albarka tamkar yana wajan. Haka na dinga baza kunnuwa dan naji lokacin da za'a fara Jamb din, ai kuwa lokaci nayi Haysam yayi min magana, aka yi komai aka gama.

Kaduna mukaje muka zana jarabawar jamb d'in mu tare da rakiyar Haysam da wata kanwar abokinsa wacce itama zata zana jarabawar. Bayan wata biyu dai komai ya fito. Alhamdulillah na samu gurbin karatu a jami’ar Ahmadu Bello dake nan Zaria. Wato ABU ZARIA. Lallai ALLAH qadirun ne ala manyasha’u, Domin fannin dana keso shina samu, wato digiri a fannin zallar turanci. B.A ENGLISH. A dai-dai wannan yanayin ne shima Haysam aka kammala shirye-shiryen tafiyarsa karo karatu, shima kuma sai da ya tabbatar ya bar komai da zan tafi makaranta ta a hannun babban abokinsa mai suna Suraj. Lokacin da yazo yi min sallama sai da naji tausayinsa, naji tamkar nayi masa alkawarin zan auresa, sai dai idan na kalleshi na kuma tuna shekarunsa da kadan suka wuce nawa, gashi in mace ce ko a yanzu za'a iya yi min aure, sai naja guntun bakina nayi shiru ina binsa da addu'ar fatan alkairi.

Tunda ya juya ya tafi bai sake waigowa ba, shikenan ko sai yaushe zamu sake had'uwa? Naji zuciyata nata tambaya. Yana da kirki, yana sona da gasken-gaske, sai dai harga ALLAH Haysam yayi min yarinta a matsayin mijina, bana son nayi aure na raina miji na, nafi son na auri wanda ya girme ni, wanda kallona kawai zai yi idan nayi laifi na gane abinda yake nufi, ba wanda zai min kallon warning ba nayi zaton sa'ana ne ba. Na koma gida ina murmushi domin tuna kalmarsa ta karshe da ya gaya min.

''Kisa a ranki cewar Namiji baya kad'an mine.''

Daga haka naci gaba da harkokina, duk lokacin da ake neman wani abun na makarnta Suraj zaizo har gida ya sanar dani, da haka har lokacin fara karatu na Yayi. A satin da zan fara karatu na debo yan kaya na duka na wanke su tas. Suna bushewa na hada su a leda, Hijabi na na zura na dauki yar ledar kayan,

“Innar mu bari naje gidan su Fadila na gogo kayan nan. Kinga na huta idan zani makaranta kawai sawa zanyi.”

“Hakan yayi! Allah yasa ki fara a sa’a. Kar dai ki kai yamma.”

“Ameen Innar mu! In Sha Allahu bazan jima ba.”

“Yaya sai kin dawo.”

Autar mu ta fada tana cigaba da cin ragowar diddigar awarar da Baba Usaiba ta bata.

“Yauwa autar mu. Kar fa kije ko’ina.”

“Tam Yaya.”

Ficewa nayi daga daki, Tsakar gidan mu babu kowa da alamun suna ‘daka, Gidan su Fadila na nufa zuciya ta ‘k’al da ita, Gaisawa mu kai da Aunty Nana ta amsa ciki-ciki tana yamutsa fuska. Dakin Fadila na shiga bakina dauke da sallama, Tana gani na ta mike muka rungumi juna.

“Aminiyas yanzu nake zancen ki a zucia ta.”

“Allah sarki tawan! Allah yabar mu tare har gaban abadan.”

“Ameen”

Ruwa ta kawomin da cincin. Ci nayi na rage sauran aleda zan kai wa su Innar mu. Dan bama iya cin abu bamu ragewa juna na komai kankantar sa. Cire hijabi na nayi na sauka kasan carpet.

“Tawan ‘dan bani ayon din gugar ki na goge kayan nan.”

“Tafiyar tazo ne? Oh yanzu shikenan sai mun ganki.”

Murmushi nayi ina yayyafa ruwa a shaddar da Yayan mu ya dinka mana shekarun baya, Maje gaba akai mana shi yasa sai yanzun tayi cif cif ajiki na.

“Haba tawan ai In Sha Allahu had’uwa ba zata gagara ba. Da yardar Allah kuwa, Ga kuma waya ma zamu dinga hirar mu.”

“Ai na taya ki murna Aminiyas, Duk fa cikin sa’oin mu da mu ka zana jarabawar jamb babu wanda yaci, Amma ke Allah ya datar dake kinci har kin samu admishon a fannin da kike so. Ubangiji Allah yasa ki fara a sa’a Aminiyas.”

“Kinsan komai rubutacce ne daga Allah tawan. In sha Allah kuma naku yana nan tafe.”

“Ameen ya Allah! Ya labarin Yaya kuwa?”

“Yana kano abunsa inajin yanzu ko yana shekarar karshe ta kammala N.C.E d’insa.”

“Masha Allahu! Ubangiji Allah ya kara bashi nasara ameen.”

“Ameen..”

Haka dai mu kaita yan hirarrakin mu har na kammala goge kayan nawa dama ba yawa ne dasu ba. Na zura a leda ta raka ni har gefen layin mu. Na karasa gidah baki na dauke da sallama.

GIDAN MATA TARA

Zaune Bintalo take a mattakalar bene itada Innatuwa matar Kawu Khamis. Gefen bandaki kuma layi akai, Su biyar cas suna jere jiran wanda ya shiga ya fito. Sallama na sake yi a karo na biyu ganin babu wanda ya amsa wacce na fara yi. Nan ma shiru su kai suka cigaba da hirar su. Sama na haye abuna ganin yadda suke bin ledar hannu na da kallo.

Baki na dauke da sallama na shiga dakin mu. Innar mu na kishingid’e tana jin rediyo, Autar mu kuma tana yar carafke da duwatsun ta a kusa da randa. Zama nai a kusa da autar mu ina bubbuga baya na bayan na ajiye ledar kaya na akan katifa,

“Innar mu sannu.”

“Sannun mu! Har kin gogo?”

“Eh wallahi. Ai dake ayon din nasu mekyau ne kuma wutar da karfi.”

“Masha Allahu! Allah yabada sa’a.”

“Ameen”

Kayan jiki na na rage, Mun dan taba hira da su Innar mu kafin na mike na dora dumamen tuwon da matar soja taba mu jia. Munci munyi nak muka dasa hira har lokacin bacci yayi bacci ya dauke mu.

••••. •••••. ••••. ••••.

Dan kudin da Gwaggo Aminatu ta bayar aka kawomin da shi na shiga kasuwar layin mu nayi yan saye sayen makaranta dai dai namu na talakawa. Shagon gali na biya don auno omo dan aune. Yana zaune a benci ya dora wata yarinya a tsakiyar cinyar sa. Na dubi yadda ya cakwaikwaye ta yana mata wasa sai bangala daria take. Sai dana dubi yarinyar sosai na gano yar gidan Haladu Mai Guga ce.

“Humaira!”

“Na’am.!”

“Tashi kije gidah abban ku na kiran ki.”

Na fadi haka don kawai ta tafi gidah. Hankali na sam bai kwanta da Gali ba. Kad’a Kai tayi ta tafi gidan su da gudu.

“Matar Manya!”

Gali ya fada yana lashe lebe. Harara na wurga masa ina mika masa dari biyun hannu na,

“Ungo bani omo rabin rabi da sukarin hamsin da bota yar leda guda biyu.”

“Yanzu kuwa Hajjaju! Dan Allah ki dinga murmushi kinfi kyau.”

Ya karasa fada yana mikomin, Wafta nayi na fice abuna. Gidan matar soja na biya na mata sallama sannan na wuce gidah kai na tsaye.

GIDAN MATA TARA

Ina shiga naja baya nai turus, Domin gaba d’aya ahalin gidan mu rankataf suna tsakar gidah, Kawu ila ne a tsakiyar su sai zunduma ashariya yake wai an balla masa hannun bokitin zaman sa, Baki na dauke da sallama na shige zan haye sama ya kira sunana cikin kwakwazo,

“Ya ki nan. Dan uban uban ki zo ki gayamin wane iskancin ki kai aka samo miki jami’a har an biya miki zaki fara zuwa.? Kaga shegun yara yan iska wanda basu san halacci ba..”

“Jami’a? Jami’a fa kace ilyasu.! Tab sittin ta ubangiji zina take aikatawa. Uban waye ya biya mata?”

Bintalo tafada tana kururuwa, Hade da buga zanin ta...

—

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□[9/16, 11:29 AM] □: *_IGIYAR ZATO_.....□_*

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(TAKU NA BIYU)

ZAFAFA BIYAR NA KUDI NE, ME SO DAN GIRMAN ALLAH YA BIYA YA KARANTA HANKALI KWANCE😘❤

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

17

“Zina fa ki kika ce, Kutsin ubancan kayya kai! Ke Bintalo kiji tsoron ALLAH.”

Cewar Baba Usaiba da ta fito daga kan layin bandakin da suka jeru, Bintalo taja tsaki tana watsa hannu baya,

“Yo karya akai? Bata yinne? A wannan zamanin wane garan saurayin ne zai dinga yiwa budurwa hidima haka? Sittin ta ubangiji sai dai wanda bakin uwa ke binsa.”

Baba usaiba ta ja guda ta saki tana buga zanin ta,

“Ahayye kayya kai, Yo inda haka ne Alawiyyah ma da Hinde bin mazan suke d...”

Bata karasa ba Bintalo tayi kukan kura ta cafki wuyan ta, Tuni fada ya gaure a tsakani, Kawu ila yaja bokitin zaman sa ya zauna yana saka ce baki. Kankace me? Gida ya kara taruwa da mutane, Almajirai da ‘yayan ma’kota duk sun shigo kallo, Baba Usaiba sai ‘daga Bintalo take sama tana naka ta da ‘kasa, Dariya ta tahomin na danne kawai nayi sama ina godewa ALLAH da hakan tafaru, Da tuni Kawu ila ya dinga sheganta ni. Duk kuwa da nasan yanzun ma ban tsira ba, Da sun gama casuwar zai kirawo ni ya dora daga inda ya tsaya.

Daki na shiga da sauri ina dariyar da tun d’axu na rike ta, Innar mu dake jan carbi a gefe ta dago ta dube ni,

“Dariyar me kike ne?”

“Bakyaji na da Kawu ila yanzu?”

“Uhm uhm! Na dai jiyo hayaniyar sa d’axu yana kiran yaran gidan nan ‘d’ai dai kan an karya masa hannun bokitin zaman sa.”

“Ai gwara da aka karya.”

Na fada ina murmushi, Dakuwa Innar mu tayi min na zauna agefen ta, Autar mu na gefen katifa tana sakin munshari domin ita akwai bacci idan ta samu waje.

“Innar mu ga yan kayayyakin fa.”

“Masha Allahu! Sai ki harhada su waje d’aya kada ki manta wani abun”

“Toh! Ga wannan makilin ne na siyo mana naga namu ya kare, Wannan kuma gari ne na auno shima kwa sha idan babu abinci, Ga gawayi shima na siyo da sauran canji.”

“Kai ai da abun makarantar kika siya, Toh angode Allah ya saka da alkhairi, Allah kuma ya baku sa’ar karatu. Ameen”

“Amin Innar mu.”

Mi’kewa nai na shiga harhada yan kayayyaki na a leda bacco, Dama ace akwai akwati da aciki zan zuba komai nawa, Ina gama hadawa na kara kintsa dakin mu na tattare komai. Waya ta na dakko na shiga daddan nata ina goge sakonni mara sa amfani, Shafi’u Gangare shine sunan da nazo kan sa a wurin shigowar sak’onni. Bazan manta ba shine saurayin da nayi na karshe wanda Kawu ila ya tare shi bansan wane irin sharri gaya masa akai na ba amma tundaga ranar bai sake takowa inda nake ba. Sakon na kara karantawa,

“Ashe haka kike? Tir da halin tsatson ku wallahi. Meyasa ba zaki gayamin gaskiyar lamari ba? Ki farga ki canza yanayin rayuwar da kika dora kan ki, Shine mutinci.”

Sake karantawa nai ina cizan lebe na na kasa, Toh shin wane sharrin Kawu ila ya gaya masa akai na? Me hakan ke nufi? Shin *ZATON* da yake ganin an same mu ta haka gani yake kenan fasikanci nake aikatawa? Ajiyar zucia naja na sauke. Na goge sakonnin dukkanin su, Domin duk tarin su akan hakanne, Kowanne da kalar abun da yake rubuto min. Goge nambobin su nai gaba ki d’aya na ajiye wayar a gefe ina tunanin ina mafita?

“Batoul! Batoul! Batoul!”

Kawu ila ya shiga kwararawa suna na kira, Mi’kewa nayi daga kwanciyar da nai ina mika. Hijabi na na zura na sauka kasan. Shi kadai ne a kasan sai yara dake wasa a gefe, Da alamun an gama fadan kowa ya watse. Na dubi Basmah dake kusa da Buhari almajiri ko pant babu a jikin ta. Kuma mahaifiyar ta na kallon ta domin su basman na daga gefen kofar dakin. Ita kuma Hajarar na kishingid’e a wajen kofar tana fiffita. Girgiza kai na nayi cike da Takaici,

“Kawu gani..”

“Ina fa! Ga ni dai, Basarakiya ranki ya dad’e.”

Murmushi nai jin bakar maganar da ya yabamin,

“Kawu bacci ne yafara dauka ta sai daga baya naji kiran ka.”

Yamutsa fuska yayi yana sosa hancin sa, Ya curo tasono yana cilloshi waje na, Naja gefe karya fadomin akai, Kawu ila ba karamin katsami bane. Kuma nasan da biyu yayi haka. Ban gama maganar da nake a zuci ba na jiyo shi,

“Shegiya mai idon jemagu yanzu ke harnan kyankyami na kike? Ke da ke aikata zina kina bawa samari jikin ki suna biyan ki kudi? Tasono kuwa uban kowa yana ‘kwakwulewa, Shegiya almura da ido tsuru tsuru.”

“Allah ya baka hak’uri Kawu, Ba kyankyamin ka nake ba.”

“Oho dai! Zaki gayamin uban da ya biya miki makaranta ko kuwa?”

Ajiyar zucia nayi, Na cire tagumin dana zabga,

“Kawu wallahi ina ranar da nake ta cemaka zanyi magana da kai kaki saurara ta?”

“A ubanki? Yaushe akai haka?”

“Ranar da zan tafi gidan aiki da safe kwanaki?”

Tsaki yaja yana wurgomin harara. Nayi murmushi kawai ina cigaba da lankwasa hannu na kafin na cigaba da cewa,

“Toh sai na samu Kawu Ishaq na gaya masa cewar an samamin gurbin karatu a jami’ar Amadu bello dake nan zaria.”

“Uban uban wanda ya sama miki karatu nake so inji. Yanzu ke har kin isa ki je jami’a? Dan uban ki agidan nan wa kika ya shiga jami’a?”

“Kawu naga su Hinde suma sunyi jamb din basu ciba..”

“Na had’aki da jamb din na gunguri uban uban ki. Zaki gayamin wanda ya biya miki karatun ko sai na lallasa ki awajen nan?”

“Kawu Haysam ne ya samamin..”

Sallallami Kawu ila ya shiga rafkawa yana tafa hannaye, Alokacin Bintalo ta fito daga dakin ummita da alamun lab’e take dama. Zaro idanu tayi tana bubbuga kafafun ta. Cikin tsantsar kidimewa ta rafka salati tana tafa hannuwa,

“Wannan yaro ya kawo kansa, Sittin ta ubangiji sun kai sunan sa an magance shi. An daiji kunya wallahi.”

Nayi murmushin yak’e kawai ina jiyo su suna aibata ni, Kawu ila ya kwaso rantsuwa ya dire yana wallacewa kan babu jami’ar da zani, Gaba d’aya sai sauran y’an gidan suka firfito, Ana kacaccala maganar zuwa na jami’a da bada jiki na da nake yi wai maza na amfani dani.

“Yo dubi jikin ta mana, Duk ya saki alamun ana tattabeta.”

Cewar Bintalo tana dungure min kai, Na dubi jiki na bansan sanda na saki wani marayan kuka ba, Baba Usaiba ta sakko da gudu tana karkadawa Bintalo hannnu,

“Kutsin ubancan kayya kai, Kiji tsoron ALLAH Bintalo, Yo du gidan nan akwai wanda ya kai Alawiyya da Hinde sakakken jiki ne? Nonuwa sun rafke suna reto alamun a...”

“Sittin ta ubangiji sai nayi maganin ki yau Usaiba..”

Bintalo ta lailayo ashariya ta d’urawa usaiba, Itama ta lailayo ta rama, Sai ruwan ashar ne ke zuba daga bakunan su, Na goge hawaye na ina takaicin irin rayuwar gidan mu.

”Ke de Usaiba ki fito kice kawai bakin cikin goshin su Alawiyya kike, Yo Idan ba haka ba ke meye naki aciki? Ta kira Larai ne ko Talatuwa da zaki dinga shiga abinda babu ruwan ki.”

Cewar Ummita matar Kawu ila tafarko, Wato aminiyar Bintalo kaf gidan mata tara. Baba usaiba ta kece da dariya tana kururuwa,

“Kutsin ubancan kayya kai! Wa zan wa bakin ciki? Alawiyya ko Hinde? Duk cikin su babu budurwa, Gaba d’aya sun gama yawo a kwararo kaf garin nan babu wanda bai sani ba, Yaran da ake dibar su suna fito Kaduna.”

Usaiba tafada tana sakin gud’a. Bintalo ta shatalo kafarta ta fad’i a kasa ta hau ruwan cikin ta, Dake kakkarfa ce Usaiban tuni ta janyota itama ta maida ta kasa ta shiga dukan ruwan cikin ta. Sauran suka sa dariya. Dai dai shigowar Gwaggo Aminatu dake kaduna. Tana gaba yaran ta biyu na biye da ita abaya, Dayan yana rike da madaidaicin akwati, Dayan kuma ya rik’o wasu ledoji shake da kaya, Suna ganin ta suka dena fadan, Ta shiga bin mu da kallo gaba ki d’aya tana girgiza kai,

“Gidan Mata Tara kenan, Ashe har yanzu baku girma ba? Fada ai an barwa karnuka su dinma basu cika yi ba.”

“Yaya sannu da zuwa!”

“Sannun mu ilyasu, Kana nan dai da nacaccen bokitin nan? Dan Allah ka jefar dashi haba!”

Gwaggo Aminatu tafad’a tana firfita da gefen mayafin ta, Daria kawu ila yayi yana sosa keya bai ce mata komai ba, d’aya bayan d’aya manya da yaran gidan mu muka shiga gayda Gwaggo Aminatu. Amsawa tayi cike da fara’a.

“Ina wuni Ya Naseer? Ina wuni Ya Faysal?”

Na gaishe da yaran Gwaggo Aminatu wanda ke tsaye suna kallon mu. Ya Naseer shine na biyu a yaran ta shi kuma Ya Faysal na hud’u ne, Sauran duk mata ne, Biyu sunyi aure, Biyu suna karatu. Amsawa su kai da fara’a kowanne a fuskar sa,

“Batoul meya faru na gan ki a tsugunne kuka kike yi?”

“A’a Gwaggo! Abune ya fadamin ido na.”

“Karya take yi, Yaya yarinyar nan da kike gani fasika ce.”

Salati Gwaggo Aminatu taja tana kallon Kawu ila,

“Haba Ilyasu? Kasan me kace kuwa?”

“Toh Yaya jikin ta take baiwa wani yaro dan gidan Alhaji Kabeeru Mai Wafa shine bayan sun gama tambadancin su ya nema mata makarantar jami’a.”

Tsaki Gwaggo Aminatu tayi tana girgiza kai, Cike da bacin rai tace dashi,

“Dan ALLAH ilyasu ka dinga yiwa bakin ka linzami, Maganganun da kake fada sam basuda ce ba, Kai sauri ka roki gafarar ubangiji da ta yarinyar nan. Shin me zaka gayawa ALLAH ranar lahira? Shi fa *ZATO* ba abune mai kyau ba, Kuma har gaban abadan inde ba gafarar yarinyar nan ka roka ba wallahi sai ALLAH ya kama ka da aibata tan da kake yi. Maganganu marassa dad’in ji, Sam basu da kan gado, Shi fa *ZATO* wanda kakewa kallon haka daban me aikatawar kuma da baka ganin bameyiwu bane sai kaga akan sa abin yake. Dan Allah ka gyara halin ka. Idan an girma asan an girma.”

Kawu ila ya tab’e baki yana harara ta,

“Ni dai na yi rantsuwa babu inda zata je, Ba zata shiga wata jami’a ba.”

Gwaggo Aminatu tayi daria mai sauti tana kallon Kawu ila,

“Toh sai kayi azumi uku, Domin da yardar ALLAH jamia kuwa tamkar ta yi tane, Kaga akwatin nan ita nazo kawowa shi, Mun je ganin gonar Baban su Faysal nace mu biyo na kawo mata, Domin nasan da tafiyar ta jami’a. Kuma dai ni ce gaba da kai. Kaga kuwa babu zancen hanata zuwa jamia karma ka fara.”

“Amma Yaya..”

“Mubar maganar nan haka ilyasu, In de na isa da kai a matsayi na na babbar yarka sai kayi hak’uri. Duk banga abun tashin hankula anan ba. Abu kadan a gidan nan sai kuyi ta kicincina shi kuna mai da shi babba. Wallahi tun daga bakin titin layin ku ake jiyo hayaniyar yan gidan nan. Ace kullum dai magana d’aya za’ai tayi, Kun janyo kaf gari babu wanda baisan halin ku ba? Dan Allah ku canza ko dan na ‘kasa su taso cikin bin nagaba dasu.”

Fuuu Bintalo ta haye sama tana cuno baki tamkar bazawarar akuya, Kawu ila ma ya dauki bokitin sa ya shige da’ki. A haka aka fara watsewa daga tsakar gidan. Gwaggo Aminatu ta girgiza kai kawai cikin takaici tace,

“Allah ya kyauta!”

Kafin wani dan lokaci tuni su Kawu Ishaq dake majalisa suka daddawo dan gaisawa da Gwaggo Aminatu. Sama na haye baki na dauke da azkhar na yamma. Sai da Gwaggo Aminatu ta shisshiga ko’ina a dakunan kasa sannan ta hayo sama, Dakin Usaiba ta shiga suka gaisa sannan ta shigo dakin mu. Gayshe ta muka sake yi ni da autar mu da ta tashi a lokacin, Amsawa tayi suka cigaba da gaysawa da Innar mu,

“Yasu Meenal duk sunanan qalau?”

Innar mu ta tambayi Gwaggo Aminatu,

“Kowa lapia lou Karimatu. Ya Najibu har yanzu bai dawon ba?”

Kamar na fad’awa Gwaggo Aminatu sharrin da akai masa sai dai nayi shiru kawai? Don gudin abinda zai je ya dawo, Kar ta tafi tabar baya da ‘kura. Innar mu tayi murmushi kawai, Domin duk abinda ya danganci Yayan mu bata sa baki saboda kunya ta ‘dan fari.

“Kai! Mikomin akwatin nan”

Gwaggo Aminatu tace dasu Ya Faysal dake bakin kofa a zaune domin dakin ba zai dauki dukkanin mu ba, Kawo akwatin yai ya koma ya tsaya,

“Faysal ma ya taddo Naseer a tsaye TubarkAllah!”

Cewar Innar mu data bi Ya Faysal da kallo lokacin daya kawo akwati, Gwaggo Aminatu tayi murmushi kafin tace,

“Ya fishi ma, Ai shi Naseer tsawon dangin baban sa yayo.”

“TubarkAllah ba lefi kam.”

“Ungo Batoul rike zai isheki ki zuba kayan ki ko? Sanda mu kai waya dake shekaran jia na manta na tambaye ki yadda zai ci.”

“Nagode Gwaggo! Wallahi harna zuba suma a leda.”

Gwaggo Aminatu ta ri’ke haba tana daria,

“Kayan jami’ar acikin leda? ki rufamana asiri kar ayi damu.”

“Nagode k’warai ALLAH ya saka da alkhairi ya kara bud’i Ameen!”

“Ameen Ya Rabbi! Ga dan tarkace nan inji su Meenal, Sunce ace miki suna miki murna, Allah yasa ki fara a sa’a.”

“Ameen ya Allah! Nagode sosai Gwaggo! Allah yabar zumunci. Allah ya yalwata muku arziki ya saka muku da alkhairi Ameen..”

“Ameen Batoul! Me sunana baki da lapia ne?”

Gwaggo Aminatu ta dubi autar mu tana fadin haka. Murmushi nayi ina gyarawa autar mu d’aurin d’ankwalin kanta,

“Daga bacci ta tashi ne yanzu.”

Na fa’dawa gwaggon haka. Hira aka dan yi sama-sama , Gwaggo dasu Ya Naseer suna ta dorani kan yadda zanbi jamia sannu a hankali. Na kuwa ji dadin hakan domin na kad’an ba na karu sosai. Sai bayan anyi magriba su Gwaggo Aminatu suka tafi bayan ta biya ta dakin Bintalo sun gaysa. Naira dubu biyar tabawa Innar mu kan ta sissiyi kayan abinci wadatacce wanda zai da’de mana. Har mota muka rakasu ta babbamu dari bibiyu ni da sauran yaran gidan baki d’aya. Har suka ja mota bandena d’aga musu hannu ba, Zuciya ta kal da ita na shige dakin mu. Ina mai jin da’din samun Gwaggo Aminatu a matsayin yayar mahaifina wadda ke mana son ‘kauna marar gauraye. Allah dai ya dore mana zumuncin mu har gaban abadan..

Bintalo kuwa na daki itada su Alawiyya, Motsi kadan taja tsaki tana rafka tagumi. Wayar Alawiyya ce tai ‘kara ta dauka tana kada idanu tamkar wanda ya bugu mata wayar yana ganin ta,

“Hello sweet! Okay kana waje? Toh gani nan..”

Katse wayar tayi tana yafa yalolon mayafin ta, Fuskar nan tata ta kwailaye taci uban bilicin.

“Baba bara naje na dawo.”

“Toh sai kin dawo, Kada ki manta dai kya ce yasiya mana yar kaza da biredin nan mai laushi.”

“Kai Baba uwar kwadayi, Bara dai naje.”

Ficewa tayi tana rausaya, Ta wuce ta gaban usaiba dake tsaye tana jiran layin ban’daki yazo kanta, Usaiba ta kece da daria tana buga zanin ta,

“An tafi yawon ta zubar, Dan ALLAH a dinga tunani in an girma asan an girma. A hayye kayya kai..”

Alawiyyah taja tsaki ta sauke, Can gaban teburin haladu mai shayi saurayin nata ya tsaya a motar sa, Wajen babu haske kullum anan suke zance, Bayan mota ya bu’de musu suka shjga shi da ita, Babban mutum ne a haife ya haife ta, Sai wani rausayar da murya yake yana kashe mata idanu,

“Alawiyyah ta Alewar zucia ta. Son ki kullum kara luntsuma yake a kogin zucia ta.”

Alawiyyah tayi murmushi tana bankaro masa kirjin ta,

“Alhaji na banki na, Wai yaushe zaka turo ai zancen auren mu ne kai da Mu’azzam ‘kanin ka (saurayin Hinde)?”

“An kusa Alewar zucia ta, Kinsan ginin da ake muku ne maginan dake ginin daga kasar waje muka dakko su, Sati na gaba ma zamu je daku kuga gidajen naku, An kammala ginin kasa sauran na saman.”

Alawiyyah ta dashe baki tana kwantar da murya,

“Sama da ‘kasa ne Alhaji?”

“Tab hawa uku ne ai, Akwai ‘kasa munace masa ondagurawun (underground) da falon ki, Sai na kuma sashin tsakiya me tankama tankaman dakuna uku da falo biyar, Sai saman karshe me dakuna takwas da falo takwas.”

Alawiyyah ta rungume Alhaji tana murna, Ya lakuce kumatun ta yana tande harshe kamar maye. Kasa kasa ya ke mata magana yana sake nanukata ajikin sa,

“Na nawa zan tab’a?”

“Haba Alhaji wannan albishir din da ka gayamin ai yafi kowanne dadi, Taba na nuna godia ta agare ka. Kawai dai Idan zaka tafi ka biya musiyo kaza da biredi.”

Alhaji ya kece da daria yana zura hannun sa a rigar ta, Hade da janyo kofar motar ya rufe su ruf, Dama gilasan duk a rufe suke.....

___

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *_IGIYAR ZATO_.....□_*

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(TAKU NA BIYU)

ZAFAFA BIYAR NA KUDI NE, ME SO DAN GIRMAN ALLAH YA BIYA YA KARANTA HANKALI KWANCE😘❤

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

18

Sai da Alhaji ya jagwalgwala Alawiyyah son ransa sannan ya matsa gefe yana gyara botiran rigar sa. Ya sanya hular sa ya gyaggyara ko’ina sannan ya bude ya koma kujerar tuki yana sai ta mudubi sai tin Alawiyyah.

“Muje ko?”

“Eh Alhaji na..”

Cewar Alawiyya dake zuge zip din rigar ta, Can wajen tukubar nama suka je. Alhaji ya futa ya siyo dakwalan kaji guda biyar, uku daban biyu daban. Ya karb’i biredi guda biyar shima uku daban biyu daban. Mika mata guda bi biyun yai ya ajiye sauran a gaban mota, Lekawa tayi tana hararar ledar.

“Alhaji waccen fa?”

Yamutsa fuska yayi yana baya da motar,

“Ta yarana ce.”

Tsaki ta saki tana zundumawa yaran ashar a zuciar ta. Har kofar gidah ya kai ta,

“Toh Alewar zucia ta, Sai munzo daukar ku ganin gidajen ku ko?”

“Okay Alhaji na, Yadda kace ai hakan za’ai.”

“Haka yake, Toh a gayda min da Hinde taki fitowa mu gaysa saboda bada mutumin ta akazo ba.”

“Ai kuwa dai! To zataji.”

Sumba ta kai masa ya dashe Hakora yana murmushi,

“Godia nake Alawar zucia ta.”

Daga masa hannu tayi ta shige gida tana karkada jiki, Ya ja mota ya tafi kaduna.

GIDAN MATA TARA

Kayan da su Ya Meenal suka bawa Gwaggo Aminatu ta kawomin na shiga dubawa ni da Innar mu da auta. Kayane kala goma cif, Kunce suka bani kuma masu kyawun gani, Wasun su daga ciki ma sababbi ne basu sassasu da yawa ba. Ga takalma shima dede ni dama kusan kanmu d’aya TubarkAllah, Suma kala biyar da jaka ta gayu guda uku sai ta ratayawa a baya ta yan jamia guda biyu. Sai mayafai guda uku da hijabai guda biyu sabbi fil fil. Kayan basu tsaya anan kadai ba. Harda su kayan kwaliya da zanin gado na kwanciya da jakar filo. Da yan kwanuka masu kyau madedeta. Dayar ledar kuma risho ne dan karami dashi sabo acikin kwalin sa, Da fulas na shayi da kular abinci. Sai Indomie zatai guda ashirin da kwamfulas da madara da bonbita. Sai ledar maganin sauro na kunnawa. Saboda tsabar farin ciki mik’ewa nayi na shiga taka rawa ina murna, Innar mu da autar mu sai dariya suke kyalkyala min suma cike da farin ciki. Dan dadi wallahi sai dana zubar da hawayen farin ciki,

“Alhamdulillah! Allah kai ne abun godia. Allah ga bayin ka yadda suka faranta mana ya ALLAH ka faranta musu ninkin ba ninkin namu, Ya ALLAH ka kara musu yalwar arziki da wadatar zuci. Allah ka kare su daga sharrin mutum dana aljan. Ya ALLAH ka biya musu bukatun su dunia da lahira.”

Na fada ina goge hawayen farin ciki,

“Innar mu kalli yadda su ya Meenah suka futo dani, Da me zan saka musu? Wallahi Inna har cikin magudanar jini na nake jin su. Allah ya azurta mu nima na yi musu wani abun.”

“Ameen! Allah ya saka musu da alkhairi. Ki tsaya ki karatu sosai ta yadda zasu ji dadi suma.”

“In Sha Allahu Innar mu.”

Da temakon Innar mu da autar mu na karasa shirya kaya na a akwatin Da Gwaggo Aminatu taba ni, Sai ga Fadila tazo hannunta rike da wata leda cike da kaya itama. Zama tayi a gefe na bayan ta gayda Innar mu. Nunnuna mata kayan da Gwaggo ta kawo min tayi nai. Sosai ta taya ni murna hade da adduar Allah yasa na fara karatun a sa’a. Mun ‘dan taba hira kafin tayi min sallama tatafi bayan na rakata har kofar gidah tana hawaye ina yi. Ledar data kawomin na bude ina nunawa Innar mu.

“La Innar mu kinga itama ta kawomin kayan shayin, Wannan soyayyiyar miya ce. Kai ALLAH sarki Fadilah, Nagode k’warai ALLAH ya dorar mana da zumuncin mu har abada..”

“Ameen ya Allah! Yarinyar kirki. Allah ya shi mata albarka. Maza ki hada karki manta wani abun.”

“Tab Innar mu kenan wallahi kayan sunyi yawa, Ku rike na wajen Fadilan wancen sun isheni ni kadai ce fa. Miyar ma ku diba kwa barmun yar kadan.”

Sam Innar mu taki yadda ta karba, Sai da nai ta mata naci ina had’ata da ALLAH sannan ta dauki kayan shayin. Ta kuma tsakuri miyar yar kadan. A daren dai na shirya kayan tafiya ta tsaf. Safiya kawai nake jira idan ALLAH ya kai mu sai tafiya.

Tuni bacci daddad’a ya dauke mu bayan munci biredi da miyar da Fadilah ta kawomin.

***Alawiyya na shiga daki kuwa tsalle ta dire tana dukan Hinde a takashi, Hinde ta sosa tana mikewa tsaye haka ma Bintalo da Hauwa ganin yadda Alawiyyan ke farin ciki sun san ta samu ne.

“Lasamin naji mana.”

Hinde tafada tana murna, Alawiyya ta lelleka ko’ina kar ajiyo su sannan ta rufe kofar dakin tana jan hannun su suka dawo tsakiyar dakin. Ledojin ta janyo ta kai gaban Bintalo tana murmushi,

“Mu fara da taune ‘kashi kafin kuji kanun labaran.”

“A hayye nanaye..”

Bintalo tafada tana bawa Hinde hannu suka tafa ji kake ‘cassss. Gwaggwafe wa Bintalo tayi ta raba musu naman da biredin, Ba zancen bismilla haka suka tattaune suka cinye suka gyatse. Bintalo ta tsotse diddigaggen kashin tana jujjuya tukar a hannun ta,

“Sittin ta ubangiji bai isheni ba.”

Alawiyya ta yamutsa fuska tana sake karyo biredi kamar jaka. Ta cusa a baki tana cewa,

“Shegun ‘yayan nan nasa zai kai wa wai. Ina jiyo shi yana cewa da Falalu mai kaji wai kashi biyu zeyi, Leda d’aya kaji uku d’ayar kuma kaji biyu. Su zai kai wa ukun ni kuma biyu. Ai da sake wallahi, Ina shiga gidan nan zan fitar da shegiyar matar nan tasa.”

“Haba Alawiyya, ai bama sai kin fad'a ba. Yo irin wannan matayen ai da sun ganki ma zasu bar gidan da kafafuwansu, saboda itama matar tashi tasan kuna da tazara sosai. Kedai Alawiyya kice gaba da faranta masa rai, duk abinda yace kiyi kawai kiyi, dan yasan ma tun yanzu zaki masa biyayya.”

“Ai dama Baba ina masa, shifa baik'i ba, ace yau ya turo magabatansa ayi magana. Abu d'aya ne yake hanashi turowa, yace min so yake sai an gama gini kinsan hawa uku yake yi, kuma nice zan fara shiga, sannan ni zan fara zab'a na darje.”

“Aiyirrrrrr..yirrrrrr..riiiiii, a hayye nanayee. ALLAH na gode maka da ka azurtani da 'ya'ya mata, masu farin jini a kaf gidan *MATA TARA*, Iya gani iya kyalewa wallahi, sunsha tabara sunsha suratul yasin, kuma kurwarsu d'aci gareta. Idan kashi banza ne kaza tayi itama.”

Bintalo ta fito tsakiyar gidan mu tana wannan hayaniyar, wacce tasa baccin da muke yi mai dad'i ya kaurace mana nida wasu mutanan gidan harma da Innar mu. Cikin ikon ALLAH babu wanda ya fito bare ya tanka mata, haka tayi ta habaice-habaicenta ta koma d'aki tana cewa su Alawiyya wai bakin ciki ake musu, shi yasa babu wanda ya fito yi mata ALLAH ya sanya alkairi na murnar da ta fita tana yi.

WASHE GARI

Tunda asubahi na tashi nayi wanka na sake kimtsa kayana, Innar mu kuma ta dora min taliya da manja wacce taji daddawa da albasa. Bayan ta kammala ne ta zuba mana nida Autar mu, muka yi bisimillah muka faraci cikin raina ina tunanin daga yau shikenan bazamu sake cin komai tare da 'yar k'anwata ba sai idan ta dawo gida hutu. Bayan mun kammala ne na tashi na wanko hannuna, na koma d'aki na dauki hijabi nasa sannan nace da Innar mu.

“Bari naje na yiwa su Kawu Khamis sallama, sai nazo na tafi, Suraj yace mu had'u a tashar mota zai sani a wata wadda zai karb'i lambar direban.”

“Toh mai sunan uwa jeki dawo d'in, duk abinda suka gaya miki na 6acin rai karki bari ya zauna a zuciyarki saboda kinga doguwar tafiya zaki yi, kinji ko.?”

“Toh Innar mu.”

Na fad'a sannan na fita, kai tsaye d'akin Kawu Khamis na nufa, nayi sallama daga bakin k'ofar ya amsa min tare da cewa na shiga. Da sallama a bakina tare da dorkusawa kasa na gaida shi, ya amsa min yana ya faman sakace da tsinken tsintsiya, kai kace yaci wata lafiyayyar suyar ne da sassafen nan.

“Kawu Khamis ayi mana addu'a zamu tafi makaranta.”

Sai da ya zare tsinken daga cikin bakin shi, sannan ya kalleni tsab kafin ya maida tsinke yace dani.

“ALLAH yasa da gaske karatun zakije Batoul, nidai babu ruwa na idan kikaje kika lalato rayuwarki. Bazan hanaki tafiya ba, domin 'ya'yana ma ba hanasu abinda suke sonyi nake ba, kije ALLAH ya bada sa'a shikenan abinda zance miki.”

“Na gode Kawu Khamis, ni daman addu'a nake buk'ata daga bakunanku.”

Daga haka na mike ina jin dad'in yadda ya yi min addu'a, sannan nabi sauran dakunan kafin na karasa majalisar Kawu ila wato bakin k'ofar shigowa gidan akan bokitinsa na gado. Tunda ya hangoni ina nufowa gurinsa naga ya had'e rai kai kace zuwa zanyi na rokeshi kudi, na karasa dai zuciyata na lallashi na akan jure duk wani cin kashi da zai min. Har k'asa na durkusa na fara gaishe dashi amman fur yaki amsawa, ganin haka yasa na dora da abinda ya kaini gurinsa.

“Kawu ila zan tafi makaranta ina bukatar addu'arka.”

Kamar daman jirana yake na furta hakan, cikin fad'a da masifa tare da hargagi ya fara magana.

“Karya kike yi munafukar yarinya, ba bu wata addu'a ta da kika zo nema. Ni zaki rainawa hankali? Da kinso addu'ar tawa mai ya hanaki tunda aka fara zancen zakije baki zo kin same ni ba na baki shawara da kuma addu'ar a matsayina na d'an uwan mahaifinki, shine sai yanzu zaki tafi yawan ki na shaid'anci daman ga d'an uwanki can yaje ya dad'a koyowa yazo ya fara bata mana yara, shine ke ma kika zo salon na tofa wata maganar, kije ki dawo da cikkunan shege ace nine na miki addu'a. Toh ba zanyi ba, tashi ki bani waje, ALLAH ya raka taki gona.”

Duk iya k'ok'ari na wajan danne zuciya ta sai da na kasa, wani irin kuka yazo min nayi saurin sannya tafukan hannayena na toshe tare da rugawa da gudu na haye sama. Ina shiga na soma k'ok'arin had'iye kukan amman sai da ya bayyana.

“Sai da nace ki daure da duk abinda zasu gaya miki, musamman ma shi Ilyasu da ba kaunarmu yake yi ba. Tashi ki wanke fuskarki kizo ki tafi kar yaron can yayi ta jiranki”

Jikina a sanyaye na mike na gyara fuskata. Karfe takwas da mintuna hud'u agogon wayata ya nuna, a kuma lokacin ne Suraj ya bugo min, na dauka bayan nayi masa sallama yace na fito ni yake jira, na amsa masa tare da maida wayar cikin jakata da gwaggo Aminatu ta kawo min. Kayan na dauka na yiwa Inna sallama, sai naga ta sanyo hijabi tana cewa ai zata rakani har tasha sai ta dawo. Naji dad'i kuwa, daga nan muka fito harda Autar mu. Muna cikin sakkowa sai ga 'yan gidan mu sun firfito suna ta kallon mu kamar wasu bakin fuska, sai da muka gama sakkowa zuwa kasa mukaji muryar Bintalo tana cewa.

“Ohh la'ilaha'illallahu, wannan duniyar tamu tazo karshen d'anewa. Ku duba min ku gani, yau Kaltume da kanta zata kai 'yar cikinta tashar 'yan iska, to dai idan an kunso abin kunya kar a sake a dawo mana gidan nan ahe!.”

“Ahaiyeee nanaye babu mijin aure za'a tafi rakashewa.”

Cewar Ummita matar Kawu ila ta farko. Shi kuwa yana bakin k'ofar ya babbake yasa k'afarsa alamun bazamu fita ba, sai da Innar mu ta sanyayya tace masa.

“Zamu wuce.”

“Toh Kaltume ku wuce”

Ya fada yana sake tare hanyar. Inna ta kalleshi sosai taga ya murtuke fuskarsa tamkar ba'a sanya mishi dariya ba a cikin tsarin halittar sa.

“Ke yanzu Kaltume da kanki zaki kai yarinyarki jami'a? Kuma bama zuwa zata yi tana dawowa ba, a'a kwana zata dinga yi a can ke babu abinda ya dameki ko?”

Kawu ila ya fad'a yana kallan Innar mu wacce itama shi take yiwa kallon kaji dashi.

“Indai nice toh na amince mata taje duk inda zata neman ilimi ba zan hanata ba, karka manta ko barinta nayi anan kafi kowa aibata min ita, to yanzu zata yi nisa daku, yadda bakunanku zasu huta akan ta, kuma indai bakin ku ba zai furta mata kalmar alkairi ba, toh ku barshi amman tafi kam kamar tayi ne”

Innar mu na kaiwa nan ta nufi hanyar da nufin idan bai dauke kafarsa ba zata hamb'are shi mu wuce. Cikin tsananin mamaki dajin irin kalaman da Inna ta gayawa Kawu ila, yana zaro ido yaga ta nufoshi, da sauri yaja baya, yadda yayin yaso bani dariya saboda naga alamun tsoro a tare dashi. Amman dan karna janyo wata matsala sai na had'iye dariyar muka bi bayan Inna mu wacce tuni ta fice ranta a b'ace.

Muna tafiya Innar mu na sake jamin kunne akan kula da kaina, nayi mata alkawarin insha Allahu zan yi yadda take so, a haka har mukaje tasha inda muka tarar da Suraj yana ta kalle-kalle da alama ni yake nema. Karasawa wajan shi muka yi, ya gaida Innar mu sannan ya nuna min motar da zan shiga. Kayan ya karba ya sanya a booth, sannan aka ce na shiga, a lokacin ne naji wasu zafafan hawaye sun biyo saman kumatuna, na rungume Innar mu wacce itama kukan yake shirin kwacewa.

“Sai hakuri mai sunan uwa, ayi ta hakuri aje a dawo. ALLAH ya bada sa'a yasa a samu abinda akaje nema.”

Daga haka Innar mu ta b'anb'aroni daga jikinta, taso taga tafiyar mu, amman yadda taga ina kuka yasa ba zata iya jura ba, taja hannun Autar mu suka tafi babu ko waiwaye daga ita har Autar tamu. Na san kuma Inna ce zata hanata waigowa saboda kar suga yanayi na. Na kalli Suraj cikin share hawaye nayi masa godiya da addu'a ta gamawa da duniya lafiya.

“Babu komai Batoul, ALLAH dai ya baku nasara gabaki d'aya keda mutumin.”

Murmushi nayi masa bance komai ba, mota na shiga na zauna. Har muka tafi Suraj na gurin, na dinga jinjina irin amincin sa domin banyi tsammanin zai rik'e alkawarin da Haysam ya bashi akai na ba.

BATOUL TABAR BAYA DA K'URA

Tunda wannan abun ya faru muka bar gidan, shikenan Kawu ila ya dinga surfa masifa yana tsine musu albarka. Kowa na gidan yayi tsit ko Bintalo da ta take d'an taya shi, itama yanzun shiru tayi saboda babu wanda yayi tsammanin Inna zata iya shafawa idanunta toka ta zazzaga bayanan nan. Bokitinsa na gado ya jawo ya zauna yana huci kamar wani kumurci, ya karewa mutanan wajan kallo tsab kafin ya mike yana yafufo Bintalo da hannu alamun tazo. Tana karasawa ya matsala gab da ita a saitin kunnanta yana cewa.

“Ni babu wanda zai kawo min wulak'anci a cikin gidan nan wallahi, kinga Bintalo yau dole a tona asirin da ake rufewa nasu Kaltume.”

“Babu shakka, ai daman kaine kaki yadda tuntuni ayi komai a gaba. Yanzu mai kake so ayi?”

Kawu ila yaja Numfashi ya sauke, ya kuma komawa kan bokitinsa ya zauna yana hura iskar cikin bakin shi tana fitowa waje yace.

“Gidan Alhaji Kabeer Wafa zakije, ina nufin gidan da Kaltume take aikatau, idan baki fahimce ni ba, ina nufin gidan su wannan d'an iskan yaron ya biya kud'in d'akin da zasu zauna idan taje jami'ar suyi masha'arsu. Can zaki ki warwarewa asararrun iyayensa abinda yake faruwa. Bintalo karkije kiyi min ba dai-dai ba a gidan can, sittin ta alkur'ani zamu raba k'afa dake. Duk wani iskanci da kika san ana yi, da irin kayan da yake kawo musu duk ki fad'a, kafin Kaltumen ta dawo ta same ni anan wajan.”

“An gama Kawu na kowa, ALLAH yaja da ranka yayi k'asa-k'asa da idanun makiyanka, bari naje na dawo.”

Bintalo tayi maganar tana mai juyawa ta koma sama cikin d'aki ta dakko mayafi.

“Ayi dai mu gani idan tusa zata hura wuta, kuma duk sharrin mai sharri kansa yake komawa, kowa yasan masu bin maza a gidan nan. A hayye kayya kai... Ana yi muna jin dad'i, ana bari muna jin haushi billahillazi.”

Usaiba ta fad'a tana daga matakalar bene na uku. Bintalo da ta kusa kaiwa fita daga kofa ta juyo tana shirin cire mayafi, da sauri kawu ila ya dakatar da ita ta hanyar cewa.

“Yi tafiyar ki Bintalon mu, kinsan ai idan d'an tasha yana baka kayan tashancin da yayo, toh komai za'a ce d'an tashar yayi shi wanda ake bawa ba zai yadda ba har sai lokacin da aka yi masa abinda ranshi baya so. Wuce kije, ALLAH ya baki nasara.”

Bintalo kuwa ta juya ta fita, yayin da Ummita ta harareshi tana hura masa hanci kamar zata rufe shi da duka. Cikin d'akin ta ta koma tana la'antar su, saboda mijin nata ko ita baya bawa umarni kamar yadda komai ya jajibo sai ya fara yiwa Bintalo. Nan fa guri ya kaure da gutsiri tsoma, kowa ya fara fadar albarkacin bakinsa.

—

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IGIYAR ZATO...

_*19_*

Yadda kukasan sabuwar mahaukaciya haka Bintalo ke tafe akan hanyar gidan su Haysam. Tana tafe tana magana ita kadai tana watsa hannu baya, Dayan hannun kuma tana sosa takashi,

“Sittin ta ubangiji ba zata sab’u ba. Y’ar ‘kundin uba, Sun gama kai sunan sa dana iyayen sa. Yo neme shi su kai m..”

Bata k’arasa ba sakamakon shan gabanta da wata mata tayi, Zasu yi sa’anni d’aya da alamun ma kawar ta ce.

“Ah Bintalo ina zaki ne kike ta magana ke kadai? “

“Hmm! Kede bari Ruma. Gidan Alhaji kabeer wafa zani ayi ta ta ‘kare.”

Ruman ta zare idanu tana dafe kirji,

“Me zakiyo agidan Haj Husnah?”

“Sittin ta ubangiji zuwa zanyi na ceto su daga hannun mayun gidan mu.”

Ruma tayi daria tana buga zani. Bintalo tai murmushi tana sosa takashi,

“Yasin tsutsa ce ke damu na, Yar kund’un uba ina komawa zan cusa mata marsaleta”

“A hayye! Shi yasa naga kina soshe soshe. Bakin kasuwa zani ko zan samu na tsiren dare.”

“Uhm! Nima fa so nake na kauda su Alawiyyah daga gaba na nayi auren nan a matse nake sittin ta ubangiji.”

Ruma tayi tsalle ta dire tana watsa hannu baya,

“A hayye! Har mula yadi (atamfa) zamu fitar muyi anko, Yasin cakarewa zamu yi. A hayye.”

Bintalo ta bata hannu suka tafa, Daga nan sukai sallama ita Ruma tatafi bakin kasuwa, Bintalo kuma ta cigaba da tafiya tana gwaggwafewa hade da cusa hannu ta sosa takashin ta dake radad’in tsutsa. Dakyar ta karasa gidan su Haysam tana harharde kafafu.

Tunda Bintalo ta shiga gidan Alhaji Kabeer ta fara kalle-kalle tana jinjina kai alamar girmama tsaurin ido irin na Batoul da har take mafarkin zama 'yar gidan. Da karfi ta dinga kwad'a sallama taji shiru, ta sake bud'e murya, kafin ta bud'e bakinta Inna Rabi ta fito daga wani d'an corridor tana amsawa. Ta dubi Inna Rabi ta mata kallon tara saura kwata ta watsar zata shiga cikin gidan Inna Rabi ta tsaida ita,

“Baiwar Allah sannu, daga ina haka?”

''Yauwa sannunki, Hajiyar bata nan ne?''

''Tana nan, amman dai bata tashi daga bacci ba, sai dai kije ki dawo zuwa anjima, lokacin nasan ta fito parlourn ta.''

Bintalo ta yatsina fuska cikin ranta tana girmama jin dad'in da Hajiya Husna keji, ace wai har zuwa yanzu mutum bai tashi ba. Kuma abin k'arin mamakin shine, matar gidan ce bata tashi daga bacci ba, tana kwance ana yi mata komai saboda jin dad'i.

“Toh baiwar Allah ko matar gidan tasan da zuwan ki ne?”

“Zanzo gamon kai na ne? Ai kema kinsan dole da akwai wani abun. Bama wannan ba. Shin kinsan kaltume me aiki anan?”

Inna Rabi tayi murmushin jin dadin Bintalo ta ambaci Kaltume mahaifiyar su batoul, Domin suna zaman mutinci silar aikatau din da suke tare. Cike da farin ciki Inna Rabi tace,

“Eh na santa. Da kinyi bayani t..”

“Ya isa Babah ba neman karin bayani nake ba. Daga ambatar sunan shegiyar matar nan har kin fara murmushi, Tab sittin ta ubangiji kema ta ha’da da sunan ki awajen boka. Ki taimaka ki taso min ita, magana ce nazo da ita mai matuk'ar muhimmanci akan Hashimu.”

“Waye kuma Hashimu?”

“D'anta mana, da yace ya tafi k'asar waje dan karya.”

Cewar Bintalo tana kallon k'ofar da take da yak'inin cewar nan ne Hajiya Husnah ke bacci. Inna Rabi ta gyara tsayuwa tare da cewa.

“Gaskiya sai dai ki hakura sai zuwa anjima, bana shigar mata d'akin baccinta, sannan zuwa na tashinta zai iya janyo min rasa aikina a gidan nan. Kije ki dawo kawai.”

Wani banzan kallo Bintalo ta aikawa da Inna Rabi na baki isaba, sannan ta sake wage murya tana kiran.

“Hajiya.. Hajiya.. Hajiya kinyi bakuwa.”

Inna Rabi ta dafe hab’a tana cigaba da kallon Bintalo, Sosai take mamakinta. Ajiyar zucia ta sauke tana jinjina kai,

“Toh Kaltume dai bata zo aiki yau ba a.”

“Dakata Baba. Ya isa, ba Kaltume nake nema ba! Nuna min kofar shiga ciki kawai”

Inna Rabi tayi shiru tana tunanin abinda zata gayawa Bintalo kada ta shiga ciki, Domin kallo d’aya zakai wa Bintalo kasan sharri zata had'a.

“Gaskia kiyi hak’uri baiwar Allah! An hanamu shiga sashen matan gidan. Kinga tafiya ta ni, bazaki jazamin masifa ba ina zaman zamana lafiya.”

Inna Rabi ta fad'a tana saurin barin wajan dan kar Hajiya Husnah tazo ta ganta tace tana sane ta janyo mata hayaniya.

‘Mtcew! Bintalo taja tsaki tana bugawa Inna Rabi zani, Tana tafe tana susar takashi haka ta karasa wajan Haj Husna, Irin kofar nan ce wadda ake janta ta bud'e (sliding door) Ta dubi kofar tana dafe haba, Kamar mudubi haka k’ofar take, Ta dubi kanta tana zare idanu, Hannu tasa tana nuna ‘kofar tana kallon jikin ta,

“‘Dan ‘kundin uba. Yasin karya kake kace haka kamanni na suke..”

Ta fad’a tana yiwa kofar dakuwa, Kasan mayafin ta ta nannade ta shiga durza hakoran ta na gaba tana kara matsawa kusa da kofar,

“Sittin ta ubangiji sunyi jajur kodan saboda goro ne. Gwara na goge kar matar gidan tayi tsantsami na.”

Duddurje hak’orin ta tayi sosai sannan ta gyara zaman mayafin ta. Kasa taba kofar tayi ta tsaya tana cizan lebe,

“Nashiga uku ni Bintalo, Ya ake budewa ne? Karfa naje na fasa musu su lakadamin na jaki.”

Matsawa tayi tana hangen gidan ko zata gano wani, Cikin sa’a ta hangi wani yaro yana baiwa fulawa ruwa, Yafito shi tayi da hannu ya taho,

“Nan kofa ce?”

“Eh tura ta zaki.”

Ido ta ware tana dafe kirji,

“Rufamin asiri haka kawai naje na fasa musu a gark’ame ni a folisitashon (police station).”

Yayi daria kawai yana girgiza kai, Hannun sa yasa ya tura kofar ta budu, Mamaki Bintalo tayi tana jaddada kai, Shiga ciki tayi tana bin ko’ina da kallo,

“Dankari Mak’ari! Aljannar duniya kenan. Kai kai kai. Kudi yayi kuka anan gidan.”

Ta karasa fada tana shafa kujerun. Harda su lumshe idanu ta zauna akai tana nanata,

“Bara na zauna na dandali arziki. Wohoho gidan masu hannu da shuni akwai dadi. Su Alawiyyah nama fa an kusa shiga daga ciki a hayye.”

Ta karasa fada tana sosa takashin ta, Ta taskawa takashin nata duka cike da takaici,

“Yar ‘kundin uban tsutsar nan sittin ta ubangiji ina komawa gida zan balle kan shegiya..”

Ta karasa fada tana sake dadawa takashin ta duka ji kake d'ass. Ai kuwa Bintalo tana daga zaune ta dinga kiran Hajiya Husnah tana d'an waige-waige, babu b'ata lokaci kuwa sai gata ta fito tana yatsina tana kumbura fuska. Haj Husnah ta sakko daga sama, Ta dubi Bintalo dake kan kujera a hakimce ta dalla mata harara, ba shiri Bintalo ta sauka daga kan kujerar tana sosa kanta. Zama Haj Husnah tayi akan doguwar kujera tana mata kallon ‘kask'anci. Bintalo ta fara matsawa kusa da ita tana dashe hakora. Haj Husnah ta dakatar da ita tana daga mata hannu,

“Hajiya an tashi lafiya?”

“Kin dai tashe ni, da uwar safiyar nan, daga ina? Wacece ke?”

Bintalo ta kuma washe hakora tare da jingina bayanta jikin kujera tace.

“Ai Hajiya mu 'yan nan unguwar ne, amman mu muna daga can layin Gali mai shago. In takaice miki dai ni a gidan *Mata tara* nake, gidan su mai aikin ki Kaltume.”

“Sai kuma aka yi yaya? Ko yanzu ma bata da lafiya ta turo ki? Dan naga yanzu haka take yi min, ta turo 'yar na hakura toh itama 'yar tace makaranta zata koma shine kema ta turo minke?”

Dafe kirji Bintalo tayi tana gwalo ido, cikin girgiza kai take cewa.

“Wallahi ba ita ta turo ni ba, ai wannan matar 'yar bakin ciki ce Hajiya, ko ciwon mutuwa take yi ba zata turo wani ba idan ba 'ya'yanta ba s...”

“Ya isheni, fad'i abinda ya kawoki, kar dai kice min taimako kika zo nema saboda kinsan ranar laraba ake yin sadakar kudi a gidan nan.”

Da sauri Bintalo tace.

“A'ah a'afa Hajiya, wannan batun da nazo gaya miki yaci uban kud'in taimakon da ake bayarwa ranar laraba. Bari kiji idan kudi na banki ma, wallahi tallahi zakije yanzu ki d'ebo dan kawai ki bani tukwici.”

“Ina jinki, ya aka yi?”

Bintalo aka tankwashe kafafuwa tamkar wace zata ci farfesu, ta dora da cewa.

“Wato Hajiya kina nan kina tarbiyantar da d'anki, ana daga waje ana lalata miki shi, koda yake ba yin kanshi bane ba sharrin sihiri ne.”

“Uhumm, ina jinki.”

“Wato Hajiya d'anki Hashimu a...”

“Badai Hashimu ba, kodai Haysam.”

“Kwarai kuwa sunan ne Hajiya, ihi..ihi ai kinsan da yake sunan ne irin na 'yan gayu. Toh in gaya miki su Kaltume sai tatsarsa suke yi, karki so kiga yadda yake yiwa 'yar b'arin kudi, kamar shuka su yayi yana zuwa d'ebowa. Na takaice miki labari Hajiya, ya samarwa Batoul makaranta daga can zasu dinga had'uwa. Wallahi Hajiya har kamo junansu suke yi, bamu yadda ba da sai yanzu da yarinya ta kafe cewar ita fa sai taje kuma duk tabi 'yan uwan mahaifinta ta zagesu tasss, Kaltume ta taya mata.”

“La'ilaha'illallahu ni Asma'u, Haba! Shi yasa yaron nan yake kasa yin sakat idan yarinyar tazo aiki gidan nan. Ooh ashe kullalliya suka shiryo min suna son su mallake min d'ah, toh ba zai yiwu ba, wallahi nafi karfin su koda k'asar shuri suke yawo nasha gabansu. Kinga baiwar ALLAH muna ta zuba zance ko sunanki ban sani ba.”

Bintalo ta sake bajewa jin yadda Hajiya Husnah tayi amanna da zancenta, sannan ta dashare baki tace.

“Hajiya kira ni da Bintalo domin dashi kowa yafi sani na, ko alheri zaki aika min kice ace ina Bintalo uwar Alawiyya, Hinde da kuma Hauwa'u, nice uwar mata masu farar laya.”

Kai Hajiya Husnah ta jinjina sannan ta cije leb'e da hakoranta. Numfashi taja ta kalli Bintalo tana fad'in.

“Na gode kwarai da wannan batun da kika zo min dashi, kinga nima sai na tashi tsaye akan su, domin d'ana bakalar 'yarsu bace. Kije gida zan yo miki aike na ladan zuwa tonawa matsiyatan can asiri, amman yanzu Haysam yana k'asar waje mu da kanmu muka kaishi airport sai da jirgin su ya tashi sannan muka taho. Ina kyautata zaton sun mallake min shi ne saboda ya zama saniyar tatsar su, toh wallahi basu isa ba. Makarantar da ta tafi kuma sasan uban da zai bata kudin karasawa.”

“Ai kuwa dai Hajiya, gara ki tashi tsaye dan Kaltume summun mukasau ce, (green snake), tana yin abubuwa na mugunta a cikin wannan salon nata na suffar salihai. Zan tafi Hajiya sai naji tukwici, ALLAH ya kara rufa muku asiri fiye da wannan wanda kuke ciki.”

Hajiya Husnah bata ce komai ba saboda tsantsar mamakin da ya kamata, lallai biri yayi kama da mutum, ashe kullalliya aka shirya mata akan d'an ta, shi yasa kila taga ko magana ta yiwa Batoul ko Inna indai na fad'a ne sai Haysam din ya nuna beji dad'i ba, ashe an asirce mata shi bata sani ba. Dole ta mike tsaye tasan duk yadda zata yi wajan raba idanuwan Haysam akan Batoul. Zuzzurfan tunani ta shiga, wanda yasa bata san lokacin da Bintalo tabar gidan ba.

Ita kuwa Inna suna dawowa ta nufi gidan aikinta, a cewar ta ba zata koma gida ba su b'ata mata rai ta kasa fitowa aikin. Tana zuwa ta ajiye Autar ta a can inda ake ajiye motoci tace karta sake taje ko'ina ta jira anan ta gama tazo su tafi. Juyawa tayi ta nufi cikin gidan bakinta dauke da sallama...

—

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *_IGIYAR ZATO_.....□_*

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(TAKU NA BIYU)

ZAFAFA BIYAR NA KUDI NE, ME SO DAN GIRMAN ALLAH YA BIYA YA KARANTA HANKALI KWANCE😘❤

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

20

Kuma yin wata sallamar tayi da taji shiru, Haj Husnah dake hakimce a kan kujera suna waya da wata kawarta tana gaya mata duk labarin da Bintalo ta gaya mata, jiyo muryar Kaltume na sallama yasa ta katse kiran. Ba tare da ta amsa mata ba, ta kwad'a mata kira cikin d'aga murya. Inna ta jiyo ana kiranta daga cikin parlour, hakan yasa ta nufi wajan fuskarta d'auke da kwantaccen murmushi, ta shiga ta durkusa daga bakin k'ofa tana gaishe da ita.

“Dakata min malama.”

Haj Husnah ta katse gaisuwar da Inna take yi mata, kanta a sunkuye tana jiran taji wane irin kwandon rashin mutunci za'a sauke mata yanzu, duba da yadda taji Hajiyar na yi mata magana.

“Toh yau duk wani kullin da kuke yi min keda 'yarki, an kwance min shi tass! Ke yanzu Kaltume banda cusa kai ina ke ina had'a jini da mu? Ki rasa ta inda zaki cucuni sai akan yaro na? Toh wallahi tallahi, idan ma jaki kuka binne, yau kuje ku tonoshi.”

Cikin rashin fahimtar inda maganar ta dosa, Inna ta d'ago kai tana kallon Haj Husnah.

“Kiyi hakuri Hajiya, amman wallahi ban fahimci inda maganar taki ta nufa ba, wane jakin aka rufe?”

Cikin b'acin rai Haj Husnah ta harari Inna, tare da cewa.

“Ki rufe min baki, yau asirinku ya tonu. Haysam ne ya zamar muku saniyar tatsa ko? Duk da kud'in watan da ake baki na aikin ki, ga kudin sadaka duk laraba da ake baku, amman sai kin janyo ra'ayin d'ana yayi muku abubuwan da koshi yi masa ake yi. Har Batoul ya biyawa kud'in makaranta, amman tsabar munafinci baki yi min zancen ba bare ki gode masa a gabana. Toh daga yauma kin dena aiki a cikin gidan nan, karna sake ganin k'afarki a cikin gidan nan. Sannan kuma ko kud'in watanki ba zan bayar ba, kunci kudinku na gurin Haysam, tashi ki b'ace min a nan wajan.”

Jikin Inna har rawa yake yi, saboda tsabar shiga cikin tashin hankali. Sai dai bata musawa Haj Husnah ba, ta mik'e kamar zata dora hannu aka ta fashe da kuka, amman ta jure ta sa takalmanta tayo waje inda ta samu Autar ta zaune tana ta wasanta ita kadai. Kamo ta tayi suka fita daga gidan zuwa gidan Mata tara.

GIDAN MATA TARA

Tunda Inna ta sanya kafarta cikin zauran gidan taji yo shewar su tasan suna cikin farin ciki, kome ya sanya su wannan jin dad'in oho. Ciki-ciki tayi sallamar ta shiga, ba ta kula kowa ba tana rik'e da hannun Autar ta suka fara k'ok'arin hawa sama,Da sauri Hafsatu matar kawu Dawood tayi saurin tare Inna wacce idanunta ke kallon k'asa.

“Wallahi Kaltume kin bani mamaki, wai da hannunki kije kisa sanya d'iyarki a mota ta tafi karuwanci. Kin lalace wallahi da son kud'i Kaltume, bayan kinsan shi arzik'i nufin ALLAH ne, yanzu idan ta kawo miki d'an shege ko 'ya zaki rik'e ne?”

“Kaji wani shirme a wajan Hansatu.”

Cewar Bintalo dake karkace baki ta dora da cewa.

“Ahhh ba ta saba rainon shegun ba? ko kin manta cewar suma Najibu da Batoul d'in babu tabbacin suna da sahihin uba. Tsab zata raini abubuwanta, ita ai yanzu so take kawai tayi arzik'i, a hayyeee nanayeee.”

Hafsatu ta buga tsakiyar zaninta, tare da dora yatsu biyu a saman katon hancinta tana gud'a.

“Aiyirrrrrrr shagali, kwarai kuwa na tuna Bintalo, wannan shi ake kira tuwo na mai na. 'Ya'ya shegu jikoki shegu, ALLAH ya shirya.”

“Amin.”

Sukaji Inna ta fad'a tare da ture Hafsatu gefe ta haye cikin sauri zuciyarta na barazanar fad'owa saboda tsabar tashin hankali. Gefe d'aya ta zauna bayan ta shiga d'akin ta, ta rungume 'yar autar 'yarta hawaye na zuba daga cikin idanuwanta zuwa kasa. Ta rasa wace irin rayuwa ce ALLAH ya zab'ar mata ita da yaranta, a ce kaf cikin dangi na kusa-kusa babu mai kallon su da mutunci bare a tuna maraicin su. Muryar kawu Ishaq taji yana kiranta daga can k'asa, amman tayi shiru saboda ba

tason suci mata mutunci a gaban yara, dan a yadda yake kiran zai tabbatar maka da cewa rashin mutunci zasu yi mata.

“Ka dauka ni kawai ta raina a cikin ku? Ai kowa yanzu ganinsa kawai Kaltume keyi, amman babu wata maganar girmamawa”

Inji kawu ila yana tabbatarwa da kawu Ishaq cewar Inna bata da kunya. Tana jiyo yadda suke ci musu mutunci amman bata kula ba, a cikin maganganun nasu ne ma ta jiyo cewar ashe Bintalo ce taje ta fad'i karya da gaskiya a gidan Alhaji Kabeer wafa. Inna ta dinga girgiza kai saboda al'ajabi. Shi kenan sun rabata da aikin ta, kuma babu wanda zai kula da rayuwa ta da ta yaranta idan ba ALLAH ba, kuma yanzu zata sake kai kukanta garesa domin shine yasan gaskiyar zuciyarta.

Tunda wannan abun ya faru, shikenan wulak'anci ya karu akan Inna. Kowa ya kwaso iskancinsa sai ya juye a kanta, haka zata jure dan ma dai tana da hakuri ba komai take tankawa ba.

BATOUL.

(ABU SAMARU CAMPUS)

Toh masu karatu, A shafin baya wasu daga cikin ku sun shiga rud’ani kan tayaya Batoul tana zaria kuma ace ta hau motar zuwa ABU ZARIA? Toh duk da dai na bawa masu tambayan amsar su har sun gane sune su kai kuskuren fahimtar a d’aya daga cikin comments grp dinmu. Hakan yasanya kuma zan muku bayani domin cire rud’ani (To avoid confusion upon confusion)😂□□

Ba mistake bane. Kaf igiyar zato ba inda aka saka unguwar su Batoul bare sunan area din da suke. Saboda yanayin tsarin gidan da suke ma da yanayin rayuwar plus gundarin labarin a gaba yake. Toh da farko dai A LIMANCIN KONA suke, Sannan ABU ZARIA guda biyu ce. Akwai SAMARU shine MAIN CAMPUS akwai kuma na CONGO shine ANNEX.

SANNAN DAGA UNGUWAR SU TA *LIMANCIN KONA* SUKA TAKO DA KAFA ITA DA INNAR MU DA AUTAR MU ZUWA KASUWAR ZARIA INDA SURAJ YA TARAR MATA MOTAN *PZ* DA GA NAN MAI MOTA YA KAITA INDA AKE LODIN SAMARU COMPUS□□

Batoul kuwa cikin nasara ta isa ABU, (samaru campus) bata sha wahalar wasu abubuwan ba, saboda ta tarar da sababbin zuwa da yawa hakan yasa ta shiga cikin su har sai da ta samu hostel din da zata zauna wato *Amina hostel, Samaru campus*. Zuciyarta cike da tunanin Inna da kanwarta a haka ta gama shirya gadon ta da kayanta cike da kewar su.

BAYAN WANI LOKACI.

Tun lokacin da Bintalo tayi sanadin barin Inna daga gidan Alhaji Kabeer wafa, shine ita kuma da shishigi da kai zancen karya da gaskiya ta samu ta maye gurbin aikin Inna a gidan. Ai kuwa tunda ta fara aiki komai na ta ya sake gyaruwa saboda komai ta kyalla ido ta gani anyi wasarairai da shi a gidan, toh insha Allahu sunansa satacce, da ta kyalle ido taga ba'a ganinta zata zabare takai gida.

Ita kuwa Kaltume rayuwa ta sake yi musu zafi, ta buga ta bincika amman bata samu wani aikin da zata yi ba, ya zamana ko garin kwakin da zata had'awa Autar ta gagarar su yake yi. Wannan halin kuma ta da tsinci kanta a ciki ya yiwa ilahirin gidan mata tara dad'i domin basu da buri irin suga d'aya daga cikin gidan ya shiga kuncin rayuwa. Gashi ita Inna daman ba wani maula ta iya ba, bare ta dinga zuwa gidajen mutane tana neman taimako.

A yau ne ta kama su Alawiyya zasu je gano gidajen da samarin su suka ce zasu kaisu su gano. Bintalo sai murna ake ana yada habaici ana shewa a tsakar gida. Su kuwa su Alawiyya sai kara gyaggyara wa suke yi suna kara lafta hoda da gyatuma rad’au bakin su. Hinde ta dakko dankwalin ta na wata atamfa ta raba shi biyu tana cusa shi a kasan kirjin ta domin dago dasu, Alawiyyah ta kece da daria tana nuna kirjin Hinde,

“Duk kwaliiyar ganin Mu’azzam din ce?”

Hinde tayi fari da idanu tana girgiza,

“Iyyi! Ke kuwa harda sirikai fa zasu ganka gwara ka shirya.”

“Ai kuwa dai nima bari na ‘danyi cikon nan.”

Ta karasa fada tana dariya, Dariya Hinde ta ‘babbake itama tana sake lafta kayan cikon, Alawiyyah ma skirt uku ta ‘dora acikin zanin kayan jikin ta. Suna saka takalman a temaki wada, Kansu kuma zare-zaren jikin mayafin gyale suka soka a cikin ‘daurin yayi kamar gashi. A haka suka fara sakkowa daga bene suna taku ‘dai-dai tamkar yammatan agwagwa. Bintalo dake mattakalar bene ganin su yasa ta kara callara kara tana buga zani hade da shewa,

“A hayye nanaye! Sittin ta ubangiji kaf gidan mata tara babu kyawawan ‘yaya masu kalar matan manya da samari masu hannu da shuni irin su Hinde na. An buga daku an barku, An buga ‘kasa an nuno ku sittin ta ubangiji babu mahaluki a gidan nan daya zarta ku komai, A hayye nanaye..!”

Ta karasa kirarin tana taka rawa, Baba Usaiba dake tattare kayan shanyar ta a kusa da Bintalo ta buga tsaki ta haye sama cikin sassarfa. Kawu ila ma dake kan bokitin zaman sa sai kwararawa su Alawiyyah kirari yake yi yana tafa hannaye,

“Kaga dangin tsatson farin jini, Kaga wanda samari kewa layi a kofar gidah, Kaga wa’enda kuttin farin jini ya fashewa, Kaga ‘yayan iri na albarka, Gaisuwar ban girma gare ku, Allah ya kai ku a sa’a ya dawo mana daku lapia.”

Bintalo taja guda ta saki tana kururuwa,

“A hayye nanaye! Ameen kawun su. Fadi da kyau ka kara da karfi. Nasan anacan an haye kan buzu ana narka bakar addua, Toh bakunan ku su sari danyan kashi. A hayye na gaba yayi gaba wallahi na baya sai labari, Kai labarin ma ba wanda zai bayar. Me za’a fada banda tarin tsiya da shegan taka? A hayye nanaye!”

Har kofar gidah Bintalo ta raka su tana daga masu hannu, Alhazawan su suka dauke su sai hanyar kaduna. Ita kuma ta koma ciki tana cigaba da yada magana.

KADUNA

Alhaji Labaran Tumbin kudi shine sunan Alhajin Alawiyyah, Sai Mu’azzam kanin sa a cewar su. Alhaji Labaran dai sanadiyyar had’uwar su dasu Alawiyyah a yar kasuwar zaria ce. Alhajin da Mu’azzamun suka hada bakin su yan uwa ne na jini, Nan dai su Alawiyyah mai idanun cin nera ba tare da wani bincike ba suka fara lulawa duniyar soyayya.

Gate din wani gidah Alhaji ya zura kan motar sa, Gidan ba ginanne bane, An dai gama wasu sashen dake cikin sa (uncompleted building). Alawiyyah da Hinde suka hangame bakuna suna bin gidan da kallo. Lalle naira tayi kuka.

“Wohoho! Alhaji na gi..Gidan ne nan?”

Alhaji ya shafa tumbin sa yana gyatsewa,

“Iyyi Alewata, Gidan ku ne nan ke da Hinde.”

Alhaji Mu’azzam ya murmusa yana nunawa Hinde dayan sashen da hannu,

“Kinga can shine naki. Yanzu ake ginin..”

Hinde ta buga tsalle, Har kullin cikon ta ya kusa fadowa ta maidashi tana daria,

“Dankari Mak’ari! Yasin ji nake kamar mafarki.”

A tare suka shige cikin wani sashe, Shiru ba ma’aikata a gidan gaba d’aya. Alawiyyah ta dubi Alhaji labaran,

“Ina ma’aikatan kuma?”

Alhaji labaran ya sosa k’eya yana murmushi,

“Sun je gano gida su dawo.”

Alawiyyah ta dafe kirji tana zare idanu,

“Kasar wajen suka koma? Jar uban can! Lalle kudi na aiki.”

Alhaji labaran da Mu’azzam suka tafa hannaye suna kyalkyalewa da dariya. Cikin wani babban parlor suka shiga babu komai cikin sa sai taburma da kayan abinci fal akanta.

“Bismillah! Ku fara ci kafin muje wajen su hajian ko?”

Daga kai Alawiyyah da Hinde su kai sannan suka zauna gaba dayan su akan taburmar. Ba kunya haka suka zage suka dirki abincin nan tas. Alhaji ya tsiyaya musu lemo suka kafa kai suka shanye tas. Mikewa su kai bayan sun gama suna nuna musu yanayin gidajen, Sai murmushi su Alawiyyah suke zukatan su fal da farin cikin wai nan gidajen zasu zama mallakin su nan ba da jimawa ba. Jiri ne ya fara dibar su Alawiyyah da Hinde, Cikin watangariri Alawiyyah ta dafe kai ,

“Al..Alhaji ka...Ji.jiri na...”

Luuu tayi sai kirjin Alhaji labaran, Ya sunkuceta yayi cikin wani daki yana lashe lebe, Hinde tuni ta kife tana jan munshari. A takaice Alhaji Labaran da Mu’azzam sai da su kai masha’a dasu Alawiyya suka wanke garori tukun suka sarara musu. Akan taburmin dake daki suka yasar dasu,

“Kai na dauka zanji ni garau wallahi ashe fanko ce?”

Mu’azzam yace da Alhaji yana gyara tazugen wandon sa, Alhaji ya bushe da dariya yana kallon tarin cikon dasu Alawiyyah su kai,

“Ciko ne ashe, Gwarama tawa tafi gwab’i gwabi.”

Suka sake bushewa da dariya suna tafawa. Su Alawiyyah basu farfado ba sai washe gari. Da kuka kowacce ta tashi, Alhaji labaran ya shiga basu hak’uri yana kalallame murya,

“Wallahi al’adun yaren mu kenan, Kuma ba wai me gaba d’aya akai ba. A’a! Gwaji ne wannan na ganin ku din yammata ne ko kuwa? Amma hakan shine ya nuna mana kudin yan halak ne. Har shedar haka muka dauka mu ka kai gidah wajen su Hajian mu. Sun amince, Mun gama shawarar a wannan shekarar za’ai au..”

Bai karasa ba Alawiyyah ta rungume shi tana hawayen farin ciki,

“Wayyo dadi! Alhaji wannan daddadan labari naka kwarai ya kauda duk wani bakin ciki dake zucia ta. Na amince da kai domin da yaudara ce ta kawo ku da tuni kun gudu kun bar mu anan.”

Alhaji ya girgixa kai yana murmushi, Hinde ma ta kwanta a kirjin Mu’azzam tana jan majina. Abinci suka basu suka ci suka k’oshi, Sannan suka yawata dasu a garin na kaduna, Sai gab da magriba suka mai dasu zaria cike da kayan k’walam da makulashe. Bintalo sai shewa take tana kururuwar kayan dadin da suka zo dasu, Babu mai tambayar a’inda suka kwana. Tun daga wannan rana Alhaji Labaran da Mu’azzam suka mai dasu Alawiyyah tamkar matayen su. Bidirin su kawai suke dasu acewar al’adar yaren su ce ta kawo hakan.....

—

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *_IGIYAR ZATO_.....□_*

_*NA_*

_*NANA HAFSAT_*

_*(MISS XOXO□□)_*

_®ZAFAFA2020_*

(TAKU NA BIYU)

ZAFAFA BIYAR NA KUDI NE, ME SO DAN GIRMAN ALLAH YA BIYA YA KARANTA HANKALI KWANCE😘❤

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

21

BATOUL

Hutuna na farko da nazo gida naga tashin hankali wanda yasani yin nadamar dawowa gidan mu, gashi Innar mu ta shiga halin ciwo domin jininta ne yake yin k'asa, daga sakkowa kasa zuwa hawa sama sai tayi fad'uwa biyar, amman babu mahaluk'in da zai taimaka mata, daman Usaiba ce, to itama tunda taga kwana biyu bana gari kayan dad'i sun dena shigowa Innar mu dai ta dena kulata. Kowa a gidan mu bashi da mutunci yaransu da manyan su, na kalli Innar mu dake kwance akan tabarma nace.

“Yanzu Inna kina da katon saurayi mai jini a jiki amman ki bari a yi miki nisa dashi? Haba Inna, ya kamata kema ki dinga kwato hakkinki a cikin gidan nan, su waye ya korar mosu d'a ko 'ya daga gidan nan? Dubi yadda kike fama da ciwo duk kin kuma ramewa babu mai kulaki bare ya taimaka miki. Inna kisa Yaya Najib ya dawo gabanki kodan kula da lafiyar ki, idan kuma ba haka ba ni na tattaro na dawo gida, domin lafiyar ki tafi komai a tare damu.”

Na karasa maganar ina zumb'ura baki, dan har cikin raina abun da ake mana ya isheni. Gabaki d'aya sun tarwatsa farin cikin mu bayan babu abinda muka tare musu.

“Uhmm! Mai sunan uwa ba zaki gane duk wani abun da nake son ki fahimta ba, gani kike yi kamar rashin wayo ko rashin fitowa nayi rashin mutunci shine ya jaza mana shiga cikin wannan matsatsin rayuwar. Ba haka bane, kinga na farko gidan nan ina zauna ne albarkacin haihuwar ku da nayi a cikinsa. Sannan ke da Auta mata ne, dole nan gaba wajan su za'a zo neman auranku, toh idan nace zanyi cece ku ce dasu ki gaya min waye zai zama dangin ku koda bayan babu nawa ran? Kina gani

yanzu a hakan ba wa bai gama yadda sukai cewar mahaifinku shine ya haifeku ba saboda tsabar kiyayyar da suke yi min.”

“Toh Innar mu a haka zamu barki cikin wannan larurar bayan su basa kulaki?”

Nayi saurin tambayarta domin naga alamar ba zata gane irin zafin da nake ji ba da na ganta a haka.

“Eh kubar ni a haka ina tare da Allah, kedai ki dage kiyi karatunki nan gaba zakiji dad'i koda babu ni a raye nasan zaki kula da kanwarki. Bana son ki kuma cewa zaki dakatar da karatunki, kiyi shi koda babu dad'i saboda watan wata rana.”

Kwallar da ta taru a cikin idona suka fara zubar da hawaye, nasa hannu na share ina kuma jin tausayin Innar mu. Kud'in da na dawo dasu sune naje na saro kayan siyarwa saboda na tara wanda zan koma dasu da kuma abubuwan da zan tafi dasu, cikin hukuncin ALLAH Awarar da na fara yi kuma a cikin gida sai ALLAH ya sanya min albarka a cikin ta, duk da cewar 'yan gidan mu bashi suke karb'a kuma basa biya. Amman Alhamdulillahi! domin ina samun riba duk da suna kin biya na. Kafin na koma makaranta Innar mu da Autar mu har sun maida jikin su saboda a kalla zamuci sau uku, gashi Yayan mu ya turo da kudi dan haka kafin na tafi sai da na tabbatar suna da d'an abun da zasu yi amfani dashi.

Ina tafiya babu dadewa aka yi biki a gidan mu, wato bikin Fareedah yar gidan kawu Dawood, wadda bikin ya haddasa hatsaniya inda akai ta yiwa su Alawiyya gorin cewa sunki auruwa sai yawo da suke faman yi babu mai kwab'ar su. Da kyar aka gama bikin nan, lokacin da na kuma komawa hutu ne Innar mu take gaya min, cikin zuciyata ina addu'ar ALLAH yasa ni dai kar lokacin biki na 'yan gidan mu su wulak'anta ni domin ba mutunci gare su ba.

Haka nayi karatu na cikin zan gama ko kuwa ajiyewa zanyi, saboda kud'in registration yana matuk'ar bamu wahala. Haysam kuwa tunda ya lula k'asar waje ban sake jin duriyarsa ba har lokacin da na kammala Degree d'ina.

2013

Cikon ikon Allah na dawo gidah da dimbin alheri, Domin na samu yabo sosai daga wajen malamai na kasancewar Allah yayo ni da kaifin daukan darasi komai yawan sa. A shekarar dubu biyu da goma sha uku na kammala karatu na a jami'ar Ahmadu bello dake nan Zaria, Na karanta 'bangaren zallar turanci wato B. A English! Shekaruna a yanzu haka ashirin da uku.

Bayan wasu yan watanni sakamakon kammala karatun mu ya fito. Masha Allahu! Domin na samu sakamako mekyau inda na fito da upper second class! Hakika nayi farin ciki fiye da tunanin mai tunani, Wai ni batoul ni ce na kammala digiri har ana shirye shiryen tafiya bautar kasa. Hakika na sake gogewa da kyau domin akwai cima me kyau a makarnta da muke ci muke dafa abinmu da yan dakin mu na hostel, Sannan ruwan famfo ne acan wanda ya kara gyaramin jikina, Fata ta kara kyalli da laushi.

Tsangwama da kyara kuwa sai abunda yai gaba a gidan mu. Musanman yadda yanzun muke samun ci da sha abinci sau uku babu fashi. Allah ya sanya albarka a awarar da nake yi. Layi layi ake zuwa siyan ta domin inayin mai inganci a kuma tsaftace, Bayan watanni biyu sunan mu ya fito a wanda zasu tafi bautar 'kasa. Alhamdulillah domin kaduna aka tura ni. Yar ribar awara ta bayan na bawa Innar mu nasu kason na hada sauran nayi yar siyayyar shiga camp. Wohoho zo kuga bakin ciki awajen yan gidan mu, 'karara suka fito kowannen su bai ji dadin yadda nake samun cigaba ba, kan kace me? Tuni sun yanyana maganar na zama me yawan tazubar gari gari. Toshe kunnuwa na nayi a daddafe na tafi kaduna a gidan Gwaggo Aminatu na sauka washegari suka kai ni can camp. Sati uku na yo acan aka turani kaduna state affairs office, acan na fara service dina, duk ranar jumu'ah nake zuwa zaria nayi kwana biyu na koma can gidan Gwaggo Aminatu. A haka har na kammala shekara d'aya.

2014

Alhamdulillah ba abunda zance da ALLAH sai godia da kuma fatan karawa annabi daraja hade da yalwar farin ciki a tattare damu, Lalle Allah qadirun ne mamallakin kowa da komai. Yayan mu ya sanar mana cewar ya kammala karatun sa a sa'adatu rimi collage of education, Yanzu haka mai gidan sa dake kasuwar singa ya fara koya masa harkar sarrafa shinkafa da fulawa, Ya na aiko mana da sakon kudi lokaci zuwa lokaci, Gwaggo Aminatu tayi ciku-cikun samamin aiki amman hakan yaci tura, Daga karshe ta samamin tallafin karatun digiri na biyu a jami'ar Abu dake nan zaria. M.A

English! (Master of Art in English). Alhamdulillah ya ALLAH lalle Allah mai daga wanda yaso ne a duk sanda yaso. A kuma shekarar ne Haysam ya dawo daga k’asar waje ya kammala karatun sa har zuwa matakin PhD!!

Ina shirin tafiya fara karatun masters d'ina ne kawu ila yace ALLAH ya kashe shi ba zan tafi makarantar ba, a lokacin ne ya kawo min wani abokin Yusha'u wai sai na aure sa. Rigima ta b'alle a tsakanin Gwaggo Aminatu da kawu ila domin ita tace sai naje nayi, kuma babu mai yi min auran dole. Shi kuma ya dage cewar idan har banyi aure ba daga can master's d'in na kara gaba, shi duk a tunaninsa karatun da zanyi shima boarding ne, bai sai zuwa zan dinga yi ina dawowa gida ba.

Lokacin da na fara zuwa lectures a lokacin ne Haysam dan yaga ya kara girma da wayewa domin d'an gayu ne sosai. Sai dai yana zuwa da batun aure na gurin Haj Husnah wato mahaifiyarsa, ta nuna masa cewar sam bata yadda ya aure ni ba.

-

Ignore all typos□□Afuwan ido ya matsa, Ma hadu a next page □□

-

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

ZATO IGIYAR TARA MATA

23

Kawu ila yaja bokitin sa ya zauna yana kwakwular hanci.

“Sai dai kaltume amman ummita ba za tai miki shiri ba.”

Baba Ummita dake gefe ta buga zani tana sallallami,

“Kai Bintalo kiji tsoron mai sama. Ki dena sharri, Du gidan nan akwai me bin bokaye ne irin ki?”

Baba ummita ta karasa fada tana gud’a. Usaiba ta tayata tana shewa,

“A hayye kayya kai, A nayi munajin dad’i a bari muji haushi.. Kutsin ubancan kayya kai.”

Bintalo tayi kukan kura ta cafki wuyan ummita tana gwara ta da bango,

“Sittin ta ubangiji karya kike yi. Shegiya almura, Shi yasa dan bakin halin ki akayo miki kishiya...”

Ummita ta kwace hannun ta tana yarfe shi, Domin ita batada jiki sai tsiwa, Ai kuwa ta daku awajen Bintalo,

“A hayye nanaye! Bintalo, Bintalo, Bintalo! Kowa yasan cikin shege ki kai, Aka rufa miki asiri akai auren ki sadaqah.”

Bintalo ta shatalo kafar ummita ta buga ta da kasa, Itama tai saurin riko Bintalon suka fadi tare,

“Ubanki ne ya mini? Kaji mata mai bakin hali. Sittin ta ubangiji du gidan nan keda mijin ki kune munafukai rikakkun mugaye.”

‘Ayiririri!’ Ummita ta saki guda tana dukawa,

“A hayye duniya labari, Yanzu ke har kece zaki cewa da wasu mugaye? Duk wata kutingwila dake ake shirya ta. Makira, ai gashi nan kin gani akan yayan ki.”

Nan dai fada ya kaure a tsakani, Baba usaiba sai rawa take takawa tana gud’a,

“A hayye kayya kai! A nayi muna jin dadi a bari muji haushi. Kutsin ubancan kayya kai...”

Kawu ila sai janye Ummita yake, Bintalo tana kara dankota. Cikin fada aka yagewa Bintalo jelar gashi. Ta kutuntumo ashariya ta durawa ummita tana sosa wajen,

“Kika cusge min gashi? Sittin ta ubangiji sai na karairaya ki yau.”

Haka su kayi ta fada suna yayyage kayan jikin su. Wasu daga cikin yan gidan mu suna zuga su wasu suna ko’karin rabiyar fada. Lilis su kai wa junan su, Domin Bintalo ta jibgi ummita sosai, Ita kuma ummita ta yayya kushe Bintalo a jiki. Kawu ila yaja dogon tsaki ya fice yana mita. Girgiza kai na nayi na koma cikin Daki na cigaba da nazarin wani aiki da aka bamu.

WASHE-GARI

Ana idar da asubahi Bintalo ta figi mayafi ta fita tun gari na duhu bai waye ba sosai. Mashin ta hau ya kai ta wani waje mai nisa. Sauka tayi ta shiga cikin wani dan karamin gidah. A kofar gidan an rubuta: Gidan Malam Mai Gani Har Hanji (Nesa tazo kusa). Mutane fal sun jeru a acikin gidan layi akeyi d’aya bayan d’aya ake shiga wajen malamin har layi yazo kan Bintalo ta shiga. Katon daki ne dauke da allunan karfe an musu rubutu, Gaban malamin kuma kasa ce fal akan buhu ya kannanade carbi a wuyan sa yana zuba gari a wata tukunya a gaban sa sai hayaki ne ke tashi a ciki. Barkewa Bintalo tayi da kuka tana face majina,

“Malam Zurqallaini mai gani har hanji temako nazo wajen ka..”

Malamin ya callara ‘kara yana ambatar wasu sunaye na tsibbu,

“Kin kawo kuka gidan share miki shi, Tabbas an sako ki agaba nagani gashi nan..”

Bintalo tasa kasan zanin ta ta fyato majina tana cigaba da shararar hawaye,

“Sittin ta ubangiji malam sun min zobe, An yiwa babbar ‘yata asiri mijin ya sake ta yace ‘yaya ba nasa bane. Sannan biyun dake gabana sittin ta ubangiji suma malam anyi musu sammu, d’aya anyi mata ciki ya’ki zubuewa ma dayar kuwa cutar kashe jiki aka sa mata malam. Gaba d’aya an nakushe mu...”

Malam ya jinjina kai yana hargitsa k’asar gaban sa,

“Saka hannun ki anan.”

Dora hannun ta tayi yace ta cire, Ya hargitsa kasar yana zana wasu kalmomi ajiki,

“Zahiri gashi nan nagani, An sako ki agaba domin so ake gaba d’aya a lalata muku rayuwar ku.”

“A hayye! Sittin ta ubangiji ahalin gidan mata tara ne. Malam duba kagani ummita da kaltume ne ko?”

Ya k’ada kansa alamun Eh yana sake dudduba kasar,

“Sune, Bakomai bane fyace dan kinyi musu zarra ne. Kinfi su cigaba a rayuwa.”

“Sittin ta ubangiji haka ne malam, Domin yarana biyun har an kusa bikin su fa. Wallahi Malam sai gashi an fasa an nemi masu neman nasu ma an rasa. Gidan da suke gina musu ma anje, Sittin ta ubangiji masu ginin gidan sunce basu san kowa ba.”

“Ai tsafi suka miki, Da jaki akai aka binne shi. Ba karamin bakin asiri bane.”

Bintalo ta dafe kirji tana raba idanuwa, Cikin rawar murya tace,

“Dagaske malam? Sittin ta ubangiji dama lamarin da ka gani kasan sihiri ne.”

“Yanzu dai abinda nake son kiyi shine, kije ki tsamo min jinin al'adar ko waccen su, ina nufin su Kaltume da Ummita sai ki kawo akwai shu'umin maganin da zan hada miki dashi idan kin kawo. Karki ce min ba zaki iya ba, saboda dole sai kin kawo tunda kika zo nan wajan.”

Mutuwar zaune Bintalo tayi a wajan, saboda bata san inda zata samo wannan abun da yace ba, hasalima bata sani ba ko har zuwa wannan lokacin Kaltume nayi ko ta dena duk da cewar bata dena haihuwa ba. Taja numfashi tare da sake matsawa kusa dashi tayi k'asa-k'asa da murya tamkar wani ne a kusa da su, ta share saman hancinta tare da cewa.

“Babu wata hanya da za'a sake min Malam? Wallahi wannan abun da kace na samo maka zai min wahala saboda bansan lokacin yin al'adarsu ba.”

Wani banzan kallo ya dokawa Bintalo wanda yasa hantar cikinta kadalawa, sannan ya janyo wani katon carbi a can gefenshi yana cewa.

“Dole sai kin kawo sannan zaki samu biyan bukatarki, sannan duk gurin da zakije suma hakan zasu gaya miki. Karki sake rik'o ta wani canjin dan ba samu zaki yi ba, tashi ki ban guri.”

Kamar zata fashe da kuka haka taji saboda tsabar tashin hankali, wannan aikin yayi mata sauri, sam bata da sanin inda zata samo abinda aka buk'ata. Ta mik'e tsaye jiki babu kwari ta kuma tarar mai mashin. Kai tsaye tayi masa kwatancen gidan Alhaji Kabeer saboda taje tayi aiki ta kuma samo musu abinda zasu sanya a cikin su ita da 'ya'yan ta da jikokinta da mahaifinsu yace ba zai karb'e su ba. Da sallama ta shiga cikin sa'a ta tarar Haj Husnah tana kitchen tana bawa Inna Rabi umarnin abinda za'a dafa. Bintalo ta gaisheta sannan ta jira aka sallami Inna Rabi ita kuma tabi bayan Haj Husnah.

“Ya aikai ne Bintalo?”

“Hajiya wani mummunan labari ne na kawo miki, sittin ta ubangiji da idanuwana naga abin.”

“Ai ke kam Bintalo ba kya tab'a kawo min maganar arzik'i sai wacce zata tayar min da hankali. Yau kuma me aka yi?”

Murmushi Bintalo tayi domin tasan duk maganar da ta kawo ko babu dad'i sai an saurareta, dan haka ta gyara tsayuwar ta tare da jan majina tace.

“Sittin ta ubangiji Hajiya basu bar miki yaron nan ba, har yau suna tare kuma bakiga yadda suke mishi ba kamar wani d'ansu, uwar ta tatseshi itama 'yar ta kwashi abinda zata kwasa, yanzu yace idan bai aureta ba zai kashe kanshi.”

Haj Husnah ta dafe faffad'an kirjinta tare da zaro manyan idanunta tana kallon Bintalo, guri ta samu ta zauna saboda wani jiri da yake neman kai ta k'asa. Ita sam ba kyautar da yake musu bace take bata mata rai, maganar auran Batoul da yake cewa zai yi shine bata so saboda yarinyar bata yi mata ba. Da hannu ta yiwa Bintalo alamar ta tafi ta bata guri, wanda da alama zuciyarta ce bata yi mata dad'i.

Bintalo kuwa tana fita ta saki dariyar keta, sannan taje tayi aikinta ta shiga kitchen lokacin Inna Rabi tana parlour tana gyarawa taje ta kwashi d'anyan abinci, su taliya da macaroni da indomie sai ledar Maggie star ta kulle a cikin buhun da take zuwa dashi. Sallama tayi musu tabar gidan tana tsinewa Haj Husnah, harda cewa idan bata yi wasa ba sai ta zama kisjiyar ta.

Haka dai aka ci gaba da rayuwa a gidan mu, Yayan mu da ya gaji shima ya shaidawa innar mu cewa zai dinga dawowa gida saboda ya dinga ganin mu. A haka wattani suka shude anata gwagwar mayar rayuwa, rashin zaman lafiya ya karu a gidan mu, kasan cewar Kawu ila da Bintalo yanzu ba'a zaman lafiya tun lokacin da aka kama Bintalo tana d'aga underwear d'in Ummita a cikin kayan wanki ta, shikenan zargi ya shiga, kuma ita Bintalo jini taje nema yayin da Ummita tace ai

sace mata zata yi daman ta saba ganin undress d'inta a jikin Bintalon wai shiru kawai take yi sai yau abin ya tonu.

Ni kuwa karatu na nake yi hankali kwance domin Yayan mu yana taimaka min da wasu abubuwan ga kuma gwaggo Aminatu. Wata ranar talata ne ina makaranta bayan na dawo na tarar da Hinde ta haihu d'anta kato mai kama da Alhaji Mu'azzamu sak, ni dai tunda nake ban tab'a ganin bakin jariri ba sai wanda Hinde ta haifa. Su kuma ganin da wanda yake kama yasa suka kira Alhaji Mu'azzam suka sanar dashi, aikuwa ya rantse ya kuma rantsewa ba zai karb'a ba domin taci kud'in sa da yawa, dan haka taje tasan yadda zata yi da d'an.

Bintalo kuwa itama tace ba'a d'akinta za'a raini shege ba, rigima ta b'arke tsakanin Hinde da Bintalo.

“Kinsan Allah Hinde yaron nan gidan marayu zaki kaishi domin ba zaki ja min zagin mutane ba a gari, haka kurum ke ba aure ba ace kin haihu, ga shegen mutumin yace ba zai karbi d'an ba.”

“Kwarankwatsa dubu Babah bazan kai d'an nan ko ina ba ina son abina, haka kurum, duk bake bace kike samu a hanyar lalacewa ba. Me yasa idan muka kawo miki kayan dadi bakya cewa mu mayarsa sai yanzu da d'ah yazo zaki ce a kaishi gidan marayu, sittin ta ubangiji babu inda zan kai shi idan ba haka ba zan kaiki kotu.”

“Ke Hinde! Ni zaki kai kotu saboda baki da mutunci? Wabillahillazi kinyi kad'an yarinya, gaki ga d'an nan ai daga yau na dena nemowa kowa abinci dan uban ku, kowa ya fita ya nema da kanshi tunda abun haka ne.”

“Aiyirrrrrrr nanaye!”

Cewar Usaiba da Ummita abin ya kuma b'atawa Bintalo rai ta kuwa dinga zaginsu tana cewa suma sai sunga fiye da abinda ake yi mata ita da yaran ta. Ni kuwa tunda na shiga d'aki Inna ta dora yatsanta saman labbanta tayi min alamu da karna sake nayi mata maganar da ake yi a gidan, duk da gulma na cina haka na hakura nayi

shiru dan nasan abun ne ya ishi innar mu shi yasa bata son maganar. A haka dai aka ci gaba da zama, Hinde ta sanyawa d'anta suna Ibrahim ana kiransa da Khaleel, a cewar ta gara tasa mai sunan uban shi saboda ta konawa Alhaji Mu'azzamun rai, nan gaba zata nemo har gidan iyayensa taje ta kai musu d'an. Alawiyya kuwa sai sake figewa take kasan cewar babu wadataccen magani gashi kullum cikin fad'a suke da 'yan uwanta dan basa ko rab'arta wai karta goga musu.

***Haysam kuwa gabaki d'aya ya d'auke k'afarsa daga k'ofar gidan mu, ko a hanya bana ganinsa sai abun ya d'an fara damu na, saboda ko babu komai shi d'in yana da muhimmanci a cikin rayuwata, sai dai ban san yadda zanyi na nemeshi ba hakan yasa na tattara shima na rabu dashi da niyar duk lokacin da muka had'u ma gaisa. Naci gaba da karatuna cike da nasarori masu tarin yawa wanda banyi tunaninsu ba a cikin rayuwata, na sake wayewa, kaina ya kara girma sai dai bana fad'in rai ba, a'a na zallar karatu.

A ranar da na kammala karatun degree d'ina na biyu (masters) na dawo cikin murna, a ranar ne Yayan mu shima yazo kuma dawowar da yayi yana son ya d'an jima kafin ya koma kano kasan cewar yafi sabawa da can, ga kuma sana'o'i yana ta yi babu mai takura masa bare yace yayi wani abun. Innar mu ta siyo zabi guda biyu kasan cewar tana d'an adana kud'ad'e idan Yaya ya aiko mata dasu, kuma nima idan na samu kyautar kudi daga wajan lecturers d'in mu ita nake bawa, ta siyo kayan miya tayi mana farfesu mai dad'i. Yayan mu ya siyo lemuka da buredi ya bawa Innar mu aka kasa Autar mu takai ko wane d'aki, muma muka zauna muka ci namu muna farin ciki dajin dad'i.

“Kaga su Batoul manyan gari, yanzu kuma sai neman aiki ko?”

Nayi dariya har hakorana suna bayyana, na ture ledar buredin daga kusa dani ina cewa.

“Wallahi kuwa Yayan mu, sai fatan alkairi ALLAH yasa mu samu aikin nan mai tsoka.”

“Zaki samu da yardar ALLAH, babban kwali fa gareki sister.”

Kafin nayi magana muka jiyo muryar kawu ila yana kiran Yayan mu, kai daga jin kiran kasan cewar babu lafiya. Innar mu ta kallesa tare da cewa.

“Karka yi masa rashin kunya, kabi shi a hankali bana son tashin hankali.”

“Toh Inna bari naje naji menene.”

Yana tsaye kusa da bokitin sa da alama zama yake so yayi amman yana jiran fitowar Yaya Najib, ai kuwa yana gama sauka shi kuma kawu ila ya zauna akan bokitin. Kusa da kafar bene Yaya Najib ya zauna yana gaishe da kawu ilan.

“Bana amsawa rik'e abarka munafuki, kai ni nan da kake gani na kyar nake kallon kowa a cikin gidan nan. Ashe zaka dawo?”

“Kayi hakuri kawu wallahi ina son zama ne a kusa da 'yan uwa na, kayi hakuri duk inda zanje ba zai kai nan ba duk lalacewarsa.”

Gyara zama kawu Ila yayi yana zabgawa Yaya Najibu harara kamar kwayar idon zata fad'o, ya kuma jan bokitin yana matsowa kusa da Yaya yana cewa.

“Ai dole ma ka dawo duk gidan uban dakaje, ka dauka kaci banza ne da zaka lalata min yarinya kace ba zaka dawo ba? Toh bari kaji in gaya maka, dole ne ka auri Basmah, yadda ka b'ata min 'ya haka zaka zauna da ita har tsawon rayuwarka marar mutuncin yaro.”

Cikin razana da rashin fahimtar inda maganar kawu ila ta nufa, Yayan mu ya mike tsaye baki na rawa yace.

“Ka.. Kawu wac.. Wacce Basmah???”

“Ta gidan ubanka, nace ta gidan Ubanka, banda wacce ka lalata kana da wacce ka sani ne?”

Nan da nan jikin Yaya Najibu ya hau rawa yana faman girgiza kansa tare da ja da baya, ba tare da ya sani ba har ya kusa zuwa wajan rijiya gata a bude.....

—

Ghen Ghen!□□MUN kusa shiga ainihin labarin😂□□INA fatan kuna nishadantuwa da foundation din da mukayi☺ A dinga rike shekarun sbd labarin a gaba yake IN SHA ALLAH□□Parte afta parte😍□□□□□□□

•

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

_*SITTIN TA UBANGIJI..._*

(Labarin sarqaqiyar rayuwa cunkushe da kauna)😘❤❤

_NA_

HANSAI ME GLASS

22

•<>•<>•<>•

Gyara zama Haysam yayi tare da ajiye remote d'in dake hannunsa yana fuskantar mahaifiyar sa, cikin yatsina fuska yake cewa.

“Ummah ni ya zaki ce ba zan auri Batoul ba? yarinyar nan tana da nutsuwa da hankali, uwa uba biyayya, shin menene aibunta na cewa ba zan aure ta ba ummah?”

“Kai tafi can sakarai kawai, toh tsaya ma, duka-duka nawa kake da har zaka ce min zaka yi aure banda neman rigima? Toh ba zaka auri Batoul ba indai da gaske kake yi na cewar ka matsu kayi auren, toh kaje ka samo ko wace yarinya ce zan amince maka, amman banda Batoul, sam yarinyar bata kwanta a raina ba.”

Haysam ya rintsa ido yana jin tamkar kansa zai tsage saboda bai yi zaton hakan zata kasance ba na k'in amince masa.

“Ummab me yasa?”

“Kaga Haysam karka takura min da maganar wannan yarinyar, nace maka ba zaka aure ta ba, idan kai mai biyayya ne a gare ni toh karka kuma yi min maganarta na gaya maka.”

Jikinsa yana rawa haka ya mike ya nufi sashen sa hankali a matuk'ar tashe ko ganin gabansa baya yi saboda tsabar tashin hankali.

GIDAN MATA TARA

Dawowa ta daga kaduna kenan na shiga gidah ina sallama, Gaba na kuwa banda fad’uwa babu abinda yake yi. Runtse idanuna nayi ina addu’oi a hankali. Gaba d’aya tsakar gidan namu a hautsine yake da hayaniyar 'yan gidan mu. Kowanne kara-kainan sa kawai yake, Yan layin bandaki nayi, Yan wanke-wanke nayi, Masu wanki nata dirjewa, Masu tsegumi kuwa kowanne kusufa kwa ga curin su. Innatuwa dake gugar kaushin kafar ta ta dago ta dube ni Ina k’ok’arin dorawa autar mu ledar kayana a kanta don hayemin dashi daki. Ta sake barbajewa a kafar benen taki ta

matsa na wuce, Na dubi wawan zaman da tai na dauke kai na ina girgiza kai cike da takaici, Innatuwa ta kaikace tana sakin murya, Wanda kai daka ji abinda take cewa kasan gugar zana ce dani take,

“A hayye tayi kwantai, Godiyallare babu mashinshi ni, Yawan ta zubar shine agaban su, Gandar-dar, Rasausau, A hayye babu mashinshi ni. Sai nanaye kwararo kwararo da sunan karo karatu..”

Dafe kai na nayi, Jin shirmen zantukan dake fita daga bakin ta godai-go’dai da ita. Cikin kosawa da maganar ta na muskuta zan wuce ta gefe,

“Maman Yusha’u zan wuce.”

“Toh kai! to kai! to kai! Taka ni mana ki wuce sai nasan ke ‘kwankwararriyar yar bariki ce.”

Saurin shigewa nai ina jan hannun autar mu domin nagaji da masifar yan gidan mu ta gaira babu dalili. Ina hayewa na jiyo sautin muryoyin su suna zuga Innatuwa wai na mata rashin kunya karta yadda, Bintalo dake tsaye tun sanda aka fara caftar ta callara kara tana buga zanin ta,

“Sittin ta ubangiji innatuwa karki ragawa shegiya, Ki daka ta ki gurji bakin yar bariki, Wai dan ta zama karamar yar tasha fa shine take irin wannan zantukan. A hayye nanaye!”

Murmushin takaici nayi ina jiyo su daga dakin Innar mu, Na cire hijabin jiki na na ajiye a gefe ina firfita da murfin bokiti. Gaba d’aya ni yanzu hayaniyar su ciwon kai take sani, Saboda na kara hankali. Kuma Innar mu kullum cikin yi mana nasihar zaman duniya take. Hira muka dan taba da Innar mu dake sakace kunnanta da tsinken kaza. Bayan sallar magriba na jiyo sautin wasu yara suna ambatar sunana,

“Wai ana kiran batoul awaje.”

Kawu ila dake zaune yana gyara bokitin sa yaja tsaki yana watsa hannu baya had'e da zare musu idanu yace,

“Kai kunci bantan uban ku! Wai tazo inji uban wa?”

Cike da rawar jiki suka fice aguje ganin yadda ya razana su. Ba jimawa wani almajiri ya sake shigowa a karo na biyu da karfi ya shiga dankarawa sunana kira,

“Wai ana sallama da Batoul a waje.”

Kawu ila ya sake jan dogon tsaki a karo na ba adadi, bokitin nasa ya dauka ya shige dakin sa ransa a matukar b’ace, Da alamun wani abun ne ya samu rabin ran nasa.

Hijabi na na zura na sauka kasan bayan na cewa Innar mu ana sallama dani, Daman da niyyar duk wanda yazo zance masa anbada ni gudun kada Kawu ila ya kara ‘kagamin wani sharrin, A soro nai kicib’is da Haysam sanye cikin kananun kaya samfarin jins sa riga mai dogon hannu, Ya sanya hular sanyi kasancewar ranar sanyi na dan busawa, Hannuwan sa zube cikin aljihun wandon sa.

Murmushi na dan yi masa ina lankwasa yatsun hannaye na, Ganin yadda yake wani shasshafe saje yana kobarewa irin ta samarin nan sai abun yaban daria, Lalle mai hali baya fasa halin sa,

“Ya Haysam! Barka da dawowa.”

Na karasa fada ina lekawa cikin gida gudun kar Kawu ila ya taho ya sauke mana kwandon rashin mutuncin sa. Idanuwan sa ya narkar a kai na yana wani langab’ar da kai,

“Mine! Nayi kewar ki da yawa wallahi har rama nayi.”

“Lalle yaron nan!”

Na fada a zuciata ina mamakin kalaman sa. Gaskia yana da tsaurin ido ba ka’dan ba. Ajiyar zucia na ja na sauke kafin cikin kallon kasa nace dashi,

“Ya Haysam an dawo lapia?”

“Alhamdulillah mine! Anya kinyi kewata kuwa?”

Murmushi nayi kawai,

“Ai dole nayi kewar Yaya na! Da fatan an kammala karatu lapia? Allah yabada nasara mai dorewa Ameen!”

“Mine ko sau d’aya baki taba kira na ba da ina cyprus meyasa?”

“Bani da number ka ne shi yasa”

Karkada kai yayi yana cizan leben sa na kasa,

“Shikenan mine, Har yanxu dai alamu sun nuna bakya ra’ayi na ko? Shin har yanzu ban isa ba ne ko kuwa ban kai ba. Ya kamata ki cire *ZATON* da kike a kai na. Dan ALLAH ki sassauta min Batoulll..”

Cikin son kauda maganar da yake yi na sake gyara tsaiwa ta ina girgiza kai,

“Ya Haysam na kammala digiri dina fa, Yanzu haka na dora da master. Kai ne kai tushen komai, Nagode ALLAH ya saka maka da alkhairi.”

“Toh ya batun fara zuwa zance?”

Dan satar kallon sa nayi yana sake tura hannun sa a aljihu alamun sanyi yake ji sosai ganin yadda yake karkada k’afafuwan sa. Na rasa amsar da zan bashi ma, Gashi ba naso Kawu ila ya fito ya ganshi.

“Kayi hak’uri Ya Haysam zanyi tunani Allah ya zabi abunda yafi alkhairi..”

“Ameen Mine! Haka kika kara girma?”

Murmushi nai kawai ina juyar da kai na gefe,

“Lalle kaga makwanci na.”

Na fada a zuciata ina mamakin tsaurin idon sa. Keya ya sosa yana murmushi. Sallama yai min zai fita Bintalo ta shigo zauren da gudun ta. Ganin sa yasa ta kunduma uban ihu tana kururuwa,

“Ilyasu! Ilyasu Ilyasu..”

Komawa ciki tai da sauri tana kiran Kawu Ilyasu, Nayi saurin sallamar Haysam na koma ciki ina raba idanuwa sanin sharrin da Bintalo zata gaya masa. A tsakar gida nagan su tsaye tana kwaso rantsuwa tana direwa hade da watsa hannu baya tana buga zani,

“Sittin ta ubangiji ta bada maka kasa a idanu, Toh ga tanan ma makira algunguma.”

Bintalo tafada tana nuna ni da shigowata kenan, Kawu ila ya kumbura tamkar zai fashe don takaici. Hannu yasa yana karkada shi a kai na,

“Ai dole ki fandare kin rigada kinfi karfi na, Tacacciyar yar iska! Wato ke ishasshiya ko? Shine zaki watsa min kasa a idanu ki sake tsayawa da yaron nan? Shin iskancin naku bai isa acan ba har gidah yake biyo ki?”

Shiru nayi ina girgiza kai na yayin da ambaliyar hawaye ke tsiyaya a idanu na. Shin wannan wacce irin rayuwa ce? Ya Allah ka kawo karshen wannan sarqaqiyar rayuwar! Subhan’Allah.

“Ba magana nake miki ba? Kinci bantan uban ki. Ai dole kiyi shiru tantiriya.”

“Kayi hak’uri Kawu”

“Hak’urin uban uban ki? Bance karya sake zuwa ba?”

Shiru nayi kukan da nake yaci karfi na, Naja majina ina goge hawayen fuska ta. Muryata na rawa na shiga girgiza kai ina hada hannuwa na alamun ban ha’kuri,

“Kayi hak’uri Kawu! Nayi kuskure ba...”

Ban karasa ba Bintalo tasha gabana tana buga zani hade da watsa hannu baya,

“Sittin ta ubangiji karya kike yi, kina sane. Ilyasu ku aurar da yarinyar nan ko da ga d’aya daga cikin almajiran gidannan ne. Kar taje ta ebo mana abun kunya, Kaga dayan shegen da yasan abunda ya aikata tun da ya gudu ba mu kara ganin keyar sa ba.”

“Abunda za’ai kenan, Tunda ta watsa min kasa a idanu. Gwara a d’aura da wuri tun kafin Yaya Aminatu taji ta hana, Bara na sami gwani shu’aibu yana wajen d’axu.”

Kawu ila ya fada yana zura takalman sa hade da gyara yar sharar rigar jikin sa. Ficewa yayi kamar walqiya yana mita shi kadai. Bintalo ta callara gud’a hade da tafe hannaye tana buga zanin ta.

“A hayye nanaye! Sittin ta ubangiji mun kusa rabuwa da ‘kaya.”

Girgiza kai na nayi na fara hawa mattattakalar bene ina sharce hawaye ganin auren sadaqa za’ai da ni akan abunda bai taka rawa ya karya ba. Ina hawa kafar bene ta biyar kenan muka jiyo ihu, An shigo gidan da gudu da yara rab’e rab’e su biyar suna binta a baya. Juyawa nai ina don ganin waye? Zabbau ce yar Bintalo ta farko ta shigo itada yayanta su biyar. Ta baje a kasa tana birgima hade da kurma ihu. Tuni makota da ahalin gidan mu suka bayyana. Cikin muryar kuka hade da shure-shure da zuban ruwan majina zabbau ta callara kara tana surutai,

“Ya sau ni Baba, Walle talle ya sau ni. Shika uku yayi min, Y’aya kuma yace walle bana shi bane”

Cewar zabbau cikin hausar ta ta yan karkarar kod’e. Tana gama fada ta shiga bubbuga kanta a jikin rijiya tana kuka, Bintalo ta yage zani tana ihu,

“Na shiga uku ni Bintalo. Sittin ta ubangiji yaron nan ya cucen. Ke ‘yarnan gayamin gaskiyar lamari.”

Dede da shigowar Kawu ila kenan shi da badamasi mai kwasar kwata kuma almajiri a makarantar almajiran gwani shu’aibu dake kofar gidan mu. Da alamun shine mijin da zai aura min, Domin badamasin sai dashare yalayen hakoran sa yake yana susar duwawu.

“Na shiga uku! ALLAH ka tsare ni.”

Na fada ina runtse idanu na. Gaba d’aya a hargitse yake, Sanye cikin kananun kaya duk sun daddare sun kode sai hamamin wari ne ke tashi a jikin sa. Kawu ila ya janyo bokitin sa ya zauna yana kallon yadda zabbau ke birgima tana nana ta,

“Ya sau ni Baba, Walle talle ya sau ni. Shika uku yayi min, Y’aya kuma yace walle bana shi bane.”

Baba usaiba dake gefe taja guda tana watsa hannu,

“Kutsin ubancan kayya kai!”

Salati kowa ya hau yi ana tafa hannaye, shidai gidan mu kullum ta Allah sai an samu wasu abubuwan na rashin jin dad'i da zai faru, gashi aka rasa wanda zai ce Zabbau tayi shiru tana ta b'are baki kamar wata jaririyar akuya, yaranta na tsaitsaye sun zuba mata ido suma.

“Rabu dashi Zabbau, dole ki koma gidan mijinki. Shi dan bashi da mutunci tuntuni bai san yaran ba nashi bane ba sai yanzu? Naji ance aure yake nema ina jin shine dalilin da yasa ke ya sakeki dan ya samu dakin da zai sanya sabuwar.”

Cewar kawu Ishaq wanda ke tsaye yana asuwaki da ican darbejiya, nan fa Bintalo ta sake bud'e murya tana kutuntumo zagi ta dorawa surukin nata, da kyar dai aka lallaba Zabbau ta shiga d'aki, yaran na biye da ita kamar bindi, Alawiyya na ta faman yatsina fuska dan tasan d'akin nasu kuma cunkushewa zai yi. Wannan sakin na Zabbau shine ya shafe maganar auren da aka ce za'a min, na dinga godewa Allah saboda shine ya rufa min asiri na kin yiyuwar auran da almajiri.

••••••; •••••••; •••••••

Tsab na shirya saboda a ranar karfe goma muke da lecture, amman saboda na isa da wuri sai na shirya da wuri. Jakata na d'auka na yiwa Innar mu sallama, ita kuma

Autar mu tana shan kunu da Awara gefenta uniform d'inta ne tana so idan ta kammala itama ta shirya ta tafi makaranta. Ina fitowa tun daga saman bene na hango 'yan gidan sun zage wata a tsakiyar gidan, na sauka a hankali ina satar kallan wajan dan na hango ko wace aka kewaye ana ta faman caccakar ta, naji muryar Hafsatu matar kawu Dawood tana cewa.

“Daman duk kayan da suke shigowa dashi tukwici ne na bada jikinsu da suke yi, gashi dai yau ALLAH ya bankado asirin ku su Hinde. Wai cikin shege Hinde, su Bintalo ana min gorin nayi saurin yiwa Fareedah aure, wai dan naga bani da budurwar da za'a dinga yiwa hidima. Ahayyeee nanayeee yau ga jika mun samu na shegu.”

Da gudu Bintalo ta fito daga cikin d'akin ta ta diro kan bayan Hafsatu jikake dim..tim..ragajaf..jaf, tana dukanta. Nan da nan fad'a ya tashi, ni dai dana lek'a naga yadda Hinde take jibga uban amai, nayi sif..sif na bar gidan. Yau ALLAH ya nunawa 'yan gidan mu kalar wad'anda zasu kwaso abin kunya, ni da suke tunanin zanyi gashi nan ko tsayayyen saurayi bani dashi saboda duk maso son nawa wad'an da nake so na aura yawancinsu suna da mataye, wasu kuma su kawo min maganar banza hakan yasa har zuwa lokacin ban samu mijin aure ba.

Sai da naje na dawo nake tambayar Inna yadda aka kare, ta kalleni tare da cewa.

“Kin san dai ni ba shiga harkarsu nake yi ba, ban fita ba ina dai jiyo su suna zage zage, shi kuma kawun ku Ilyasu yana tarewa Bintalo kinsan aminaine, haka suka taru suna ta rashin mutuncin su, sai daga baya ne naji ana cewa akai Hinde asibiti a zubar da cikin kafin ya fara girma asirin gidan mata tara ya tonu.”

“Ikon ALLAH kenan, Inna kinga dai yadda suka so na lalace ALLAH bai yi ba.”

“Eh shi yasa nace ku dena damuwa indai kunsan cewar baku sabawa mahalicin ku, Shi sharri dan aike ne. Gashi yau k'aik'ayi ya koma kan mashekiya, ALLAH ya kara karemu daga son zuciya.”

“Amin Innar mu.”

Daga haka na juya na d'auki abun karatuna ina kuma dubawa, su kuma can anje asibiti an basu maganin zubar da ciki tashi, Alawiyya kuma bata da cikin sai dai bincike ya nuna cewar tana dauke da ciwo mai karya karkuwar jiki shine ma yasa ta d'an fara ramewar nan ba kamar yadda take ba a baya. Hinde kuwa tunda tasha maganin nan take yin wani abu tamkar zata mutu dan Bintalo sai kuka take yi ta riga ta cire rai da rayuwar 'yarta ta, duba da yadda take sumewa tana dawowa, kuma cikin yaki b'arewa ballantana hankalinta ya kwanta.

“Wallahi kun cuce ni yaran nan, wannan daga gani aikin sihiri ne banda haka ya za'ai ace duk tambad'ewar da Mariya tayi a garin nan amman bata yi ciki ko ta samo cuta ba sai yarana. Ku duba kuga yadda tsinanniyar yarinyar can take bin makarantu tana bin samari ace itama bata da komai sai yarana dan an gansu da farin jini, wallahi ba zata zabu ba. Kaltume da Ummita kune kukai min makarkashiya.”

“Ke..ke Bintalo menene hakan? Wace irin magana ce kike yi haka?”

Cewar kawu ila saboda yaji ta ambato sunan matarsa akan sunyiwa yatanta asiri.

“Bafa zaka yi min jan ido ba ilaysu, kyar nake kallon kowa a cikin gidan nan. Kai ka manta lokacin da aka yago maka Basmah, nan kazo kana cewa Najibu ne bayan duk munsan sharri kayi masa,To sittin ta ubangiji su Ummita da Kaltume ne suka janyowa Hinde da Alawiyya.”

Bintalo ta karasa fada tana jan majina ji kake 'fyaat...'

___

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IG😘❤

24

••. ••. ••. ••. ••.

Kowa ya bud'e ido amman babu wanda ya bud'e bakinsa yayi masa magana akan inda yake nufa, ni kuma dana fito daga d'aki zan sakko kasa na zubar da burbushin biredin da muka zubar kawai na hango Yayan mu yana tafiya da baya, sauran kiris ya fad'a ciki na kirashi da sauri ina sakkowa da gudu.

“Yayan mu rijiya a bayan ka.!”

Jin magana ta yasa shi juyawa a hankali yana kallon bayan nashi, Ni kuma ban luraba skirt d'ina na take da kafata, ai kuwa na fado na dinga gangarawa har sai da nazo k'asa. 'Yan gidan mu dake lebe suna ganin yadda kawu ila ke ciwa Yaya Najibu mutunci, sai gashi nima na fado sai duk suka fito wasu na dariya wasu na min Allah ya kara yayin da wasu ke yi min sannu. Duk na kurje harma na samu targad'e a kafata ta dama. Innar mu ta sakko kasan tare da d'ago ni dan har lokacin Yayan mu bai gama dawowa cikin hayyacinsa ba akan maganar da kawu ila yayi masa. Innar mu na rungume dani ina zubar hawaye saboda na bugu da yawa, ta tsaya tana kallon kawu ila wanda yake ta faman kumbura fuska tace dashi.

“Duk ka gama abinda zaka yi akan 'ya'yan d'an uwanka, dashi da ALLAH duk suna kallon ka, Basmah kuma kaje can ka samu wanda ya lalata maka ita amman ba dai d'a na ba, kuma babu aure a tsakaninsu domin ka riga ka iskanta min yaro, ka sheganta min shi, ka tsine masa, ka aibata shi, insha Allahu ba zai tab'a auran jikinka ba bare har ka sake kulla mishi wani abun.”

Tana gama fad'a taje ta janyo hannun Yayan mu, ni kuma tana rungume dani ina d'ingishi muka haye sama, 'yan gidan mu suka bimu da ido babu wanda ya iya cewa uffan saboda sunga yau Innar tamu a kule take kowa zata iya sauke masa abinda yake damunshi.

“Ah lallai Kaltume kin rik'a, ni kika zazzage ko? Toh zaku zo ku neme mu da kanku, ba dai mune dangin 'ya'yan naki ba? Mu zamu aurar dasu, haka kuma mu zamu je

nemo auran shi munafukin yaron naki, toh zaki yi nadama dan sai kinzo kin shanye duk wad'annan kalaman da kikazo kika gasa min.”

Mudai muna d'aki Innar mu na jajjamin kafata, Yayan mu kuma ya dafe goshi da alama abinda kawu ila ya fad'a ne yake damunshi. Can dai ya numfasa tare da cewa.

“Inna wannan abun na kawu ila ba wai kiyaya kawai yake mana ba harda hassada, wallahi Inna hassada ce kawai yake mana dan yaga Allah yana kare mu daga duk wani mugun baki da suke yi mana. Amman banda haka mene na cewa nine na lalata masa 'ya? Inna wallahi tallahi ba Basmah ba kadai kowace mace ban tab'a sha'awar kusanta ba bare wannan figigiyar yarinyar, Allah ya isa kuma ban yafe ba da wannan kageggen sharrin da yayi min.”

“Kuyi hakuri, kuci gaba da addu'a insha Allahu babu abinda zai sameku sai alkairi.”

Haka mukaci gaba da rayuwa, Yayan mu yaci gaba da business d'insa yana samun kud'in kashewa, nima bayan na warke daga targad'an da nayi naci gaba da yin Awara ta kuma alhamdulillah ina samu sosai. Ganin ina samu yasa Zabbau itama ta fara yin awarar itama, sai ya zamana ita a zaure take yi, duk wanda ya shigo zai siya saita tare shi tace ai ni na dena yi, a haka ta kashe min kasuwa, sai ban hakura ba saboda yanzu bana son zaman banza sai na fara yin meat pie na siyarwa, nan ma ALLAH ya kuma sanya min albarka a ciki domin matasan unguwar mu haka zasu yi ta aikowa suna siya. Ganin haka yasa na fara yin zobo ina siyo kankara ina sawa idan na kulla a leda, shima Yayan mu yana fitar min dashi can wajan aikinsa da yake zuwa, bakin ciki ya sake dira a zuciyar 'yan gidan mu ganin mun fara basu zarra dan har ledar d'aki muka sanyawa Inna muda Yayan mu, muka siyo katon bokiti na zuba ruwa yadda idan muka cika shi sai mu dad'e bamu nemi ruwan famfo ba.

•••

GERMAN EMBASSY SCHOOL

ADDIS ABABA

Gaba d’aya ta gama gajiya da jiran yayan nata. Ta fito daga owners corner din da take ta tsaya a bakin gate tana hango shi yana tafiya kamar ba zai taka kasa ba. A hankali yake tafiya yana jan jakar kanin sa dake biye dashi yana shan ice cream. Girgiza kai Jannat tayi ta dan daga murya dan kiran yayan nata. Cikin harshen Amharic na Ethiopians tace dashi,

“tolo tolo ibakihini wenidimē MM”

(Yaya Mm kayi sauri please)

Ko kallon ta bayyi ba ya bude murfin motar ya shiga bayan ya budewa ‘kanin sa gaba ya zauna driver ya jasu.

ETHIOPIA

(Addis Ababa)

AMBASSADOR SALEES MUHAMMAD RESIDENCE

Gida ne ‘kerarre wanda ya amsa sunan gidah samfarin ginin ‘kasar Ethiopia, Fari ne tas haka ma kayan furnitures din ciki duk farare ne. Wani ‘kayatattan parlor ne daya amsa sunan sa, Komai na cikin sa fari ne da silver.

Wata farar yar dattijuwar mata ce zaune a parlorn tana kallon news a tashar cnn. Center table din dake gaban ta dauke yake da kayan alatu fal akan tray, Lokaci zuwa lokaci takan dauki d’aya daga cikin fruits din ta kai bakin ta. Da alamun itace matar gidan. Domin ga babban family photo nan dauke da hotan ta da mijin ta da kuma wasu mata da maza su hudu da alamun yaran su ne.

Driver na gama parking suka firfito daga cikin Motar, suka shiga cikin gidah bakunan su dauke da sallama. Su ukun suka tafi suka rungume mahaifiyar su suna murna. Shi kuwa babban namijin hanyar sashen sa yayi mahaifiyar tasu ta kira shi,

“wedezīhi k’its’ibeti wedezīhi na”

(Zo nan yanzun nan..)

Har ya kai kafar bene na uku ya juya ya koma yana jan kasan lips dinsa, Harara mahaifiyar tasu ta dankara masa. Dan murmushi yayi yana sosa ‘keya, A haka wani dattijo ya shigo da alamun mahaifin su ne. Da sauri matashin saurayin ya bashi hannu suka gaysa yana mai sannu da zuwa da harshen hausa,

“Papa sannu da dawowa.”

“Yauwa Muhammad. Ya school?”

“Alhamdulillah!”

Muhammad Mubeen ya fada yana kallon mahaifiyar tasu,

“Mamma can i?”

Ya karasa fada yana nuna kafar bene alamar ya tafi? Kad’a kai tayi tana girgiza kai. Sama ya haye da sauri yana cire agogon dake daure a wutsiyar hannun sa. Su kuwa sauran yaran bararrajewa su kai suna hira da iyayen nasu, Suyi da yaran Amharic wani zancen kuma su yi da Hausa gwanin ban sha’awa.

**Tsaye take a kitchen kusa da gas cooker, dan wake take sakawa d'ayan tukunyar kuma kwai ne take dafawa, mai aikin ta kuma tana gefe domin a ka'ida duk wani abunda mai gidan yake son ci matar gidan itace ke girka masa idan ba haka ba toh ba zai ci komai ba har sai ya fita wajan harkokinsa. Muhammad Mubeen ne ya shigo, Sanye yake cikin kananun kaya, ba tare da yace komai ba ya zaro cokali yaje kusa da Maman tashi yana taya ta jefa d'an waken a cikin ruwan dahuwa.

“silezīhi wede tachi weredu?”

(An sakko kenan?)

Yayi murmushi kad'an ba tare da yayi magana ba, daman tasan hakan zata kasance dan haka bata damu ba suka ci gaba da sakin d'an waken har suka gama. Kallonsa ta d'an yi shi kuma ya juya zai fita tace masa,

“migibuni le’irisiwo mesit’eti ālebinyi?”

(Zaka ci ne na zuba maka?)

Yanzu ma girgiza kai yayi alamun a'a bazai ci ba ya kuma sanya kai ya bar cikin kitchen d'in, shu'umin yaro ne wanda miskilanci ya yiwa yawa, sam baya kaunar magana

SHIN WANENE AMB SALEES MUHAMMAD?

Ambassador salees muhammad ambassador ne dake wakiltar Nigeria a kasar Ethiopia. Ya kusa retiring ma saboda permanent ambassador ne bana appointing ba. Cikakken dan usulin kaduna-zaria ne. Babban ‘dah ne ga marigayi Alhaji Muhammad Mai Taya. Su uku ne jal awajen iyayen su. Shine babba sai kanin sa Alhaji Bilalu wanda senator ne shi dake wakiltar wani yanki a jihar kaduna, Sai kanwar su Rahilah wadda ke aure a Zaria kuma awajen ta mahaifiyar su take. Mahaifin su Allah yayi masa rasuwa tun shekarun baya.

Amb. Salees babban mutum ne wanda ya rik’e mukamai da dama a kasar Nigeria dama ketare, Matar sa tafarko Allah yayi mata rasuwa bata taba haihuwa ba . Bayan rasuwar ta da wa’ensu shekaru aka bashi mukamin Ambassador for peace dake wakiltar Nigeria a kasar Ethiopia. Anan ALLAH ya hada ransa da sakatariyar sa wadda musulma ce yar kasar Ethiopia mai suna ‘Ahlaam Bnt Jauhar’ Har ALLAH yayi da rabon aure a tsakin su ya aure ta. Shekarar farko ALLAH ya albarkace su da samun ‘yaya hudu. Maza biyu mata biyu.

Muhammad Mubeen shine ‘dan su na farko, Sai Jannat wadda taci sunan mahaifiyar Amb Salees wato Inna Hauwa. Sai Mashkour da kuma autar su Aeedah. Gaba d’aya yaran sai su kai ruwa biyu, Sun dakko yanayin fatar mahaifiyar su da yanayin gashin kanta, Sai tsayi da siffar jikin su irin na mahaifin su hausa fulani. Sun kasance tun sanda aka haife su acan suke. Hutu ne kawai ke kawo su Nigeria. Hakan yasanya suke jin hausa sosai domin acikin Nigerian embassy din suke, Kuma akwai ma'aikatan da suke aiki anan suma da matan su da yaran su, Shi yasa suka iya hausa kamar wanda aka haife su a kano. Amma sunfi yin yaren kasar ta Ethiopia wato yarukan Amharic da Oromo.

A yanzu haka Ambassador Salees ya fara musu shirye shiryen komawa ‘kasar Nigeria domin yanason yayi takarar zama gwamnan jihar kaduna..

___

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

HELWA....□

62

LIMANCIN KONA

GIDAN ALHAJI KABEER MAI WAFA

Bintalo na tafe tana kwaso rantsuwa tana direwa ita kadai, Sai watsa hannu baya take tana magana a hargitse. Dayan hannun nata kuma tana dukan takashin ta ta baya.

“Yar kundun ubar tsutsa, Sittin ta ubangiji kwalbar mursaleta zan siya na gwaggwuda miki duka.”

Haka ta karasa shiga cikin farfajiyar tana dukan takashin ta, Daga wajen filawoyi ta tsaya ta dan dubi koina kafin ta daga zani ta kaikaice ji kake,

‘Sittt..’

Tana gama sakin tusar ta mai shegen doyi ta karkade zanin tana rufe hancin ta,

“Kai, gumama! Sittin ta ubangiji aiken dan waken jia ne da alalar hinde.”

Sai data bari ta huce sosai sannan ta karasa cikin gidan tana doka sallama hade da cire mayafin ta ta rataye a bakin kofa. Ta corridor ta hango Alhaji Kabeer Mai Wafa yana sakkowa daga k’afar bene. Murmushin fuskar ta ne ya fada’da. Inna Rabi dake tsaye tun shigowar ta ta tsaya tana duban ta da kyau. Tun ba yau ba ta lura Bintalo na neman shisshigewa Alhajin. Ai kuwa mutuniyar ku ta kara bankaro kirji tana kara rambada gyatuma radau din bakin ta. Parlorn ta karasa da sauri tana rage sautin murya,

“Alhaji ina kwana? An tashi lapia?”

“Alhamdulillah sannu!”

Ya bata amsa yana zura takalmin sa sau ciki . Tsayawa tai tana kallon sa harda su lumshe idanu. Ya dan kalle ta yana mamakin tsaiwar da take. Sosa kai tayi tana kara dashare hakoran ta,

“Ya akai?”

“Uhm uhm w...”

“Ke! Meye haka? Me kikeyi anan?”

Cewar Haj Husnah wadda ke sakkowa daga sama tana taunar cingom. Bintalo ta shiga inda-inda tana nuna kofa. Alhaji Kabeer ya girgiza kansa kawai yana duban Haj Husnah.

“Haj ni zan fita. Na gaya miki Amb Salees yazo gari ko?”

“Eh haka kace. Can zaka je yanzu?”

“Eh zan biya ta can. Saboda akwai kwangilar gini da zamuyi magana dashi, Kinsan a gidan sa na bomo yake. Toh shine yake so a fara gina masa wanda zasu zauna anan cikin gari area din Hanwa low-cost.”

“Kai Masha Allah! Shine mai matar sa yar Ethiopia ko?”

“Eh...”

Ya bata amsa yana duba agogon wutsiyar hannun sa. Murmushi Haj Husnah tayi tasa hannu d’aya tana gyara masa karin hular sa,

“Komai yayi dai-dai Abban su. ‘Yayan sa nawa ne yanzu? Ta farkon data rasu bata taba haihuwa ba ko.?”

“Toh godia nake Umman su. Eh bata taba haihuwa ba. Wannan ‘yayanta hudu. Maza biyu mata biyu.”

“Kai Masha Allahu! Sai a daura zumunci. Babban ‘dan na....”

“Hajia sauri nake yi. Kar na tsaida shi kinsan manyan nan. Idan na dawo mayi magana.”

Alhaji Kabeer yai saurin katse ta yana mai ficewa daga parlorn da sauri. Rakiya ta masa. Bintalo dake tsaye kamar gunki ta cire hannun data sa abaki tana susar takashi. Sam ba taji dadin bata mata lokaci da Haj Husnah tayi ba. Da tuni tayiwa Alhaji magana ta sanar masa zuciar ta. Wayaga k’arfin hali. Cikin murtuka fuska Haj Husna ta koma parlorn tana jera kwan cingom. Zama tayi a kujera tana karkada kafafuwa. Bintalo ta fara jan kafafuwan ta zata fita ta kira ta a tsawace,

“Zo nan Bintalo. Munasura! Ina zaki ko guduwa zaki yi?”

Bintalo ta koma tana sadda kanta a ‘kasa. Haj Husnah taja dogon tsaki tana kwallawa Innar Rabi kira,

“Rabi, Rabi, Rabi..”

Da azama inna Rabi ta shiga parlorn hannun ta dauke da ludayi.

“Me kike yanzu?”

“Hajia abincin Haysam nake dafawa.”

“Ok yayi kyau. Dan Allah karki masa me magi irin rannan.”

“IN SHA ALLAH! Hajia.”

“Kina nan Bintalo tazo yau?”

Bintalo ta shiga raba idanuwa tana kallon Inna Rabi, Inna Rabi ta kad’a kai alamun Eh. Kafin cikin sauri tace,

“Ina nan Hajia. Wani abun ne?”

“Sanda Alhaji yana nan. Sunyi wata magana da ita?”

Inna Rabi ta girgiza kai,

“Gaskia bansani ba ko sunyi. Da dai tare muke a kitchen da ita. Toh sanda Alhajin ya sakko kuma sai naga ta shiga parlorn. Toh bansan ya su kai ba kuma.”

Hajia Husnah tayi murmushi hade da yiwa Inna Rabi alama da hannu da ta tafi. Bintalo ta shiga zare idanu. Dayan hannun ta kuma tana sosa takashi. ‘Das ta ‘dada ma takashin duka hade da dukawa ta soso wajen sosai. Haj Husna ta taja tsaki tana jifanta da harara,

“Meye haka?”

“Sittin ta ubangiji wata yar kundin uban tsutsa ce kecin zarafi na a ‘duwaiwai. Mursuleta zan cusawa shegia ta mutu sa..”

“Kina jina? Kada ki ‘kara takomin shegiyar k’afar ki gidan nan. Daga ya...”

Bintalo ta zube a kasa tana kururuwa,

“Wayyo ni Bintalo yar marainiya. Hajia kiyi hak’uri. Sittin ta u..”

“Karki wata rantsuwa. Bara kiji ma nayi miki yadda xaki gane kema, Sittin ta ubangiji zama na dake ya ‘kare daga yau. Ki tattara naki ya naki ki tafi. Mai gidana kike so ina hankalce da duk shige da ficen ki. Ina ke ina miji na? Dube ki dan ALLAH. Wata sad’od’o dake ba gaba ba baya. Sai kaje namiji, ‘kirji kamar silifas. ‘Kazama baki da aiki sai susar takashi. Saboda tsabar kazanta. Ficemin daga gida yanzu kafin na rufe ki da duka.”

Haj Husnah ta karasa balbalawa Bintalo fada tana huci. Bintalo ta shiga runtuma ihu jin kalaman hajian na karshe. Hawaye na zuba majina na kwarara haka Bintalo ta kara gwaggwafewa tana bawa Haj Husnah hak’uri,

“Kiyi hakuri Haj. Kinga an gama lalata min rayuwa ta data ‘yayana. Babbar ‘yata mijin ya saketa da ‘yaya rab’e rab’e, Sittin ta ubangiji wasu kan wasu muke kwanciya a daki. Ga ‘yata ta biyu itama ta kamu da cutar shan inna kowa ‘kyamatar ta yake. Ga Hinde itama ta haife shege. Sittin ta ubangiji bamu da cin yau bare na..”

Haj Husna taja tsaki tana karkada mata yatsa,

“Tashi kificemun a gidah. So kike ki aure nawa mijin. Mumugunciya, munasura, Tashi ki fita..”

Cikin kururuwar kuka Bintalo ta yage zani sai ga robar curry ta fado. Hajia Husnah ta kira Inna Rabi ta caje jikin Bintalo. Bintalo sai kyarma jikin ta yake tana raba idanuwa hade da kwaso rantsuwa kala kala ta dire. Rayco da Curry sai cokali aka samu a kullin dan bantan ta. Da gyatuma rad’au din taa kulli d’aya.

“Sittin ta ubangiji tsautsayi ne Hajia.”

Hajja husnah ta kwashe Bintalo da mari. Bintalo ta baje a kasa tana jera rantsuwar sai dai Inna Rabi ce ta saka mata. Hajja Husnah kuwa sai huci take taci ka fam zata fashe,

“Dama ana tamin yan sace sace duk na dauka sabbin almajirai ne ke mana. Ashe kece barauniyar. Shegiya, Ku dai bakuji dadi ba wallahi. Daga mai asircemin ‘da tana nanuka masa yarta. Sai mai min sace-sace da son aure min miji, Fi ce min daga gida kafin nasa a dauke ki da shegen duka. Karyai gulai kawai.”

Bintalo ta tattare zanin ta tana sake dadawa takashin ta duka, Ta dubi Hajia Husnah dake jiran ta fice mata daga gida,

“Kudin aiki na fa Hajia..”

Hajja Husnah ta saki guda tana tafe hannaye,

“Ah lalle! Wane kudi? Ai duk sace sacen da ki kai a kudin ki ne. Miji na kuwa ko a mafarki ba zaki samu me kama da inuwar sa ba. Ficemin daga gida.”

Bintalo ta dire tsallen albarka kan bata yadda ba wallahi sai an biyata kudin aikatau dinta.

“Ke ko kunya bakiji ba? Wallahi tallahi kinji rantsuwar musulmai? Sisin kobo bazan baki ba. Allah kadai yasan abinda kika sassace mana.”

“Sittin ta ubangiji Indomie ce guda biyar wancen satin da madarar ruwa guda uku. Sai sauran kashin miyar Alhaji da kuma ragowar lemon roba, Danyen sa...”

“Rabi futar min da barauniyar figalalliyar matar nan kafin nai kasa kasa da ita anan.”

Bintalo ta shiga kwaso rantsuwa tana direwa kan sai an biya ta kudin aikin ta. Dakyar Inna Rabi ta jata ta fitar da ita daga gidan. Bintalo kuwa ta tsaya a tsakar gidah ta shiga kwararawa Haj Husnah kwandon tsinan taka itada ahalin ta. Tana yi tana gwafe zani tana dukan takashin ta, Haka ta jima tana lailayo ashariya tana

durawa sai da tai mai isarta sannan ta fice daga gidan tana tafe tana mita har ta karasa layin su.

GIDAN MATA TARA

Tunda shagunan Kawu ila suka kone ya zama mazaunin gidah. Masallaci ma tuni yayi sallama dashi. Kullum yana gida. A tsakar gida akan bokitin sa. Ya lailayo ashar ya durawa wancen ya shararawa wasu mari. Gaba d'aya ya kara zama rigimamme marar mutunci. Fada kuwa kullum sai anyi rabiya dashi. Lamarin dai sai addua kawai. Toh kamar kullum yau ma yana zaune a tsakar gidah ya zabga tagumi yana sakace hakora. Lokaci zuwa lokaci yakan jera tsaki akaro na ba adadi. Yaran sa su takwas cif ba d'aya suna tsakar gidan ana harkijimi dasu kamar kullum da sauran bataliyar yan gidan mu. Cikin haka Mariya yar sa ta shigo kanta dauke da kwanon tallar gyadar da take. Babu sallama bare sallallami haka ta wuce shi ta zauna a kusa da mahaifiyar ta. Sai hararar kudin hannun ta yake da alamun tayi ciniki sosai. Domin tun sanda gobara ta samu kayan sa ya zamto ciyarwa ta gagare shi. Mahaifin Ummitan dake tallafa musu kuma ya rasu tuni an raba gadon ta bashi yaja musu jari ya cinye su tas. Shi yasa yanzu Ummitan ke dorawa su Mariya tallan kayan koli da gyada. Kawu ila sai hararo kud'in hannun Mariya yake yana sauraron yadda take lissafawa Ummitan cinikin da tayi. Hamma yake ta jerawa yana mikar yunwa. Ya sake kaikace kunne yana jiyo su,

"Abbas ne ya siye ta duka yasin. Yace gobe ma akai masa sai siye. Kayan kolin ma kingani rabi ya siya."

"Ah dakyau! Ya kyauta gaskia. Na gangaren cikin tasha ko?"

"Eh shi."

"Ai kuwa da yawa za'ai gobe. Ri'ke ungo nan naki ne."

Ummita tafad'a tana mika mata gudar dari biyar. Sauran kudin kuma ta kukkulle ta d'aure a bakin zanin ta. Kawu ila yaja dogon tsaki yana hararo kudin hannun Mariya. Cike da jin haushi yasa kafa ya hambare butar kusa dashi yana hararar ta tamkar

ita tayi masa lefi. Mik’ewa yai daga kan bokitin sa. Ya gogge shi ya shigar dashi d’aki. Gungun yaran dake wajen ne suka tashi suna musu suka nufe shi, Dauke da wani katin biki a hannun Furera yar Hajara ta uku,

“Baba karanto mana ka fassara mana. Musu muke yi.”

Kawu ila ya shiga zare idanu yana gyaran murya. Dauke katin yake da wasu sunayen amarya da ango christians an rubuta:

‘Happy married life Uchenna and Ikke.’

Kawu ila ya sake gyara tsayuwar sa ya tsurawa katin idanu kafin cikin Irin nuna iyawar nan ya fara karantowa,

“Hafafeya maredade li-fe ukeniya anaduwa ikko. wato birnin ikko kenan legas.”

Walidi ya buga tsallen murna yana rawa irin baban nan nasa ya amsa musu. Basmah dake gefe tace,

“Toh baba me hakan ke nufi?”

Kawu ila ya zauna a bakin rijiya ya takarkare yana shiryo bayani,

“Ita wannan matar da kuke gani. Haifaffiyar birnin ikko ce wato legas hada lefe take yi. Shi kuma wannan lefen sa ne ya ‘bata shine suke tallatawa ma’ana, idan ansamu kayan lefen akai lagos. A takaice dai itace ta hada lefen ya ‘bata shine suke cigiya, Hafafeya maredade li-fe ukeniya anaduwa ikko. Wato Idan an samu lefen akai birnin ikko.”

Usaiba dake gefe ta sheke da dariya tana buga zani,

“Kutsin ubancan kayya kai, Allah ya raba mu da sharota.”

“Waye ya sharota Usaiba?.”

Usaiba ta dafe haba tana kwashe kayan wankin ta,

“Da wanda ya tsargu nake..”

Kwafa kawu ila yayi yana girgiza kai. A lokacin Bintalo ta shigo gidan tana tale kafafu. Tana ganin Kawu ila taja ta tsaya tana daure mayafi a kugu.

“Ilyasu bani hamsin dita daka ara satin baya. Sittin ta ubangiji sai ka biya ni domin ba yadda zan ba.”

Baba Usaiba taja guda ta saki tana taka rawa,

“A hayye! Fatara mai tada tsohon bashi.”

Kawu ila ya cire tagumin daya zabga yana baje kofofin hanci,

“Yanzu babu sai dai idan na samu.”

Bintalo ta dire tsallen albarka tana yarfe hannu,

“Sittin ta ubangiji ba yadda zanyi ba. Alo tsiya alo danja, Shege ka fasa dan halak sai yanka..”

Baba Usaiba ta kara sakin gud’a hade da dukawa ta zana layi agaban su da gawayi,

“Ku casu banban ku casu, Ku casu ba mai raba ku.”

Sauran y’an gidan suka bushe da daria. Baba Ummita da Mariya suka shige ‘daka abinsu. Bintalo kuwa ta shiga lailayo ashariya tana durawa kan sai ya biyata kudin ta.

Tun daga farkon layin mu nake jiyo sautin muryoyin yan gidan mu. Ruwan zagi kuwa sai zuba yake. Na dafe kai na da hannu na na hagu ina girgiza shi. Wannan wacce irin rayuwa ce akeyi a gidan mu. Babu abinda ya canza tun ina kankanuwa har girma na. A zaure na jiyo duk fadan nan akan nera hamsin akeyin sa. Ja nayi na tsaya a tsakar gidah bayan nayi sallama. Na zuge zip din jaka ta na ciro nera dari na mikawa Bintalo ganin yadda take huci. Tak’i karb’a tana jijjiga. Hinde ta tunkubar da darin ta fad’i a kasa. Aka bushe da dariya. Bintalo taja tsaki tana tura dauri gaba, A yamutse ta dube ni cike da kumfar baki tace dani,

“Mikomin.”

Na kalli kudin na kalleta na kuma maida kallo na ga Hinde, Ita ko kunya bataji dan ta khaleel na gefe hancin sa yayi dumu-dumu da majina. Ya tsaya a tsaye ya sau fitsarin sa. Daga abin kirki sai abu ya dawo na tsiya? Na fada a zuci ina murmushi. Ko kallon su banyi ba na fara hawa matattakalar bene,

“Zo ki mikomin kyallukazar kaya. Anje yawon ta zubar an ciko jaka da kudi dole a nuna mana.”

Ban kulata ba na cigaba da hawa sama, Sai nanatawa take cike da umarni. Na tsaya daga hawan da nake ina murmushi. Bansan ya akai ba ni dai kawai naga bakina na furta kalmomin,

“Baba kenan. Kyallukazar kaya ai gasunan kin haife su. Sannan yawon ta zubar kinga sakamako a dakin ki. Daga tsatson ki. Domin ga d’aya daga ciki nan a kusa

dake. Tamkar uban sa yayi kaki ya tofar. Dari na bayar, Hinde ki rike hamsin din kya siyawa wannan yaron naki pampers ko ze dena sakin fitsari a tsaye.”

Ina gama magana na haye sama, cirko cirko na bar yan gidan mu. Gaba d’aya tamkar anyi ruwa ya cinye su. Tsit kake ji da alamun maganganu na sun dake su. Domin tunda Allah ya halicce mu bantaba maida martani ba irin yau. Ko meyasa oho? Murmushi nayi na shige d’aki. Autar mu dake lab’e tayi tsalle ta rungume ni tana jinjina min. Alhamdulillah na fad’a ina ajiye jakata agefe. Domin Innar mu bacci take yi. Kilan data jiyo ni da kashi na ya bushe yau. Ina jiyo muryar baba usaiba tana sakin gud’a,

‘"Ayyiriririririir! Kutsin ubancan kayya kai! A hayye kayya kai..."

Unedited

**

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

27

*

*

*

GIDAN MATA TARA

Bintalo ta zube a ‘kasa tana kururuwa hade da sallallami.

“Ilyasu kana jin bakaken maganganun da yarinyar nan ta gasamin?”

Kawu ila ya buga tsaki yana shigewa d’akin sa, Usaiba ta doka guda tana taka rawa,

“A hayye kayya kai, Mungan su a rana.”

“Du’kurkusar banza.”

Bintalo tace da Baba Usaiba hade da tsirtar da yawu a gefe. Baba Usaiba taja guda ta saki tana buga zani.

“Kutsin ubancan kayya kai, Ai gwara ni, Ke kuwa figalalliyar banza da wofi. Ta gama ‘kare miki da gayyar ‘yaya rab’e-rab’e kowanne da bakin cikin da yake kunsa miki sa...”

Bintalo tayi kukan kura ta cafko wuyan Usaiba suka shiga dambe, Yan gidan mu suka yanyana akan su ana kallon su. Hijabi na zura na tafi gidan su Fadilah domin gaba d’aya karakainan fad’an su ya ishe ni. Can naje muka baje tashar hira da Fadilah, Fadilah taja ajiyar zucia ta sauke tana zabga tagumi,

“Tawan munyi kwantai fa, Ko kinsan Harira y’ar bayan layi aure zatayi kuwa? Kanwar kanwar bayan mu.”

Nayi murmushi kawai ina cigaba da kurbar lemon da ta kawomin, Sai da nasha mai isata tukun,

“Komai lokaci ne Aminiyas, Wallahi da mutuwa da aure da haihuwa duk lokaci ne. Idan Allah yayi toh fa ba makawa sai anyi ko ana muzuru ana shaho sai anyi.”

Fadila ta sake sakin wata bahaguwar zuciar kafin cike da sanyin murya tace,

“Hakane kam! Toh Allah yabamu ikon cin wannan jarabawar. Ai gwara ke ma kin gama karatu kina sana’ar ki ga koyarwa. Ni kuwa rayuwa ta sai cigaba da tabarbarewa take yi.”

Harara na dankara mata ina rufe lemon da murfin sa.

“Karki sabo k’awata. Toh duk abunda nake da shi na kama kafar rufin asirin ki ne? Ai Allah baya hada maka duka, Kada kiyi sab’o. Ki cigaba da godewa Allah a duk halin da kika tsinci rayuwar ki. Allah ya cigaba da dafa mana kede kawai”

“Toh Ameen dai! Ya labarin Haysam kuwa?”

“Yana gidan baban sa.”

Daria Fadilah ta tuntsire da ita tana bubbuga k’afa,

“Meya baki daria? Na raba ki da yaron nan.”

“Tunowa nai mune rabin hamsin din. Yanzu ai shi ya haura haka. Har yanzu kina kan bakan naki ko kuwa?”

“Mu bar zancen nan Aminiyas, Ni tuni mun raba hanya dashi domin wutsiyar rak’umi tayi nesa da k’asa. Allah yabani wanda ya fishi, Shima Allah yabashi wadda ta fini.”

“Ameen tawan..”

Haka dai mukai ta jajantawa junan mu sannan na tashi domin tafiya gidah. Fadila ta yimin rakiya, A tsakar gidah muka ha’du da mahaifiyar su wato Aunty Nanah tana gani na ta dashere hak’ora tana murmushi. Na juya baya na don ganin da wa take? Ganin ni din takewa murmushi yasa nayi yak’e ina sosa kai na,

“Ina wuni Aunty?”

“Lapia qalau Batoul.. Ya mutan gidan?”

Murza idanu na nayi don tantance ko mafarki nake yi.? Ai kuwa dagaske ne, Hakan yasa na amsa ta da sauri cike da farin ciki,

“Sunanan qalau Aunty, Suna gaishe ki.”

“Ina amsawa. Dan Allah ki gayda Innar taku. Uh uhm nace makarantar ku sun fara daukan sabbin dalibai kuwa?”

“Zataji Insha Allahu Aunty! University?”

“Eh nan.”

“Farkon shekara inajin zasu fara IN SHA ALLAH!”

“Masha Allahu! Toh dan Allah yar kanwar ki zaki samawa, Kinsan komai sai da hanya.”

“Toh babu damuwa, ALLAH ya kai mu lokacin.”

“Ameen Ameen.”

Haka dai mukai sallama da Aunty, Fadilah tamin rakiya har farkon layin mu. Ina tafe ina mamakin Auntyn su. Lalle Allah qadirun ne ala Manyasha’u, Ya daga wanda yaso a duk sanda yaso. Wai ni ce yau Aunty ke neman alfarma awaje na?

“Alhamdulillah Ya Allah for the unlimited blessings..”

Na fada a zuciata ina murmushi. Can kofar Ghali mai shago naga dandaxon mutane. Karasawa nai ina jiyo sautin dukan da ake lakadawa galin yana callara kara. Wani yaro na tambaya menene? Nan ya sanar min cewar ai kama galin akai yayiwa wata yarinya fyade. Sai da yaci duka ya lissafo sauran sunan yaran daya lalata. Ciki harda Basma da Farida. Kasa b'oye farin ciki na nayi. Na shige gidah ina hamdalah da karfi hade da kururuwar shelar fadar gali ne yayiwa su Basma fyade. Kankace me? Tuni gidan mu da unguwar mu ya kacame da hayaniyar zancen. Mu kuwa dadi ne fal xukatanmu. Innar mu har hawaye se da tayi. Yayan mu agaban kowa yayi sujjada yana godewa Allah. Ranar dai baccin dadi muka yi ni da su Innar mu. Banda su Bintalo da abun ke 'bararrakar zukatan su. Domin sam basu ji dad'in hakan ba.

**

Dukawa Bintalo tayi ta gwagwada mursuleta a duburar ta. Ta dadawa takashin duka tana sakin tsaki,

"Yar kundin uba, Yanzu mursuletan zai hallaka ki. Baki da aiki sai cin zalina a duwaiwai.."

Ta karasa fada tana sake 'dadawa takashin ta duka. Gaba d'aya a hautsine suka a dakin. Kan katifar Alawiyyah ce da Hauwa da Khaleel dan Hinde. Sai daga 'kasa a gefe kuma Bintalo ce a tsakure itada Hinde, Daga gaban katifar kuma zabbau ce itada yaranta su biyar wasu kan wasu. Bintalo ta dube su duka taja tsaki tana sosa diddigaggen gashin ta. A lokacin daya d'aga cikin yaran zabbau ya tashi yana kuka,

"Mama kahi, Kahi zanyi."

"Kashi kuma? A daren nan? Dan kundin uba."

Bintalo ta fada tana dungure masa kai, Zabbau ta mike tana sakin hamma,

"Tahi muje. Shege tsinanne nafara bacci ka tahe ni."

Kankace me? tuni sauran yaran sun tashi suma, Wasun su suka fara kuka wasu kuma suna neman abinci.

“Ni gaskia shegun yaran nan sun isheni, Zabbau ki samo mafita dan Allah.”

Cewar Hinde tana sake jan hijabin data rufe jikin ta dashi. Zabbau har ta kai bakin k’ofa ta juya tana tafa hannaye,

“A hayye! Ke Hinde har kinada bakin magana? Su da uban su ai, Ke kuwa kece uwar shege. Ga shege nan kin haife batare da hanyar aure ba. A hayye.”

Nan dai fad’a ya kaure tsakanin su. Bintalo taja tsaki ta fita daga dakin tana dura musu ashar. A k’ofar dakin ta shimfida dan buhun ta da matashin kai ta kwanta tana rantsuwar da safe sai taci mutincin su.

“Sittin ta ubangiji Allah ya kai mu safiya duk sai kunbar gidan nan. ‘Yayan iska..”

Haka dai su kaita fada suna doke-doke. Mu kuwa sama sama muke jiyo hargagiyar su. Kwanciya ta na gyara ina lumshe idanu. Sakamakon daddadan baccin daya fara ‘dauka ta....

BOMO ZARIA

Tunda suka koma gida ya wuce side d'insa bai fito ba sai dare, daren ma sai da mahaifiyarsa taje ta kamo shi ya d'an sha tea sannan ya koma, bai sake fita koda bakin gate ba har yau da suka yi kwanaki biyu da zaga garin. Muhammad Mubeen kenan, yana kwance sai faman juyi yake akan gado tamkar wani mai ciwon jiki. Wayarsa ya janyo ya kunna ya shiga daddanwa yana hira da abokansa da suke can k'asar.

“Mubeen! Mubeen!!”

Amb Salees dake bakin k'ofar side d'in Mubeen d'in yake ta faman kiransa, da yaji shiru yayi tunanin ko bacci yake yi, ya juya zai tafi sai yaji alamun tafiya ya waiga.

“Ohh Mubeen, kanaji amman amsawa ya gagara, oya zo muje kayi min rakiya wani guri.”

Yatsansa wanda ake d'agawa idan za'ai zaman tahiya ko za'a nuna abu shi Mubeen ya zura a cikin kunnansa na b'angaren hagu yana sosawa. Amb ya kuma binsa da kallo wayarsa rike a hannu ana ta faman kiransa amman bai d'aga ba saboda yana son ya gama tabbatar da abinda d'an nasa yake nufi.

“Karka ce min ba zaka ba, kaje ka shirya kazo ka sameni a wajan mota.”

Amb Salees na gama sanar masa ya juya ya wuce cikin gida, yabar Mubeen a tsaye yana faman had'e rai. Shi yasa baya kaunar zuwa k'asar nan saboda sam ba'a bari su huta, kodai a d'auke su akai su gidan 'yan uwa da abokan arzuk'a, ko kuma 'yan uwa suzo gidan duk su ishi mutane da surutu. Mubeen ya kad'a kai ya juya cikin bedroom tare da zama a bakin gado, sam baya son fitar nan musamman bugun zuciyar da ya dinga yi ranar da suka fita, da ya kwanta da kyar ya iya yin bacci saboda rashin samun nutsuwa da yayi. Ya jima zaune yana tunanin inda zasu je, can kuma ya kalli agogon dake kafe a jikin bango. Karfe hud'u da kwata na yamma (4:15pm), ya tashi ya bud'e wardrobe yana karewa kayan ciki kallo.

A hankali idanunsa suka sauka akan wasu riga da wando na shadda kallar ruwan toka (ash colour), ya d'akko su tare da ajiyewa akan gadon ya nufi inda takalmansa suke a jera sai walwali suke yi. Wani had'add'an covered shoe ya d'akko shima kalar kayan sannan ya dire su a k'asa ya bud'e cikin wani show glass, huluna ne a jere suma kala-kala abin gwanin ban sha'awa, ya d'akko ash wadda mahad'ar kayan ce itama ya ajiye akan gado. Bathroom ya nufa ya sakarwa jikinsa shower, ya gama wankan tsab sannan ya fito sanye da bathrobe fara kal. Wajan mirror ya nufa yana karewa dukan ilahirin jikinsa kallo, kafin ya d'akko d'an karamin towel ya fara goge sumar kanshi, wacce take a kanannad'e. Sai da ya tabbar ya shafa mai da body spray sannan yaje ya sanya vest ya saka kayan.

Watabarakkallahu Ahsanilkalik, ko wanda yafi kowa hassada da kyashi, idan yaga Muhammad Mubeen dole ya yabeshi dan ba karamin kyakyawa bane. ALLAH ne mai yadda yaso a lokacin da yaso kuma yayin da duk yaso sai ya tsara abu. Wannan bawan nasa kam ya had'a komai, ya taso cikin arziki yana rayuwa cikin daula, wajan hallita tamkar shine aka bawa damar ya halicci kansa. Fitowa yayi yana d'aura agogo a wutsiyar hannunsa, ya tsaya a wajan freezer d'in dake parlourn ya bud'e tare da janyo kwalin hollandiyya ya zuba a cup ya sha sannan ya mayar ya rufe ya fita.

Shima Amb Salees fitowarsa kenan shi da su Aeedah, Maman su kuma tana bakin k'ofar zata rufe.

“Yayya Mm muje ko?”

Cewar Amb Salees yana kallon babban d'an nasa dake tsinkar wani pink d'in fure a jikin wata shuka. Ba tare da yayi magana ba yaje yaja hannun kaninsa Mashkur suka nufi wajan mota.

Zaria city suka nufa, can unguwar Kwarbai gidan sarkin zazzau d'in. Kai tsaye gidan suka dosa, ganin irin motar da ta nufo gidan yasa aka fara yi musu kirari, ana mik'a musu gaisuwa. Mubeen dake zaune a gefe kusa da glass ya kawar da kai saboda hayaniyar fadawan da suke ta yiwa Amb Salees kirari domin tuni suka gane shi.

“Mm please ka dinga gaida mutane, kaga nan ba Ethiopia bane, karka ja min surutu kaji big son?”

Amb Salees ya fad'a bayan sunyi parking yana lek'en Mubeen, maganar yake masa cikin tausasa harshe da nuna tsantsar kulawa had'e da lallashi. Kai tsaye cikin fada aka nufa dasu sai gaishe su bayi suke yi, ran Mubeen gaba d'aya a b'ace yake, tunda ya dora kwayar idanunsa a gabas bai sake waigawa ya kalli wani abun ba har suka shiga. 'Yar gaisuwar da Amb ya roki yayi kasawa ya yi saboda rashin sabo, ga tafiyar mota yasa ranshi ya kuma b'aci, har suka shiga fadar sarki bai saki fuska ba. Duk gaida shi suka yi, sarkin ya kirawo Mubeen ganin yayi shiga ta kamala, gashi da kunya kamar ba matashi d'anye sharaf ba.

“Amb wannan ina yiwa little princess d'ina kamu, amman yanzu tana primary 2”

Gabaki d'aya gurin aka yi dariya amman ban da Mubeen wanda yake jin tamkar yayi k'asa. Albarka ya dinga sa masa iyayen suna amsawa.Mamma Ahlaam suka fito ita da yaran zuwa side d'in Fulani Aisha matar sarki ta farko aka bar Amb da Mubeen dake zaune a can gefe yana kallon wasu zanuka da aka yi a gurin. Cikin girmamawa Amb Salees yake mayarwa da maimartaba amsoshin tambayoyin da yake masa.

“Yanzu dai ka dawo da karfinka kenan na tsayawa takarar ko?”

“Eh ranka shi dad'e ALLAH karama lafiya, jiya ma munyi maganar da party leader d'in jam'iyar, ya kuma tabbatar min da cewar ni za'a nad'a d'an takarar gwamna a jam'iyar tamu.”

“Toh Amb sai kun dage sosai, ni dai ina bayanka, amman kasan ba zan fito fili na bayyana ba. Kuma kasan abu ne da kamar wuya a ce jam'iya mai mulki sun bari ta adawarsu ta samu galaba akan su ba. Ka dage sosai wajan janyo talakawa a cikin shekara d'ayan nan da zaka yi kafin zabe, kaji?”

Amb Salees ya dinga jinjina kai alamun zai yi k'ok'ari wajan ganin hakan ya tabbata. Sun dade a gidan domin har wajan 9:00pm suna gidan, maimartaba sai janyo mutane yake yana sake had'a Amb dasu wad'anda zasu dad'a taimaka masa wajan campaign. Mubeen kuwa tun yana jin dad'in gidan har ya fara takura kasan cewar yaki zuwa ya d'an zazzaga gidan, yana zaune ne kawai a cikin wani kayataccen parlour yana kallon kwallo.

Kira ya dinga dannawa Mamansa idan ta d'aga kuma yaki magana kuma yana ji, bud'e baki yace suzo a tafi shine yake masa matuk'ar wahala. Ita kuma Haj Ahlaam ba zata iya kiran Amb ba, dan tasan tunda bai fito ba har lokacin magana suke yi. Sai da taran tayi sannan Amb ya kirawo su suka fito, Mubeen sai kuma had'e rai yake kamar zai fashe dan haushi har suka karasa gida bai yi magana da kowa ba.

LIMANCIN KONA

Kwanaki sun shud'e sun koma sattitika, yayin da sattitika suka koma watanni, wasu da dadi wasu sai addu'a, a gurin mu kuwa sai hamdala, domin duk irin yadda 'yan gidan mu suke tozar tamu hakan bai hana ALLAH rayamu ba. Ina ta yin teaching d'ina ana biya na muna cikin rufin asiri sosai. Mazajen aure kuwa sai hamdala domin zuwa suke yi kamar ana kai musu talla ta, sai dai nakan samu matsalar su kawu ila. Gabaki d'aya sun hana samari na zama, wasu da aure na suke zuwa gadan-gadan amman sai 'yan gidan mu suyi yadda sukai wajan wulak'anta ni har sai sun tabbatar na rasa saurayin sannan zasu kyale.

Watanni na bakwai da fara yin teaching, ina zaune a staff room ina marking d'in wasu test da na yiwa yara sai ga massege ya shigo ta cikin waya ta sabuwa dana sake saya, ta wajan Haysam kuwa Inna na barwa ita. Zaro wayar nayi daga cikin jakata na duba.

''Kizo da takardunki gobe da safe office d'ina.''

Nayi murmushi bayan na karanta, cikin rai na nace Mrs Suleiman bata san na samu aiki ba, ina ji a jikina cewar kila aiki take son samar min itama, saboda tun ina degree take cewa insha Allahu zata samar min aiki, bayan na kammala masters na sanar mata nan ma ta min fatan alkairi tare da cewa zata tuntub'eni wani lokacin. Ni kuma dana samu aikin teaching d'in nan sam ban sanar da ita ba, amman a raina na kudiri aniyar zuwa goben wato ABU d'in na kai mata takardun sai na gaya mata ina aiki.

Da muka tashi daga school na nufi gida, yau kam gidan mu babu hayaniya na shiga cike da kasaita har wata iska nake ji tana shiga jikina. Nayi mana sha'awar ina ma mu kadai ne a gidan mu, nasan da tuni nafi haka kyau da kiba, amman su Bintalo ba zasu barni ba kodan shegunan bakunan su. Na shiga cikin d'aki Innar mu ta gama abinci sai kamshi yake na kifi, na zauna ina cewa.

“Washh Inna yau kam na gaji.”

“Toh sannunki sai ki huta ai kiyi sallah.”

“Tom Inna. Gashi gobe ma zanje can makaranta ana nema na nakai takardu.”

Inna ta tsaya da abinda take yi tana kallo na tace.

“Wacce makarantar kuma?”

“Inna can ABU Mrs Suleiman na nema na.”

“Allahu akubar, kedai taku tazo d'aya da wannan matar, toh ALLAH yasa alkairi ne yasa take nemanki.”

“Amin Inna, a ci gaba dayi mana addu'a insha Allahu alkairi ne.”

Daga haka muka danyi hira kafin na tashi naje nayi alwala, ina cikin yin sallah Yayan mu suka dawo shida Autar mu itama sun had'u ne tana dawowa daga makaranta. Shima na sanar dashi zuwa na can makaranta yayi min fatan alkairi har yace shine zai rakani. Da safe kuwa da wuri muka shirya nida Yayan mu muka tafi, bayan munje na shiga office d'inta shi kuma Yayan mu ya jira ni daga waje. Na shiga na gaida ita ta bani lemo da ruwa na jarka sannan ta karb'i takardun tace na tafi duk yadda ake ciki zanji. Haka nayi mata godiya bayan na sanar da ita ina koyarwa a primary tace dani ba komai naje zata nemeni, muka tafi ina bawa Yayan labari.

Bayan wata daya ina zaune ina shirya result d'in yara da suka yi exam sai ga kiran Mrs Suleiman, na gaida ita cike da girmamawa, kawai naji tace min na samu lecturing a nan cikin ABU samaru campus.....

—

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

29

IGIYAR ZATO....❤

UNGUWAR BOMO

Da d'an gudu-gudu ya sakko daga d'an steps d'in da zai shigar da kai sashen Haj Ahlaam, hannunsa rik'e da jota da biro ya nufi wajan da ake ajiye motoci. Cikin sauri sabon driver d'in da aka kawo musu gidan ya bud'e masa k'ofar, Mubeen ya shiga gidan baya ya zauna. K'ok'arin shiga driver yake suka ji muryar Amb Salees yana magana.

“Ya zai tafi shi kadai? Kasan fa bai san ko'ina ba a can, kuma a irin wannan lokacin da nake cikin campaign dole sai yaran nan suna fita da masu kula dasu, ba wai ina cewa mutanen sune zasu kula da shi ba. A kallah dai muma muyi wani abun sai ALLAH ya dafa mana.”

“Na fahimceka ranka ya dad'e, amman yanzu kam karka damu zan taya shi shiga wasu guraran.”

Driver ya fad'a yana d'an rissinawa. Amb ya jinjina kai, sannan ya karasa wajan Mubeen dake zaune a cikin motar yana game a cikin wayarsa.

“Mm.'”

Ya d'ago yana kallon mahaifin nasa cike da girmamawa, ya kuma ki bari ya had'a ido dashi.

'”Allah ya tsare kaji? Nasan bani da matsala da kai, but be very carefull.”

Kai ya d'aga sannan driver yaja suka tafi. Shi kuma Amb ya shiga mota shida mutanansa suka nufi kaduna yin wani taro su da magoya bayanshi.

Cikin ABU suka nufa, Mubeen ya sakko bayan sunyi parking. Tunda ya fito mutane ke kallonsa maza da mata, shi kuwa babu abinda ya damesa domin bai ma san suna yi ba kasan cewar idanunsa kasa suke kallo. Kai tsaye admin block ya nufa, yana shiga dai-dai lokacin Batoul ta fito daga office din wani HOD. Mubeen yaji zuciyarsa na harbawa, nan da nan ya d'ago kai yana d'an jujjuyawa tamkar mai neman wani abun. A hankali ya juyar da kansa gefen hagu, dai-dai lokacin ita kuma Batoul ta wuce ta gefensa na dama tana sakarwa Haysam murmushi. Mubeen dake tsaye ya juya dama sai dai baya ganin komai da yake sa shi fad'uwar gaba, hakan yasa shi rintsa ido yana karanta hasbunallahu wani'imal wakil.

Kai tsaye office d'in wani dean ya shiga, ya jima a ciki dan kamar ba zai fito ba, ashe da ya shiga kwanciya yayi sai da yaji kirjin nasa ya lafa sannan ya fito yana wani yatsina fuska. Can cikin school d'in ya zazzaga, 'yan mata da sauran samari sai kallansa suke yi, wasu suyi masa maga amman sai ya kasa koda sakar musu fuska, ko d'an murmushi kasa yi yayi saboda rashin sabo. Yaje ya gama zazzagawa sannan ya nufi mota suka koma gida.

Batoul kuwa sun jima ita da Haysam a tsaye, bayan sun d'an yi gaisuwa take tambayar sa mai yasa bata ganinsa, ya shaida mata cewar baya garin ne yayi tafiya. Tare suka taho a motarsa abinsu gwanin ban sha'awa tamkar wasu sababbin amare, ya kalleta bayan ya d'an rage gudun da yake yi yana cewa.

“Mine har yanzu baki bani damar fitowa ba, ko dai banyi miki bane?”

“Sam ba haka bane Yaya Haysam, idan nace bakai min ba toh wa nake son yayi min? Kuma karka manta ka zama wani babban jigo a rayuwa ta. Yaya Haysam mahaifiyar ka bata san mu'amular mu, musamman irin wacce kake son mu kulla shin ya zan yi na amince maka nazo zuciyata ta rikirki ce. Na baka dama kaje ka karbo mana yarda da amincewar iyayenka, ni nawa basu da matsala, ALLAH ya tabbatar mana da alkairi.”

Wani irin sanyin dad'i ya ziyarci zuciyar Haysam, ya kalli Batoul sosai kafin yace.

“Insha ALLAHU yadda kika bani dama a yanzu baki wani gaddama ba. Suma wannan karan zasu bani goyan baya.”

Murmushi nayi masa dan ko a raina banji cewar zamu iya yin aure da Haysam ba, gashi na tsani mahaifiyar sa tun lokacin da ta yi mana rashin mutunci. A zuciyata na dinga addu'ar ALLAH karya tabbatar da wannan abun, dan har ga ALLAH na kasa mantawa da abinda Hajiya Husnah tayi mana. Kafin mu karasa unguwar mu, nace ya sauke ni saboda kar wani ya ganmu yaje yayi mana sharri. Nayi masa godiya bayan na sauka daga motar na wuce, ina jinsa har sai da na karya kwana sannan ya tashi motar shima ya wuce gidan su. Ina komawa gida na sanar da Innar mu duk yadda muka yi a makaranta, sannan na sanar da ita ranar da za'a yi mana interview da screening tayi min fatan alkairi.

•••••; •••••; •••••;

ABU

Saukarta kenan daga keke napep, sanye cikin riga da zani rafa na wani green d'in lece da ratsin milk na zare a jiki, tayi amfani da mayafi milk jaka da takalimi suma duk milk color tayi kyau sosai. Mai napep din ta tsaya ta bawa kud'in sa, dai-dai lokacin motar da aka kawo Mubeen tayi parking a saitin su Batoul wacce ke sanya canjin da aka bata a cikin jaka. A hankali ya fito daga cikin motar ya tsaya, dai-dai lokacin Batoul taje ta wuce ta gefensa tare da bula masa mayafinta da take gyarawa ya gogi kumatunsa.

Kallonta yayi amman baiga fuskarta ba kasan cewar ta wuce. yaji kirjinsa ya ci gaba da bugawa, hakan yasa shi ya fara bin bayanta ba tare da ya san yana yi ba. Driver d'in sai magana yake masa amman baiji ba, mutane sai kallansa suke yi sun d'auka tare suke. Sai da Batoul ta shiga office sannan ne hankali da tsantsar bugun zuciyar Mubeen suka tsaya. Ya kuma neman ta inda yake jin bugun amman ya kasa gano manufar zuwan shiga riki cin.

Dafe kansa yayi tare da lumshe idanunsa na tsawon lokaci. Muryar driver d'insa shine ya dawo dashi cikin nitsuwarsa inda yake tambayarsa ina zashi bayan ba nan ne hanyar department d'in su ba. Bai ce komai ba sai karb'ar kayan karatunsa da yayi sannan ya juya ya tafi. Har ya zauna yana tunanin wadda ya gani, wacce yana

kyautata tsammanin itace take sanya shi jin bugun zuciyar nan, amman abin da yake daure masa kai shine, tun fa ranar da suka fita yawo shida 'yan gidan su ya fara ji, gashi yazo makaranta abin ya tsananta, kodai wata ce take bibiyarsa?. Shi dai a ranar yaji lectures ne kawai amman idanunsa basu dena hango bayan matashiyar da ta dinga jansa a sihirce ba. Bai san wane department take ba, uwa uba bai san yanayin fuskarta ba bare nan gaba ya gane ta.

Ranar alkhamis shine ranar da zan fara lecture, bayan na gama shiryawa cikin wata atamfa brown da ratsin orange a jiki, na d'auki orange d'in mayafi na yafa sannan nayi amfani da black flat shoe da jakarta da na zuba komai da zan buk'ata a ciki, na kalli Innar tare da cewa.

“Wallahi ina gabana fad'uwa yake yi, anya zan iya gabatar da lecture d'in nan a gaban zafafan students?”

“Uwa ta zaki iya mana, ai da koyo aka san gwani, kiyi ta addu'a insha Allahu zaki iya.”

Ta fad'a cike da karfafa min guiwa, na jinjina kai tare da d'aukar turaren da Yayan mu ya siyo mana na shafa, na juya zan tafi sai gashi ya shigo d'akin, yayi murmushi tare da cewa.

“Weldone sabuwar lecturer, kinga yadda kikai kyau kuwa?”

“Yayan mu nifa fargaba ta fara min yawa, wallahi gani naje yi tamkar ba zan iya yin lectures d'in ba.”

Yayan mu ya tuntsure da dariya, hakan yasa ni turo baki ina kallansa.

“Yayan mu dariya ma zaka min ko?”

“Sorry k'anwata, kece da abin dariya, menene abin jin tsoro sai kace wata 'yar kauye? Ki daure daman komai na farko ai sai ya tsorataka, amman karki bari zuciyarki ta karaya. Kiyi addu'a idan zaki fita, sannan in zaki shiga lecture d'in nan ma kiyi addu'a.”

Sai naji kwarin guiwa ganin yadda duk suka karfafa min zuciya, na kallesu tare da yin dariya har hakorana suka fito nace.

“Zan iya, nima yanzu naji tabbacin zan iya, sai na dawo, ina alfahari daku baki d'aya.”

“Ya Batoul ki siyo min abin dad'i.”

Cewar autar mu, na amsa mata da 'toh' sannan na wuce na fita ina ta addu'a. Da kawu ishaq muka had'u yana jan ruwa daga rijiya, na gaida shi bai amsa ba sai kallo da ya bini da shi yana tab'a baki, ganin abinda yake min ne yasa ni fita ba tare da na kuma bi ta kan kowa ba. Sai da na fara zuwa office na zauna har zuwa lokacin ya cika wato karfe takwas, na dauki jaka ta na wuce venue d'in da zanyi lecture d'in. Baki na dauka da sallama, da basmala na shiga, kai na a k'asa na kasa kallon kowa har naje na tsaya a wajan da ya kasance gurin tsayuwar duk wani mai gabatar da jawabi. Na ajiye jakata sannan na d'ago kai tare da dora idanuna akan d'aliban.

-

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IGIYAR ZATO.....□

30

Sallama na fara musu, Da farko muryata ta fara rawa, Amman daga baya sai na fara bayani dalla-dalla. Sunana da gurbin karatu na na fada musu cikin harshen turanci,

“Assalamu Alaikoum sunana Batoul Salisu idris Najibullah, Kuma ni ce malamar ku ta wannan course din. Da farko kafin mu tsunduma cikin abunda ya kawo mu. Zan fada muku gurbin karatu na dama sunayen darussan da zan d’inba d’aukar ku. Nayi

karatu na na degree anan makarantar bangaren B.A English kamar ku. Inda na dora da degree na biyu a jamiar dake kaduna. Alhamdulillahi bayan wasu lokuta kuma Allah yasa na fara koyarwa akan ku. Inda zan dinga koyar daku subjects/courses, ‘History of English literature. Da kuma The Essay in English: The Twentieth Century: Theory and Practice.’ Wato courses biyu kenan..

Tunda ta shigo yaji yana neman rasa tunaninsa duk kuwa da cewar bai d'ago ya kalleta ba, ya sake rintsa ido yana karanta hasbunallahu wani'imal wakil. Tunda ta fara magana Mubeen ya nemi ji da ganin sa ya rasa na 'yan wasu dakikai, Gaba d’aya bugun zuciar sa ya tsanan ta. Zazzakar muryar ta sai karakaina take a cikin kunnen sa. Wani irin shauki yaji yana d'iban sa akan yaje gare ta. A hankali yasa hannu ya dafe saitin zuciar sa. Da k’yar ya iya d'aga idanuwan sa ya dora su a saman fuskar ta. Ya cigaba da mata wani irin kallo tun daga kan yatsun ta zuwa fuskar ta. Kasa dauke idanun sa yai daga gare ta yana mata wani irin mayen kallo. Saurin sunkuyar da kansa yayi yana istigfari. Gaba d’aya baya jin bayanin da take yi. Muryarta ce kawai ke masa yawo a kunnuwan sa, Yayin da kyakkyawar fuskar ta ke bayyana a idanun sa.

Ni kuwa gaba d’aya yana yin yadda yan acikin suka bani nutsuwar su yasa naji dadi na cigaba da kwararo bayani na,

“Yau zan fara daukar ku course din; The Essay in english: The 20th century(Theory and practice). Ranar Friday’s kuma zan dinga daukar ku course din: History of english literature. Kafin nan zan fa’di doka na, Banda latti, Banda shige da fice idan ana lectures sannan banda yawan magana, Sai abu na karshe attendance dole ne shi da presentations. Kuna jina?”

“Eh...”

Suka fada da karfi, Gaba d’aya mazan ajin sun sake bada nutsuwar su ganin ta budurwar malama gata yar kyakkyawa. Ai kuwa wani daga cikin su ya daga hannu zai yi tambaya. Alokacin Mubeen yai saurin juyawa yana masa wani irin kallo, Domin Haka kawai yaji bayason yaron yai magana da ita.

“Ma’am shekarun ki nawa? Sannan matar aure ce ke ko budurwa?”

Yana fad’an haka gaban Mubeen ya yanke ya fadi. Tsura mata idanu yai dake seat din da yake shine na farko dayake kallon podium din da take a tsaye. Murmushi kawai Batoul tayi kafin cikin dakewa tace,

“Na wuce shekaru ashirin sannan bani da aure amma an kusa..”

Mazan ajin suka sa ihu suna tafi. Mubeen ya bata rai yana dankarawa wanda yai tambayar harara. Batoul kuwa na gama introducing na course din ta fice kan nextweek za su fara shiga kundin darasin. Da sauri Muhammad Mubeen ya bi bayanta hannun sa d’aya dafe da saitin zuciar sa. A hankali cike da nutsuwa take tafiya, So yake ya tabbatar da salon sabon takun zuciar sa. Waya take yi da Yaya Najibu alokacin batasan ma yana biye da ita a baya ba,

“Eh wallahi Yayan mu, Yaran basu da matsala gaskia. Eh nagama musu yau kawai na fada musu course outline d’inne. Ameen Ya Allah Yayan mu. Yauwa sai na dawo..”

Murmushi Mubeen yai yana shafa kansa. Ko kad’an bai damu da yadda mutane ke binsu da kallo ba. Idan har ba sani kai ba zaka dauka a tare suke. Ja yai ya tsaya a bayan ta lokacin da take kokarin shiga office din ta. Juyawa tai jin motsin mutum a bayan ta. Karaf idanuwan su suka hadu. Kowanne sai da wani abu ya ziyarci jikin sa. Kasa dauke idanun sa yai daga kanta. A hankali ya fara kokarin bude baki ya mata magana amman ya kasa. Shigewa tai ciki ya bi bayanta. Zama tayi akan kujera bayan ta ajiye laptop din hannun ta akan desk. Dagowa tayi ta kalle shi a karo na biyu.

“Baka iya gaisuwa bane?”

Murmushi yai yana sake sunkuyar da kansa kasa. Zuciyar sa kuwa tamkar zata fito ta fadi saboda tsabar yadda take bugawa. Kallon sa Batoul ta sake yi tana dan hade rai,

“Baka jina ne?.”

Girgiza kai kawai yayi ya juya ya fita. Ita kuma ta zauna tana dudduba wasu syllables. Yana fita ya dena jin yadda bugun zuciar sa ke dokawa idan yaga wulgawar malamar tasu. Mota ya shige ko takan sauran lectures din da za’ai bai bi ba. Jingina yai da kujerar motar yana lumshe idanun sa. Gaba d’aya duk wani motsi da ganin sa ita yake gani. Kama kasan lips dinsa yai yana ciza. A hankali ya zaro wayar sa yana danna recording din muryar ta da yai sanda ta fara lectures. Tamkar mai ciwon lebe a hankali dakyar ya furta kalmar

“Ayana..”

(Beautiful flower)

Ya karasa fada yana jingina wayar a k’irjin sa hade da lumshe idanu yai murmushi. Direban dake jan motar ya tsaya yana kallon sa ta mudubi,

“Oga ba lapia kuwa?”

Girgiza kai Mubeen yai alamun a’a. A haka suka karasa gidah. Lokaci lokaci Mubeen kan saki murmushi shi kadai.....

Kodah Mubeen ya koma gidah gaba d’aya sai walwalar sa ta ‘karu. Mahaifiyar su ta kasa shiru sai data tambaye shi ganin ya zauna a parlor yana murmusawa lokaci zuwa lokaci,

“Mm da alama wani abun farin cikin ne yasame ka ko?”

Murmushi Mubeen yayi yana sosa girar sa da yatsa daya. Beyi magana ba, Hakan yasa Mamma Ahlaam yin shiru kawai tana girgiza kai. Mikewa tai ta shiga kitchen. Bata jima ba tafito da tray dauke da abinci. Ajiye masa tayi akan center table din dake gaban sa.

“Mamma a ‘koshe nake.”

Ya karasa fada yana rausayar da kai, Sam bayason cin abinci tamkar wani dan karamin yaro. Sa shi tayi a gaba da lallami har ya fara ci. Cikin haka Amb Salees ya dawo. Shima ya zauna yaci abinci, Suna tab’a hira lokaci zuwa lokaci shi da Haj Ahlaam. Banda Mubeen da ke danne danne a wayar sa.

“Mm ya school din? Tayi ko kana nan akan bakan ka na kai bakason ta?”

Wayar sa ya ajiye akan table yana kallon mahaifin nasa. Ajiyar zuciya ya sauke domin haka kawai yaji kuma bayason ya dena zuwa.

“No papa zan cigaba da zuwa.”

Amb salees da Mamma Ahlaam suka kalli juna cike da mamakin abinda Mubeen yace. Sam basu taba kawowa zai yi saurin sakkowa haka ba. Du bada idan ya tsani abu ya tsane shi kenan har gaban abadan. Idan kuma yanason abu to duk rintsi sai ya mallake shi. Shin ko meyasa ya sauya ra’ayin sa? Amb Salees ya jinjina kai yana daga kafada,

“Masha Allah! Toh Allah yasa albarka a karatun naku. Kaga hakan shine dai dai, Na fito takara za’a ga ‘dan ciki na bai je waje karatu ba kamar yadda sauran yan siyasa keyi. Toh Allah ya bamu nasara gaba ki d’aya..”

“Ameen Papa.”

Mubeen ya fada yana tsotsan kasan lips dinsa. Amb Salees ya kurbi ruwan gaban sa kafin yace,

“Toh har an gama lectures dinne ka dawo gidah?”

Girgiza kai Mubeen yai alamun A’ah.

“Toh this should be the last, Ka dena fashi. Saboda attendance is compulsory and ...”

Ai tuni Mubeen ya dena jiyo muryar mahaifin nasa, Take sautin muryar Batoul ta shiga yawo a kansa. Inda take musu maganar attendance compulsory ce. Sai lumshe idanu yake hade da kara jinginar da kansa a kujera.

“Ina fatan kana saurara?”

Sai a sannan Mubeen ya farfad’o daga day dreaming din daya tafi. Saurin kada yayi hade da mik’ewa ya tafi sashen sa. Yana shiga dakin sa ya wurgar da wayar sa akan gado. Ban’daki ya fada yayo wanka hade da alwala. Sallah yayi yadan taba karatun qur’ani kafin ya sake mikewa ya haye gado ya kwanta. Tuni bacci daddad’a ya dauke shi, cike da mafarkin Batoul wadda batasan ma yanayi ba. Wayaga karfin hali soyayya da malamar aji.

GIDAN MATA TARA

Ina gama abubuwan da zanyi a makarnta na dawo gidah. Gaba d’aya a gajiye nake wallahi. Lalle lecturers suna k’ok’ari wallahi. Rana d’aya har na fara fita daga hayyaci na. A gajiye likis na shiga layin mu. Tun daga farkon layin mu nake jiyo kwakwazon yan gidan mu. Allah ya kawo mu. Na fada a azuciya ta ina girgiza kai. Da sallama a baki na na shiga gida. Gaba d’aya a hautsine tsakar gidan mu yake. Ba babba ba yaro an zagaye Bintalo da Kawu Ishaq sai surfa zagi take yi tana buga zani hade da watsa hannu baya,

“Sittin ta ubangiji hak’uri na ya kare. Idan ita Kaltume ta bar maka toh ita taga zata iya. Ni kuwa sai ka sallame ni a satin nan. Idan kuma ka ‘ki. Toh Sittin ta ubangiji dole ne ku tattara naku ya naku daga dakin nan tunda ba mallakin ka bane.”

Kawu Ishaq ya daga hannu alamun ban haku’ri. Bintalo ta buga tsallen albarka ta dire, Hade da kwararo zagi da rantsuwa kan bazata yadda ba.

“A hayye nanaye! Yau ga gaye ba makilis, Sittin ta ubangiji isyaku ba yadda zanyi ba. Shekara da shekaru kana zaune ka gaje daki tamkar wanda akace an bar maka? Sittin ta ubangiji hak’uri na ya kare.”

Tana gani na tayo kai na tana susar takashi hade da dada masa duka. Ta watsa hannu baya tana nuna Kawu Ishaq,

“Kinga Batoul idan kaltume ta barwa isyaku rabin dakin can a tumunin takabarta shikenan. Ni dai yau dole ayi mai yiwuwa ko dai ya biya kudin hayar dakin ko kuma ayiwa daki kudi ya bani hakk’i na aciki. Sittin ta ubangiji nagaji.”

Shiru nayi domin na rasa ta cewa. Duba da ko Innar mu ta bar masa kason ta ba burge su za miyi ba. Kuma muma kadarar mu ce. Saboda me zamu bar masa? ‘Karawa me karfi- karfi kenan. Saurin girgiza kai nayi alamun a’a. Ina kokarin fara hawa bene. Bintalo tayi guda tana buga zani,

“A hayye nanaye! To isyaku kaji dai ko? Itama kaltume bata bar maka nata kason ba. Kai ne ka tattago aure kana zaman zaman ka. Toh yanzu dai tunda Rabi’atu bata ‘yaya ita ka’dai ce kawai ta koma dakin usaiba s..”

Ai bata ‘karasa ba Baba Usaiba dake gaban rijiya tana janyo ruwa ta saki guga ta fada ciki. Cike da masifa hade da kwakwazo baba usaiba taje gaban Bintalo,

“Kutsin ubancan kayya kai. A hayye kayya kai! Kin taba ganin inda kishiyoyi suka zauna a daki d’aya? A gidan uban wa ake haka?”

Bintalo taja guda ta saki tana yarfe hannu,

“A hayye yau ga gaye ba makilis. Kwarai kuwa, Sau nawa ma idan miji fatararre ne? Dakin da kike shi ne mallakin sa. Kuma dududu yaranki nawa ne? Su biyu ne jal sai ke ku uku, sai uban Iyali hud’u kenan. Sai ita Rabi’atun ku biyar kenan. Sittin ta ubangiji sai dai ku gwamatsu haka.”

Baba usaiba taja dogon tsaki cike da takaici ta cakumo wuyan Bintalo suka haura da dambe. Nai hayewa ta sama ina dariya. Domin wani lokacin sai diramar fad’ar su tasa ka murmusa ko kayi dariya. Dakin mu na shige. Akwai wuta fanka sai wulwulawa take yi. Innar mu ce kadai ta kishingida tana jin rediyo, Autar mu kuma da alama ta tafi Islamiyya. Gaida Innar mu nayi tayimun sannu da zuwa. kayana na shiga ragewa ina bawa Innar mu labarin makaranta. Hijabi na zura na dauki kwandon kayan wanka na nayi kasa. Suna nan suna fada har lokacin dana fito daga wanka. Anan na hango Bintalo tayi kukan kura ta shige dakin Rabi’atu tana watso kayan dakin waje tanayi tana surfa masifa. Sai gumi ne ke reto a fuskar ta,

“Sittin ta ubangiji dole ne yau ko dai ku bar dakin nan ko kuma ka biya kudin hayar dakin. Ai kaci moriyar dakin mun maka hak’uri..”

Kowa yayi shiru yana binta da kalllo ciki harda Kawu ila dake kan bokitin sa, Ya zabga tagumi yana sakacen hakoran sa. Girgiza kai kawai nayi na haye sama abuna cike da mamakin tijarar Bintalo. Itace maganin su.

X•••. O•••X•••O

Ranar juma’a da wuri na tashi tun farar safiya. Domin a ranar zan yiwa yan level one lectures din course na biyu da zan dinga daukar su wato ‘History of English literature..’ Wanka na na falla na turara kayan da zansa akan kabbasa. Dake jumu’ah ce shigar doguwar riga nayi baka ta abaya. Sosai nayi kyau. Yar farar hoda na shafa kadan hade da jan jambaki. Na zura zobe na hade da ‘daura agogo a wutsiyar hannu na. Kunshin da nayi daren jia ya kara turuwa yayi maroon sosai. A tsaitsaye na sha kunu da fanken da Innar mu ta ajiyemin agaba na. Laptop dina na zura a jaka ta hade da sauran littaifai na.

“Innar mu zan tafi..”

“Toh me sunan Uwa ta! Allah ya tsare ya baku narasa Ameen.”

“Ameen Ya Hayyu Ya Qayyum Innar mu.”

Ficewa nayi daga dakin da sauri Ina mai duba agogon hannu na ganin zan makara. Bintalo na hango tana janyo ruwa a rijiya. Ta sha goyo asusu da zani na adashen da take ajiyewa a baya tamkar dan karamin jariri. Dariya ce ta kufce min na shiga darawa, Dagowa tayi ta dube ni tana wake-waken ta,

“Meya baki dariya ke kuma?”

Dena dariyar nai ina karasa sakkowa daga bene,

“Baba goyo naga kinyi..”

Watsa hannu baya tayi dayan kuma tana sosa takashi.

“Ke sittin ta ubangiji dole na sab’e abuna na goye, Har ‘daka aka biyo sahu aka sace shi satin baya. Gida fal cike da ‘barayi da iyayen barayi ga fatararru da masu nakashasshiyar zuciya, a hayye yau ga gaye ba makilis! Sittin ta ubangiji dole na goye kudin mutane.”

Murmushi nayi kawai na fice, Domin dana tanka abun kai na zai dawo. Tinda maganganun da ta fada dasu Kawu ila take da Kawu Dawood da Kawu Ishaq. Ina fita na samu mashin na haye ya kai ni wajen lodi nan ma ba jimawa mota ta daga sai makaranta...

MUHAMMAD MUBEEN...

Tashin sa kenan daga bacci, Yana duba agogo yaga ya kusa latti. Cikin sauri ya fada bandaki yayi wanka. Shigar ‘kananun kaya yayi samfarin Calvin Klein. Da sauri ya faffesa turare ya goga chapette a jajayen labban sa. Parlor ya fita hannun sa dauke da notepad da biro. Amb Salees ne kawai a zaune yana karatun jarida. Da alamun Mamma Ahlaam tana kitchen. Jin yadda parlorn ya cike da k’amshin girki,

“Papa! Good morning.”

“Morning Mm! Ya jikin naka ashe jiya da zazzabi ka kwana?”

Murmushi kawai Mubeen yayi yana kallon agogon hannun sa,

“Bara naje na kusa latti..”

“Kaji sauk’i ne har xaka tafi sch? Abincin fa?”

“E..”

“Toh! Allah ya dawo da kai lapia ya bada sa’ar karatu.”

“Ameen Papa.”

Sauri yai ya fice domin idan mahifiyar su ta fito ta ganshi dayan biyu ne ko dai ya hakura da zuwa makarantar ko kuma ya tsaya ya ci abinci. Mota ya shige driver yaja shi sai school...

Suna tafe yana duba agogo, Sam bayason yayi missing lectures dinta. Lokaci zuwa lokaci yakan furta,

“My Ayana...! irisiwoni isikīyayu diresi yit’ebik’u.”

(My beautiful flower can’t wait to see you...)

TWIN THEATER

Ruwa ake tsugawa tamkar da bakin ‘kwarya, Gashi ban taho da lema ba. Tagumi na zabga ina kallon yadda dalibai ke gudu suna shigewa cikin lecture hall din. Gani ni malamar a waje ina tsoron kada ruwa ya doke ni, Domin inada saurin yin mura. Agogo na na kalla saura minti goma lokacin fara lecture din yayi. Wata k’atuwar mota mai numfashi ce tazo ta tsaya agaba na. Wa zan gani? Miskilin yaron nan na jiya shine ya fito daga ciki yana gyara zaman P-cap dinsa. Direban sa da sauri ya fito ya zuge lema ya rike masa. Karbar lemar yayi hade da da yiwa direban alamun ya tafi. A hankali ya shiga takowa inda nake. Hannun sa d’aya ya rike lemar da notepad d’ayar kuma ya saka shi a aljihu. Tsayawa nayi ina kallon ikon Allah.

Har inda nake ya tako tamkar zai shiga jiki na, Na ja baya ina dalla masa harara. Handkerchief ya zaro a aljihun sa ya sunkuya kasa yana gogemin takalmina da cakwalin ‘kasa ya batamin. Shiru nayi ina kallon ikon Allah! Yana gama gogewa ya mike tsaye yana murmushi. Yau ma ba zai gaishe ni ba? Na fada a zucia ta ina kallon sa a dakile. Lemar hannun sa ya sanya a saitin kai na. Cikin maganar sa a hankali tamkar rad’a na jiyo shi yana nunamin hanya hade da cewar,

“Ayana...Shall we?!”

Ka’da kai nayi kawai nayi muka fara tafiya, Ya sakalo lemar guri na. Ruwa sai dukan sa yake. Dan matsa masa nayi ya shigo ciki. Tamkar wasu wanda suke a tare muka karasa bakin kofar ajin. Zan fita daga ciki yai saurin riko jakata yana girgiza min kai. Tamkar wanda ake koyawa magana haka ya shiga girgiza kai yana wani marairacemin,

“Ayana...Please don’t....”

Gaba d’aya sai kai na ya kulle da al’amarin renin hankalin balaraben yaron nan. Menene kuma Ayana? Bai gaishe ni ba yana matsayin dalibi na sai nunamin iko sai kace shine malamin? Muka shiga kallon kallo dashi. Sai shine ya sunkuyar da kansa kasa yana sake rike jakata da karfi,

“Please ki bari na raka ki...”

Fuzge jakata nayi na shige cikin theatre din. Ina kallon sa ta gefen ido yana min kallon kin kyauta. Ciki ya shigo ya zauna yana kallona ‘kasa-kasa. Na sake daure fuska ta na shiga basu hak’urin rashin shigowa ta da wuri. Duk wani movements dina a idanun sa yake. Ya kasa ya tsare ni da kallo har da wani kishingid’ewa yana lumshe idanu. Lalle zanyi maganin ka ko wanene kai. Na fada a zucia ta ina rubuta kalmomin ‘Concept Of Literature’ a board. Juyawa nai na tambaye su cikin harshen turanci shin kowanene zai iya fadamin ma’anar literature? Dan renin hankalin ku shi ya fara daga hannu yana murmushi. Daga kai nayi alamun ina jinsa. Cike da k’asaita murya ‘kasa kasa ya fara fadar,

“Literature is an imaginative work of art, That uses languages, Plots etc to express the beauty of life..”

“Excellent...”

Nai saurin fada to avoid his gaze hade da nuna wani dalibin. A daddafe na karasa musu lectures din ranar. Domin na tsani mayen kallo. Wani irin kallo yake bina dashi mai dauke da tarin ma’anoni....

——-

Assalamu Alaikoum dearest fans😘❤Toh masu comments suna maganar na bawa Batoul dan shekaru arba’in da biyar ko kuma wanda ya girmeta sosai ku RUNGUMI sorry □□□wannan LITTAFI yana dauke da wasu rassa na cikin sa wanda suka faru a gaske. Kunga kuwa babu damar canza akalar littafi. A zahirin gaskia ma duk wanda ke bibiyar books Dina yasan bana canza yadda na dakko littafi na. Fatana dai yan darussan dake ciki kawai mu amfana dasu. Kurakuren ciki Allah ya yafemu duka□□ So IGIYAR ZATO is 'Almost Based on a true story' And almost based on a true story refers to the recreation of a story with changes to the storyline to suit the

audience's understanding and expectations. Often done to entertain the audience and dramatises certain events for that purpose. □□□□□□ Get that puh lease dearest fans😘😘 Na son zaku so littafin nan fiye da rubuta na baya, Saboda yana dauke da salo na daban.

Da fatan munsha ruwa lapia? Toh Allah ya biya mana bukatin mu na alkhairi AMEEN SUMMA AMEEN. Gobe sallah□□HAPPY EID AL ADHA MUBARAK in advance 😘 May Allah accepts it form mine and yours❤❤ALLAH YA MAIMAITA MANA... ASHA HUTUN SALLAH LAPIA□□□□ZAFAFA NA MUKU SON KAUNA MARAR GAURAYE...□😍😻❤ □□□

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

31

Har ina tuntub’e haka na fice daga theatre din ina zabga sauri. Office dina na shiga dauke da sallama na bararraje ina jujjuyawa a kujera. Gaba d’aya I’m worn out. So nake kawai na jini a katifar Innar mu. Sallama na jiyo a saman kai na. Miskilin yaron nan ne ya shigo. Amsawa nayi a dakile ina cigaba da duba takarddun gaba na.

“Yes.”

Na fada don jin shirun yayi yawa. Zama yayi a kujera mai kallon wadda nake zaune. Ya harde kafafu yana kallo na. Ajiyar zuciya na sauke na dube shi ina hade rai.

“Ya akai?”

Murmushi yayi yana shafar hard'add'iyar sumar kansa wacce take ta faman kyalli tamkar anyi b'arin mai a kanta. Ya sake gyara kujerar da yake kai yadda zai dinga kallo na sosai, na kallesa cike da b'acin rai nace masa.

“Kai! Wai menene haka ne? Ni sa'arka ce da zaka dinga min abu kamar mate d'inka?”

“Sorry ma'am, wata tambaya ce nake son yi miki.”

Yayi maganar cikin sigar da nake so, wato girmamawa. Hakan kuma ba karamin dad'i ya yi min ba, domin ji nayi lallai ni malama ce a gurinsa, amman duk da haka sai na kara d'aure fuska ta tare da janyo wani littafi ina budewa ina masa magana.

“Okay yi tambayarka dan sauri nake yi ina da aikin yi. Kuma karka min tambaya wadda ba ta shafi darasin da muka yi daku ba. Idan kuma bai shafi karatu ba to karka saka ran zan baka amsar tambayarka.”

Tunda na fara magana idanunsa suna kaina baya ko kiftawa, ni kuma sai bud'e Page's nake yi babu abinda ya shafeni da irin kallonsa a kaina. Mubeen ya saki wani sihirtaccen murmushi wanda ina da yakinin cewar dad'i yake ji gani gashi harma yana min magana ina bashi amsa. Shiru ya kuma ratsawa hakan yasa na rufe littafin na d'ago ina kallonsa, sai naga ni ya kurawa ido, na d'auki biro tare da nuna masa hanyar fita naji yace.

“Sorry ma'am, daman akan darasin mu ne na yau.”

“Ina jinka, mai ya faru?”

“Ma'am, duk ban gane ba shine nazo ki sake min karin bayani badan hali na ba.”

Wani irin kululun takaici ne yazo min wuya ya tokare, haushi da bakin ciki suka taru suka zauna a cikin zuciyata, rai na a cunkushe na kallesa.

“Idan kace duk baka gane darasin mu na yau ba, shin daga ina kake d'akko duk wasu amsoshin tambayar da kake bani? Idan ban manta ba, bana jin kabar wani ya bani amsa a cikin hall d'in, duk kai ka amsa shine yanzu zaka ce baka fahimta ba?”

Mubeen ya shafa keyarsa yana yin kasa da idanuwa, ni kuma na hararesa tare da kuma tsuke fuska nace.

“Okay naji abinda kace, yanzu dai kaje ka samu wasu wadanda suka fahimta sai su yi maka bayani ni yanzu akwai abinda zanyi, idan na dawo next lecture sai na d'an sake yi muku bayani ku duka ajin.”

Ina gama yin magana na sake nuna masa hanyar fita, kamar zai yi gardama sai kuma ya rausayar da kai ya mike yana dora p.cap d'insa a kansa, kasan cewar da ya shigo office d'in nawa cirewa yayi ya dora akan desk. Har ya kai bakin k'ofa zai fita kamar wanda aka tsikara ya sake dawowa baya yana kallona, na yi masa kallon karka kuskura ka kuma tambaya ta, sai kuma naji yace.

“Thank you Ma'am.”

Na yatsina fuska bance komai ba naci gaba da rubutu cikin wani file, shi kuma ya fita yana sakin murmushi yasan cewar sarai ya takura min duba da yadda nake bashi amsa. Wasu lectures d'in ya shiga sai kusan karfe hud'u sannan ya gama. A dai-dai lokacin kuma na fito zan tafi gida, jakata rataye a kafad'a kaina a kasa kamar yadda na saba idan zanyi tafiya saboda bana son yawan kallo ji nake kamar zan fad'i. Dan yayyafin da ake yi shine yasa ni tafiya da d'an sauri ina tsoran kar wani ruwan ya kuma ke cewa na rasa yadda zanyi. Mota naji tana bina a baya a hankali, can kuma sai naji ta tsaya a gabana hakan yasa ni tsayawa. Driver d'in ne ya fito ya karaso kusa dani yana gaisheni tamkar wata shugabar shi, naji ya fara magana.

“Hajiya ki shigo a kaiki saboda wannan yayyafin zai iya haddasa miki zazzabi”

Na kalli mutumin sosai, ban san shi ba na kuma manta da kalar motar su Mubeen. Nayi murmushi domin naji dad'in yadda yaso taimaka min, sai dai ba zan iya hawa ba saboda ban tab'a ganinsa ba, hakan yasa nace dashi.

“Babu komai zan karasa bakin gate na samu abun hawa, na gode da taimakon ka gare ni.”

Ina kaiwa nan na juya zan tafi bawan Allahn nan ya kuma biyo ni, har kasa ya tsugunna yana rokona yana had'ani da girman Allah harda cewa.

“Wallahi hajiya ni ba barawon mutane bane, kuma ba macuci bane ni bazan cuceki ba taimaka miki kawai zanyi.”

Naja numfashi tare da gyara jakata sannan nace masa toh, muka nufi motar abin mamaki ya bud'e min gaban motar na kallesa shima ya kalleni kafin nayi addu'a cikin zuciyata sannan na shiga. Abinda ya daure min kai shine ganin Mubeen yazo ya bud'e wajan driving ya zauna tare da rufe motar, shi kuma wancan na lek'a ta window na hango shi yana tafiya hanyar gate. 'Had'in baki ne kenan?' Na ayyana a cikin zuciyata sannan na kama kofar zan fita naji ta gam sai na kalle shi ina masa kallon ka raina ni tare da cewa.

“Kai kuma lafiya ka sake biyo ni nan?”

Bai yi min magana ba ya fara k'ok'arin yiwa motar key, na kuma juyawa ina kallansa cike da takaici nace.

“Naga alamar akwai rashin girmamani a tattare da kai, kasan matsayina a wajanka kuwa? Bud'e min na fita tun kafin na sab'a maka.”

“Kiyi hakuri ma'am ruwa ake yi, zanje na kaiki gida ba wani abun. Ban raina ki ba, hasalima wani irin girma da daraja gareki a cikin idanuwa na. Kiyi hakuri na kai ki wallahi ba zan iya jin dad'i ba naga ruwa yana dukan malamata ba, bayan ni d'alibinki ne akwai taimakekeniya a tsakani. Nasan kema wata rana zaki iya taimako na ta hanyar ba banyi tsammani ba. Ina respecting din ki har cikin zuciyata, kiyi hakuri.”

Jikina ne yayi sanyi jin tabbas haka ne abinda ya fad'a, toh amman mai yasa duk ga mutane nan da suka cancanci ya taimaka musu bai yi ba sai ni? Ga makafi nan da guragu duk ya tsallake su ya taho gareta? Wannan akwai ayar tambaya a tare dashi dole akwai dalilin da yasa yake shishige min. Na d'auke kai daga kallansa ina cewa.

“Toh amman mai yasa baka je kace na shigo ba kasa wani?”

“Mah nasan idan ni naje ba zaki hau motar ba, shi yasa nace da driver d'in yaje kuma gashi anci sa'a.”

“Ya akai ya tafi bai tsaya ya hau ba.?”

“Ma'am, na bashi kudi ya hau abin hawa mu had'u dashi a gida. Kinga idan nace ya hau baya ai ba tsari tunda shine fa yake tukani.”

Kallansa nayi naga yana lumshe idanunsa haushi ya kuma kamani, cikin rai na ina ayyana cewa kila d'an gidan mai kudi ne saboda gashi nan komai nasa neat, gashi har wani driver gareshi motar kuwa ta koshi sai wani kamshi take mai matuk'ar sanyaya zuciya. Jan motar Mubeen ya fara yi a hankali, hakan da na gani shine yasa ni yin magana nace.

“Kodai baka iya motar ba? Karka jefa ka watsar damu a banza.”

Ya saki murmushi tare da lasar lips d'insa na sama sannan ya kalleni tamkar wani babba. Tafiya yaci gaba da yi ba tare da ya sake ce min komai ba, hakan ya bani haushi matuk'a duk da cewar na fi bawa zuciyata laifi domin nice na yarda na shiga motar dole duk abinda zan gani na kawar da kai tunda yaron naga akwai jin kai. Sai da muka fita daga gate ya tsaya saboda zamu hau titi ya tambaya wane hannu zamu bi hagu ko dama, sai nima nayi shiru tamkar banji ba. Kamar daman haka yake so sai naga ya koma damu gefe ya yi parking tare da dora kansa jikin glass din window yana lumshe idanunsa.

“Ya haka? Baka da lafiya ne?”

“No ma'am, na tambaya ina zamu nufa baki yi magana ba, ni kuma bana son takurawa malamata da surutu na, shine na tsaya.”

Haushi ya sarke zuciya ta yaro karami ya tsaya yana rai na min hankali kamar wata sa'ar shi. Sai na d'auki jakata dake kan cinya na rataya ina k'ok'arin bud'e murfin motar na fita.

“Bud'e min na gode da taimakon ka, zan iya karasawa da kai na.”

Mubeen yayi shiru yana sauke ajiyar zuciya, na kai ido na kan mukullin motar zuciya ta na raya min na murd'a idan na murd'a ta kunnu sai kawai na bud'e na fita dan yaron akwai rainin hankali. Sai dai ina kai hannu tamkar shima an sanar dashi abinda zan aikata sai naga ya kunna motar ya fara tafiya, ganin mun hau titi yasa nace dashi.

“Limancin kona nan zamu tafi.”

Sai ya kalle ni yana zaro ido, na kauda kai ina had'e rai, kamar ba zai ce komai ba sai kuma yace dani.

“Wane hannu zanbi kenan? Bansan hanyar ba, sai dai nasan mun tab'a zuwa unguwar har naji mahaifina ya fad'i sunan limancin kona.”

Tsaki na saki a cikin zuciya ta kafin na nuna masa da hannu, shima bai kuma magana ba ya karya motar muka tafi. Gabaki d'aya nice na dinga nuna masa hanyar da zai bi har muka kusa zuwa gida sannan nace dashi.

“Yauwa nan ya isa na gode sosai.”

Na karasa maganar ina shirin bud'e motar amman gam yaki, na sake kallonsa fuskata babu yabo ba fallasa nace.

“Bud'e min na fita, idan kuma baka son gobe na sake yadda da taimakon ka karka bud'e min har sai na kuma yin magana.”

Babu musu Mubeen ya bud'e motar yana bin ta da kallo, haka kawai yaji wani irin nishad'i a cikin ransa. Ni kuma na bud'e nayi ficewa ta ko godiya banyi masa ba saboda ya b'atamin rai kwarai. Shi kuwa Mubeen ina tafiya ashe ya biyo ni ba tare da na sani ba, kuma banyi zaton zai biyo bayana ba hakan yasa koda ina tafiya ban waigo ba har sai da na sha kwana na shiga gidan mu. Shi kuma ya tsaya ya tambaya shin nan ne gidan mu? Aka tabbatar masa da nan ne sannan ya kad'a kai ya koma mota, sai da ya zauna sannan hankalinsa ya tashi domin bai san ina zai bi ya koma gida ba, ya bud'e murfin motar yana faman kalle-kalle tamkar mai neman wani abun.

“Ranka ya dad'e mu wuce ne?”

Mubeen yaji muryar driver d'insa, abin ya bashi mamaki ganin yace masa fa ya tafi gida amman ya akai ya ganshi anan? Cike da rashin son magana yace.

“Ya akai ka biyo ni?”

“Kayi hakuri ba zan iya barin ka tafiya kai kadai ba saboda amana ce kai a gare ni, shi yasa na tari napep na dinga binka a baya.”

Baice komai ba sai komawa baya yayi ya zauna shi kuma driver din ya shiga yaja suka tafi. Mubeen na zaune yana ta murmushi saboda d'an zaman nan da suka yi da malamar tashi ya gama gano cewar tana da son girma, duba da komai yayi zata ce ya manta matsayinta a gareshi. Da wannan ya shiga gida bayan yayi wanka yayi sallah kwanciya ya yi kota kan abinci bai bi ba har sai da mahaifiyar sa tazo masa dashi ya d'an ci kad'an sannan ta fitar da sauran bayan ta yi masa gargad'i akan ya tabbatar yasha maganinsa.

Yatsina fuska yayi sannan ya juya ya kalli kan bedside locker d'in dake d'akin, magungunan ya harara saboda ya gaji da shan su. Juyawa yayi ba tare da ya dauka ba ya janyo remote ya kunna tv wacce ke kafe jikin bango, yana kwance yana kallo hankalinsa a kwance, cikin ransa yana tuno malamarsa wacce salonta yake neman kai shi inda bai cancanta ba. Labarai ya kunno, cikin sa'a kuwa yaga an hasko inda mahaifinsa yake gudanar da campaign d'insa, yaji matar tana cewa.

“Amb Salees kenan wanda yake shugabantar mazauna kasar Najeriya a can kasar Ethiopia, yana kaddamar da campaign neman zabe ta kujerar gwamnan jihar kaduna, a unguwar rigasa, tare da amininsa Alhaji Kabeer wafa, sai mataimakin sa Dr Hafiz M Baba, wanda ke gefe yana d'agawa jama'a hannu kafin kaddamar da kamfen din. Amb Salees ya kaddamar da kamfen d'in tsayawa takara a zaben gwamna da za'a gudanar cikin watan janairu na sabuwar shekara da zata zo. Amb ya sanar da haka ne a jiya Asabar a gaban dubban magoya bayan shi da suka hallara a unguwar rigasa. Amb ya shaidawa magoya bayansa cewa jahar Kaduna tana cikin wani irin yana yi na son canji. Bisa ga cewar shi, zai tsaya takara ne sabida ya hakikanta cewa, zai iya jagorantar jahar zuwa samun sabon canjin. Ko mai sauraro da kuma kallon mu zai iya amincewa ya bawa Amb kuri'arsa?”

Mubeen ya kurawa tv d'in idanuwa yana kallon yadda ake nuna mahaifinsa yana ta yiwa al'ummar annabi alkawarurruka da dama. Tsaki yaja dan shi bai sai abinda mahaifinsa zai yi da siyasa ba, suna da komai yana da kud'in sa wanda duk Nigeria babu wanda ya isa ya takashi bai rama ba, amman meye na shiga harkar siyasa salon suna tafiya a hanya ana zagin su idan ba'a cika alkawarin da aka d'auka ba. Sumar kansa ya shafa yana sauke numfashi, can kuma ya d'akko jota d'insa yana duba darasin da tayi musu, sannan yana shiga google ya duba wasu abubuwan saboda ya samu na bata amsa idan tayi tambaya.

GIDAN MATA TARA

Cike tsakar gidan mu yake da ahalin mu. Kowanne yana kara-kainan gaban sa. Zabbau dake kankare ‘kanzo a tukunya gayyar ‘yayan ta na gaban ta suna lashe lebe. Ta mike hade da gantsarewa ta sakarwa d’aya daga cikin ‘yayanta ran’kwashi ji kake ‘kwas.

“Hegun yara, ‘kanzon ma don mayata sai kun cinye bayan abincin da nasamo muku.? Tahi kubar nan kafin na muku lahani..”

Ta ‘karasa fada tana binsu da murfin tukunya. Ficewa su kai suna kuka Ita kuma ta cigaba da kankaro ‘kanzon tana afawa a baka. Shigowa ta kenan na fara cin karo da karakainan su. Sama na haye ina mai yiwa Allah godia a zuciata bisa ga yadda ahankali yake canza mana rayuwar mu. Na sake duban zabbau dake cin kanzo

ka’indana’in tamkar zata ‘kware. Na tuno muma a shekarun baya muke cikin halin rashi suna na samu. Amman yanzu duniya ta fara canza musu sun fita daga cikin halin samu suna na rashi. Daki na shiga da sallama. Innar mu da autar mu ne kawai. Suka amsa kowanne fuskar sa dauke da fara’a. Autar mu ta rungume ni tana murna. Lumshe idanu nai don jiyo ‘kamshin man kuli dake tashi. Ina wa man kuli son so wallahi. Musanman a shinkafa da wake. Ai kuwa ban gama maganar da nake a zuci ba autar mu ta mikomin kwanon abinci na. Shinkafa da wake ne da yajin tafarnuwa a gefe. Sai dan karamin filet dauke da salak da tumatir da cucumber ga magi shima a gefe. Sai kamshi ne ke tashi. Saurin sakkowa nai daga kan yar katifar mu. Na wanke hannu na a robar da autar mu ta kawomin. Bismillah nayi na shiga cin abincin nan ina daga kai cikin jin dadin abincin.

“Innar mu mungode Allah ya saka da alkhairi, Wallahi tun satin baya nake son cin wake da shinkafa. Wayyo Allah dadi.”

Autar mu ta kyalkyale da daria, Innar mu kuma tayi murmushi kawai ganin yadda suka ga ina santi harda ka’da hannuwa na. Robar zob’o autar mu ta sake matsomin da ita. Tayi sanyi kau da alamun ba’a dad’e da siyo shi ba. Had’adden zo’bo ne da matar soja keyi. Ga dadi ga tsafta naira talatin kuma me sanyi.

“Kai yau dai na zama yar gata. Harda zob’on matar soja? Alhamdulillah Allah ya kara budi.”

“Ameen..”

Haka dai na karasa cinye abincin nan ina santi. Bayan na gama na gyatse da hamdalah. Na rage kayan jiki na hade da daukar kayan wanka na don sauka kasa yin wanka. Har na kai kofa na juya,

“Innar mu a dan zubamin abinci na bawa zabbau naga tana cin ‘kanzo.”

Innar mu ta mike daga kishingiden data ke tana kokarin janyo kular abincin gaban ta,

“Kai haba dai? D’axu ma na bata nace ta bawa yaran wallahi..”

“Wlh Yayya Batoul Bintalo tazo nan tai ta zagin...”

Autar mu bata karasa fada ba Innar mu ta mata dakuwa tana zuba abincin,

“Tashi ki fara shiri ma kada ki makara.”

Mikewa autar mu tayi tana mika. Murmushi nai don tuni na gano Bintalo ce tayiwa Innar mu tijara akan ta bawa zabbau abinci. Gashi ita ta dena yi dasu. Girgiza kai nayi kawai na karb’i abincin da Innar mu ke mikomin. Sauka nayi kasa. Usaiba na wanki, talatuwa na sab’e mata. Zabbau kuma ta zubawa rijiya idanu da alamun tunani take. Kofar band’akin na hango an karo ta. Da alamun wani ne aciki. Ajiye kayan wankan nawa nayi agefe kafin na karasa kusa da zabbau ina mai mika mata kwanon abincin,

“Zabbau gashi ki bawa su ‘dan abbasi..”

Zabbau tasa hannu zata k’arba Bintalo ta fito daga bandaki tana kururuwa hade da buga zani ta watsa hannu baya, Usaiba dake gefe taja guda ta saki,

“A hayye kayya kai.”

Bintalo ta wafce abincin ta kifar dashi a kasa, Hade da sa kasan kodadden jemammen takalmin ta ta take abincin,

“A hayye yau ga gaye ba makilis! Sittin ta ubangiji naki jinin makirci a rayuwata. Makirai, Algungumai, Shin wai ana dole ne? Sittin ta ubangiji sai yanzu na gano. Wato ku kunfara dandalar arziki shine zaku fara yiwa mutane annamimanci? Dan bakin munafunci ina ku ina bawa tsatso na abincin ku? Bama dake zanyi ba matsa.”

Bangaje ni Bintalo tayi tana huci. Ta buga zani tana yarfa hannaye,

“Kaltume fito nan babbar munasura. Duk ke kike kitsawa ‘yayan ki komai. Kaltume, Kaltume ba zaki fito ba sai na hawo?”

Shiru nayi na ja gefe ina zabga tagumi daga abun arziki sai ya koma na tsiya? Bintalo sai lailayo ashariya take tana durawa ita kadai. Kanzil Innar mu bata ce ba. Domin ko fitowa ba tai ba. Zabbau ta saki hamma tamkar bakinta zai zazzago tana rufe baki,

“Baba gaskia ni yunwa nake ji, Ke kin ki bamu, Sannan kin hana a bamu. Ni gaskia na gaji tun d’axu ruwa nake dankwarawa ciki na . Bayan naga burodi kin hyafehi da buta keda Hinde kuna ci...”

Bintalo ta dankarawa zabbau harara tana watsa hannu baya,

“Itama mashinshinnin ta ne ya aikonta yaron kirki mai hannu a sake. Zan zauna ina ciyar daku ne gand’ama-gandama daku? A hayye yau ga gaye ba makilis! Bayan ku ga gayyar yara? Sullutuwar wofi idan baki sani ba barbade ki suke yi a abincin da suke baki suna kalallameki da zance cikin tsohon munafurci. Sahorama, Ki tashi ki zaga gari idan da rabon ki kya samo.”

Girgiza kai kawai nayi nayi hanyar shiga bandaki Bintalo tasha gabana tana nuna ni da yatsa, Dayan hannun ta kuma tana sosa takashi. Nayi murmushi ina gumtse dariyar data tahomin.

“Wa kike wa dariya iyye?”

“Ah bazan yi daria ba baba? Toh bada kowa nake ba.”

“Da kaltume kike sittin ta ubangiji.”

Wani kallo na watsa mata wanda yasa tasha jinin jikin ta,

“Uhm uhm dai baba, Ki tsaya akai na banda tab’o uwata wallahi.”

Usaiba dake gefe ta saki guda tana buga zani,

“Jar ubancan kayya kai! A hayye kayya kai..”

Bintalo ta dora hannaye a kirji tana min wani kallo,

“Ni kike zagi Batoul?”

“Wa? Kinji na zage ki? Ai banma iya ba domin ban tashi naji anai ba.”

“A hayye yau ga gaye ba makilis. Toh waye me zagin iyye? Sittin ta ubangiji zan zugewa mutum tazuge duk girman sa kuwa.”

Daria na kyal’kyale da ita. Don wallahi gani nake tamkar wasan kwaikwayo, Guga na dauka na shiga janyo ruwa na Ina wak’a ta ahankali.

“Ga yar iska tana magana ko?”

“Hajia Baba Bintalo kenan. Ni fa wanka zanyi, Allah ya huci zuciyar babar mu.”

Dogon tsaki taja tana watsa hannu baya sai bambamin mita take ita kadai. Ni kuwa bandaki na shige nayo wanka na na haye sama. Sallah nayi na dan kishingida tuni

bacci ya dauke ni. Ban farka ba sai gab da magriba, Alwala na dauro nayi sallah. Ina zaune ina lazumi Basmah ta shigo daki kira na,

“Wai kizo inji baba.”

Kada kai nayi kawai na cigaba da lazimi na domin banason a katse min shi. Sai da Innar mu ta min magana tukun sannan na sauka k’asan. Dakin sa na shiga ummita tacemin yana waje. Soro na leka. Tumbin wani mutumi na fara cin karo dashi, Gefen sa kuma Kawu ila ne sai dashare hakora yake. Yana gani na ya gyara tsayuwar sa yana nuno ni da hannu,

“Yauwa Alhaji ga.. Ga yarinyar da nake gaya maka nan ta fito.”

Alhajin ya mike yana shafa tumbi hade da sake matsowa yadda zai gano ni sosai. Ni kuwa kallo na shiga binsu dashi tamkar wata mutum mutumi...

**

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *32*

NANA HAFSAT

•••

Alhajin ya shiga shafa tumbin sa yana dagemin gira duba da yadda wutar lantarki ta haskaka zauren. Kawu ila ya shiga gyaran murya yana yafito ni ciki. Hade rai nayi na karasa bakin kofa na tsaya ina bin Kawu ila da kallon karin bayani,

“Ina wuni..”

Na ja a hankali ina k’arewa mutumin kallo ‘kasa-kasa. A haife ya haife ni, Sanye yake cikin wasu kaya farare kirar yadi. Kasan wandon ya tattare. Ya bulala babbar riga tana sharar kasa. Hular da ya sanya a kansa tayi wa kansa kadan. Sai ta tsaya a tsakiyar kan. Kallo na ya tsaya akan silifas din daya saka kafafuwan sa yayi masa kadan ainun. Shin meke tafe dashi? Na fada a zuciata ina sakin gwauron numfashi. Kawu ila dake gefen sa yana dashare hakora ya dube ni yana min kallon na saki jiki na. Ai kuwa na kara kudundunewa acikin hijabi ina kallon gefe, Na gaishe shi bai amsa ba mezan yi kuma?

“Alhaji itace wadda nake baka labari. Tayi?”

Na tab’e baki, Sai kace kayan sawa. Alhajin ya murmusa yana sosa gemun sa wanda ke dauke da furfura taso taso a cuccure. Ahankali yake bina da kallo kafin ya maida duban sa ga Kawu ila

“Tayi Ilyasu. Shi yasa ma na kasa magana. Tab carkwai mazwai. Komai yaji acan-acan ragad’au-dau abun ba acewa komai. Allah yayi halitta.”

Na kalle shi a kaikai ce ina maimata kalaman sa a hankali hade da nanata TubarkAllah! Shakka babu akwai alamun tambaya a tattare dashi. Kawu ila yai murmushi yana kokarin shigewa cikin gidah Alhajin ya dakatar dashi ta hanyar cewa,

“Zan ciko maka sauran alqawarin anjima ilyasu.”

“Toh Allah godia nake. Ke idan kun gama tad’in kya kirawo ni.”

Cewar Kawu ila yana kallo na. Naki hada idanu dashi ina bin gansamemen da yake cewa zamuyi tad’i da kallo.

“Amshi nan yar budurwa ya sunan ki?”

Alhajin ya tambaye ni yana sake dage girar sa dukka biyun. Ko me zan amsa oho?

“Sunana Zara’u.”

“Madallah malama zarau. Amshi nan diba, Toh ni dai sunana Alhaji Usman Usman Jibiya. Kuma anan zaria nike da zama, Amma a kankiya aka haihe ni. Nace ina neman matashiyar budurwar da zan aura ta haifamin yara dagwai-dagwai Ilyasu yace akwai yammata anan kala-kala. Banyi ‘kasa a gwiwa ba kuwa nace ya rako ni. Sai gashi ina tozali da ke wani abu yazo ya soke ni a zucia ta,

“Na da’de inason kara aure, Domin matana uku biyu sundena haihuwa, Dayar kuma data samu ciki sai ya bare. Ni ba wani babba bane da kike gani na haka, Furfurar kudi ce ta yanyane min kai...”

Kallon sa nayi na kalli kan nasa. Mutum ya tsufa amma ya ki amincewa. Wai furfurar kudi? Na maimaita a zuciata ina murmushi. Daga masa kai nayi ya cigaba da cewa,

“Yayana talatin ba biyu. Biyun kai mahaifiyar su mun rabu tuni. Yan biyu ne su. Aure nake son ‘k’arawa saboda inason yara. Ilyasu yace min bakida tsayayye na aure. Nace toh ni nasan ba zaki kini ba. Akwai abinci agidah na sosai yammata. Domin ni dan kasuwa ne ina da tafkeken shago a layin mu, Sannan ina kiwo. Zaki

sha shayi da burodi a gidah na da bota, Akwai shinkafa yar gwamnati da cous-cous. Kinsan cous-cous? Kin tab’aci?”

Daria ya bani wallahi, Yadda ya zage yana zayyano irin cimar gidan sa. Ko ta hakan aganin sa shine cinyewa oho?Wai cous-cous zai tambaye ni. Girgixa masa kayi na alamun bansani ba. Ai kuwa ya shiga zayyono bayanin cous cous yana fadar yadda akeyin sa da dafa shi, Sai sharara karya yake yi. Gaba d’aya nagaji da surutan sa. Na rufe hammar data tahomin ina kade hijabi na saboda guggun saurayen dake cinye mun naman kafafu na.

“Toh Zahra’u amshi nan kiji. zaki dinga cin cimar yan gayu, Ciki harda bombita da madarar ruwa. Da komfules.”

“Allah sarki...”

Na bashi amsa ina sakin wata hammar. Wallahi nagaji.

“Yauwa amshi nan nayi karatu naje har matakin sakandire. Anan na hab’aka a harkar kasuwanci. Kin ‘kare sakandire kuwa?”

Tari na shiga yi da alamun tambayoyin nasa sun ishi mak’ogoro na.

“Alhaji nayi karatu sosai.”

“Amshi nan. Diba! Sakandire ko iya karamin aji?”

“Jami’a n...”

Gwalalo idanuwa yai yana sarqafe hannuwa a kirjin sa,

“Jami’a fa kika ce? Ke zahrau amshi nan. Fadamin gaskia.”

“Alhaji dagaske nayi har matakin digiri na bi..”

“Digiri?”

Ya sake maimatawa cike da mamaki. Yasa hannu ya naushi bango yana cizan yatsa. Lokaci zuwa lokaci yakan nanata,

“Ilyasu ya cuce ni.”

Na karkad’e saurayen dake bina ina sakin wata hammar a karo na ba adadi.

“Amshi nan zaharau, Diba. Kirawo min ilyasu yanzu.”

Kada Kai nayi cike da murna na shige gidah ina murmushin Allah ya raba ni da alaqa-qai cikin sauki. Kofar parlorn Kawu ila na tsaya. Yana zaune a tsakiya yaran sa sun zagaye shi yana karkasa kullin tsire. Yana gani na ya tukwikwiye takardar naman ya dora hular sa akai.

“Ya akai? Kin taho fankan-fankan kin tsaya min akai?”

“Ca yai kaje.”

“Ayyo to! Kun gama kenan?”

Daga kai nayi shi kuma ya zura yar sharar rigar sa yana lashe hannu. Zauren ya nufa,

“Alhaji ashe har kun gama?”

Ina jiyo muryar Alhajin yana rufe Kawu ila da bambamin masifa. Kawu ila sai kwararo rantsuwa yake yana wallacewa,

“Akwai su kala kala agidan nan. Sai a samo maka wata ai..”

“Ai ba haka mu kai da kai ba. Yanzu dai dakkomin kudade na dana babbaka. Da rabin gonar da na yanka ma duk dawomin da su.”

Kawu ila ya zube a kasa yana hada hannu alamun ban hak’uri,

“Alhaji kayi hak’uri dan Allah. Ka yafemin, Wallahi gonar nan tuni na sayar. Kudaden kuma na sissiyo ka..”

“Karya kake yi mutumin banza da wofi. Diba nan! Na baka kwana ki uku rak ka tattaro min duk abunda na baka ka dawomin dashi.”

Alhaji na gama magana ya fice yana kade wa Kawu ila riga a fuska. Kawu ila ya shiga tambotsewa yana rigingine kamar bal a zaure. Yaran gidan mu suka taru akan sa. Bintalo da shigowar ta kenan Itada Ruma taja ta tsaya tana kallon Kawu ila,

“Meye haka ilyasu?”

Kawu ila bai ce mata kanzil ba sai ma bige-bigen kansa da yake gwarawa a bango duk ya fara fashewa yana jini.

“Wayyo Allah na! Wallahi sai na biya shi. Ina zan gan su?”

“Ilyasu su wa zaka gani? Ko aljanu ka samu ne? Oh ni Bintalo.”

Kawu ila ya cigaba da birgima yana ife-ife. Meya tuna oho? Yai parlorn sa da gudu yana leken yaran sa,

“Kada wanda ya dauki naman nan. Zan raunata mutum idan naga ba d’aya. Domin na irge su kafin na fita.”

Baba usaiba ta kyalkyale da dariya tana tafa hannaye,

“A hayye kayya kai? Kaji da abunda ya dame ka amman hankalin ka na kan nama?”

Ya wurga mata harara. Sannan ya kara runtumawa zaure yana kururuwa. Bintalo ta ja tsaki tana janye da hannun Ruma,

“Zo mu tafi Ruma. Sittin ta ubangiji dadi ne yai masa yawa..”

Sama sukai hayewar su. Hannun Ruma dauke da leda. Da alamun kudin adashen ne Bintalo zata ajiye. Girgiza kai nayi zan haye sama Kawu ila ya kirawo ni yana sharce gumi,

“Uban uban me kika fadawa Alhaji Usman ya janye neman auren ki? Wato bakin ciki kike min ko? Zan samu alkhairi a wajen sa shine kikasan makircin da kika kitsa yace ya fasa?”

“Kawu bance masa komai ba wallahi. Lapia muka rabu.”

Dogon tsaki yaja yana kwak’ular hanci,

“Rantamin kudi.”

“Ba ni dasu.”

“Karya kike yi.”

“Babu Kawu. Bani dasu.”

Tsaki yaja ya gyara zaman rigar sa hade da zura takalmin sa ya fice yana banbamin mita. Ni kuwa sama na haye ina mai kaiwa Innar mu korafin Kawu ila,

“Wallahi nagaji Innar mu. Wai shin mena tsarewa Kawu ila? Nima dan babu yadda zanyi ne. Mutum baya janyo lokacin sa. Babu wani nagari dake zuwa fyace Kawu ila ya kore su. Allah Innar mu mutumin yau ma baki ganshi ba. Allah ya rufa asiri ma bayason me zurfin karatu. Don tinda ya tambaye ni gurbin karatu na na fada naga ya canza fuska.”

Innar mu taja ajiyar zucia ta sauke tana murmushi,

“Toh adai yi hak’uri me sunan uwa. Duk ma abinda ya miki ai dan ya isa ne ko? Ilyasu uba ne awajen ku. Ballantana yanzu da babu ran mahaifin ku. Duk inda zakije ki zaga ki dawo su dinnan dai su ne iyayen ki. Saboda haka ki cigaba da addua. IN SHA ALLAH ke da duk masu nema Allah zai baku mazajen kwarai. Tabbas mutum baya janyo lokacin sa. Komi lokaci ne da mutuwa da haihuwa da aure duk tare suke. Fata dai Allah ya zaba muku abunda yafi alkhairi kawai. Kina jina?”

Daga kai nayi ina goge hawayen dake zirara a idanu na. Fisabilillahi banda Haysam ba wani wanda yake sona tsakani da Allah. Shi kuma Haysam mahaifiyar sa bata so na. Bama wannan ba wutsiyar rakumi tayi nesa da ‘kasa. Dai-dai ruwa dai-dai tsaki. Cikin haka Yayan mu ya shigo inda yake tambayar abunda ya sani kuka, Innar mu ta gaya masa. Suka hadu su kai tabani baki. Gaskia daren ranar naci kuka sosai. Anan Yayan mu yake shaida mana cewar baban su Fadila ya bashi damar ya turo manyan sa ayi magana. Sosai na yiwa Fadila farin ciki. Nima ina fatan Allah ya kawo wanda zai zo neman aure na. Muradin zucia ta. Daren ranar kuwa nayi sallar nafilfili inda nai kuka sosai a sujood ina gayawa ALLAH bukatu na. Hade da neman mafificin alkhairin sa.

ABU

Da wuri ya shirya ranar saboda suna da lecture d'in ta. Ya riga kowa zuwa hall d'in ya zauna ya dan tab'a karatu kafin daga bisani ya mike ya nufi inda zai dinga hangenta idan ta shigo makarantar. Ko minti talatin beyi ba sai gata tana fitowa daga napep domin har ciki ya kai ta kusa da office d'inta. Kudi ta zaro ta bawa mai napep din ita kuma ta bude office ta shiga dan ajiye wasu takardu dake hannunta. Mubeen da tun sanda ya dora idanunsa akan ta ya dan ja tsaki, saboda sam ba tayi kala da wadda za'a ce an ajiye a napep ba, kasan cewarta kalar wayayyu. Ya mike tsaye tare da gyara rigar dake jikinsa, kamshin turaren jikinsa sai bugun hancinan 'yan mata da samarin dake kusa da yake.

Sai da yaga ta fito sannan ya nufi hall d'in yana murmushi dan ba karamin kyau ta sake yi mishi ba a lokacin. Sanye take cikin wata atamfa kalar coffee da ratsin fulawoyi ruwan madara, hakan ne yasa tayi amfani da milk d'in mayafi, sai dai jakarta baka wacce ita ce dai take kare yawa da duk kalar kayan da tasa, sai takalmi baki shima. Cikin nutsuwa take tafiya har ta karasa inda zata yi lecture, students suka gaida ita, Mubeen ya gyara zama yana kuma karewa hallitar ta kallo.

Gyaran murya nayi sannan nayi musu kallo d'aya gabaki d'ayan su, naga lallai sunzo da yawa. Sai nayi murmushi ba tare da na kallesu ba idanuna ma yana kan handout d'in da nake bud'ewa nace dasu.

“Kowa ya yago paper ya rubuta reg number d'insa kar wanda yasa suna, zamu yi test.”

Nan da nan d'aliban suka hautsena hall din da surutu, wasu na cewa basu shirya ba yayin da wasu suke cewa amman dai open test ce, wasu kuma suna cewa ayi sun shirya. Idanuna ne suka fara zagaye d'aliban fuskata cike da fara'a, can suka sauka akan Mubeen wanda ya yi tagumi ya zuba min na mujiya kamar wanda aka dankwafar a gurin. Marker na dauka nasa kasanta ina bubbuga desk d'in dake gabana alamun suyi shiru. Da kyar suka yi saboda kowa da abinda yake cewa, na kuma tabbatar musu da cewa test zanyi koda sun shirya koda basu shirya ba, domin kullum idan muka gama darasi na yi tambaya cewa suke min sun fahimta.

Questions na karanto musu sannan na koma gefe ina kallansu one by one. Sai da na basu lokaci isashe suka kammala sannan na kalli Mubeen dake zaune a gaba yana cizon kasan biron shi, idanuwansa a kaina, dan na tsaida hakan sai nace dashi.

“You..!”

Amman takaicin yasan dashi nake amman sai yaki koda motsawa, kuma idanunsa suna kaina amman d'an rainin hankalin baiko kifta ido ba bare na tabbatar yaga sanda nake nuna shi.

“Heyyy you..! What's your name?”

Yaron nan yayi shiru har sai da ta gefensa ta tab'a kafad'arsa da biron ta, sannan ya d'an kalleta. Murmushi ta sakar mishi dan tun zamanta a wajan taga yaki koda kallon ta, sannan ta yi masa nuni dani tace.

“Ana maka magana.”

Mubeen kenan, maimakon ya kalle ni, sai kawai ya fara waige-waige shi adole bai san daga ina ake kiransa saba. Karaf kuwa muka sake had'a ido na watsa masa hararar ka rainawa kanka hankali, sai kuma naga wannan ta kusa dashi d'in tana kuma yi masa magana tana nuna masa ni, sannan ne ya taso yazo gurina.

“Kaje ka tattaro min papers d'in ka kawo min.”

Nayi maganar ina bude wani littafi dake hannuna ba tare da na ko kallesa ba, ya sunkuyar da kai k'asa alamar to ya juya yana murmushi. Ashe hakan da nayi ba karamin dad'i yasa shi ba, ni kuma nayi masa hakan ne dan na takura masa nasan irin wannan yaran basu fiye son ana shiga harkar su a irin wannan abubuwan ba. Sai da yaje ya karb'o su tas sannan ya kawo min, ban karba ba na fara kwashe kayana ina sawa cikin jaka, na juya zan tafi nace dashi.

“Biyo ni dasu office.”

Wani shegen murmushi ya saki wanda har sai da fararan hakoransa suka bayyana a waje, sauran students da suke kallansa aka fara mamakin sa ganin wa yake yiwa wannan murmushi da basu tab'a gani ba a fuskarsa. Bayan ta yabi da ta cire kafarta zai dora tashi akan sahun takalminta, tana tafiya tana waya da Yaya Najeeb inda yake ce mata zasu tafi kaduna yanzu shida Inna duba gwaggo Aminatu wacce aka yo musu waya d'azu aka sanar musu ruwan zafi ya kwarar mata a k'afa duk ta sale suna ma asibiti. Yana jin yadda take wayar cike da damuwa, har suka karasa cikin office d'in.

Sai da na zauna akan kujera ta sannan na mik'a masa hannu alamun ya mik'o min takardun sai naga ya kawar da kansa gefe.

“Bani mana.”

Daman so yake ya kuma jin murya ta kuma yaji, hakan yasa ya miko min, na karba sai naga yana shirin jan kujera ya zauna. Na had'e rai fuskata babu alamun fara'a nace dashi.

“Tashi ka tafi na gode”

Kamar ba zai mik'e ba sai kuma ya tashi ya fara tafiya, yau ma sai da yaje har ya bude k'ofar ya waigo, nima kamar an d'ago da tawa fuskar dan ba'a san raina hakan

ya faru ba, sai muka had'a ido ya sakar min murmushi wanda ya kara kona min rai dan naga alamun yaron ya yi bala'in rai na ni. Fita ya yi ni kuma na mai da kwayar idona kan papers d'in ina karanta ta farko wacce ke daga sama, ashe tashi ce ya dora ni kam ban sani ba kasan cewar ba sunayen su bane. Ina karantawa ina jin dad'in ganin yadda mai ita ya tsarge duk tambayoyin da nayi, musu. Haka na fara dubasu tun a office babu laifi sunci da yawa, na ware mutane goma da suka cinye duka da nufin idan zan mai da musu zan yabe su sosai.

Koda lokacin tafiya ta yayi na fito na tafi dan nasa a raina ba zan koma shiga lift ba ganin yadda yaron nan ya yi min kwanaki.

Bayan sati d'aya da na koma yi musu lecture, kafin mu fara sai na ki dawo registration numbers d'in d'in mutane goman dana ware, abin mamaki kiran farko da nayi sai naga Mubeen ya fito. Na kallesa na kalli paper d'insa ganin ashe shine mai wannan had'add'an rubutun, na mik'a masa yasa hannu zai karb'a yatsunsa da nawa suka hadu sai naga yayi saurin lumshe idanunsa. Sakar masa nayi ganin yaki rikewa sosai, aikuwa ta fad'i kasa amman yaki ya bud'e idon bare ya d'auka. A raina na fara zargin anya yaron nan ba d'an iska bane? Kafin na kuma kallonsa lokacin ya bud'e idon shi wanda ya soma canza kala, kwayar idansa sun tara ruwa kamar wanda yake shirin yin kuka.

“Why Ma'am?!”

“Pardon?”

Nima na mayar masa da tambayar domin ban gane abinda yake cewa why ba. Takardar yabi da kallo kafin ya sunkuya ya d'auka yana bin good d'in da nayi masa a jikin paper da kallo. A kirji naga ya dora takardar sannan ya juya ya koma gurin zamansa. Babu laifi yaron akwai nutsuwa, komai nashi a hankali yake yinsa tamkar wani mace. Ni kuma naci gaba da kiran sauran ina basu har na gama, ragowar kuma na kira monitor na bashi nace ya tabbatar ya bawa kowa kar wani yazo yace min baiga tashi ba. Nayi musu lecture na tafi abu na, domin yanzu ni kaina ina jin dad'in yadda nake koyar dasu kuma suke fahimta harma basa son lokacin tafiya ta yayi.

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□

[9/16, 11:29 AM] □: *33*

NANA HAFSAT

Ranar lahadi wajan karfe goma na gama shiryawa zanje saloon, su Innar mu kuma suna ta shiri zasu je kuma duba gwaggo Aminatu kasan cewar ranar da tayi kunar da suka je basu samu ganinta ba asibitin basa bari a shiga a lokacin. Yau duk suke saka ran suwa duba ta, na yiwa Inna adawo lafiya nace tayi mata sannu sai nazo, na kama hannun Autar mu da zata min rakiya muka tafi. Ashe bayan fitar mu Yaya Najeebu ya taro musu mota bus zasu yi shata su tafi, sai duk aka taru a tsakar gidan mu. Kawu Ila ya karka ce kai yana cewa.

“Ke Kaltume ai banda ke aka lissafa za'aje, dan haka sai kiyi hakuri ki koma tunda an dauki Najeebu a d'akin ki.”

Maganar ta bawa Innar mu haushi ganin ai ba a bayansa zata je ba, kuma kudin mota bashi zai biya mata ba bare ya hanata yin abinda ranta yake so. Ranta a bace itama ta kawar da kai tace masa.

“Zuwa kuwa ko a taya sai naje, idan Najeebu yaje wannan ra'ayinsa ne. Yanzu kuma ni nake son zuwa dan haka babu mai hanani tunda nima ban hana wani ba”

“Iyeeeeh! Lallai ma Kaltume ni kike gyarawa cewa babu wanda ya isa ya hanaki? Ni zaki nunawa cewar komai kike yi gaban kanki ne baki da mashawarci? Yayi kyau, duk laifin mu ne da har muka barki a cikin gidan nan duk kika raina mu. Toh kuwa babu inda zakije kinji na gaya miki”

Innar mu ta yi murmushi mai kona zuciyar wanda yasan dashi ake, sannan ta girgiza kai tace.

“Toh naji ba zanje ba sai kun dawo. Kai Yayan su ka biyo ni d'aki zan aike ka wani guri.”

Innar mu na kaiwa nan ta koma sama sam bata bari maganar kawu ila ta zauna a cikin zuciyarta ba, tana barin wajan Yayan muzo zai bi bayanta kawu ila ya yi saurin janyo masa riga. Kallo ya watsa masa ba ina zaka? Cikin kumfar baki yace dashi.

“Ka dai gama biyan mai motar kud'in ko?”

“Kawu wane kud'in?”

“Kai kaji min yaro da wata tambaya. Kudin mota mana da zai kai mu gidan gwaggon taku, mu nan duk kai muke jira ka biya mana mu tafi.”

Zaro ido Yaya Najeebu yayi yana kallan jama'ar gurin da suke jiransa ya biya musu kud'in mota shi kadai sai kace wani don. Girgiza kai ya shiga yi domin duka kudin dake aljihunsa naira dubu uku ne, idan ya kwashe ya basu ya zai yi? Gashi bai san kiran da Inna take masa ba, dan haka yace.

“Kawu bani da isassun kud'in da zan iya biyawa kowa, sai dai kai da kawu khamis na biya muku.”

“Toh shikenan su sauran kowa ya biya idan yana son zuwa.”

“Ahayye nanaye kai, yau kuji min Ilayasu da wani batu. Wato kai tunda an biya maka shine harda saurin cewa mu kar a biya mana ko? Toh bani da kudi na fasa zuwa ai daman kara zanyi muku naje dubata.”

Cewar Bintalo tana buga tsakiyar zaninta tare da juyawa ta koma d'aki tana jefar da mayafi. Nan da nan duk wad'an da ba'a biya musu ba suka ce sun fasa zuwa duba gwaggo Aminatu. Yayan mu ya tab'e baki ya haye sama bayan ya bawa kawu ila dari biyar ya bawa kawu khamis dari biyar. Kawu Dawood daman ba dashi za'a je ba saboda tun asali da aka ce za'a yi tafiyar cewa yayi bashi da lafiya, yana zaune a k'ofar d'aki yana hangen bidirin da ake yi.

“Karda Allah yasa kuje d'an matsiya ta, idan itace ai bata duba alak'a zuwa take yi kowa yaci darajar masu daraja wato iyayen mu. Khamisu zo mu tafi bar shegu mu zamuje.”

Kawu ila ya fad'a yana jan numfashi tare da yin hanyar k'ofar gida.

“Zan biyawa Babar mu itama taje.”

Cewar Bala d'an kawu khamis. Innatuwa ta saki murmushi tana taka rawa yatsunta biyu a saman hancinta ta matse shi tana sakin gud'a.

“Ahaiyeee ragas ragajab jab, haihuwa mai rana, kaji irin yaran albarka. Balele Allah ya tsundumaka a aljanna yau kam ka fito dani wallahi.”

Wannan ya sake kular da Bintalo ta dinga harbin kafafuwan su Hinde dasu Hauwa'u tana dankara musu zagi.

“Ke Hafsatu zo karbi kudin mota kema kije a madadi na tunda ba zan samu damar zuwa ba. Nima jiya da daddare malam Hamza ya bani rancenta.”

Hafsatu tayi murmushi aka fara taku cikin gadara aka nufi gurin miji. Kawu Dawood ya karkace ya zaro kud'in aljihunsa naira d'ari biyar da talatin, ya mika mata d'ari biyar d'in ta karb'a tare da zurawa cikin jakarta tana yi masa godiya. Haka suka runtuma suka tafi mota sai dai driver yace musu tunda basu cika motar ba zai tsaya ya kara dibar wasu, kawu khamis yace to dan yasan idan ba hakan aka yi ba sai an karbi kudi da yawa a gurin su kuma babu wanda zai bayar. Suna tafiya Inna da Yaya Najeebu suka fito suma, can sukaje suka shiga mota suma suka tafi. Sai da aka je can suka had'u kawu ila kuwa ya dinga surfa masifa wai inna ta raina shi amman zai gyara mata zama, tayi dariya kawai bata ce komai ba...

2018

GIDAN ALH KABEER MAI WAFA

Haysam ne ya shiga zagaye a dakin sa. Hannuwan sa saqale da bayan sa. Lokaci zuwa lokaci yakan sauke gwauron numfashi yana cije lebe. Kada kai yayi ya fita daga dakin yana jin karfin abunda zai aikata. Parlorn mahaifiyar sa ya nufa. Tana hakimce a kujera me cin mutane uku. Wata yar matashiyar yar aikin ta na matsa kafafu. Tana hango sa ta fadada murmushin ta tana rage volume din tv,

“Ka tashi?”

“Na shi Umma. Barka da safiya! Nazo da asubah ai naga baki fito ba.”

“Barka dai dan Umma. Alhamdulillah wallahi. Eh yau ban fito parlor ba dake an zabga sanyi da asuba. Ka tashi lapia?”

“Alhamdulillah Umma..”

“Meya same ka? Naga idanuwan ka sunyi jajir. Wani abun ne?”

Kallon mai aikin tasu yayi ta gefen ido. Hajia Husnah ta janye kafafuwan ta,

“Je ki hanziyya. Zan kiraki anjima”

“Toh Hajia.”

Tana fita ya koma kusa da mahaifiyar sa yana marairace murya,

“Ummah...!”

“Dan Ummah! Meya faru ne yau?”

“Ummah ina cikin wani hali Umma, Dan Allah ki dubi zance na. Wallahi ina matukar sonta Ummah.”

“Wai kake so ne Haysam? Kanata magana a baibace. Ka fito ka fadi meke damun ka. Yar gidan wanene taki ka? Uhm?”

“Ummah tace naje na nemo yardar ki tukunna..... Ummah Pls ki amince. Banason rasa ta.”

Hajja hUsnah ta cire tagumin data xabga tana kallon Haysam daya birkice. Wacece ta kuncewa kan danta noti oho. Muskutawa tayi ta matsa.

“Ban fahimce ka ba Haysam. Wacece tace ka nemo yarda ta.?”

“B..Batoul..”

Ya karasa fada yana in’ina gaban sa na dukan tara tara. Wani banzan kallo Haj Husnah tayi mai hade da shure kafar sa dake kusa da ita,

“Matsa kafin na sharara maka mari, Ashe har yanzu kai sullutu ne? Shashasha, Sakarai wanda bai san ciwon kan sa ba? Kai wai dan girman Allah wane irin bakin asiri suka maka ne uhm? Me za kai da wannan kaskantacciyar yari...”

Bata karasa ba ya rik’o kafafunta yana zubar da hawaye,

“Ummah Ki duba zance na. Wallahi Wallahi Inason Batoul. So mai tsanani ummah. I can’t take it shiysa nazo na gaya miki. Zuciya ta tana rad’ad’i ummah. Ummah karki manta yarinyar nan ma yanzu tafasa mu aikin yi. Allah ya canza musu rayuwar su. Inason ta a haka ..”

“Toh sallamamme! Sun gama da kai ai. Har kake kallon tsabar idanu na kana gayan Allah ya canza musu rayuwar su? Dan uban ka ko farcen uban ku sun dakko a kudi ne? Ana nuna ma gabas kana ga yamma?”

“Ummah dube ni mana har yanzu bansamu aiki ba Ummah. Bakya ganin hakan ma wata jarabawa ce?”

“Zaka dena kalaman nan ko sai na hanbare ka? Kai bakada zuciya ma Wallahi. Yarinyar data gama watsewa a jami’a har biyu? Nan aka kawomin zancen ta samu lecturing a jami’ar dai. Tun muna sheda juna ka rabu da figalalliyar yarinyar nan.”

“Ummah Pls..”

“Sannu bature. Na hada ka da pls din na gungurin uban ka. Banda rai ni da kaskanci me zaka debo a auren ta? Wallahi nasan layi layi ana nuna ni ga sirikar matsiyata. Tashi kabar mun waje.”

“Ummana ki yafemin. Dan Allah ki barni na auri Batoul.”

Yatsa Hajia husnah tasa a baki ta ciza tana dankara masa harara,

“Tashi ka bani waje sallamamme. Kayi duk abunda kaga dama.”

“Allah ya baki hak’uri. Allah ya huci zuciyar ki. Ki dai duba zance na Ummah.”

Yana gama magana ya mike ya fice daga parlorn yana dafe zuciar sa dake masa zugi. Yarasa wane irin kiyayya mahaifiyar sa ke yiwa Batoul. Yana fita tabi bayan sa da harara tana jan tsaki. Tacika tayi fam tamkar zata fashe. Cike da bacin rai take maimata,

“dole ka sakko daga doron *ZATON* da ka hau wallahi. Wacace Batoul? Allah ya sawake na hada zuri’a da matsiyata.”

Shi kuwa Haysam takalmi yasa ya fice daga gidan. Motar sa ya hau yayi layin su Batoul. Ata’kaice gidan su ma yai niyyar shiga sai dai ayita ta kare. Akan titi yagano ta tana tafiya. Sanye cikin bou-bou riga red and black. Ta yafa mayafin ta red. Tayi kyau kwarai dagaske. Sai zambada sauri take duba agogo. A gefan ta ya tsaya bayan yabude glass din motar. Ya dan sunkuyar da kansa yadda zata ganshi ta kuma jiyo shi,

“Yanmata na... Shigo na kai ki.”

“Ah Ya Haysam!”

Budewa tayi ta shiga bakin ta dauke da sallama,

“Ina kwana Ya Haysam? An tashi lapia?”

“Lapia qalau Mine..Muje ko?”

“Muje..”

Na fada ina mai duba takardun kan cinyata. Questions da zanyi submitting a dean office na exams din da za’a fara jibi. Lokaci zuwa lokaci Haysam ke kallo na yana mai cigaba da tukin da yake yi,

“Kinyi kyau mine..”

“Nagode Ya Haysam.”

“Yaushe zaku tashi nazo na dauke ki.”

“Kakka damu Ya Haysam. Nagode wallahi”

“No ai ni nayi niyya.”

“Kamar 5 haka IN SHA ALLAH!”

“Okay Mine. Ki jira zanzo IN SHA ALLAHU.”

Kada kai nayi ina duba agogon hannu na. Hira muke tabawa har muka karasa shiga gate din school din sannan ya rage tafiya yana gyara murya,

“Ki cigaba da sanyamu a addua Mine. In sha Allah kin kusa zama officially Mrs Haysam.”

Kallon sa nayi kawai ina kakaro murmushi. Rausayar da kai yayi yana kallo na,

“Ko bakiji me nace ba u..Uhm?”

Murmushi na sake yi wanda hushirya ta ta bayyana,

“Hajian ku ta yadda ne?”

“Sure! Why not? Tabani zab’i”

Haysam ya fada yana rintse idanu. Ya sake marairaicemin yana rage sautin muryar sa cikin so da kauna,

“Soyayyar da na ke yi miki tamkar tafiyace mai nisa da na fara yinta wadda bata da lokacin yankewa har abada Mine. Na san burina zai cika matsawar ina tare da ke domin kuwa dukkanin burina yanzu bai wuce na samun ki a matsayin matata uwar ‘ya’yana ba. Ina son ki fiye da gwal ko kud’i. I love you pass my mind beyond my soul. My Batoul..”

Yaja sunana cikin wata siga. Rufe fuska ta nayi ina murmushi. Ya kawoni har bakin office dina.

“Nagode Ya Haysam.”

Na karasa fada ina kokarin bude kofar najita a datse. Kallon sa nayi ya kara rage murya yana kallon cikin idanu na. Kunya ta isheni ga dalibai na wuce wa,

“You are the most beautiful woman in my life and it is the reason why I want to spend the rest of my life with you. No one can stop me from loving you. I am with you my lovely girl. I am with you my love all my life...”

Mubeen dake zaune a kofar office dinta tun d’axu yana jiran zuwan ta. Ya mike hango su da yai ta cikin motar tana dasharewa wani hakora. Ga dukkan alamu kuma saurayin ta ne. Taune kasan lips dinsa yai yana rintse idanu. Sai kaiwa da kawowa yake yi taki fitowa daga motar. Alokacin kuma Haysam ne ya isheta da kalamai sai ta bashi amsa. Ajiyar zucia ta sauke tana kallon waje wanda idanun su suka sarke da Mubeen ya zabga mata harara yana cuno baki.

“Babu komai Ya Haysam. Na..Na..Na amince.”

Haysam dadi ya cika shi ya kifa kansa akan steering yana kallon Batoul cike da soyayyah yama kasa magana. Ita kuwa futowa tai da sauri daga ciki har tana tuntub’e ta shiga office dinta ko kallon Mubeen batai ba. Ya bita office din yana mai rufe kofar. Kallon Misklin yaron nan nai ina ajiye kayan hannu na,

“Ya akai..?”

“Ayana....”

“Ayaba.?”

Na fada ina kallon sa. Girgiza kai yayi yana sauke ajiyar zuciya,

“Ina kwana..?!”

“Lapia lou”

Wata Ajiyar zuciar ya kuma saukewa na kalle shi naga ni yake karewa kallo. Shi kuma a lokacin so yake yace ta goge jambakin da ya hau saman hancin ta ya kasa. Gadan gadan ya nufe ta ta ja baya tana zare idanu. Handkerchief ya ciro a aljihun sa yana kallon idanun ta. Ta kasa motsi sai raba idanu take. Murmushi yai. Ahankli yasa handkerchief din ya goge mata saman hancin ta. Ta kalle shi tana zare idanu. Nuna mata kasan handkerchief din yai yana murmushi,

“Kar ka sake yi min haka.”

“Sorry Ma'am.”

Ya fad'a a hankali. Daga kai nayi ina kallon sa. Mekyau dashi ga nutsuwa acikin sauran students. Murmushi ya min yana zuge zip din jakar sa. Wani kwali ya ciro ya ajiye a gaba na. Kallon sa nayi alamun Ya haka? Lumshe idanu yai ya bud'e su a kaina, a hankali mai makwan ya bani amsar tambaya na sai ji nayi yace,

“You luk breathtaking Ma!”

“Lower your gaze.”

Murmushi naga ya sake yi. Ya zauna akan kujera yana zubamin idanu. Kasa jure kallon sa nayi na dubi gefe. Sake jiyo shi nayi yana cemin,

“I know you have a busy day ahead of you, but could you add me on to your to-do list?Pls Ma.”

“Me zan maka ne. Meye baka gane ba uhm?”

“Ma waye wanda ya kawo ki?”

“Banda personal questions..”

“Wai.. So pestiferous!”

“Kace me?”

“Nace kinyi kyau..”

Nama rasa amsar da zan bashi,

“Toh Nagode tashi ka tafi.”

“Mah dan Allah zan kai ki gidah yau.”

“No thanks.”

“Why??”

Mubeen ya bani amsa a marairai ce. Naja numfashi kawai na dan juya baya ina gyara gyale na saboda office din dean xani. Har nayi kofa ya riko mayafi na yana girgiza kai,

“Pls ki kara gyarawa yana yayewa mayafin.”

“And what does that have to do with you..?”

Ajiyar zuciya na sauke na gyara mayafin ina jinjina karfin hali irin nashi.

“Zan kai ki gidah Pls.”

“Nace a’a. Ni fa malamar kace meyasa ka rena ni ne?”

Sunkuyar da kansa kasa yayi. Ya girgiza kai yana kokarin saka gwiwoyin sa a kasa. Idanuwan sa sun kawo ruwa. Na bud'e baki ina kallon ikon Allah.

“please mah.''

“Meye haka? Tashi karka tsugunna meye haka? Mena maka uhm? Afuwan please.. wanda zan aura ne zai zo ya d'auke ni.”

“Kika ce me?”

Ya tambaye ni da karfi a tsawance😮 Gaba d’aya ya hautsine. 'Na shiga uku' na furta a hanakali ina ja da baya. Har bakin kofa muka kai a haka. Na tukwikwiye jiki na sai rawa yake. Domin ya fini tsawo ba sosai ba. Sai yai min rumfa ina jiyo bugun zuciar sa. Ahnkali cikin wani irin yare na jiyo sautin saukar numfashin shi akan fuska ta yana cewa,

''Dan Allah, dan girman Allah kibarni na kai ki gida.''

Bangajeshi nai zan fita ya rikomin yatsu yana kikkifta min ido. Cikin sarkewar harshe yake cewa,

''Wallahi bazan miki magana ba har muje mah, please mah ki taimaka dan Allah.''

Gaba d’aya ji na da gani na sai suka dauke na yan wasu dakikai...Kujerata na koma na zauna ina sauke numfashi, cikin raina ina cewa yau nayi gamo, daman ina jin labarin yadda wasu students d'in suke raina lecturers d'insu mata, shi yasa yawanci ba'a fiye bawa 'yan mata aikin koyarwa ba yawanci sai masu aure da zawarawa. Balle ni da nake d'anya sharaf, kuma babu wanda zai ce nakai wad'an nan shekarun. Yana can inda na baro shi a tsaye yana kallon k'ofa bai juyo ba, nima bance masa ya juyo ba domin banga amfanin yin hakan ba, nace dashi.

“Ban san me yasa kake yi min hakan ba, amman koma menene kai ka sani a cikin zuciyarka. Kabar yi min hakan domin a koma menene ina gaba dakai ya kamata kasan hakan.”

Ko motsawa Mubeen beyi ba, sai ma jinjina kai da ya dinga yi, daga baya ma sai ya fita daga office d'in ba tare da ya kuma ce min komai ba. Ko'a jikina domin ni kaina jira nake ya tafi yaban gurin dan banga abinda ya had'a mu ba bare ya takura mini. Tashi nayi na wuce office d'in Deen nayi submitting questions d'in exam, yana karb'a muka d'an yi magana dashi sannan na koma nawa office d'in. Karfe biyar nayi har na fito zan tafi naga ashe Haysam yazo, na saki murmushi tare da nufar motarsa na bud'e na shiga. Ashe duk akan idanun Mubeen wanda tun zuwan motar Haysam yaji gabaki d'aya hankalinsa ya kuma tashi, ya kasa tabuka komai ji yake kamar ya fashe da kuka, yana ji yana gani muka wuce dan yasan ko ba Haysam ba zan shiga motar su ba..

..

Kunji shiru ko? Afuwan wlh banida Lpy yanzu ma daurewa nayi. Allah ya bamu Lpy mai dorewa AMIIN□□

-

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

_Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□_*ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

28

SARQAQIYAR RAYUWA

1□

Ina daga zaune ban san lokacin dana mik'e tsaye ba saboda tsabar farin ciki, nayi zaton ma kunnuwa nane basuji ba sosai, sai da na kuma tambayar Mrs Suleiman ta tabbatar min. Kamar a gabanta haka na durkusa tsakiyar d'akin mu ina ta zuba mata godiya da addu'o'i, har sai da ta katse dan kankin kanta. Innar mu ta tambaye ni abinda yake faruwa na sanar mata, itama ta dinga zambad'a addu'a. Yayan mu

kuwa ban bari sai da ya dawo ba, a take na buga masa waya na fara sanar masa, Babu network inda yake sam bai ji me nake ce masa ba. Mi’kewa nai na zura hijabi,

“Innar mu bari na fadawa Yayan mu wannan daddadan labari.”

“Toh Allah ya temaka, Yasa a fara a sa’a.”

“Ameen Innar mu..”

Ina sauka matattakalar bene na jiyo muryar yayan mu daga zaure yana magana da kassim almajiri. Sai da ya shigo ciki a tsakar gidah na sanar dashi ina murna, Ban damu da ahalin dake tsakar gidan mu ba. Ai kuwa Yayan mu ya tayani murna sosai, Yan bakin ciki kuwa sai zund’e suke yi suna tsegumi a hankali.

Kawu Ishaq dake gefe yana alwala a bakin rijiya ya daga kai yana duban mu,

“Menene ne kuke ta murna kuna dashare hak’ora kamar gonar auduga?”

Yaya Najibu cikin fad’ad’a murmushin sa cike da girmamawa yace da Kawu Ishaq,

“Kawu ta samu babban aiki ne..”

“Ai me..?”

Cewar Kawu ila dake fitowa daga dakin sa yana sakin hamma. Sai da yai mika mai isar sa tukun sannan ya zura takalmi wari da wari hade da d’akko bokitin zaman sa ya zauna yana goge kunnen sa da dan yatsan sa karami,

“Ai me kace?”

Ya sake tambayar Yayan mu dake tsaye yana jiran sa. Ni kuwa jingina nayi ajikin bango ina dudduba waya ta,

“Nace ta samu babban aiki ne.”

Yayan mu ya sake fa’da masa. Kawu ila yaja dogon tsaki ya sauke yana karkada hannuwa,

“Kiramin kawunnin ku. Shikenan gandar-dar da ita sai ta zauna tana aiki babu batin aure a gaban ta? Yasin ba zata sab’uba..”

Yayan mu yayi murmushi yana gyara tsayuwar sa,

“Kawu ai komai lokaci ne.”

“Lokacin uban uban ka? Aina ake haka? Gandamemiyar budurwa ta zauna banda karatu babu abinda tasa a gaba? Ba za tai aure ba kenan. Ke Mari hau sama ki kirawomin sauran kawunnin ku.”

“Sittin ta ubangiji dai abin yayi yawa, Kuma duk Kaltume ce ta dora su a hanya..”

Bintalo ta fada tana watsa hannu baya cike da zuga. A sanyaye nace,

“Kema fa baba ga su Hinde nan agaban ki...”

“A hayye nanaye! Ni kike duba tsabar idanuna na kike gayawa haka? Ah lalle kin zama cikakkiya.”

Ba a dau lokaci ba Kawunnin mu dik suka hallara a tsakar gidah. Lalle ba karamar tijara za’ai ba. Fuska na murtuke ina cigaba da addua a zuciata domin a shirye nake da mai da martani ga duk kanin su wallahi. Kawu ila ya gyara murya yana nuna ni da yatsa,

“Ga tanan wai aiki ta samu. Dan tsohon munafunci ma ba gaya mana akai ba ji mukai a gari.”

Na murmusa kawai ina kallon sa da mamakin kalaman da yayi. Kawu Ishaq dake shimfida buhu zai yi sallah ya dube ni,

“Aina ne wajen aikin?”

“Koyarwa ce fa Kawu..”

“Ba koyarwar kike ba ko wata ce daban?”

“Eh Kawu... Ta jami’a ce wannan.”

“Jami’ah! A hayye nanaye. Sittin ta ubangiji yau ga gaye ba makilis. Kece zaki fara koyarwa a jami’a? Shin ta yaya ma kika samu aiki a jami’a?”

Banza nayi mata na cigaba da salatin da nake a zucia ta. Bintalo sai maganganu take yi ni kuwa nayi biris da ita, Su Kawu khamis sun biye mata suna tayata,

“Gaskia dai wannan zance babu shi a soke shi...”

Cewar Kawu Khamis, Kawu Dawood shi dai sakacen hakorin sa kawai yake yana daga kai. Kawu ila ya cika yayi fam. Ya dube ni shakeke yana yamutsa fuska,

“Kinsan kuwa shekarun ki nawa? Waton ba zaki aure ba sai neman duniya?..”

Kai na a kasa bance dashi komai ba na cigaba da wasa da kasan hijabi na. Shi ko kunya bayayi, Bayan dukkanin samari na shiya koremin su da sharri.

“Tab sittin ta ubangiji ta rena ka, Har kai kana magana tana yi maka shiru?”

Bintalo ta ceda Kawu ila haka cikin kururuwa, Kawu ila ya dankara min harara kafin yace,

“Ai wuyan ta ya isa yanka, Taga yanzu zata fimu arziki, Dama ta kere mu. Shiysa rainin ya ‘karu.”

“Kuyi hak’uri Kawu. Wallahi babu wanda na raina acikin ku.”

“Raini kuma ai kingama raina mu, Kinsan shekarun ki kuwa? Ke nan ba zaki aure bane ko kuwa kwantai kikai ba samari?”

Girgiza kai na nayi. Cike da murmushin yak’e nace,

“Kawu shekaruna ashirin da shida (26) kuma su Alawiyyah agaba dani suke..”

Bintalo ta saki guda tana buga zani hade da watsa hannu baya,

“Bashakka! Kwarai, Lalle yanzu kika fito da abunda ke zuciar ki. Dama sittin ta ubangiji tun ba yau ba nake da masaniyar da sa hannun ku a dagula lissafin rayuwar ‘yayana. Guda d’ayan dake gidan aure ma kun fiddo ta saboda ta tsone muku idanu.”

Murmushi nayi kawai ina wasa da wayar hannu na,

“Baba *ZATO* zunubi ne ko da ya zamto gaskia, Akan wane dalilin zamuje mu gurbata rayuwar yayan ki.? Yan uwanane fa na jini. Sannan ni wallahi tallahi hanyar malamai ma bamu sani ba ballantana mukai sunan ‘yayan ki.”

“Rufemin baki, Makira. Malam mai gobe da nisa sittin ta ubangiji yace dasa hannun kaltume da Ummita a tabarbarewar rayuwa ta da yarana.”

Bance komai ba, Saboda ba nida amsar jahilar maganar da take yi, Domin mu da ALLAH muka dogara, Shine zai yaye mana dukkanin lamurran mu. Haka dai Bintalo tai ta maganganun ta yan amshin shatan ta na taya ta. Kawu ila ya sake gyaran murya yana sakace da zaren taburma,

“Babu wani jami’a da zakije koyarwa, Idan kuwa kin tilasta toh zaki dinga bada wani sashe na kudi a albashin ki.”

Murmushi Yayan mu yayi yana kallo na kafin cike da girmamawa yace da Kawu ila,

“Babu damuwa Kawu, In Sha Allah hakan ba zai gagara ba. Allah ya dai ya kai mu lokacin da za’a fara biyan nasu.”

Bintalo ta buga tsaki hade da sab’ar mayafi tafi ce waje. Ni kuwa Yayan mu na cewa haka na haye sama abuna. Ina shiga da’ki na sanarwa Innar mu yadda akai, Har Yayan mu ya shigo shima muka cigaba da maganar,

“Wallahi Innar mu bakin cikine kawai sunga na fisu ilimi kuma Allah yana bani nasara a karatun nawa.”

Na fada ina girgiza kai na cike da takaici , Yayan mu yai murmushi

“Babu komai wanda ya isa yai yawa shi akeyiwa hassada. Zallar hassada ce gani sukai idan su kai wasa zaki fisu arziki. Kuma da yardar Allah sauran daukaka ma na gaba.”

“In Sha Allah kuwa! Allah ya daukaka mu baki d’aya Yayan mu.”

“Ameen Ya Hayyu Ya Qayyum.”

Haka dai muka shiga hirar mu cike da so da kaunar juna. Na dafa mana taliya da kifin gwangwani muka ci a tare da Yayan mu da autar mu. Innar mu kuma taci nata ita kad’ai. Fankar da Yayan mu ya siyo sai wulwulawa take yi tana bamu iska. Domin tuni aka gyara mana wutar dakin mu. Munci sa’a kuma ana kawo wuta sosai babu lefi.

WASHE-GARI

1st January, 2017.

Bintalo taja majina hade da cigaba da yanka tuwon da take yi a faranti. Tana yi tana sakin tsaki a karo na ba adadi. ‘Kandas tuwon yake ba mai bare magi. ‘Yayan zabbau kuwa sun jeru su biyar suna binta da kallon tagama ta basu. Tsaki ta sake ja tana mai dankara musu harara,

“Sittin ta ubangiji yaran nan ko mayu sai haka. Sai kace masu cikin randa sam bakwa ‘koshi? Sittin ta ubangiji ko su’din kwano ba zan baku ba. Daga yau kowa ici da kansa a dakin nan.”

Hinde ta wangame baki tana hamma cike da yunwa. Dukawa tayi ta sab’i danta a baya ta zura hijabi. Alawiyyah dake numfarfashin ciwo ta dube ta dakyar tace,

“Ina zaki?”

“Bara zani! Zanci babu ne ni da ‘dana?”

Alawiyyah ta girgiza kai tana mai komawa kishingidar da tayi cikin ciwo. Bintalo ta mike da sauri ta fice da kwanon tuwon nata. Ranar dai kowannen su shi ya samawa kansa abincin safe. Da rana Bintalo ta zauna a kafar bene tana neman magana. Baba usaiba ta shiga yan wakokin ta tana yagawa Bintalo magana,

“Idan ta ‘karewa mutum shikenan kuma. Kusufa-kusufa zaka ganshi ya zauna yana neman magana. A hayye kayya kai.•

Bintalo taja tsaki tana mai da kanta gefe.

“Aikin banza.”

Baba Usaiba tai ta kyalkyalawa Bintalo daria, Irin dariyar nan mai sanya mutum kuka, Ta ‘kularwa sosai. Daga karshe Bintalo ta figi mayafi ta fice bayan ta kwararo rantsuwa ta direwa Usaiba kan zata sab’a mata. Ita kuwa usaiba dariya taita kyalkyala mata tana sake ‘kular da ita. A can gangare ta ha’du da Ruma, Suka tsaya suna gaisawa.

“Dama wajen ki zani fa.”

Bintalo tace da Ruma dake sake gyara zaman mayafin ta.

“Haba? Ai kuwa Allah yayi zamu hadu da munyi sab’ani..”

Bintalo taja gwauruwar ajiyar zucia ta sauke,

“Ruma ina cikin gararin rayuwa. Kinga in takaice miki zance dai na bar aiki a gidan Alhaji Kabeeru.”

Ruma ta gwale baki hade da jan Bintalo su koma inuwa. Cike da mamaki take duban Bintalo,

“Dagaske?”

“Sittin ta ubangiji kuwa..”

Bintalo ta shiga ha’da karya da rantsuwa tana gayawa Ruma. Ruma ta jajanta mata sosai,

“Toh yanzu ya za’ai Bintalo?”

“Sittin ta ubangiji Ruma bansani ba, Ba nida mafita. Ta ‘karemin, Abinci ma gagarar mu yake.”

Ruma ta kad’a kai tana tunani can ta nisa kafin tace,

“Zan cigito miki ko zaki samu wani gidan aikin. Yanzu dai idan zaki iya muje bakin kasuwa kya samo yan chanji ko ki zama uwar dashi.”

“Yauwa Ruma. Nagode.”

A tare suka taka har yar kasuwa. Ba ita ta dawo ba sai bayan isha’i. Hannun ta rike da biredi dan yanka-yanka da asusu ta karb’o na adashi. Ruma ta bata tace ta zama uwar ajiyar su. Idan karshen wata yayi anzo d’auka sai ta dauki zubin karshe itama,

wato ladan ajiya kenan. ta haye bayan ta tsaya a band’aki ta kwarara fitsari. Tana shiga d’aki yaran zabbau suka yanyane ta. Kowanne yana jiran ta bashi. Harara ta daddankara musu tana mai basu uku uku,

“Dik wanda na bawa ya tashi yabar nan wajen. Shegun yara da kayuwa runtuma-runtuma.”

Kankace me tuni har sun lankwame suna sake zubawa Bintalo ido don ta kara musu. Karamin cikin su ya tafi wajen ta tinkis-tinkis yana kwakwalwar tasono, Domin kullum cikin kazanta suke, dikin-dikin dasu ba wanka bare wanki.

“Ban kohi ba. Ki k’aramin”

Bintalo taja tsaki tana hararar sa.

“Bazan kara ba. Marasa godiyar Allah. Kunsan yadda akai na samo shi ne? Zaka zo da wani runtumemen kanka wai baka koshi ba.”

Bintalo ta k’arasa fada hade da sakar masa rankwashi a kwanyar kansa, ji kake ‘kwas. Yaran ya hau kuka yana kururuwar yunwa. Sai da Bintalo taci tai nak sannan ta jifesu da sauran tana binsu da kwandon tsinantaka.

Cikin dare kunnuwana suka fara jiyomin tamkar ana sand’a, An wuce ta gaban dakin mu. Na rintse idanuna ina mai kwararo addu’ar tsari saboda dare mahutar bawa ne, Yayin da wanda bama gani kuma ke karakainan su. Gilmawar mutum naga ni da koriyar riga. Cike da fargaba na rintse idanu ina cigaba da adduar kariya. Ashe Yusha’u ne dan innatuwa ya shiga dakin Bintalo da sand’a. Suna kwance wasu kan wasu a dakin. Bintalo tayi bacci da Asusun a hannunta tana jan munshari tamkar bijimin sa. Ai kuwa Yusha’u ya zare asusun ya gudu. Da asubar fari Bintalo ta cika gidan mu da kururuwa da hargagi, Kai harda kumfar baki take tana watsa hannu baya hade da kwaso rantsuwa da zallar zagi marar surke.

“Sittin ta ubangiji duk barawo ko barauniyar data dau asusun nan sai ta bani shi, Wallahi tallahi ba yadda zanyi ba, Wato har fakar idona akai, Sai da aka bari dare yayi nayi nisa a bacci aka sad’ado aka dauke min shi, Sittin ta ubangiji ba yadda zanyi ba. A hayye yau ga gaye ba makilis, Munsan shafe shafe munsan mai. Sittin ta ubangiji ko gidan nan sai an sayar an biyani kudin mutane..”

Yan gidan mu su kai tsit, Kowa kallon ta yake. Ta zama kamar sabuwar tabi. Sai maimatawa take tana had’awa da zagi kala kala.

“Wai me aka dauke miki ne Bintalo?!”

Hansatu matar Kawu Dawood ta tambayeta tana zabga tagumi. Bintalo ta buga zani tana kwaso rantsuwa,

“Sittin ta ubangiji asusu ne na zubin adashen su Ruma kawata. Shine aka biyo dare aka sace shi. Kuma sittin ta ubangiji yan gidannan ne. Kuma sai an biya ni a yau. Tab yau ga gaye ba makilis. Sittin ta ubangiji ba zata sab’uba. A’hayye...”

Idar da sallata kenan na futo ina mamakin abunda take fada, Tabbs da cikin dare naga wulgawar mutum da koren kaya. Na tsaya ina bin yan gidan mu da kallo. Ai kuwa na hango Yusha’u da koriyar rigar shadda sai sunne kai yake abinka da maras gaskiya.

“Kuna ina ahalin gidan mata tara? Sittin ta ubangiji sai an biyani kudi na.”

Baba usaiba dake alwala a kasa taja tsaki tana buga zani,

“Wanda ya sace dai shi zai biya ki. Amman billahil lazi banci nanin ba nanin ba zata ci ni ba. A hayye kayya kai..”

Bintalo ta shatalo kafar usaiba suka fara dambe, Ni kuwa na shiga daki na d’akko bokitin wankan mu na sauka k’asa nayo wanka na. Domin da wuri nake son zuwa makaranta saboda sanin gurbin da aka bani. Wanka na na fallo na koma daki. Ina jiyo hargagiyar su sai yi akeyi. Fata na dai Yusha’u yace shine ya bata kawai ba sai anyi tone-tone ba. Innar mu na gaydar na fara kintsawa ina azkhar. Har wajen bakwai saura suna fada banajin akwai wanda yai sallah acikin yan kallon nan ma. Na karya kumallo na. Inata sauri na fara shafe jiki na da tururuka na dana sissiyo masu sanyin kamshi. Sanye nake cikin royal blue din doguwar rigar material dinkin A shape. Na yane kaina da mayafi silver, Takalmi na ma da jakata duk silver ne. Banyi wata kwalliya ba kawai dai na dan shafa hoda da man lebe na taje girata. Nayi kyau sosai, Tamkar ka dauke ni ka gudu. Saboda yanzu Alhamdulillah akwai ishasshen abinci ga wuta muna kunna fanka, Dan mai na da sabulu suma suna karawa fatata sheki. Light brown color dina ta kara turuwa sosai. Hakama kirar jiki na komai dai dai, Domin tamkar ni na kera abuna. I look younger than my age. Domin idan ka kalle ni zaka bani shekaru ‘kasa da nawa. Murmushi nai bayan na kalli kai na ta mudubi na dubi Innar mu dake lazumi,

“Innar mu komai yayi?”

“Komai yayi uwa ta. Tamkar zaki gasar zaben kyau. Masha Allahu! Allah ya bada nasara akan abunda akaje yi. Yasa ki fara a sa’a.”

Nan danan gaba na ya fadi tunowa da nai da dimbin daliban da zan koyar. Dubada yadda muma aka koyar damu. Na hadiye yawun daya tsayamin na tsoro kafin nayi karfin halin cewar,

“Ameen dai Innar mu. Ki tayani da addua. Har gabana ya fara fa’duwa wallahi.”

“In Sha Allah alkhairi ne. Allah ya shiga lamurran ki. Kede ki kara tsare mutuncin ki kawai. Allah yabada sa’a.”

“Ameen Innar mu. Nagode Allah ya saka da alkhairi. Allah ya jikan baba da sauran magabatan mu.”

“Ameen Ya ALLAH..”

Kasa na fara sauka ina kallon Yusha’u dake dibar ruwa a rijiya. Zan fice kenan Bintalo ta janyo ni tana kwaso rantsuwa tana direwa,

“Wa? Ina zaki? Ai baki ga ta tafiya ba ‘yar nan. Sittin ta ubangiji ko dai kuyi karo karo ku biya kudin mutane ko kuma a sayar da gidan nan a biyani kudin mutane.”

Agogo na na kalla dake daure a hannu na ina girgiza kai,

“Baba ni ban daukar miki kudi ba wallahi, Sauri nake zan tafi dan Allah ki sake ni kada na makara.”

Bintalo ta callara kara tana buga zani,

“Sittin ta ubangiji babu inda zaki ko hansatu dake fita yawon bara yau na hana ta saboda sai an biyani kudin mutane sannan kowa keda kwanciyar hankali..”

Baba usaiba ta taka rawa tana gud’a,

“Ayyiriririrrir! A hayye kayya kai! Nifa banyadda ba sai dai idan acikin yayan ki ne wata ta d’auka.”

“Sittin ta ubangiji babu wadda ta dauka acikin su. Asusu dauke shi aka yi. Cikin dare aka sad’ad’o aka dauke min shi., Barayin banza, Barayin wofi.”

Haka su kaita ja’inja, Ta fada, Baba usaiba ta maida martani. Sauran yan gidan na kallon su kamar wasan kwaikwayo. Ganin zata sa na makara yasa naja tsaki ina kallon Yusha’u.

“Kai Yusha’u kune bakwa baccin wuri. Bakuga wanda ya dauka ba.”

Saurin girgiza kai yayi yana dora bokitin ruwa a kansa. Na sake jan wani tsakin a karo na biyu ina kallon agogo na.

“Baba ni dai cikin dare naga wulgawar mutun da koren kaya..”

Bintalo ta buga zani tana sallallami, Ta kara matsowa kusa da ni jin karin bayani, Nayi baya ina dan rufe hanci na jin tashin warin da take yi.

“Wane barawon ne kikaga wulgawar sa? Mace ko namiji? Fad’amin yanzun nan na zugewa mutum ta zuge. Sittin ta ubangiji duk girman sa kuwa.”

Ni kuwa nayi murmushi kawai ina kallon Yusha’u. Har ga Allah banason na tonashi nafuso ya dakko ya bata abinta. Amma yak’i magana. Kuma yanzu duk yadda zata kai ta kawo kan yan dakin mu za’a ‘kakaba mana sata bamuji ba bamu gani ba.

“Ni dai koren kaya nagani. Kuma dik wurin nan babu mai koren kaya fyace Yusha’u.”

Innatuwa tai kukan kura ta tsaya a gaba na tana huci,

“Mak’aryaciyar banza da wofi. Kun sace mata shine zaki kakaba masa sharri? Wallahi karya take Bintalo. Duk yadda akai sai dai idan Najibu ne ya dauka.”

Bintalo ta callara guda tana watsa hannu baya,

“Nide babu ruwana, Sittin ta ubangiji a biyani kawai. Amma dai tunda taga koren kaya, Wajibi ne ai yar caje anma takan kayan Yusha’u za’a fara..”

Innatuwa tai kukan kura hade da buga tsalle ta dire kan ai ba Yusha’u ne yai sata ba sharri nake masa. Ai kuwa dai Bintalo ta bangaje Yusha’u daya runtuma da gudu ya rungume buhun kayan sa. Wafcewa tai ta zazzage a kasa sai ga asusun ta ya fado. Ta buga tsalle tana kururuwa tare da faffallawa Yusha’u maruka kala biyar ya zube yana kuka a kasa. Innatuwa tayo kai na tana haki naja gefe ina murmushi,

“Sai dai idan kece kika sace kika saka masa acikin k...”

Yusha’u ya mike yana kuka ya dakatar da innatuwa.

“Yasin yazeedu ne ya koya min shi dasu Fareed kancewar idan na dakko za’a raba dai dai. Hakama su kai da wayar Innar su Batoul shekarun baya. Kuma harna makota suke dauka dana shaguna..”

Nayi murmushi kawai jin kalaman sa na karshe. Innatuwa sai dankara min harara take yi. Ni kuwa hamdalah nayi domin taga sakayya akan bakaken maganganun da take gasamin hade da sharrin da take binmu dashi, Sai gashi dan ta na cikin ta ‘barawo ne. Ai kuwa Bintalo tayi wata uwar kara ta shiga bubbugawa Kawu ila kofa,

“A hayye yau ga gaye ba makilis. Toh Fitonan ilyasu, Kai ma Dawood ka sakko.Munafukan banza da wofi. Ashe kunsan ‘yayan kune suke sace sace shiysa tunda na fara maganganuna babu wanda ya fito acikin ku.? Toh sittin ta ubangiji anyi na farko anyi na karshe. Ku jawa barayin ‘yayan ku kunne kada su kuskura su kara maimaita rana irin ta yau. Domin idan aka kara karo na biyu sittin ta ubangiji duka sai na makaku a kotu.”

Kawu ila ya fito daga dakin sa hannun sa na hagu dauke da bokitin zaman sa. Ya wangale bakin sa ya saki hamma yana sosa ciki. Ni kuwa sauri nayi nai ficewa ta na barsu suna ta ruguntsumi. Har titin yar kasuwa ana jiyo hayaniyar su. Ni dai mashin na hau ya kai ni inda ake lodin samaru campus. Bakina dauke da adduar samun nasara a rayuwar mu, da karatuna dama sabuwar shekarar 2017 da muka shiga....

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

MX□□[9/16, 11:29 AM] □: *34*

NANA HAFSAT

Alhamdulillah komai cikin tsari da lapia aka fara gudanar da jarabawar zangon karatu na farko na daliban dake nan jami’ar Amadu bello. Ranar Friday yan level one zasu zana jarabawa d’aya daga cikin courses biyu da nake daukar su. Wato course din, The Essay in English: The Twentieth Century: Theory and Practice I.

GIDAN MATA TARA

Da wuri na tashi. Tunda nai sallah ban koma ba. Wanka nayo na shirya cikin wani lesi da Fadila ta mana sallar bara, Green ne da ratsin yellow. D’inkin samfarin doguwar riga ne kirar A shape. Hakan yasa na zura wani hijabi da nasiya sabo shima yellow. Ba kadan ba nayi kyau. Yar hoda na shafa kadan da man lebe bayan na bi jikina da turaruka masu sanyin kamshi. A gagguace na tsaya naci abincin safe na. Wainar fulawa ce lafa-lafa ta manja tasha kayan hadi. Naci biyu na zuba uku a yar roba na zura a jakata kan anjima naci a makaranta.

“Innar mu zan tafi.. Kinsan yau zasu zana jarabawa ta ta farko.”

“Masha Allahu! Ubangiji Allah yasa su fara a sa’a. Allah ya tsare ya kare. Sai kin dawo.”

“Amin Innar mu, Sai na dawo.”

“Toh Allah ya dawo daku lapia. Allah ya bada sa’a.”

“Amiin Innar mu.”

Mikewa nayi na fita ina ta sauri. Na gayda yan tsakar gidan mu wasun su sun amsa wasu su kai biris. Na daga kai na fita. A kofar gida naci karo da motar yan sanda tanata jiniya. Zan wuce wani police daga ciki ya dakatar dani,

“Yayata Sannu ko!”

“Sannu ina kwanan ku?”

“Lapia Alhamdulillah. Anan gidan kike?”

Ya fada yana mai nuna kofar gidan mu. Na juya na kalli cikin gidan mu ina daga kai. Gaba d’aya gabana faduwa yake. Ofisan ya shafa rantal din kansa yana cusa hannu a aljihu,

“Ilyasu yana ciki...?”

“Gaskia bansani ba ofisa.”

Murmushi yai ya juya ya kalli sauran yan uwan sa yana daga musu kai. Kutsa kai kawai sukai cikin gidan mu. Binsu nayi a baya ina dafe da kirji na. Gabana sai barazanar faduwa yake. Suna shiga suka zagaye tsakar gidan mu. Sunci magani, D'aya daga cikin su yana busa sigari ya dora kafar sa d'aya akan rijiya,

"Ina Ilyasu????"

Wani daga cikin su ya tambaya da karfi. Yan gidan mu sukai cirko cirko suna raba idanuwa. Ashe Kawu ila na cikin daki ya dora bokitin sa akan sa. Sai rawar tsoro jikin sa yake.

"Zaku fadi inda yake ko sai mun tattare ku duka munyi gaba daku?"

Bintalo ta gwalalo idanu tana watsa hannu baya,

"Sittin ta ubangiji yana daka ya b'uya. Yana jiyo ku. Ga d'akin sa nan."

Ta karasa fada tana nuna dakin. Suka kutsa kai ciki sai gasu da Kawu ila dumu-dumu a hannun su sun mai ri'ko. Sai neman k'wacewa yake yana kumfar baki,

"Ku sake ni. Me nai muku?"

Talla masa mari d'aya daga cikin su yai a k'eya. Na rintse idanu ina tausaya masa ko meya musu oho? Yayan mu da shigowar sa kenan ya tsaya yana kallon su,

"Ah ofisa ya haka?"

“He’s under arrest. Mun kama shi da lefin cinye hakkin wani mutumi. Yaki biyan sa, Ko dai a ya biya kudaden ko kuma ya zauna agidan yari.”

“Har nawa ne ofisa?”

Ofisan ya sosa hancin sa yana kallon Kawu ila,

“Toh akwai dai fili na gidan gona da kuma wasu kudade wanda adadin su babban mu ne yasani.”

Kowa ya shiga raba idanu yana jinjina kai, Kawu ila ya bi kowannen mu da kallo yana mamakin kin bayansa da akabi.

“Ishaq, Khamis da Dawood ba zaku sa baki ba?”

Zagayewa su kai suka fice suna sunne kai, Kawu ila ya dafe kansa yana girgiza shi. Haka aka fice dashi cikin kaskanci abun tausayi. Jiki a sanyaye na fara tafiya titi. Na samu dan mashin ya kaini na hau motar makaranta. Gaba d’aya raina duk babu dadi. Komai Lalacewar naka naka ne. Hannunka baya rubewa ka yanke ka yar. Haka na shiga cikin makaranta a sanyaye. Har an fara exams din suna cikin hall.

1k SEATERS AUDITORIUM

Tunda suka shiga hall din Mubeen ke kallon k’ofa yana saka ran hangota shiru. Sam ya kasa samun nutsuwa ko rubutu d’aya bai ba. Fatan sa dai Allah yasa lapia. Sanarwar shigowar ta aka fad’a musu. Sannan ya sauke gwauron numfashi yana lumshe idanu jin yadda zazzakar muryar ta ke karakaina a kunnen sa. Inda take basu hakuri hade da gyara wasu questions din da aka bugo ba dai-dai ba. Tana gamawa ta sarke hannu tana bin kowannen su da kallo, Kowanne fuskar sa dauke da farin ciki yake amsa jarabawar duba da yanayin tambayoyin data basu masu sauk’i.

Ina bin takardun kowannen su amman zahiri gangar jiki na ce anan ruhi na nacan yana tunanin yadda take kwashewa da Kawu ila. Haka na k’arasa gaban Mubeen da abun mamaki da takaici sai alokacin ya fara rubutu yana sakarmin murmushi. Na dube shi na dubi answer sheet din nasa da agogo na. Girgiza kai nayi na wuce gaban wani student din. A takaice kusan atare suka gama rubutawa da sauran yan ajin. Na tattare takardun nai office dina. Ina shiga ciki Muhd Mubeen ya biyo ni,

“Ma.. Barka da rana.”

“Yauwa sannun Mu.”

“Ya..Ya akai bakizo da wuri ba?”

“Something came up.”

“Ayyah!!!! Today’s exam was..Amazing”

Har zan tambaye shi abinda yasa ya Fara rubutu a late sai kuma nai shiru ina k’ok’arin bud’e robar wainar fulawar da nazo da ita. Cikina sai zafi yakemin. Ina jin yunwa.

“Bismillah!”

Nace dashi ina bu’de ledar yaji. Lek’a wainar yayi yana yamutsa fuska.

“Ya sunan shi?”

“Bakasan wainar fulawa ba? Y’ar kalallaba ba?”

Girgiza min kai yayi yana taune lips,

“Nasan dai danwake kawai.”

Murmushi nai kawai, Saboda yanayin sa kad’ai zai nuna bai san taba,

“Wane yare ne kai?”

“Hausa Fulani da Amharic.”

“Amharic? Ethiopia ko?”

“Yes Ma! Mamana ce Ethiopian. Baba na kuma Hausa fulani ne.”

“Woah! Masha Allah.”

“Ma kinyi kyau yau.”

“Nagode! Tashi kaje karatun exams”

Kamar da bango nake haka ya kara karkacewa a kujera yana kallo na. Na kauda kai ina sake jefa lomar waina a baka.

“Ma kinyi kyau...”

“Tashi ka fita, Naga alamun ka fara renani.”

“Haba a’a! Kawai hijab d’inne ya miki kyau. Kinyi kyau ma.”

Bude baki nayi ina kallon sa. Kayan haushi Na fada a zuciata ina kurbar ruwa. Sallamar Haysam na jiyo a bakin kofa,

“Shigo ciki..”

Shigowa yayi. Sukai idanu hud’u da Mubeen . Mubeen ya watsa masa wani kallo domin bai mance fuskar sa ba. Haysam kuwa jan kujera yai ya zauna yana kallo na,

“Mine...! You luk stunning.”

Dan tari nayi alamun da mutum awajen. Sai asannan Haysam ya mika masa Hannu. Dakyar Mubeen ya bashi yana yamutsa fuska,

“Do excuse us Muhd.. Allah ya bada sa’an exams.”

Dak’yar ya mike yana min wani kallo dana kasa fahimtar ma’anar sa. Har ya kai bakin kofa ya kalle ni ciki ciki yace,

“Zan dawo anjima. Take care”

D’aga kai kawai nayi. Na juya wajen Haysam. Mubeen kuwa ya jima awaje yana sakin tsaki. Ni kuwa bayan nagama y’an abubuwan da zanyi Lokacin sun shiga wata exams din har sun kusa fitowa yasa nabi Haysam na koma gidah sabodah hankali na yak’i kwanciya da yadda aka sungumi kawu ila aka tafi dashi.

Muna tafe akan hanya Haysam na zuba min kalamai. Ni wallahi har na gaji.

“Mine sau da yawan lokaci idanuwana sukan yi kishi da zuciyata!!! Kin kuwa san mene ne dalili? Saboda a koda yaushe kece abu mafi kusanci da zuciyartawa su kuma idanuwa kin kasance mai yin nesa da su. Ina son ki sosai da zuciya d’aya. Ke kamar hasken wata ki ke mai hasken da ke haske idaniya, haka kuma kalamanki tamkar siga suke ma’abocin za’ki, tabbas kin yi kama da kanki hakan ya sanya na ji ina son ki so mai tsanani, Pls ki bani dama na fara zuwa zance, Domin fara gudanar da soyayyar mu kafin mu dora data aure?”

“Na’am..”

“Nace.. “Mine sau da yawan lokaci idanuwana sukan yi kishi da zuciyata!!! Kin kuwa san mene ne dalili? Saboda a koda yaushe kece abu mafi kusanci da zuciyartawa su kuma idanuwa kin kasance mai yin nesa da su. Ina son ki sosai da zuciya d’aya. Ke kamar hasken wata ki ke mai hasken da ke haske idaniya, haka kuma kalamanki tamkar siga suke ma’abocin za’ki, tabbas kin yi kama da kanki hakan ya sanya na ji ina son ki so mai tsanani, Pls ki bani dama na fara zuwa zance, Domin fara gudanar da soyayyar mu kafin mu dora data aure?”

“Ko Yaushe.”

Buga sitiyari Haysam yai cike da murna , Sai surutai yake yana jin dad’i. Na girgiza kai kawai ina kallon titi. Natsani yarinta wallahi....

Mubeen na fitowa daga exams yai office din Batoul. Ai kuwa ya tarar ta tafi gidah. Cike da bacin rai ya shige mota yace da direban sa,

“Muje area din limancin kona d’innan.”

Gyada kai direban yai. Ai kuwa yana zuwa ya tarar dasu daga gefen layin. Haysam ya fito daga motar ya dora hannayen sa akan motar yana zance da batoul dake facing d’insa tana dashare hakora. Wani malolon bak’in ciki ne ya taru ya tsayawa mubeen a makogoro,

“Kai ni gidah..”

“Yallabai har ka...”

“Yes muje.”

Shigewa yai suka kama hanyar gidah. Ya rufe idanun sa. Yana jiyo yadda sautin zuciyar sa ya canza. Ahankali ya lumshe idanun sa yana cije lebe.

“Ya Rabbi....”

Tun bayan sauke Batoul da Haysam yayi ya takura mata da nacin karbar soyayyar sa, Kullum cikin yi mata waya da zuwa gidan su yake. Ya kanainaye ta da soyayyar sa bata da zabi sai Na hakura ta karbi soyayyar sa. Hakan kuwa akayi. Cikin satin tuni suka kulla zazzafar soyayyah mai wahalar fassara muku.

Mubeen kuwa dakon soyayyar malamar su ke dawainiya dashi. Gashi kullum Haysam yana tare da ita ko a school. Hakan yasanya shi dan ja baya da ita sai gaisuwa kawai da yake da ita. Hakan ma dan baze iya kwana ba tare da yayi tozali da fuskar ta ba. Domin da soyayyar ta yake kwana ya tashi..

Successfully suka kammala exams din first semester. Abun ba acewa komai sai godiya ga mai duka. Domin gaba ki d’aya exams din tazo musu cikin sauki da kuma annushuwa.....

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *35*

IGZ

•. •. •

NAKORE POLICE STATION

Wani basamuden murdadden mutumi ne ya shiga laftawa Kawu ila wayar inji a jikin sa. Ji kake ‘rigijib-jib, Fas,Tas. Jikin sa yayi rud’u-rud’u da shatin duka ya faffashe. Gaba d’aya ya rame ya jeme idanuwan sa tamkar na mujiya sun ‘kara shigewa ciki, Sai yawun wahala ne ke dalala daga bakin sa. Mutumin ya sake zuba masa wani dukan yana huci,

“Kaga kafaffen tsoho. Nace ina ku’dade da takardar filin Alhaji Usman suke?”

Kawu ila ya sau fitsari a zaune ji kake ‘Tsiiii. Cikin wata irin wahalalliyar murya ya dafe kansa yana sakin hawaye,

“Babu wallahi. Ai ca yai ya bani. Kuma na baka ta rabaka da kayan ka...”

Wani dukan ya sake zuba masa yana zare idanu,

“Aiyi kukai abisa alqawari. Kuma baka cika masa alqawarin sa ba ka sab’a. Wato daka fito dasu ka gwammace zaman nan ana narkarka ko?”

‘Jib, Rigijib, Ragas, Tas, Was.’

Wannan sune sautukan na jakin da ake lakadawa Kawu ila.

“Wayyo! Wayyo! Babu na auno abinci dasu.”

“Ya maganar filin.”

“Babu...”

“Amsar dai kenan?”

Haka yaita dukan Kawu ila yana tambayar sa. Amma Kawu ila sai wallacewa yake yana kwararo rantsuwar babu su ya auno abinci. Cikin kuka yaja majina yana sosa bayan sa,

“Allah ya saka min..”

“Kace me?”

“Ca.. Ca nai Allah ya saka maka da alkhairi.”

Tsaki ofisan yaja ya fice. Kawu ila ya gyara zaman sa dakyar. Gaba d’aya yayi jina jina da jini. Ya muskuta yana kukan radadi,

“Billahil lazi sai nayiwa ahalin gidan mata tara rashin mutinci. Ni za’a yiwa kaskanci? Babu wanda ya fito dani?”

Ya sake kwafa yana sakin wani fitsarin a zaune. ‘Kulululu’ Cikin sa ya shiga kukan yunwa yana neman agajin abinci.

GIDAN MATA TARA

Gaba d’aya na sake yin fresh, Jiki na ya murmure. Zaune nake akan taburmar dakin mu ina yanka salatip (seal-tape) din da zanyi lalle dashi. A hankali nake bin wakar dana sanya a waya ta,

‘Ka iya tsaro labari wanda yake sa annuri idan da cuta kai ne magani. Zuciya garwashi ruri dan kuwa tayo tasiri soyayyah ta tuna dani.. Ina ta guje guje. Na rasa shin ina zanaje? Kira ni kacemin inzo muje soyayyah tayiwa zuciya ah’ah’ah...’

Ni kadai ce a dakin babu kowa. Domin Innar mu da autar mu da Yayan mu sun tafi wajen Gwaggo Aminatu. Don kai mata xiyara da kuma shaida mata halin da Kawu ila yake ciki, Domin kaf yan gidan mu an rasa wanda zai gaya mata. Sai yanzu nake mamakin anya ma suna son Kawu ilan kuwa? Domin sunfi damawa dashi Lokacin da yake cikin halin samu. Yanzu kuwa da halin rashi ya riskeshi sai suka guje shi. Lalle duniya budurwar wawa ce. Mu din da bayaso mune ke neman hanyar da zamu fito dashi.

Ina gama yayyankawa na ajiye plate din a gefe domin so nake nayi cikin dare na kwana dashi. Kakkabe rigata nayi na tattare wajen dana ‘bata. Har na dakko takardun students xan cigaba da marking sai wayata ta yi kara alamun sak’o ya shigo. Duaka nayi ina murmushi ganin Haysam ne. Shi dai sam baya gajiya da kira da turo sakonni.

“Assalamu Alaiki Ya Habibaty! Mine! SO tamkar rayuwane, ba ko yaushe yake zamowa abu mai sauki ba haka kuma ba a koda yaushe yake wanzar da farin ciki ba, to amma mene ne zai sa matsawar muna raye da rai da lafiya za mu yanke alakar soyayya a tsakanin mu? Har zuwa yau babu kamar ki a cikin zuciyata domin kuwa jin muryar ki a kullum na rubanya adadin soyayyar da na ke yi miki a cikin ko wane dare ko safiya. karda ki rabu da ni dan Allah, domin hakan zai iya sanyawa na zamo mutum mai rauni a rayuwata...”

Murmushi nai kawai bayan na kammala karantawa, Ajiye wayar nai na sabi kayan undies dina da zan wanke. K’asa na sauka ina kallon sauran yan gidan mu dake hidindimin su kamar ko yaushe. Zancen sungumar Kawu ila da akayi kuwa babu shi.

Domin babu wanda ya nuna alamun damuwa acikin su. Ruwa na debo a rijiya na fara wanke su ina dauraye wa. Bintalo ta sakko da sauri tana saka hijabi,

“Yauwa yama sunan dan shafaffen abunnan mai kamar marar kwashe tuwo da yake da ‘bula a tsakiyar sa?”

Na duddubi gabas da yamma ganin ko da wani take? Ashe dani take. Mikewa nai daga durkushen da nake ina wanki. Na d’aga kai na sama alamun tunano ko me take nufi. Dan wallahi na manta menene abu mai kamar marar kwashe tuwo mai bula a tsakiyar sa. Na girgiza kai ina kallon ta,

“Bangane ba Baba..”

“Abun nan da naga kina sayowa naci dinnan. Na shagon Nata’ala. Murmushi nayi tunowa da ko menene,

“Yadda kika fasalta ne kamar wani abun daban..”

“Yasunan sa. Fad’amin da sauri ci zanyi na kora da abu mai sanyi.”

“Doughnut sunan sa..”

Bintalo ta shiga xare idanu tana sake muskutowa kusa dani. Hannun ta na dama tana aikin sosa takashi. Kasa kasa tace dani,

“Maimata min du.. me?”

“dow-nuht ake cewa..”

Na karasa fada ina gaya mata yadda zata ce. Bintalo ta watsa hannu baya tana gasamin harara daga abun arziki,

“Fadamin sunan sa da hausa”

“Bansani ba gaskia..”

Tsaki taja tana sakin gud’a. Ta watsa hannu baya tana shewa,

“A hayye yauga gaye ba makilis. Wato saboda zan siya naci shine zakimin bakin ciki ko? Wani bakisan sunan sa da hausa ba. Toh baturen ma na hadasu na zage tas. A hayye nanaye! Sittin ta ubangiji ci ya zamto dole. Mtscew.”

Ta karasa tana sakin tsaki hade da kademin zani a fuska. Nayi murmushi kawai na juya na cigaba da wanki na. Bata jimaba kuwa ta dawo hannun ta d’auke da leda shak’e dashi. Neman magana ta fara yi. Ta bararraje a matattakar bene tana ci tana jifan maganganu,

““Allah sarki dad’i. Allah gwanin hikima inji barawon zuma. Jakar ubancan kai! Sittin ta ubangiji wanga abu akwai da’di, Ga laushi ga dadi. A hayye! Yau ga gaye ba makilis. Sittin ta ubangiji duk mai bakin ciki sai dai ya mutu..”

Nayi murmushi ina karkade shanyar kaya na. Yayan gidan mu suka zuba mata na mujiya suna jiran ta babbasu. Amma haka ta takarkare ta cinye tana nishi. Wasu daga ciki suka sa kuka ta bisu da rankwashi a kwanyar kai. Dakin shanyar mu na shiga wato dakin da aka tashi Rabi’atu matar kawun mu. Na shanya kayan nawa na haye sama. Ina hankalce da Bintalo dake rike da ciki tana ziyarar band’aki cikin ta sai kara yake,

‘Kulululu...Tutututuwiyyy.... Ta sau iska tana baje hanci. Yaran suka hau dariya suna tsalle,

“Bintalo ta sau tusa.. Bintalo ta sau tusa..”

Ta kofar ban’daki Bintalo ta zuro kai tana karkada musu hannaye,

“Sittin ta ubangiji zan raunata na jijjiga yaro. Shegu da runtuma runtuman kai. Tusa ce uban kowa yana yi. Bara na fito na same ku..”

Ai kuwa suka fice suna cigaba da fadar tayi tusa. Baba usaiba ta kece da dariya tana buga zani,

“Waiii. Gumaama, Kutsin ubancan kayya kai. Sai kashe shekararren mushe. Maganin marowaci kenan. Idan baki basu ba kya bawa bandaki ai. A hayye kayya kai..”

Nayi daria kawai na koma d’aki. Kullum ne ya zama jazaman Bintalo da Usaiba su haurawa. Ina jiyo karakainan su a kasa suna tayi. Ni kuwa marking exams din dalibai na na cigaba da yi hankali kwance..

Da misalin karfe hudu da yamma su Gwaggo Aminatu da Innar mu suka dira a police station wajen Kawu ila. Gwaggo Aminatu tayi kukan ganin Kawu ilan cikin mawuyacin hali. Bata bata lokaci ba kuwa ta nemi a kira mutumin da ya shigar da karar. Mintina kalilan Alh Usman Usman ya garzayo caji ofis din. Bayn sun gaysa ne Gwaggo Aminatu ta nemi sanin kanun labarin. Inda Alh Usman ya sheda mata tundaga farko zuwa karshe ya kar’kare da,

“Amshi nan Gwaggo diba, Wallahi alkawari mukai dashi ya sab’a. Ya za’ai ace cikin yan kwanaki kalilan ya cinye makuden kudaden ya kuma sayar da gidan gonar? “

Gwaggo Aminatu ta girgiza kai tana kallon Kawu ila cike da takaici,

“Kayi hak’uri Alhaji.. Dan Allah”

“Amshi nan Hajia, Diba. Wallahi sai ya biyani tunda bashi da amana ba kuma shi da mutinci.”

Gwaggo Aminatu taja ajiyar xuciya ta sauke tana zabga tagumi,

“Toh ka kara bamu lokaci dan Allah! Zamu san yadda zamuyi da sauran yan uwan sa mu samu mu biya ka. Kada ka kai karar kotu na roke ka Alhaji..”

“Amshi nan Hajia. Diba. Idan ba za’a dau lokaci ba babu damuwa zan jira, Amman da sharadin sai dai ya cigaba da zaman sa anan har sai anbiya ni hakk’i na duka..”

“Allah ya bamu ikon biyan ka Alhaji. Mun...”

“Haba Yaya na cigaba da zama anan fa kikace? Meyakwan ku fitar dani kwa biya daga baya.”

Cewar Kawu ila hade da hararar Innar mu. Gwaggo Aminatu tayi murmushin yake tana sallama da Alhaji. Yana fita ta hau Kawu ila da fada ta inda take shiga batanan take fita ba.

“‘Yayan dan uwan ka. Kake watangariri da rayuwar su tin bayan ran mahaifin su? Tir da hali irin naka Ilyasu. Ace wai rayuwar batoul kake siyarwa kana cinikin auren ta kamar kayan sawa? Kasan hakkin zumunci kuwa? Tsaya kaji...

“FALALAR SADA ZUMUNCI DA ILLAR YANKESHI,

عَنْ أَبِي أَيُّوبَ الْأَنْصَارِيِّ، أَنَّ أعرابيا عرض لِلنَّبِيِّ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ فِي مَسِيرِهِ، فَقَالَ : أَخْبِرْنِي مَا يُقَرِّبُنِي مِنَ الْجَنَّةِ، وَيُبَاعِدُنِي مِنَ النَّارِ؟ قَالَ : " تَعْبُدُ اللَّهَ وَلَا تُشْرِكْ بِهِ شَيْئًا، وَتُقِيمُ الصَّلَاةَ، وتؤتي الزكاة، وتصل الرحم ." آداب المفرد

Ankarbo daga Abu Ayyubal ansary (R.A) wani mutumin kauye ya bijirowa manzon Allah (S.A.W) acikin tafiyarsa sai yace: Kabani labarin abunda zai kusantar dani Aljannah kuma ya nesantar dani daga Wuta ? sai Manzon Allah (S.A.W) yace: "Kabautawa Allah kar kahada shi da komai , kuma katsaida Sallah , kabada Zakkah , kuma kasadar da Zumunci "

عَنْ أَنَسِ بْنِ مَالِكٍ؛ أَنَّ رَسُولَ اللَّهِ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ قَالَ " : مَنْ أَحَبَّ أَنْ يُبْسَطَ لَهُ فِي رِزْقِهِ، وَأَنْ يُنْسَأَ لَهُ فِي أَثَرِهِ ، فَلْيَصِلْ رحمه ".

Daga Anas dan Malik Manzon Allah (S.A.W) yace: "Duk wanda yakeso a yalwata masa Arziqinsa , kuma a jinkirta masa ajalinsa to yasadar da Zumunci.

عَنْ عَبْدِ الرَّحْمَنِ بْنِ عَوْفٍ؛ أَنَّهُ سَمِعَ رَسُولَ اللَّهِ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ يَقُولُ : " قَالَ اللَّهُ عَزَّ وَجَلَّ : أَنَا الرَّحْمَنُ، وَأَنَا خَلَقْتُ الرَّحِمَ، وَاشْتَقَقْتُ لَهَا مِنَ اسْمِي، فَمَنْ وَصَلَهَا وَصَلْتُهُ، ومن قطعها بتّتّه ".

Daga Abdurrahman dan Auf, yaji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: Allah mai girma da buwaya yace : " Nine mai Rahama , kuma ni na halicci Zumunci , kuma na ciroshi daga suna na, duk wanda yasadar da shi zan sadar dashi (zuwa ga Rahamata) wanda kuma yayankeshi zan yanke shi (daga Rahamata) ".

Sadar da zuminci,shine ziyarar yan uwa da dangi da abokai na alkhairi da taimakonsu da agaza masu”.

Annabi s.a.w ya bayyana mana sadar da zuminci hanyace ta samun arziki da rayuwa mai dadi anan duniya da Lahira.

Sai yace:

(مَنْ سَرَّهُ أَنْ يُبْسَطَ عَلَيْهِ رِزْقُهُ، أَوْ يُنْسَأَ فِي أَثَرِهِ ، فَلْيَصِلْ رَحِمَهُ)

Duk wanda yake son Allah ya yalwata arzikinsa kuma ya tsawaita rayuwar sa, to ya sadar da zumincinsa).

@1693 (وأبو داود ،ومسلم) 2557 (،ومسلم) 2067 (البخاري)

Awani Hadisin yana cewa:

(الرَّحِمُ مُعَلَّقَةٌ بِالْعَرْشِ تَقُولُ مَنْ وَصَلَنِي وَصَلَهُ اللَّهُ وَمَنْ قَطَعَنِي قَطَعَهُ اللَّه)

(Zuminci yana rakaye ajikin al’arshi yana cewa ya Allah ka sadar da wanda ya sadar dani ka yanke wanda ya yanke ni).

@(مسلم) 5989 (البخاري)

ILLA DA HATSARIN YANKE ZUMUNCI

عن جبير بن مطعم؛ أَنَّهُ سَمِعَ رَسُولَ اللَّهِ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ يَقُولُ " : لَا يدخل الجنة قاطع رحم ".

Daga Jubairu dan Mud'im, yaji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: " Mai yanke Zumunci bazai shiga Aljannah ba".

عَنْ أَبِي بَكْرَةَ قَالَ : قَالَ رَسُولَ اللَّهِ صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ " :

مَا مِنْ ذَنْبٍ أَحْر.

“Ilyasu shin ba mummunan abu kake aikatawa ba? Marayu ne fa ‘yayan dan uwanka na jini? Subhan’Allah!”

Kawu ila ya yamutsa fuska yana sosa kunne alamun maganganun ta sun shiga sun fita. Gwaggo Aminatu tayi murmushi tana kallon Innar mu,

“Kaltume mu tafi ko? Zan taho yanzu.”

Kad’a kai Innar mu tayi ta fita dama tuni Yayan mu ya futo shi. Gwaggo Aminatu ta muskuta kusa dashi tana karkada hannuwa,

“Ka cigaba da abinda kake yi Ilyasu, Ai gashi nan kana girbar su ahankali. Su wanda kake uzzurawan rayuwar su na gyaruwa kai taka na shiga cikin matsatsi. Yanzu wa gari ya waya?”

Kawu ila ya shiga kunkuni tamkar karamin yaro. Gwaggo Aminatu ta mike tana gyara mayafi,

“Kasan da sanin munsan kudaden daka cinye na marayu..”

“Kudin su wa?”

“Kudaden da marigayi salisu ke bibbinka ai hakkin yayan sa da matan sa ne yanzu. Nabi diddigi ance baka bayar ba. Na tsaya na auna hankalin ka ko zakayi tunani ka basu abinsu kaki. Kai baka tunanin meyasa masifu ke addabar ka? Komai naka ya kare? Shagunan ka sun kone, Iyalanka ma wasu sun guje ka? Kar kayi *ZATON* kaci bulus,Domin duk wanda yaci dukiyar marayu ka sani Allah yace,

“Lalle dukkanin wadanda suke cin dukiyoyin marayu da zalunci, abin sani kawai suna cin wutane a cikinsu, kuma da sannu za'a kona su a wuta wacce ake rurata''Suratun Nisa'I, aya ta:10. “

Tana gama fa’da masa tayi fucewar ta fuuu cike da takaicin bakin hali da tsantsar mugun ta ta dan uwan nata da yake watangariri da rayuwar ‘yayan yan uwan sa na jini....

••

Assalamu Alaikum dearies😈 Nagode kwarai da addu’oin ku gare ni. Alhamdulillah jikina da sauki. Kunsan makarfafa a jikin mutum. Banida lapia sai kuma nazo na fadi na bugu sosai na dan zauna a asibiti. wallahi har ta kaiga nasa neck collar Alhamdulillah da sauki. Shiysa kwana biyu kuka jini shiru. IN SHA ALLAHU zan cigaba da typing amma kilan I will be Lil slow and off somedays saboda ina kokartawa nayi typing dinne kawai saboda haqqin ku akaina❤Nagode da kirana da kuka yiyyi, Messages da kuma addu’oi na comments groups. Allah ya saka da alkhairi yabar zumunci. ya kuma bamu lapia mai dorewa❤❤ Masu ganin laipi na kuyi hakuri bada niyya bane kunsan lapia uwar jiki ce. Thank you all. Jazakum Allah bil jannah❤❤

••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *36*

NANA HAFSAT

• • •

Wajajen biyar na yamma su Innar mu suka dawo da gwaggo Aminatu. Dama tuni Yayan mu ya kira ni awaya ya sheda min suna nan tafe. Don haka da sauri na dora spaghetti datasha kayan lambu da bushasshen kifi. Na kuma karb'o zobon matar soja sanyayye.

Sosai Gwaggo Aminatu da su Innar mu sun narki taliyar nan. Gwaggo sai yaba dadin da tayi take yi. Murmushi kawai nayi na cigaba da marking booklets din exams na students dina. Ba laifi naci rabin marking din na dakata domin yana bukatar hutu da kuma kulawa. Acikin wa'enda na maka wasun su sun cinye, Wasu sun fad'i wasu ba lefi. Shigar da wanda na maka nayi na na janyo 40Rabbana ina karanta addu'oin da suka zamto min lazim sai nayi.

Gwaggo kuwa suna ta hirar su da Innar mu kafin ta mike ta shisshiga sauran dakunan. Dakin Bintalo ta shiga ina jiyo ta suna maganar kudin adashin da take ajiyewa, Domin yau kusan mutane goma ne suka kawo nasu. Ruma ma ta kawo wasu cikin leda.

"Bintalo babu matsala haka? Ba zaku kai banki ba?l

Cewar Gwaggo Aminatu, Ta karasa fada tana rafka tagumi ganin himilin kudin dake gaban Bintalo tana cusashi a asusu. Domin yanzu asusun harda mai mukulli ta karo. Bintalo tai shewa tana sosa hanci,

“da ido d’aya nake bacci saboda masu dan hali..”

Gwaggo Aminatu ta tari Bintalo tana murmushi,

“Ba abinda nake nufi ba kenan. Ina nufin ku dinga ajiyewa a banki mana kamar zai fi sauki..”

“A hayye! Tabdijan. Ai Yaya sittin ta ubangiji zaman sa awaje na shine zaman lapiar sa kuma ‘karuwa tace. Domin idan aka kammala inada nawa kason mai tsoka...”

Gwaggo Aminatu ta jinjina kai tana gyara zaman mayafin ta hade da yin hanyar fita daga dakin,

“Eh zahiri! Toh Allah ya bada sa’a. Ni zan tafi idan muka gama magana dasu Dawood.”

“Toh Yaya. Agayda yaran..”

“Zasuji..”

Dakin Kawu khamis ta shiga. Nan sauran kawunin mu suka shisshiga suma. Mai suka tattauna akai oho? Bayan wani lokaci kuma na jiyo sallamar Gwaggo Aminatu zata tafi. Kasan na sauka na rakata har wajen motar ta. Sallama na mata direban ta yajata su ka koma kaduna...

Bayan sallar isha’i na dakko sauran booklets din da banyi marking ba na shiga duddubawa ina maka su. Akwai wuta ga fanka nata bamu iska. Autar mu tuni tayi bacci. Innar mu kuma tana kishingid’e tana lazimi. A hankali nazo kan wata takarda. Da farko shafin ta an fara introductory part aka soke. Daga kasan kuma yare ne kawai aka rubuta shima kad’an. Gaba d’aya sauran shafukan ba abunda aka rubuta. Na ware idanu ina cigaba da dudduba ta. Lamarin ba ka’dan ba ya dagamin hankali. Ganin koma waye dole yana d’aukar dayan course din nawa. Hakan yasanya na dakko booklets din dayan course din nawa na zakulo booklet din. Abin mamaki itama hakan akai. Har gwara ta farkon ma gaba d’aya wannan ko paragraph d’aya ba’a rubuta ba sai wasu watsattsulallun kalamai na wani yaren.

Hankali na yai mutukar tashi ganin koma wanene babu yadda za’ai na iya temakon sa na wutar dashi. Gaba d’aya gumi sai ya shiga kwaranyo min. Domin harga Allah banason bada carryover. Nafiso kowa ya wuce. Ganin daga wannan semester na rabu dasu. Son samu ne kowa ya wuce ba matsala. Domin ni da su munyi hannun riga inde a lecturing ne. Kawai dai ni ce level coordinator dinsu ta’iya level one din.

Jiki na na rawa na xakulo wani littafi mai dauke da sunayen yan ajin baki d’aya. A hankali na shiga duba sunayen ta reg number da ke kan booklet din. ‘MUhammad Mubeen Salees’ shine sunan dake rubuce baro baro. Na rufe baki na da tafin hannu na gano ko waye. Shi kuwa meyasa yai haka? Dama kenan bai iya written abu ba sai oral ko kuwa dai bashida man kai ne?

“Innalillahi wa inna ilaihir raji’un..”

Na shiga maimatawa gumi na kwaranyo min ga fanka na bada iska. Amma tsabar tsantsar tashin hankakij da nake ciki bana ji,

“Mubeen, Why?”

“Kika ce me?”

Innar mu ta fada tana rage sautin rediyon ta. Na girgiza kai ina harhada takardun waje daya. Gaba d’aya bani da lakar cigaba da maka takardun a lokacin..

“Babu komai Innar mu..”

Raina ba dadi haka na kwanta a katifar mu bayan nayi addu’a. Daren ranar dai baccin mintina nayi.

•X••O••X••O••

A yau ne ta kama za'a gudanar da zabubbukan gwamnoni da senators din jahohin dake duk fad'in Nigeria, gabaki d'aya iyalan Amb Salees sun hallara a polling unit d'in su. Amb Salees shine a farkon layin sannan matarsa hajja Ahlaam sannan Muhammad Mubeen wanda ke ta faman yatsina fuska kai da ka gani kasan ba'a son ransa ya fito gurin ba, kawai dan an tilasta masa ne. Gabaki d'aya mutanan wajan ihu suke suna murna ana cewa sai Amb Salees Kaduna tashi ce sai sun canza, bakin Amb a washe yana ta fara'a har yaje ya dangwala jam'iyarsa sannan matarsa ma ta dangwala sai Mubeen sannan aka bar mutanan gari suma suka cigaba da dangwalawa. Daga nan gurin gida aka maida hajja Ahlaam da Mubeen, shi kuma Amb Salees ya shiga cikin mutane akaci gaba da janyo ra'ayoyin jama'a har aka kammala aka kirga, Alhamdulillah sune da nasara domin mutane suna son shi sosai.

Tunda suka koma gida mutane ke shiga da fita a wajan hajja Ahlaam wacce keta rarraba musu kudade da sabulai da omo da dai sauran su. Mubeen ya fito cikin shirinsa na son zuwa unguwar su Batoul saboda ya dade bai ganta ba tun da suka gama jarabawa koya koma makarantar baya tarar da ita. Mukullin mota ya d'akko kai tsaye ya nufi inda ake ajiyewa ya bud'e zai shiga yaji an rike kofar motar. A hankali cikin mamaki ya kalli wanda keyi masa hakan yaga wani soja ransa a b'ace tamkar Mubeen din yayi masa laifi, murya a kaushe yace dashi.

“Daga yau babu wanda zai kuma fita daga gidan nan har sai bayan an fad'i sakamakon zab'e.”

Baki bud'e Mubeen yabi sojan da kallo, shi sam be ma san da zaman su ba sai yanzu ya hangesu barbaje a harabar gidan. Wani gududun haushi ne ya tukare masa a wuya kawai ya juya yabar gurin cike da haushin siyasar gabaki d'ayan ta.

Dan ba dan mahaifinsa ya tsaya wannan takarar ba da tuni yana nan yana fita duk inda yaga damar zuwa.

•X••O••X••O••

Cikin hukuncin Allah washe gari da yamma wajan karfe biyar aka yi announcing cewar Amb Salees yaci zab'en governor d'in jihar kaduna. Murna a wajan zuri'ar nan da magoya bayansa ba'a cewa komai. Gidan yayi dank'am da al'umma maza da mata yara da manya anata celebration. Hajja Ahlaam bakinta har kunne dan ko Amb Salees d'in ba zai nuna mata jin dad'in wannan lamarin ba. A dai-dai lokacin ne kuma Mubeen ya samu damar ficewa daga gidan ba tare da sojojin da aka barbaza a gidan sun lura ba. Duk inda ya tsoma kafa mutane ne majalisa majalisa suna ta murna ya sanya face mask ya dora bakin glasses a idanunsa hakan yasa ba'a gane shi gashi yasa hula, ya tari napep yace ya kai shi unguwar limancin kona.

Mai napep d'in har yaki d'aukar sa saboda unguwar da nisa gashi shi kuma rally zasu tafi da sauran abokansa masu sana'ar, ganin irin uban kudin da Mubeen ya bashi ne yasa shi cewa to zaije koma ina ne indai mai hawan zai jurewa iskar da zasu kwasa a hanya. Dubu biyar ya bashi suka d'auki titi, gabaki d'aya hankalin Mubeen yana kan malamarsa da ya jima bai sanya a cikin kwayar idanunsa ba. Suna zuwa unguwar su Batoul nan din ma a cike take da mutane anata maganar zab'en, wasu na murna wasu suna zage-zage. Shi dai Mubeen babu abinda ya damesa irin yaga malama Batoul. Yana ta neman wanda zai tura da kuma yadda zai furta wajan kiranta sai ga Autar su tazo zata shiga cikin gidan, yayi saurin tare ta yana kare mata kallo.

“Baby ciki zaki shiga?”

Ta kallesa itama sannan ta d'aga masa kai ba tare da tayi magana ba.

“Tom kice ana sallama da Malama Batoul.”

Kuma binsa da kallo Auta tayi, sai kuma ta shiga gidan ba tare da ta bashi amsar zata kira ko ba zata kira ba. Tana shiga ta sameni a kwance ina chatting a wayata, sai da ta zauna kusa dani ta janyo hannun damana sannan tace.

“Yayyah!”

“Na'am.”

Na amsa ina k'ok'arin kwace hannuna da ta rik'o amman yarinyar nan taki saki na.

“Ana kiranki a k'ofar gida.”

“Kirana kuma?”

Na tambaya cike da mamaki.

“Waye kuma a cikin irin wannan lokacin?”

“Ban sanshi ba Yayyah, amman dai dogo ne ya rufe bakinsa da takunkumi.”

D'an karamin tsaki naja sannan na mik'e zaune tare da zare hannuna daga nata. Innar mu na k'asa tana alwala kasan cewar wacce take jikinta ta warware shine take sakewa. Hijabi na na d'auka nasa tare da d'aukar sosan shafa powder na d'an goge fuskata dashi sannan na sakko k'asa inda na tsaya ina sanar da Innar mu ana kirana a k'ofar gida. Amsa min tayi da kai hakan yasa na fita ba tare da na sake cewa komai ba. Abin yayi matuk'ar bani mamaki ganin Mubeen a tsaye ya zare glasses d'in yasa a gaban aljihunsa, face mask d'in ma ya sanya a aljihu yana facing k'ofar gidan da alama baya son mutane su gane shi.

“Mubeen..!”

“Mah.”

Ya amsa yana mai karasowa cikin zauren gidan mu. Daman ina son ganinsa kuwa domin nayi masa wasu tambayoyi game da exam din sa.

“Ya akai kazo gidan nan wani abun ne?”

“No Mah, zuwa nayi kawai mu gaisa.”

“Okay na gode, but Mubeen ya akai haka? Ya akai naga duk test's d'in da nayi muku kaine me highest scores a ajinku. Sannan ko questions nayi kafi kowa bani amsa, but exams kayi failing baka rubuta komai ba sai wani irin language why Mubeen?”

Wani irin azababben dad'i yake ji idan har yaji ta kirashi da Mubeen. Lumshe idanunsa yayi tsawan mintuna ya bud'e su akan fuskata wacce nima kallonsa nake yi ina mamakin yadda naga yana dafe kirjinsa.

“Mah banyi k'ok'ari ba ne?”

“K'ok'ari kuma? Bama kayi exam din ba domin baka rubuta min abinda na tambaye ku ba.”

“Sorry ma'am

“Sorry for your self Mubeen, domin babu ta yadda za'a yi na taimaka maka. Dole kaga sai ka kuma maimaita courses d'in.”

K'asa yayi da kanshi yana jin wani irin farin ciki, yana sane yaki bari yayi passing exams din na saboda baya kaunar duk wani abinda zai sanya nisantaka a tsakaninmu. Kafin yayi magana muka jiyo hayani a cikin gidan, Zabbau da Alawiyya suna fad'a, tun suna yi a cikin d'aki har sai da suka fito tsakar gida. Had'a ido muka yi da Mubeen na dankara masa harara kafin na yatsina fuska dan bana son ayi abinda zai rage min kima a gaban duk wani mai ganin darajata nace dashi.

“Shikenan kaje na gode da ziyara.”

“Wallahi sai kin biya ni fate ne dan abu takazar ki. Kin san da k'ak'a naje na samo shi da zaki zo kisa sharb'eb'iyar kafarki ki kifar min?”

Haushi kunya takaici bakin ciki duk suka taru sukai min yawa a cikin zuciya ta. Na juya zan koma ciki na ji ya kira ni.

“Mah.”

Kamar karna juya domin a kunyace nake saboda harga Allah banji dad'in yadda yaron yaji ana fad'a a gidan mu ba. Kura min ido ya yi yana cewa.

“Ki bani numbern wayanki please Mah karki hanani dan Allah.”

Ya zanyi dashi? Ya riga ya had'a ni da Allah hakan yasa na karanto masa ya juye su a cikin wata 'yar karamar waya sannan na shige gida dan gabaki d'aya kunyar kai na nake ji akan hayaniyar da Mubeen yaji ana yi kuma akan faten tsaki da Alawiyya ta samo a yawan ta. Kota kansu banbi ba haka na haye sama takaicinsu na damuna.

GIDAN ALH KABEER MAI WAFA

Zaune Haj Husnah da Alh Kabeer mai wafa suke suke suna karin kumallo a center carpet din dake tsakiyar parlorn. Haj Husnah ta nannada wainar kwai ta cusa a bakin ta tana kurbar ruwan tea,

“Alhaji maganar yaron nan shiru fa har yanzu..”

“Maganar wa fa?”

“Autan ka mana. Har yanzu ba aikin yi alhaji? Ga karatu fal yayo.”

“Toh ni me zance hajjaju? Yaron nan he’s very selective. Yanzu aiki ko wanne ka samu ai yi kake yi yanzu. Allah na tuba yanzu hustling kawai mutum yake like a dropout. Amman Haysam ya dakkota da zafi shi sai babban aiki saboda yayi karatu me zafi. Yace ba zeyi b’angaren bureau de change ba. Yace sai nnpc ko firs da cnn. Gaba d’aya fa harkar waka sani waya sanka ne?,

“Guraren da yake daukarwa kansa ni wallahi banida wanda na sani. Shi a komai albarkar ubangiji ake so ba son zucia ba. Nima abun kwatance ne awajen sa. Yasan matsayin da na ke a karatu amman tun ina matashi na da naga tsayawa neman aiki sai kanada hanya yasa na fara bin abokai kano. Tun muna zama muna kallon yadda yan canji ke yin kasuwancin su sannu a hankali har muka zama yaran su. Dake Allah yasa arzikin mu anan yake sai gashi kowannen mu ya zama babba. Duk mun kawo yadda muke yau, Su sauran abokan nawa da yawan su sun sanya ‘yayan su a harkar ana damawa dasu. Nima kinga ai sauran yaran sun shigo ciki amman na wajen ki ya’ki. Ya kike so nayi dashi? Allah ya bashi aikin da yake so...”

Ya karasa fada yana kafa kofin shayi a bakin sa. Hajia Husnah taja numfashi ta sauke tana sake narkar da muryarta,

“Toh Alhaji ai yanzu komai yazo karshe ko?”

“Saboda me yasa kikace haka?”

“Wai Amb Salees abokin ka da naga yaci takarar gwamna.”

Alhaji Kabeer ya dire kofin shayi yana mata wani kallo baki bude,

“Lalle hajjaju ni asuwa na zama abokin Amb? Ki rufamin asiri. Tsakanin mu dashi harkar canji kawai, Sai Y’ar kwangila idan ya bamu.”

Hajia Husnah ta yamutsa fuska tana cizan yatsa,

“Toh Alhaji Yaushe zaka kai mu gidan nasu ne? Inata damun ka tun kwanaki.”

“Haba hajjaju. Ni wallahi matar sa ma ko gaisawa sau d’aya muka tab’a yi. Lokacin na kai masa ya zabi yanayin yadda yakeson tsarin gidan nasa da ake ginawa...”

“Ance wai balarabiya ce ko?”

“Y’ar Ethiopia ce dai..”

“Alhaji kuma yaran ta nawa?”

“Nakejin kamar hudu ne fa. Amma meyasa kikemin wannan tambayoyin?”

Hajia Husnah tai murmushi tana lankwasa yatsun ta,

“Babu komai kawai dai inaso mu d’aura zumunci ne. Yaran nata manya ne kuma?”

Murmushi yai irin nasu na manya ne yana tattare burbushin kwan daya zube akan carpet,

“Hajjaju kenan. Kamar biyu ne manyan mace da namiji. Biyu kuma yara ne kanana...”

“Toh dan Allah ni dai Alhaji ka kai mu gidan nida Haysam. Ai ta haka ake sabo.”

Mik’ewa Alhaji Kabeer yai yana gyara zaman kayan sa. Yasa toothpick yana sakacen hakoran sa,

“Hajjaju mutan makka. Dai dai ruwa dai-dai tsaki dai. A tsaya daga nesa nesan dai. Wutsiyar rakumi tayi nesa da ‘kasa...”

Yana gama maganar sa ya haye sama yana girgiza kai cike da takaici. Gaba d’aya halin ta ya fara gundurar sa. Sai taita kai kanta inde Allah be kai ta ba. Sarai ya gano so take ta hada Haysam da y’ar Amb Salees bayan ko a mafarki hakan ba zata taba faruwa ba. Gaba d’aya ita da dan nata suna dorawa kansu abinda sam ba zai taba faruwa ba. Shi sai yanzu ya gano ma awajen Haysam din ya dauki halin sai abinda yakeso lalle zai samu. Yana hayewa sama taja tsaki tana zumburar baki.

“Yo ai gaskia ne. Ga inda zamu dandali arziki kana zizzillewa. Ni xan samo yadda zanyi naje gidan wallahi. Mu daura zumunci. Na zama sirikar yar gwamna...”

Tana fada tana tafa hannaye cike da farin ciki.Haysam dake lab’e tun sanda suka fara maganar gidan Amb Salees. Sai asannan ya shiga parlorn cike da takaicin halin mahaifiyar tasa. Ga wadda yakeso amman tak’i yadda sam, Wadda itace dai-dai auren sa. Ina shi ina yar dadadden ambassador wanda ya rik’e matakai da dama. Gashi yanzun kuma ya zama gwamna. Kansa a kasa ya karasa nesa da ita ya zauna,

“Ina kwana Umma?”

“Lapia lou.. Yanzu Ka tashi ne?”

Girgiza kai yayi yana yamutsa fuska. Ahankali yace,

“Duk najiyo maganganun ku. Umma dan girman Allah ki dena ma dakko zancen gidan Amb Salees. Gwamna ne fa mai ci a yanzu Umma. Bama haka ba kamar yadda Abba ya fada kwarya tabi kwarya ake fa. Ina ni ina neman auren yar sa? Ni wallahi bana son ta ma..”

Harara ta wurga masa tana bantarar goro a leda,

“Sallamammen banza da wofi, Ana ga gabas kana yamma. Shashasha, Sullutu sakarai. Ai duk dan kai nake yi, Saboda ka samu aikin yi kuma ka zama sirikin gwamna riba biyu kenan. Da xakace baka sonta ita dinma ai ba son naka take ba. Kuma ko da yaya sai na qulla zumuncin nan...”

Murmushi Haysam yayi yana mai cigaba da hada shayin sa,

“Ummah kenan. Ni fa ba mace bane da za’aimin auren dole.”

“Magana dai nagama ta. Aure ne tamkar anyi an gama ne.”

Mikewa yai ya fice ya bar mata parlorn hannun sa dauke da kofin shayi.. Taja tsaki tana hararar bayan sa.

•

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈😍😍😘😘

[9/16, 11:29 AM] : _I˚˚G˚˚I˚˚Y˚˚A˚˚R˚˚ Z˚˚A˚˚T˚˚O˚˚_

N˚˚A˚˚

37

•••. •••. •••

Bayan sallar magrib na idar da lazimin da nake yi sak’una har biyu suka shigo waya ta, Daya Haysam ne d’ayar number kuma bansanta ba. Sakon Haysam na fara dubawa inda yake shedamin zai zo zance bayan sallar ishai. Dayan number kuma sakon fatan alkhairi ne kawai. Daga kasa an rubata: ‘Mms’. Mubeen ne domin nagane sunan sa. Saving number tasa nayi saboda idan ya kira bazan dauka ba domin nagano wanene.

“Allah ya taya shi ri’ko. Allah yasa ya sauke alkawarurrukan daya dauka Ameen..”

Cewar Innar mu dake sake karo sautin rediyon ta.

“Innar mu wanene?..”

“Sabon gwamna mai ci.. Bani sunan sa. Yauwa! Ambasada ne ada. Wai Alhaji Salees Muhammad.”

“Allah sarki Allah yatashi riko..”

“Ameen! Ance dai gaskia adalin mutum ne. Domin wai ya ri’ke mukamai masu yawa a gwamnati.”

“Allah ya bashi ikon cika wa’ennan ma. Alh salees...”

Na maimata narasa ina nakejin sunan. Youtube na latsa na shiga domin inason naga hotan sabon gwamnan namu mai ci. Naci sa’a kuwa shine na farko a newsfeeds. Danna kan video din nayi na matsa kusa da Innar mu. Autar mu ma ta zuro kai tana kalla. Goge idanu na nayi da kasan mayafi don ganin wani tamkar Mubeen an haskalo shi a matsayin dan gwamnan mai ci.. Shine wallahi na nanata sunan nasa sai yanzu ma nagano ‘Muhammad Mubeen Salees.’ Zamewa nayi nayi zaman dabaro. Innar mu ta dube ni tana mikomin wayata,

“Ungo nan! Allah yasanya alkhairi..”

“Innar mu yaron sa dinnan da aka nuna a ajina yake fa..”

“Allah sarki..”

Innar mu tafad’a tana jinjina kai. Naja majina ina sake duba videon wallahi shine,

“Autar mu ina wanda yazo rannan dinnan? Wanda yasa takunkumi a fuska?”

Autar mu ta gyad’a kai tana tsalle,

“Har yace min baby..”

“Oh haba? Toh shi dai. Innar mu wanda nace miki ina zuwa dinnan? Toh ashe wannan yaron ne.”

“Kai Masha Allahu! Allah ya tayasu riko.”

“Hmm Ameen! Innar mu ya fadi duka jarabawoyi na wallahi..”

Suka zaro idanu suna kallo na.

“Toh fa garin yaya haka? Ko da yake tasa kaddarar kenan.”

“Wallahi kuma bakiga ba Idan akai tambayoyi yafi kowa amsawa. Kuma sauran gwaja-gwajen zangon karatu wallahi duk yafi kowa ci. Amman ya fadi exams din. Kuma jarabawar itace mai makin da yawa.”

Na karasa fada jiki na a sanyaye. Innar mu ta jinjina kai cike da tausayi. Ta numfasa kafin tace,

“Toh Allah yasa hakane yafi alkhairi. Ai kila kuma zai bar makarantar yanzu. Kinga kaduna zasu koma ba dad’ewa.”

“Gwara ma wallahi. Ko su futar dashi waje ya karasa. Ko da yake daga can suka dawo fa. Mahaifiyar tasa ma yar wajen ce k’asar Ethiopia.”

“Au haba? Shi yake fada miki?”

“Eh wallahi wai baban nasu ne hausa/fulani.”

“Toh Allah ya hada kowa da rabon sa. Kede hakan ba zai janyo miki matsala ba ko? Kin kada dan gwamna a jarabawa?”

Na numfasa ina girgiza kai,

“A’a banaji gaskia. Saboda babu ta yadda za’ai a wutar da shi. Sai dai fa idan manyan makaranta ne suka sa baki. Tunda kinga gaba d’aya kasar ma akan tafarkin da take kenan.”

“Zahiri! Toh Allah yabamu sa’a dai....”

“Ameen Ya ALLAH...”

Cikin haka aka kirawo sallar ishai. Muka muke muka yiyyi. Bayan na idar da addua. Ina ninke sallayar mu na dubi Innar mu,

“Innar mu wai Haysam zai zo yanzu. Haka yace min ya turo sako.”

“Toh kardai ki jima. Sannan mahaifiyar tasa ta sakko ne ta yadda? Kinga uwata banason abunda zai je ya dawo.”

“Wallahi Innar mu nima banaso. Amman yace wai ta bashi zab’i. Abinda yasa ma har nake kulashin saboda babu tsayayye ne. Kamar sharar fili ne kafin Allah ya kawo wani. Wai kar ace bame zuwa wajen ka..”

“Toh Allah ya kawo muku mazan kwarai.. Masu dimbin albarka.”

“Ameen Innar mu. Ah wai duk yau ina Yayan mu?”

“Kina bandaki ya shigo dazu. Yace zai je kano wajen uban dakin sa. Akwai yan kudaden sa da zai karbo a fara siyan kaya ana ajiyewa. Daman tuni kinsan Yaya Amina tace zata biya kudin nagani inaso. Toh daga nan ma kuma yace zai je gurin wani uban gidan nasa ma ya masa alqawari kafin tahowar sa.”

“Ah Masha Allahu! Yayan mu dai aure nata matsowa. Gwara ayi dai muma mu samu guda d’aya mai auren. Allah yasanya alkhairi..”

“Ameen ya Allah..”

Gyara kai na nayi na yafa wadataccen mayafi akan rigar material dina orange color. Sallama naiwa Innar mu na sauke kasa bakina dauke da addua. A zaure na hango shi sanye cikin shadda kalar toka. Bai sa hula ba ya taje kan sa. Nayi murmushi ina kallon yadda yake bubbudawa.

“Ina wuni..?”

“Alhamdulillah Mine! Meye kike murmushi na miki kyau ne ko? Kada ki damu ni fa mallakin ki ne..”

Wani murmushin nayi, Shi da yasan murmushin me nake da beyi magana ba. Sai kace wani babban mutum yadda yake abubuwa. Ya cika son girma. Tamkar kuwa ya karanci yanayin me nake fada a zucia ta yai wani murmushin mai sauti yana zuba hannuwan sa a aljihun sa,

“Nifa yanzu ba rabin hamsin bane. Na dora talatin fa..”

Ya karasa fada yana kannemin ido d’aya,

“Ah menace Ya Haysam?”

“Ai nasan kina fadan ne a shekarun baya..”

“Banda sharri dai Yaya Haysam.”

“Ba sharri bane, Aminayar ki ce tace na muku yarinta..”

Rufe baki na nayi ina dariya kasa-kasa.

“Ya maganar auren mu?”

Shiru nayi masa ina lankwasa hannaye na. Toh me zance masa fisabilillahi? Ya sake tambayata a karo na biyu,

“Allah ya zaba mana abunda yafi alkhairi Ya Haysam..”

“Ameen. Ni dai gaskia acanzan suna. Ni ba yayan ki bane wallahi, Haka kawai kin fake da wani Yaya kin ki fitowa mu gwangwaje soyayyar mu. Adai canzan suna Mine..”

“Toh Ya H..”

“Gaskia kidena cemin Ya Haysam. Banaso wallahi.”

Ya karasa fada yana marairacewa hade da turo baki gaba alamar shagwaba. Maza na sha’anin su. Na fada a zuci ina kakaro murmushi.

“Bara na fado miki sai ki zabi wanda zaki dinga gayamin. Kinji...?”

“Naji.”

“Yauwa zabi d’aya cikin su, Good-looking, Handsome, Prince Charming, Boo, Casanova, Knight In Shining Armor, Bugs Beau, Lover boy, Sai Honey bun..”

Na gwalalo idanu ina jaddada kai, Sake maimata su yayi yana narkar da muryarsa.

“Mine...Wanne kika dauka?”

“Ai..”

“Babu wani ai wallahi. Nide.. Ni ..Ni de kawai acanza min suna..”

Yana faman bubbuga k’afa kamar dan k’aramin yaro. Wallahi yadda kukasan na sharara masa mari haka nake ji. Na danne bacin rai na ina kallon gefe,

“Boo! Na dau shi..”

“Yauwa Mine.. Nima bara na canza miki wani.”

“A’a Ya Hay.. Au aa ka bashshi Mine din issokay.”

Haka dai muka cigaba da hirar mu. Ina yi ina mantawa ina kiran Ya Haysam din. Dan wallahi bazan wani iya jurar kiran sa da boo ba kamar waata yarinya. Haka dai mukayi fada. Kunsan fadan masoya. Akan naki kiran sa da boo shine yai fushi ya tafi fuu ba ko sallama. Na karkade mayafi na nai sama dama nima cizon sauro ya ishe ni. Nifa gaba d’aya ma na tsani zance wallahi. Azauna aita magana tun ana fad’ar gaskiya har akoma sharo karairaki.

••X••O••X••O••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈□□😍😍😘😘□□□□□□[9/16, 11:29 AM] □: IGIYAR ZATO

38

MADAME_YERWA

•••. •••. •••.

Bayan zagayowar sati su Kawu Khamis da Baffa Ardo suka kai kudin nagani inaso na Yayan mu da kawata Fadilah. Nayi murnar da na kasa b’oye ta. Abun mamaki mahaifiyar Fadilah Aunty Nanah tuni ta zubar da makaman yakin ta. Har zuwa gidan mu take yanzu wajen Innar mu suna tattauna yadda za’ai komai. Yayan mu uban gidan sa ya bashi kyautar gidah karami madaidaici amma agarin kano. Dan haka acan zasu zauna. Nima yan kudaden da nake taru na fiddo su na bawa Innar mu taki karba ta dai dauki wani sashe an fara gudanar da harkar biki dasu. Tace na ajiye abuna. Saboda inda rabo nima gidan wani za’a kai ni. Anko kala d’aya na

atamfar ghana muka fitar itace ta futar biki ni da Fadilah. Munata shirye-shiryen mu kowanne sashe zukatan mu fal da farin ciki, Domin mu a dakin mu akan Yayan mu za’a fara aurarwa, Fadilah kuwa kaf gidan su akanta za’a fara aurar wa. Lamarin sai sam barka da fatan alkhairi kawai.

Zagayowar satin da zamu koma makaranta kuma aka fiddo da Kawu Ilyasu daga police station. Ya kod’e ya jeme ya zama abun tausayi. Amman abin mamaki daya shigo gidan mu ni yafara harara yana baje hanci. Gaba d’aya kayan sa sun daddare wajen mazaunan ma a bele yake. Sauran yara suka sa daria. Ni kuwa na cigaba da jan ruwan da nake a rijiya. Zama yai akan bokitin sa yana sauke ajiyar zucia kafin ya daga murya yana kwararo ruwan zagi da rantsuwa. Ya kar’kare da,

“Mutanen banza da wofi, Mahassada, Masharranta, Masu ba’kin ciki da bakar zuciya, Annamimai wanda ba komai a zukatan su sai sharri. Masu son ganin baya na. Na hada ku duka na dauke muku albarka.”

Baba usaiba dake tatar koko taja guda ta saki tana matse katon hancin ta,

“A hayye kayya kai! Sannu ilyasu! Yanzu kai a haka har kana da bakin magana? Koma me za’ai sai ayi idanma babbaka gidan za kai sai kayi. Amman fa bayan kaje ka tsaftace jikin ka. Domin banda hamamin wari da tsami wallahi ba abunda yake tashi daga jikin ka. Yo wannan idan masifa ce ke cinka sai ka amayar ka bari kayi gwabi-gwabi dai ko? Dube ka fa tamkar a hure ka ka fadi. Amma sai kwashe mana albarka ka ke. Nikam naci biride nayaga leda wallahi a shirye nake na nanuka gaddi a kasa wallahi. Naci biredi na yage lede ehe, A hayye kayya kai..”

Kawu ila yaja tsaki yana girgiza kai kawai. Bintalo dake karya kashin wuyan tayi murmushi tana sude hannu bayan ta kafa kwalbar lemo a baki, Sai data shanye tas tukun sannan tai jifa da kwalbar ji kake ‘taratsitss’ ta fashe. Kawu ila ya jaddada kai yana k’wafa,

“Hmm! Wai harda ke Bintalo, Aka juyan baya..”

Bintalo tai shewa tana sosa takashi,

“A hayye yau ga gaye ba makilis, Ilyasu! Dan bakin annamimanci irin naka ina kasan da yara a gidan nan yammata zagada zagada amman ka tsallake kai sai batoul zaka hada shi da ita? Ai gashinan ta watsa maka kasa a idanu kuma a banza ka jibgu a folisitehen. Da da ‘yayan mu ka hada shi ai da hankali kwance zaka tatsi kudin ka muma mu dandali namu arzikin...”

“Amman ko kowa zai juyan baya ke be kamata kiyi min haka ba Bintalo..”

Baba Ummita ta sha gaban sa tana watsa hannu a fuskar Bintalo,

“Nace ku auri juna mana ku huta, Ai ba kanku farau ba. Tun ba yanzu ba nake hankalce da ku. Shakuwar dake tsakanin ku ko mu matan sa bamuyi dashi ba. Kin taho fankan fankan kina turo kirji nace ki aure shi mana k..”

Bata karasa ba Kawu ila ya dakatar da ita yana daga mata hannu, Ta dalla masa harara tana maida kallon ta gare shi,

“Kai ma ahake nake da kai bakin munafiki. Kanata nanata ko kowa zai yi maka haka bai kamata ta juya maka baya ba. Matar ka ce? Ko ita ta tsugunna ta haife ka? Ko ‘yar kace ta cikin ka? Ni fa nagaji da bi ta bayan fage. Ku aure juna ku huta kawai. Aikin banza mamalam..”

Baba usaiba tai shewa tana buga zani,

“Kut-sin ubancan kayya kai. Yau ana yinta. A hayye naci biredi na yage leda.”

Bintalo taja tsaki tana buga zanin ta a fuskar Baba Ummita.

“Na auri Ilyasu fa kikace? Allah ya sawake ko maza sun k’are wallahi, Me zanyi da sauran wasu, Nawa yake dashi nawa ya tara? Nafi karfin kaf mazajen ku wallahi,

Banda abun ki da inason Ilyasu zan tsaya jin shawarar ki ne? Sanda zan aureshin zama ki sani ne? Sittin ta ubangiji a shirye nake na zugewa mutum tazuge duk girman sa wallahi.. Kina maganar na taho fankan fankan ina turo kirji ko? Toh ai nagodewa Allah inada kirjin turowar ma, Ke kuwa naki a sheme, Sekace silifas. Sittin ta ubangiji bashi da maraba da k'irjin maza. Sad'od'o dake ba gaba ba baya.."

Baba Ummita ta shatalo k'afar Bintalo suka fara dambe. Nai murmushi kawai ina daukar ruwan wanka na. Nayi matattakar karshe Kawu ila ya dokamin kira wai dan ya cusan haushi,

"Zo ki kawo min ruwan nayi wanka, Figalalliyar banza da wofi.."

Juyawa nai na koma kasan na janyo bokiti na juye masa shi,

"Sawu uku zaki min.."

Ya maimata yana dankara min harara, Janyo masa nayi har bokiti hudu ma na zuba masa a babban bokitin su. Na juya na kuma dibar nawa nai hayewa ta sama, Shiru ma ai magana ce ga mai hankali, Ai kuwa ya sandare a zaune da alamun bai tsammaci hakan ba. Ina shiga da'ki Innar mu ta nunamin wayata,

"Sai kira ake tayi wallahi.. Allah yasa dai lapia."

Ganin me kiran yasa na yamutsa fuska na dire ta akan katifa, Ai kuwa ya sake kira,

"Wai waye yake ta faman kira kina kin dauka? Iyye?"

"Innar mu wata number ce.."

“Toh ba sai ki dauka kiji menene ba? Amman ai babu dadi ana kiran ka kana kin dagawa. Yanzu idan kira ne me muhimmanci fa.? Duba da yadda tun d’axu ake kira.”

15 missed calls. Na dubi yawan kiran ina mai dagawa na kara a kunne na. Ajiyar zuciya ya sauke ina jiyo sautin ta,

“Assalamu Alaikum..”

Na fada ina hararar wayar. Shi kuwa Mubeen dake kishingid’e a cikin motar sa ya kara yin baya da kujerar yana lumshe idanu. Ba kadan ba muryar malamar tasu na tafiya dashi. Kai komai nata ma.

“Waye ne?..”

Ahankali yai murmushi yana sanyata a handsfree hade da dora wayar a kirjin sa,

“Mahhhh! Ya gidah?”

“Alhmldh da..Da wa nake magana?”

“Habba ma bakiyi saving number na ba? Muhammad Mubeen ne.”

“Ohh ya kake?”

“Alhamdulillah Ma! Ya gidah da komi?”

“Lapia lou! Ya.. Ya akai? Wani abun ne?”

“Kina gidah? Anjima?”

“Bana nan..”

Innar mu ta gallara min harara tana karo sautin rediyon ta, Nayi murmushi kawai domin da alamun batasan waye ba. Kilan ta dauka wani saurayin ne. Allah sarki Innar mu. Marairacemin yayi tamkar zaiyi kuka. Na tuno haka Haysam yake min. Ni kam na ha’du da gamo na.

“Shikenan.. Kazo. Amman wait...Me zakai ne?”

“Mah lefi ne dalibi yazo wajen malamar shi?”

Na girgiza kai tamkar yana gani na,

“A’a.”

“Toh sai nazo.. Kinason na taho miki da wani abun?”

“No..”

“Pls anything? Haka dan chocolates”

“No nagode..”

Kit na katse kiran ina jifa da wayar. Dan kuturin munafurci sai kace wani saurayi ne zai zo. Ni ko saurayi bana son kar’bar abun hannun sa ballantana dalibi hakan

kamar toshiyar baki ce ta abubuwan makaranta. Na kalli Innar mu ta gefen ido ina daria kasa kasa,

“Innar mu bafa saurayi bane, Ina wannan yaron dan gwamnan nan. Shine zai zo ya gayshe ni.”

“Eh duk da hakan dai uwata ai shi dan Adam Allah ya karramta shi, Babu kyau wulakanci. Kuma kinga dalibin ki ne koba komai zaki samu yabo mekyau.”

“Hakane, Nayi kuskure. Bazan sake ba IN SHA ALLAH..’

Tunowa nai da dan kwalin daya bani tun kafin exams nayi. Dakko shi nayi acikin jaka ta don ganin menene. Wani siririn zobo ne mekyau dashi. A gefen kwalin daga saman sa an rubuta ‘english gold.’ Ajiye shi nayi a gefe yana zuwa zan mayar masa da kayan sa. Yaron nan bai zoba sai bayan sallar ishai na fara hamma ma zanyi bacci Bala yashigo kira na wai nayi bako. Hannuwan sa niki niki da ledoji. Zoben na dauka na sauka bayan na burma hijabi. Ko kallon fuska ta banyi ba a mudubi. Yana zaune a saman motar sa yana danna waya, Na dan daga murya ina hararar sa,

“Karaso to..”

Karasowa yayi sanye cikin kananun kaya ya rufe fuskar sa da takunkumi da alamun bayason agane shi. Ashe shiyasa ranar da yafara zuwa na ganshi dashi? Naja gefe na tsaya ina muzurai jira nake ya gayshe ni amman yaron nan ya shiga murmushi yana kallon kasa.

“Ya akai ne? Yauwa ungo zoben ka rike..”

Na karasa fada ina mika masa. Kin karba yayi yana hada hannuwa waje d’aya,

“Ayana.. Barka da dare! Yasu Ummah da baby? Naga kuna kama.”

“Lapian su lou! Yes autar mu ce. Ungo zoben mana.”

Kin karba yayi yana make kafada,

“Kyauta fa na baki Ma! Ba’a mai da hannun kyauta baya. Dan Allah kakki bani.”

“Fine! Nagode. That aside. Meya kawo ka uhm? Kai da mukayi tun d’axu zaka zo. Shine zaka zo yanzu? Ko daga zance ka biyo nan.?”

Yai saurin girgiza kansa yana murmushi, Nima murmushin nai da alamun kunya ta yake. Dan matsowa yai yana haskoni da hasken wayar sa. Na galla masa harara ina kauda fuska ta,

“Meye haka? Matsa.”

“Mah kinada kyau wallahi. TubarkAllah! Kullum kara kyau ki...”

“Ya isa haka! Kaga dare yayi. Sai da safe. Yauwa dakata na dakko maka kayan daka kawo. Wai meyasa kake hakane uhm? Ka denamin haka banso.”

Kasa-kasa yake kallo na yana jan lips sa,

“Ni baby na bawa. Kuma Ma’am dan na kawo miki abu ai ba wani abu bane ko? Nifa student dinki ne. Kuma bakyau kin amsar kyauta..”

“Toh naji.. Angode kwarai. Congrats! Naga dad dinka ya xama governor.”

Rage annurin fuskar sa yayi domin sam bayason mukamin da mahaifin sa ya samu. Shikenan yanxu mutane zasuyi nisa dashi ta k’arfi da yaji? Kad’a kai kawai naga yayi yana murmushi. Na Kalli agogon wayata kafin na kalle shi,

“Amman xaka canxa sch ko?”

Saurin girgixa kai Mubeen yayi,

“A’ah! Meyasa kikace haka Ma? Bakyaso na cigaba da schooling anan?”

“Ba kaduna zaku koma ba? Ai sai yafi maka sauki. Ka fara fresh start.”

“No ina nan IN SHA ALLAH! Bazan je koina ba Ma’am. Ko a hostel ai sai na zauna.”

Kad’a kai nayi ina jaddada karfin hali irin na sa. Yana dan gwamna yana tunanin sake zama a makarantar da ba iyayen sa a kusa.

“Ni zan koma ciki.. Sai da safe.”

Kamar zai yi kuka haka Mubeen yai raurau da idanu.

“Sai da safe Ayana.....U made my nig...”

Daga masa hannu kawai nayi na shige cikin gidah. Mubeen kuwa ya dan jima a tsaye yana dafe da saitin zuciyar sa. Kafin ya lumshe idanu ya fice zuciyar sa fal da farin cikin kasancewa da malamar tasa.. Ina shiga daki naci karo da ledojin fal. Kayan kwalam da makulashe ne shak’e aciki. Na dubi autar mu dake karatu nace,

“Innar mu na dawo.. Autar mu wai ke ya kawowa. Wash! Nagaji wallahi.”

Autar mu ta buga tsallen murna tana dudduba ledojin. Innar mu ta debar mana kafin ta karkasashi autar mu ta mimmikawa kowanne daki nasu kason.

••X••O••X••O••

Da wuri na tashi na kintsa, Domin an koma makaranta. Inda Allah ya temake ni ma wannan second semester din banida koyarwa sai dai guidance da kuma shigar da electives/subsidiary courses na yan level one..

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: □□□□□□____□□□□

39

Kafin naje office tuni an gyara an tsaftace shi. Ina shiga school na je dean’s office dana head of department dama sauran senior lectures dina duk na gayda su. Kafin na wuce office dina. Na gyaggyara yan abubuwan da gyaran bemin ba sannan na zauna baki na dauke da addua. Sauri nake yi na gama abinda zanyi domin yau za’a kai lefen yayan mu kuma sati na gaban ne bikin. Akwatuna uku da kit yayan mu yayi ba laipi komai yayi domin yayi kokari sosae. Sosae students suka rika tururuwar shigowa office dina suna kawomin crfs (course registration form) Na shiga

signing da cikewa ina duban agogon hannu na. Mikewa nai bayan na gama na shiga hada kaya na acikin jaka. A lokacin Muhammad Mubeen ya shigo yana karemin kallo. Na girgiza kai kawai na lura baya gajiya da kallo kamar tsohon maye.

“Ma!”

“Yes..”

“Tafiya zaki?”

“Eh sauri nake yi. Ajiye crf din zan duba a gidah.”

K’arasowa yai wajen table din ya ajiye yana rausayar da kai. K’amshin turaren sa ya daki hanci na.

“Barka da rana Ma..!”

“Yauwa..”

Na amsa shi ina murmushi domin inason abani girma na. Harhada komai nawa nayi na zuba a jaka ta ina ratayawa, Biyoni yai a baya yana sunkuyar da kai,

“Zan rufe office din.”

“Ma zan kai ki gidah.”

“A’a nagode.”

“Dan girman Allah kiyi ha’kuri na kai ki kinji?”

Tsaki naja na sauke Ina dankara masa harara,

“Akwai lectures uku da zakuyi nan gaba. Abeg jeka class.”

“Ma elective ne wanda za’ai yanzu kuma banayi. Na anjiman ne 2-4 shine nake yi.”

Yamutsa fuska nayi nai gaba abuna yabi ni a baya yana murmushi. Kafin na karasa motar ya bude ta a key. Nai shigewa ta baya ina hura hanci. Gaba ya shiga ya zauna ya tayar da motar. Fadilah ta kira ni awaya na daga ina murmushi,

“Amaryar mu...”

“Na’am aminis! Ya kindawo kuwa ko kina school?”

“Gani a hanya zan k’araso ISA. An kawo lefen ne?”

“Ke dalla ni wajen dinki ma nakeson muje. Ance K-boy mai dinki ya hadu da hatsari.”

“Subhan’Allah! Allah ya bashi lapia. Bara na dawo sai mu zaga ko xamu samu wanda zai mana ko?”

“Eh sai kin karaso tawan.”

“Ai agidan ku zan sauka ma kawai.”

Ina gamawa na katse. Ta mudubi na hangi mubeen yana kallo na. Harara na dankara masa ina daga wayata sama,

“Ma bikin brother dinki xa’ai ko?”

Baki bude na tsaya ina kallon sa,

“Aina kaji kai kuma?”

“A status dinki nagani.”

Ashe ban rufe shi daga ganin statuses dina ba? Shaf na manta wallahi! Dafe kai na nayi da hannu na cike da takaici. Yayi murmushi yana gyara mirror din. Ina kallon sa yana gyarashi saiti na. Ya rainani wallahi. Cikin haka kafin mu karasa unguwar mu Haysam ya kira ni na rage murya ina waya dashi kasa-kasa. Mubeen ya sake hade rae yana yamutsa fuska. Batoul kuwa hankali kwance ta gama wayar ta bayan sun zuba soyayyar su. Ta katse tana murmushi,

“Har mun karaso ashe?”

Shiru Mubeen yai yana taune kasan leben sa na kasa. Na sake maimatawa ina kallon kan titin layin mu,

“Mota zata iya shiga ta can?”

Na fada ina mai masa nuni da layin su Fadila. Gyada kai yayi kawai ya figi motar, Dai dai k’ofar gidan su Fadilah nace ya sauke ni,

“Yauwa dan albarka.. Godia nake.”

Kamar ba zaiyi magana ba sai kuma yayi cikin sarqewar murya yace,

“Ba..b. ba fitowa zakuyi ba?”

“Oh wajen dinki? Ai kada ka makara kuma. Ka basshi”

“Ni nayi niyya..”

“Toh bara mu fito. Godia muke.”

Batoul na fita daga motar Mubeen ya kifa kansa a sitiyari yana lumshe idanu. Yasa hannun sa d’aya yana wargaza sumar kansa,

“Ya Rabbi...!!!”

Ba jimawa suka fito daga cikin gidan Itada Fadila da kaya fal leda. Fitowa yai daga motar da sauri ya bude musu booth. Fadilah sai kallon sa take domin bata san shi ba. Gaba batoul ta zauna Mubeen yai murmushi. Ita kuma Fadila ta zauna a baya.

“Sannu...Ina wuni..?”

Cewar mubeen. Fadilah ta amsa fuskar ta dauke da murmushi.

“Aminayas sunan sa Muhammad Mubeen dalibi na ne. Mubeen ga aminiyata Fadilah, Amaryar yayan mu.”

Gaisawa su kai shida Fadilah. Haka su kaita watangaririn neman wajen dinki. Dakyar suka samu wani Senegalese tailoring services. Mubeen ya faka suka fito suka shiga ciki. Shi kuma ya zauna akan mota yana hango su. Yana ganin sanda wani tela ya dakko tape yana gwada Batoul. Rintse idanu yayi yana cije lebe. Gaba d'aya kishi ya kama shi. Sam bayason yadda telan yake faman aune jikin ta. Kasa kasa ya shiga kallon ta yana k'are mata kallo. Ashe yadda yake kiyastata har tafi haka? Kasa jure kallon ta yayi ya koma mota ya zauna yana mita a hankali. Basu jima ba suka fito aka sauke Fadilah a makotan su, Batoul kuma ya kai ta gidah.

"Nagode Muhd Mubeen. Allah ya saka da alkhairi."

Kad'a kai kawai Mubeen yayi yana lumshe idanu,

"Ma meyasa kika bari namiji yake daukar measurement na kayan ki.?"

Batoul ta shiga ware idanu tana masa wani kallo. Mubeen yai murmushi kawai yana sake cewa,

"Afuwan Ma."

Ni kuwa na rasa abunda zance masa ma wallahi. Dubada yadda yaita yawo damu shiysa na danne bacin rai na ina kakaro murmushi,

"Babu komai.."

Cikin haka Yayan mu ya fito daga gida yana waya. Yana hango ni ya nufo ni yana murmushi,

"Yayan mu.."

“Na’am aminiyar mu.”

Murmushi nai ina rufe baki,

“Tun yanzu na koma kawar ka kenan. Yauwa an kai kuwa ko yana ciki?”

“A’ah yanzu dai za’a kai su Kawu ila ne ke gani..”

Sai a sannan ya kula da Mubeen dake danna wayar sa. Hannu ya bashi suka gaysa,

“Dalibi na ne.. Muhammad Mubeen. Mubeen ga babban wanmu Yaya Najibullah.”

Gaisawa suka sake yi cikin girmamawa.

“Ina zuwa Mubeen bara na dakko maka ruwa.”

Kad’a kai Mubeen yayi domin bai gaji da ganin ta ba. Shigewa nai cikin gidah da sauri domin dakko masa ruwa da lemon da Yayan mu ya dan siyo don baiwa wanda zasu kai lefen. Ina shiga na ja na tsaya don ganin yadda Kawu ila ke surfa masifa yana kwararo rantsuwa,

“Wato saboda an renani ba aganin girma na shine har za’a kai kayan shegen yaron can bansani ba sai yanzu? Dan jakar uba kuma yana gayamin wai sauri ake mutane sun taru. Uban uban wanda ya hada auren. Na soke ma babu wani aure da zeyi. Dan tsabar tsagwarar munafurci shine har an tambayo auren an gama komai za’a kai lefe amman sai yanzu zan sani? Na hada ku duka na kwashe muku albarka.”

“A hayye kayya kai! Ai kasan kai ka haife mu da zaka kwashe mana albarka ta kwasu. Billahil lazi naci biride na yage leda zan nunaka gaddi a kasa.”

Baba usaiba ta fada tana sakin gud’a. Kawu ila yasa kafa ya shure akwatin kayan yana bambamin bita. Baba Usaiba ta bishi da guda tana buga zanin ta,

“Wooo! An daiji kuma sai anyi. Billahil lazi naci biredi na yage leda.. A hayye kayya kai. Sandar ba’are kawai.”

Girgiza kai kawai nayi na haye sama. Daki na shiga na gaggaysa da yan Shema da suka zo kai lefen. Na dakko lemo da ruwa da sauri na sauka kasa wajen Mubeen. Suna tsaye shida Yayan mu suna hira na karasa,

“Batoul ashe ke harda dan gwamna kike koyarwa. Sai da na kare masa kallo nagane shi wallahi..”

Murmushi nayi kawai ina mik’awa Mubeen ruwa da lemo. Hannu na da nasa suka dauki wani shock na janye da sauri ina kallon gefe. Shi kuwa Mubeen lumshe idanu yai ya bude su a kai na yana murmushi.

“Ka tafi kada ka makara...”

Kallon agogon sa yayi yana girgiza kai,

“No zan tsaya mu kai kayan. lecturer din bada wuri yake shiga ba.”

Kad’a kai kawai nayi na koma cikin gidah abuna. Ba jimawa aka fito da akwatunan lefen Yayan mu. Yan gidan mu rankataf sun hadu za’a kai dasu ciki harda yara. Toh waya isa ya hana? Da kafa wasu su kai gaba suna hira. Akwatinan kuma aka sanya a motar abokin Yayan mu. Bintalo ta tsaya cakoko a kofar gida tana bin kowa da kallo. Saurin shigewa motar Mubeen nayi ina kara waya a kunne na. Cikin sauri Bintalo ta karaso wajen motar tana zuro kanta ta wundon hade da gaftarar goro tana ci tana magana dik ta feshe mu da ruwan goron bakin ta.

“Yar kundin uba gaba zaki yi kenan a mota? Sittin ta ubangiji ba zan dab’a a kasa ba ehe..”

Na kalle ta ina dafe kai na cike da takaicin abunda take gumamin a gaban Mubeen. Bintalo ta mai da kallon ta ga Mubeen dake danna wayar sa,

“A hayye yau ga gaye ba makilis! Aina kika samo dan bature ke kuma? Wannan yarinya da jajibe-jajiben masifa ki ke. Kai ‘dannan ka iya hausa ma kuwa?”

Mubeen da surutun ta ya ishe shi yai murmushi kawai yana mai da kansa gefe da alamun yan basarwar sun motsa kuma.

“Baba shigo muje..”

Bintalo ta sake gaftarar goro tana tattare zani tamkar wadda zata hau mashin, Haka ta shigo ciki tana zubar magana.

“Tab! Sittin ta ubangiji anyi kerarriyar mota. Wohoho anya bata yan damfara bace?”

Ni kuwa nai mata banxa ina rintse idanu na cike da takaicin yadda take ta bada ni agaban dalibi na. Haka muka karasa gidan su Fadilah Bintalo nata kwararo zance kamar ya’yan kanya. Tun Mubeen na sauraron ta har ya dena. Dakyar Bintalo ta sauka daga cikin motar tana mitar bata k’oshi ba. Sai kace abinci. Tana sauka nasa hannu zan bude naji ta rufe. Na kalli Mubeen dake kallo na shima yana sake sunkuyar da kai,

“Budemin xan fita..”

Bai cemin komai ba ya cigaba da kallo na. Ya d’au tsawon lokaci kafin ya bude yana cije kasan leben sa. Na fice da sauri ina lek’o da kai na ta kofar,

“Nagode sosae Mubeen. Allah ya maka albarka.”

Ina gama fada nai shigewa ta gidan su Fadilah. Shi kuwa Mubeen murmushi kawai ya yayi ya tashi motar ahankali ya nufi gidah bai koma makarntar ba. Zuciyar sa fes da farin cikin kasancewar su da malamar tashi...

••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] I GIYAR ____ZATO

42

Haj Husnah ce ta shiga mayafinta a gefen kafada ta kumbura zata fashe saboda bala’i. Idanuwan ta sun sake shigewa ciki saboda masifa. Cire mayafin tayi ta daura a kugu tana buga hannuwa a bango,

“Kaltume! Kaltume! Kaltume! Fito nan dake zanyi billahil lazi.”

Kasa shiga bandakin nayi na fito daga lungu ina binta da kallon mamaki. Innar mu dake sama a daki bata tanka taba na tabbata kuma ta jiyo. Amman rankataf din yan gidan mu kowa ya firfito. Kawu ila ya dakko bokitin zaman sa ya zauna yana zabga tagumi,

“Baiwar Allah meya faru ne? Wacce shegiyar ce ta miki abu?”

Haj Husnah ta kalle shi a wulaqance tana yatsina,

“Ance kudin duk yan uwa ne anan ko?”

“Eh toh kusan hakanne, Wasu daga cikin namu dai ana dai zama dasu ne saboda babu yadda za’ai dasu. Kamar ita matar da kike kira itada iyalin ta..”

Haj husnah taja majina tana girgiza,

“Dakyau! Shegu ne yaran ko kuma yan uwa ne na nesa?”

“Ai Hajia sai dai abar kaza cikin gashin ta kawai..”

Haj Husnah ta sake kwafa tana bubbuga hannu a bango,

“Toh ku saurare ni. Yauwa bawan Allah ina kaltume mahaifiyar figalalliyar yarinyar can?”

Ta karasa fada tana nuno ni. Kawu ila ya kada kai kafin ya haye saman mu ina jiyo shi yana saukewa Innar mu ruwan masifa da bala’i. Ba jimawa sai ga Innar mu ta leko ta saman bene tana jan carbi,

“Okay kinfi karfin ki sakko kenan? Toh keda ‘yarki ku bude kunnuwan ku saurare ni dakyau. Kuma yan cikin gidan nan inason ku zama shedu.”

Banda rawa babu abunda jiki na keyi. Wannan wane irin cin mutunci ne har gidah fisabilillahi? Daman gashi rai na abace yake tazo tana kara min wani. Wai shinma meya kawo ta? Kenan Haysam karya yamin yace ta amince? Wallahi daman sai da Innar mu taita tambaya ta nace ta amince. Innalillahi wa’inna ilaihirrajiun! Naita maimaitawa ina dafe da goshi na.

“Kada kiji komai Hajia. Tamkar agaban alqali kike kuwa. Zan tsaya miki akan komai daya hada ku. Dan basuda mutinci gaba dayan su dakika gansu. Shi yasa na hada na kwashe musu albarka..”

Cewar Kawu ila dake murmushin mugunta. Bintalo taja tsaki tana dankara masa harara,

“A hayye yau ga gaye ba makilis, sittin ta ubangiji sai dai kaga kwashewar albarka akan ka da yayan ka.”

Haj Husnah ta mata banzan kallo tana tsurtar da yawu a gefe hade da toshe hanci,

“Au ashe kema d’aya barauniyar kina nan. Ice ko andai na dan halin? Ku kuwa dai bakuji dadin rayuwar ku ba wallahi.”

“A hayye nanaye! Hajia kenan, Nifa yadda kika ganni nan sittin ta ubangiji sai na zugewa mutum ta zuge duk girman sa wallahi. Hakki na da aka hanani kwa biyani a lahira.”

“Sai ki zuge ai banza kazama, Bakida aiki sai sosa takashi kina tsamin wari. Banza barauniya wadda ke neman mijin wata..”

“Ahayye yau ga gaye ba makilis! Neman mijin wata fa kikace hajjaju? Yo ai kema mijin watan kika aure ai ba kece matar sa ta farko fa. Munsan shafe shafe, Munsan mai. Munsan jagira da hoda..”

Haj Husnah taja tsaki tana yamutsa fuska,

“Karamar yar iska. Miji na ya miki nisa wallahi. Ko a mafarki mai kama da inuwar sama ba samu zaki ba..”

“A hayye nanaye... Oho dai! Nide nagaya miki kema mijin watan kika aure. Kuma mata hudu rigis gis sai alhajin ku yayi.”

Gaba d’aya sai muka zama yan kallo mu kalli waccen mu kalli wannan. Sai bankada maganganu suke yi. Ni wallahi banmasan abinda ya faru kenan ba. Ai gashi nan tasu taxo ta hada su. Sai da su kaiwa juna wankin babban bargo tukun sannan kowannen su yai shiru. Haj Husnah taja fasali kafin ta shiga karkadawa Innar mu hannuwa,

“Kaltume ina figalalliyar ‘yarki ina ‘dana? Tun shekarun baya na miki kashedin ku rabu da ‘dana. Kun mai dashi saniyar tatse yana dauke mu wahalhalun rayuwar ku. Cin ku, Shan ku, Suturu duk shine, Hakan bai ishe ku ba sai da kuka asirce shi yaso wannan jemammiyar yar taki?

“Ai ruwa ba sa’an kwando bane. Toh ku saurare ni wallahi baku isa ku hada aure da dana ba billahil lazi. Kalle ku mana, Kuna fama a gidah duk sai hayaki da warin talauci. Ina tunanin daki dai dai ne daku ma. Kina matsayin yar aikin mu kice zaki bawa yar ki dana? A garin wani gab’a gaban mahaukatan ake haka?

“Ai wutsiyar rakumi tayi nesa da ‘kasa, Dai dai ruwa daidai tsaki. Kwarya tabi kwarya akeyi. Badan ma aikatan da kike mana ba ada ke kin isa ma ki doshi kofar parlor na? Bankadaddu, Matsiyata, Mugaye kawai. Dan tsabar ba Allah a ranku shine kuke tunanin hada zuri’a ta daku? Da wannan shegiyar yar taki? Da ake yawo

da ita a gari. Jami’a kala nawa tayi yanzu tana koyarwa ga gawan tazubar. Yar iskar ya.....”

Zubewa nai a kasa ina kuka, Wannan wane irin cin mutinci ne haka? Innalillahi wa’inna ilaihir raji’un! Haysam yamin adalci kenan? Ya nuna min ta amince yanzu gashinan tazo har gida ta dankara mana rashin mutinci. Innar mu ce ta sakko ta tari numfashin ta.

“Ya isa hajia dakata! Inaso ki koma ko ki kira dan naki ya zama sheda. Wallahi summa tallahi tun Batoul batasan menene so ba Haysam yake sonta. Yarinyar nan Allah ne shahidi wallahi tallahi bata son ‘danki. Shi kanshi ya sani. Shekaru nawa yana bibiyarta akan ta amince ya turo manya? Idan baki sani ba ki sani har ca yai mata kin amince suyi aure. Kamar yadda kika fada Hajia ba karya kikai ba,

“Tabbas wutsiyar rakumi tayi nesa da kasa. Batoul ba tsarar auren Haysam bace. Kamar yadda shima ba tsaran auren ta bane. Adduar kowacce uwa akan yarta shine ta samu miji nagari, Adali mai ilimin addini wanda zai ci da ita ya tufatar da ita ya kuma biya mata bukatun ta idan sun taso. Kuma kowacce uwa zata so yarta tasamu dangin miji wanda suke sonta sukeson iyayen ta. Wanda zasu sota tsakani da Allah su dauke ta tamkar ‘yar da suka haifa. Saboda suma za’a kai nasu yaya matan wani dangin mijin,

“Shi fa komai na duniya idan kai dakyau zaka ga dakyau wallahi. Duk abunda ka shuka zaka girbe shi Hajia. Ita bintalon data fara rura miki wutar ai ga irinta nan tagani akan nata ‘yayan. Saboda shi sharri dan aike ne duk inda yaje sai ya dawo maka ko wanin ka. Saboda haka karki kara zagemin yarinya wallahi. ‘Yata ba yar iska bace, Tayi karatun ta boko da arabi cikin aminci. Tsayuwar datai akan turbar gaskia shiysa gashinan rayuwar tata kullum kyau take. Kuma ina tabbata miki cewar dan ki ma abunda yagani kenan ya nace mata. Kuma inason ki cire ki cire *ZATON* ‘danki zai auri Batoul. IN SHA ALLAHU! Yadda bakyason ta Allah bazai sanya ta shigo ahalin ku ba. Allah ya mana tsari daga gare ku Hajia. Batoul tayiwa Haysam nisa na har gaban abadan IN SHA ALLAHU! Allah zai azurta ta da miji wanda ku kanku sai kun amfana dashi. Wanda zaki ciji yatsa da yardar Allah.

“Sama tayiwa yaro nisa sai dai yata da kai ya kallo. Toh haka Batoul zatai wa Haysam ni sa. Nisa wanda kudi ko mulki bazai taba sa ya same taba. Akan haka dama kiketa kumfar baki? Gaba dayan mu Allah ne yayi mu daga ‘kasa Hajia.

Talaka da mai kudi duk rami d’aya za’a zuramu wallahi. Kuma sai kiga talakan da aka rena shine mafi soyuwa agurin Allah. Kuma kisani badan baya sonsa bane ya yi shi a talaka. Kada ki manta gidan biyu ne akwai na lahira wanda shine na gasken gaske Hajia. Wallahi kin bani kunya da har akan wannan maganar kikazo nan gidan. Dan kine mai taurin kai. Da har zaki gindaya masa sharadi yasa kafa ya shure zancen ki. Nan yake zuwa yana mata nacin auren sa. Yace kin amince harda doriyar za’azo akawo kudin aure. Ki tambayeta gatanan dai dai da sakan d’aya bantaba son ta dashi ba wallahi. Saboda mahaifiyar sa ba sirikar kwarai bace. Saboda haka daga yau Hajia ki tsawatarwa dan ki. Kada ya kuskura ya kara zuwa wajen Batoul. Kada ya kara tako kafar sa nan gidan da sunan batoul. Alakar mu dashi ta yanke. Alkhairin daya mana Allah ya biyashi ya bashi mata tagari wadda tafi Batoul a komai. Itama Allah ya bata wanda ya fishi. Allah ya hada kowanne da rabon sa. Ku rike arzikin kudin ku. Mu rike talaucin mu da wadatar zuciyoyin mu. Ke Batoul yo wankan ki wuce sama. Allah ya sawwake.”

Kai kuma ilyasu idan tunda kai ne sheda ina fatan ka saurari duk abubuwan da nace? Ka zamo sheda Batoul har gaban abadan tayiwa Haysam nisa...”

Tunda Innar mu ta fara magana har ta gama idanuwan yan gidan mu awaje suke. Domin Innar mu bata cika maida martani ba sai dai idan abu ya kai kololuwar ba’ci shine xata maida martani mai zafi. Kowannen su yai shiru ciki harda Haj Husna dake sandare a tsaye. Haka ta tsaya tai ta kumfar baki tana gatsine gatsine kafin ta fice tana mita. Ni kuwa bandaki na shige nai wanka zuciyata cike da dadin yadda Innar mu ta wanke mu agaban kowa. Koba komai itama Haj Husnan zata san dan nata baya gaban mu. Allah yasani naji haushin Haysam amman nasan so ne yasa ya fadamin ta amince. Kuka na nai marar sauti na haye sama. Yinin ranar kai na banda ciwo babu abunda yake. Mubeen ma har gidah yazo ya turo a kirawo ni saboda tsabar bashi da kunya. Yai ta aiko yara naki fita. Daga karshe ya turo aka kawomin jakata da waya ta. Daren ranar nan haka naita sak’e-sake a zuciata ina kuka ina gayawa Allah ya zaba min abunda yafi alkhairi. Haysam ya kirawoni yafi a kirga. Dana gaji na kashe wayar gaba ki d’aya. Gaba d’aya satin banje makaranta ba. Mubeen yaita shataletalen zuwa gidan mu ko sau d’aya ban fita ba. Domin shima haushin sa nake ji. Saboda ya renani reni me tsanani da har zai dubi tsabar idanuna yace yana so na.. Ni kuma haka Allah ya qaddara min rayuwa ta?

••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😉😈😍😍😘😘

[9/16, 11:29 AM] □: □□□□□□_□□□□□□□

41

Gaba d’aya farfajiyar gidan dankam take da mutane kowa yanata hada hadar halattar liyafar da za’ai a d’aya daga cikin hall din dake gidan gwamnati na taya his excellency Dr/Amb salees muhammad lashe zaben zama gwamnan jihar ta kaduna. Yan uwa fal da abokanan arziki sun cika gidan kowanne bakin sa har kunne ciki harda yan bakin ciki dake murmusawar yak’e.

Mubeen dake baje akan gadon sa yana karewa hotan Batoul kallo a waya data sa a status ya sau nannauyar ajiyar zuciya yana dafe saitin zuciyar sa. Lokaci zuwa lokaci yakan lumshe idanun sa yana sakin murmushi. Cikin haka mahaifiyar sa ta shigo dakin nasa shirye cikin wani datsattssen lace purple tasha ruwan gold. Tayi kyau babu karya. Kallo ta kare masa ganin yadda take ta doka sallama amman bai amsa ba yana can duniyar tunanin malamar tasu..

“Muhammad Mubeen..”

Sai data kira shi sau uku kafin ya farfado daga duniyar tunanin daya tafi. Ya mike daga kwancen da yake yana sosa keya,

“Wa alaykm salam Mamma..”

“Tab! Tun daxu na gama doka sallamata ai. Inata kiran ka kuma kamar wanda baya dakin. Meke damunka ne Mubeen?”

‘Batoul...’

Ya fada a zuciar sa, A zahiri kuma yamutsa sumar kansa yayi kawai ya mike yana gyara kayan jikin sa,

“Bakomai Mamma!”

“You sure?”

“Yesss Mamma..”

“Toh shirya ka fito kai ake jira za kubi tawagar shigar da baban ku cikin wajen taron.”

“Mamma kai na ci...”

“No excuses Mubeen. Ka shirya ka fito yanxun pls.”

Kada kai kawai yayi ba don yanaso ba, Ita kuma ta fice da sauri tana amsa kiran da akayo mata a wayar ta. Cikin wata dandatsetsiyar shadda kirar getzner ya sanya hade da agogon azurfa da takalmin batozzi. Kai komai nasa yayi kyau. Ya taje kwantacciyar sumar kansa yana dora hula akai. Ya feshe jikin sa da turaruka masu kamshi da tsada. Cikin takama ya fice daga dakin nasa kai tsaye ya wuce babban parlorn mahaifin nasa shake da mutane. Mahaifin nasa na hangoshi ya kirawoshi yana mai nunawa mutanen wajen shi da matsayin sa. Daga nan suka jera su kai wajen liyafar da aka shirya. Tab tsayawa fada muku tsarin wajen bata lokaci ne wallahi. Ya hadu fiye da tunanin mai tunani. Nera tayi kuka domin komai yaji citta. Yammata sai kallon Mubeen suke. Shi kuwa gaba d’aya jinsa yake a takure saboda

bayason hayaniya da yawan mutane sosai. (Social phobia). Anci ansha an kuma gyatse. Sai dai muce gwamna Allah ya tayaka riko ya baka ikon sauke alqawarurrrukan da kayiwa jama’a.

WASHE-GARI

Da wuri Muhammad Mubeen ya tashi ya kintsa komai. Ya debi kayayyaki da yawa ya zuba a akwatunan sa. Ya jima a parlor yana jiran mahaifin sa bayan yaci abinci. Gaba d’aya ya lura yanzu mahaifin nasu kulawar da yake basu ta dan ja baya akan da. Saboda yanzun bashi da lokacin zama a jikin suyi hira kamar da. Shiysa ya tsani harkar siyasar da mahaifin nasu ya tsunduma rayuwar su. Lokaci zuwa lokaci yakan saki tsaki yana kallon agogon sa. Sai can daga baya mahaifin nasa ya shigo ciki yana gyara rigar jikin sa.

“Papa...”

“Yes MM ya kake?”

“Alhamdulillah Papa! Barka da safiya!”

“Barkan mu dai...”

Yana fadar haka yai gaba Mubeen ya bishi a baya yana sosa keya,

“Papa zan koma school..”

“School? Oh ai ina ganin zaka iya barin school dinnan Mubeen sai ka zaba wata yanzu bazan hana ka ba..”

“No papa inaso. Nafuson can..”

“Amma Mubeen yanzu fa ba’a zaria muke ba. Kuma bazan iya nisa da kai ba Mubeen.”

“Papa plsss..”

“Meyasa ka canza ra’ayin ka ne Mubeen? Kai fa ka nuna bacin ranka sosai akan makarantar. Meyasa yanzu kake so? Yanzu mun kara nisa da ita Mubeen. Da wahala ace kullum kana tafe akan titi..”

Cewar Haj Ahlaam dake tsaye a matattakar bene tana jiyo su tin sanda suka fara maganar. Mubeen ya dafe kansa yana girgiza shi. Shi kam a rabashi da komai amman banda abinda zai nisanta zuciar sa da idanun sa da malamar tasu. Muryar sa na rawa saboda baya iya doguwar magana yace,

“Mamma, Papa pls kuyi hakuri zan zauna a hostel ko a kamamin apartment pls..”

Haj Ahlaam tai saurin girgiza kai tana sakkowa daga benen,

“A’ah gaskia Mubeen. Kasan ba ishasshiyar lapia ce da kai ba so bazeyiwu kai nisa daga gidah ba gaskia.”

“Fada masa dai. Ai taurin kai ya masa yawa.”

“Ok fine! Zan zauna agidan Aunty Rahila (kanwar Amb Salees) kaji Papa?”

“Shikenan..”

Cewar Amb Salees. Yana gama fad’a ya fice cikin sauri. Haj Ahlaam ta zabga tagumi tana kallon yadda Mubeen ya rikice musu ta rasa meya canza zuciyar sa haka dayake son makarantar yanzu. Bayan ada kullum cikin korafin bayaso yake.

“Meyasa kakeso ka cigaba da zuwa? Ka zabi kayi nisa da gidah. Ya akai haka Mubeen? Shin menene a makarntar yanzu da kake sonta?”

‘Batoul..’

Ya fada a zuciar sa yana taune lebe. A Zahiri kuma ya yamutsa sumar kansa yana zama a gefen kujerar da take,

“Bakomai Mamma! Kawai dai ina enjoying courses dinne. And nayi making lots of friends..”

Haj Ahlam ta ware idanu tana jaddada kai,

“Kai ne kayi making lots of friends Mubeen? Kai taya ma kake bada fuskar da zakai abokai? Karya kake.”

“Allah Mamma.”

“Fine! Allah ya bada sa’a da narara. But duk sanda bakuda lectures ka dawo gidah kaji ko?”

“In Sha Allah mamma.”

Haka dai taita bashi shawarwari hardasu hawaye saboda so da shakuwa. Kannen sama suka tasa shi agaba suna koke koke. Amma saboda tsabar soyayyar malamar tasu ta gama zaga jinin jikin sa ko kadan baiji son zama a gida ba. Sai ma hak’uri

daya babbasu ya harhada kayan sa ya shiga mota direba yaja shi sai zaria. Ba abinda yakeson tozali da shi sai malamar tasu. Ya kuma ci alwashin sanar mata da zuciar sa a koda yaushe.

GIDAN MATA TARA

Na gama kintsawa cikin doguwar rigar atamfa mai zanen jaka baka. Na yafa bakin mayafi ina tafe a kafar bene ina daure agogon dake wutsiyar hannu na. Sauri nake ta zabgawa zan tafi makaranta naci karo da Mari yar gidan Kawu ila da Hinde a soro suna magana kasa kasa. Na musu kallon Allah ya shirya domin yanzu basa kwana a gidah kullum suna gidan magajiya (gidan karuwai) A can suke kwana da kwanaki. Sai lokaci zuwa lokaci suke dawowa gidah. Gaba d'aya sun fita hayyacin su. Sun lalace sun fige saboda masifar neman maza da shaye shaye jikin su duk ya saki. Gaba d'aya tsami suke yi. Bana jiyo mai suke cewa na dai ji kalmar 'lagos' aciki. Na rab'a ta gefen su zan wuce hinde ta janyo mayafi na tana tangarin buguwa,

"Y... Yar kanwata bamu nera hamsin mana."

"Hamsin kawai batoul. Lalubo mana ita."

Na zabga musu harara ina kwace mayafi na. Kunsan dan shaye shaye da rokon balai. Haka suka baje akasa suna rok'ona. Naja tsakin takaici ina binsu da fatan shiriya kafin na zaro nera dari na mika musu. Na fice daga gidan gaba d'aya zucia ta babu dadi.

GIDAN ALHAJI KABEER MAI WAFA

Shi kuwa Haysam tunkarar mahaifin nasa yayi da maganar batoul. Babu bata lokaci kuwa Alh Kabeer yace ya amince zai kuma tasa aminan sa su biyu agaba suje su nemar masa auren batoul din. Murna awajen Haysam ba'a magana. Haka ya dinga kwararowa mahaifin nasa godia cike da farin ciki. Haj Husnah dake labe ta sa hannu a baki ta gatsa tana k'wafa. Tana kallon sanda Haysam ya fito daga wajen mahaifin nasa ya shiga dakin sa ya dakko mukullin mota ya fita. A baya ta bishi tana hango

sanda yake bin batoul da mota harya dauke ta suka tafi. Tamkar tai hauka haka taji. Dakyar ta koma gida tana ‘kissima yadda zata warware shirin Haysam din.

A•B•U

A hankali Haysam ke tafiya da mota yana zubamin kalaman soyayyah. Agogon hannu na na kalla ina murmushi,

“Ya Haysam dan kara gudun motar mu karasa ciki zan makara.”

“Wato ni bana gaban ki kenan ko Mine?”

“Nina isa?”

“Har kinyi yawa ma mine! Nagaya miki dai Abba yace zasu zo gidan ku da abokan sa a cikin satin nan..”

“Uhum..”

“Kiyi magana kinji...?”

“Allah ya kawo su.”

“Ba zaki mana addua ba?”

“Ni kunya nake ji. Nayi a zuciata.”

“Ni kam gaskia kunyar nan na cutata.. Ki rubuta ki ajiye muna aure zan yage kunyar wallahi.”

Ban bashi amsa ba sai dai murmushi kawai dana yi masa. Muka karasa har office dina. Dakyar ya barni na fita daga motar. Muhammad Mubeen dake kallon su tun tahowar su a mota yaja tsaki yana fusgar da iskar bakin sa. Cike da bacin rai ya shige theatre yana rintse idanun b’acin ran ganin yadda take ta faman dasharewa gayen can baki. Amma dole ya fasalta mata zuciar sa shima. Har suka kare lectures dinnan ba fuskanta yake ba. Ayyana yadda zai tunkari malamar tasu kawai yake yi. Kansa sai ciwo yake masa dubada shidin ba lapia ce ta isheshi ba. A daddafe ya sha magani ya nufi ofishinta. Tana zaune akan kujera tana danna waya sai murmushi take yi ya shiga bakin sa dauke da sallama,

“Wa’alaykm Salam!”

Kujera Mubeen ya janyo ya zauna yana kifa kansa akan desk. Dagowa nayi na kalle shi ko lapia?

“Meke damun ka Mubeen? Ka tafi gidah mana..”

Bai amsa ni ba ya cigaba da sauke numfarfashi yana ajiyar zuciya. Na ajiye wayar hannu na ina kallon ikon Allah. Haysam ne ya kirawo ni na daga zan dauka kenan Mubeen yai taku biyu ya karbi wayar yana sanyata cikin aljihun sa na gaba. Nai masa mugun kallo ina mamakin renanin da yayi.

“Meye haka? Bani waya ta..”

“Pls….! Ki bani lokaci.”

“Lokacin me? Bani wayata kafin na mugun sab’a maka. Yaushe rai ni ya shiga tsakani na da kai haka? Tashi ka fitar min a office. Get out! This instant..”

Meyakwan ya fita zubewa yayi a kasa yana zubar da hawaye. Na dafe goshi na ina kallon sa. Da naga abun nasa babba ne yasa na shiga harhada kaya na a jaka ina jan tsaki. A hankali na jiyo shi yana magana cikin yaren su na jiyo sautin saukar numfashin shi akan fuska ta yana cewa,

“irisiwo be’ā‘imiroyē ina belibē wisit’i ānidi bicha newoti፡ be’inē layi mini tets’i‘ino inidasaderu yawik’alu? bech’inik’eti gīzē wisit’i inikwani ፣ kewetirowi yebelet’e irasēni āregagalehu ። benegerochi ina behunētawochi hulēmi k’eleli yale goni yagenyehu yimesilenyali፡ yihi inē kek’edimowi betek’aranī inē inidek’edimowi yalenyi gelelitenya newi ። begeneti libē wisit’i ānite bicha ānidi meli’āki nehi”

Bangaje shi nai zan fita ya rikomin yatsu yana hawaye sosai. Cikin harshen turanci yake cewa,

“You are only one in my mind and in my heart. Do you know the effect you have on me? Even in times of stress, I find myself calmer than usual. I always seem to find the lighter side in things and situations. This is so unlike me, Kin canza ni Ma,

“The pessimist I used to be. You are the only angel in my heart of heaven. Ma. Ina ‘kaunar ki ma z...”

Hannuwa na nasa da sauri ina dafe kunnuwana. Sam banason na cigaba da mafarkin da nake yi. Domin kuwa amafarki na dau hakan. Ko’karin k’wace hannu na yake ya damke hannun sosai yana ko’karin sanya idanun sa cikin nawa, Na samu na fincike zan fuce ya rufe kofar da sauri da dukkanin sauran karfin sa. Hannuwan sa yasa ya sanya ni a tsakiya ya tokare kofar yadda bazan fita ba, Na rasa meyasa kawai ji nayi na fashe da kuka. Na tabbata kukan bakin cikin yanayin da nasamu kai na ne da dalibi na,

“While I might not have the most tantalizing words at my disposal to express my love to you, I will manage these three words (I love you) to let you know that my

world revolves around you all year round. You know how I feel about you, I want you to also know that there is no mistaking in it. My love for you is real and I will love you forever because you are the only one that deserved to be loved this tenderly. Fikre....! Ina miki son kauna Ma! Ina sonki so mai tsanani Ma..”

“Baka da hankali ko kana hauka ne?”

Na fada muryata na rawa. Mubeen yai murmushi yana taune kasan lips dinsa,

“Yes! Inde akan son ki ne ni mahaukaci ne. Soyayyar ki tamin lahani. Bazan iya rayuwa babu ke ba...”

Wani k’arfi ne yazo min na bangaje shi na fuce ko takan jakata da wayata banbi ba. Na fice nai hanyar gate ina salati. Gaba d’aya a hautsine nake. Innalillahi wa’inna ilaihirrajiun raji’un. Dakyar na samu babur na haye nai gidah. Ni kam inaga zan ajiye koyarwar da nake gaskia. Wannan wacce irin musibace? Dalibi na? Wancen yaron? Ko rabin hamshin yayi ne ma? Amman tsabar baida kunya ya kalli tsabar idanu na yace ni yake so? Ina matsayin malamar sa? Shi kuwa Mubeen murmushi kawai yayi ya harhada duk abinda ta bari yasa a jakar sa. Ya kulle mata ofishin. Domin jin sa yake wasai ya sauke abinda ke zuciar sa. Kuma yaci alwashin sai ya cusa mata son sa a zuciar ta.

Batoul kuwa sai data dawo gidah ta dau kudin da take ajiyewa ta bayar aka kaiwa mai mashin din daya kawo ta. Wunin ranar ko abinci kasa ci tayi. Sai data ji dama-dama ne ta sauka kasa zata yi wanka ta jiyo muryar wata mata tana kwarara ruwan bala’i tamkar zata babbaka gidan...

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: □□□□□□_□□□□□□□

43

Tunda wannan abun ya faru na nisanta kai na daga Haysam da kuma Mubeen. Duk abunda zai janyo haduwar mu da d’aya daga cikin su na nisanta kai na dashi. Da makarantar ma na fara fashi sosai. Sai da Innar mu ta tsawatar min tukun sannan nake zuwa. Gidan mu kuwa yawancin kullum sai sun yadamin magana kan yadda Haj Husnah ta kare magana zagi. Tun abun na damu na har yazo ya dena. Nai ta addua har Allah ya cire min shakuwar mu da Ya Haysam a zuciya ta. Kullum sai yazo gidan mu ya aiko kirana bana fita hakama waya sai yai ta kira bana dagawa. Sakonni kuwa kusan kowanne minti sai ya turo. Ganin yadda yake batawa kansa lokaci yasa na shirya sako na tura masa sannan na toshe shi (blocking) ba damar ya kira ni ko turo min sa’ko.

“Assalamu Alaika wa rahamatu Allah wa barakatuh! Ya Haysam barka da dare. Ina fatan kana cikin k’oshin lapia? Ya Haysam da farko inason na miko dimbin godia ta a gare ka. Duk abunda na zama a rayuwa kai ne tushe. Kai ne ka zamto tsani na rayuwa ta. Badan kai ba da banzama abinda na zama ba ayau. Nagode kwarai da abubuwan arzukan da ka yiyyi mana. Kalmomi sunyi kadan wajen nuna dimbin godiar mu agare ka. Fatan mu a kullum shine Allah ya biya maka bukatun ka na alkhairi, Allah ya kare ka daga sharrin masu sharri. Allah ya saka maka da gidan aljanntul firdaws. Ni batoul inayi maka fatan alkhairi a rayuwar ka, Abu na biyu shine zan baka hak’uri. Dan Allah kayi hak’uri ka yafemin, Inaso mubi umarnin iyayen mu.. Duk wanda yabi zabin iyayen sa hakika zai ga dakyau. Allah ya baka wadda tafini komai wadda zata soka ta kaunace ka har k’arshen rayuwar ka.... Bissalam!”

Ina gama karantawa na goge shi tas na kashe wayar tawa baki d’aya. Form din islamiyyar da zan shiga ta matan aure na dakko na shiga cikewa. Ranar asabar da lahadi kawae akeyi kuma da safe. Gwara na shiga na ragewa kai na damuwa idan na shiga cikin mutane.

GIDAN ALH KABEER MAI WAFA

Zaune Haysam yake ya tsurawa screen din wayar sa idanu ko k’iftawa bayayi. Ya kikkira wayar Batoul taki shiga sannan ko d’axu yaje gidan su taki fitowa. Gaba d’aya ya rame ya zabge yayi baki tamkar bashi ba. Damuwa tayi masa yawa, Ya rasa mai yasa Batoul din ke masa haka, Meya canza ta oho? Screen dinne yai haske alamun sak’o ya shigo saurin budawa yayi yana karantawa. Haj Husnah na gefe tana hankalce dashi. Gumi ne ya shiga ketowa Haysam sanda ya fara karanta sak’on. Ya daga kasan rigar sa yana sharce gumin dake kwararo masa. Da sauri ya mike zai fita Haj Husnah tasha gaban sa,

“Zauna babu inda zaka je. Dawo ka zauna.”

“Ummah.. Batoul! Batoul ce Umma”

“Ban isa na saka ba kenan?”

Kansa ya dafe idanun sa sun cicciko,

“Ba haka bane Ummah! Batoul ce ta turomin wani sako wai tanaso mu rabu da juna. Dama kuma ta dena futowa Idan naje gidan su Ummah. Bata daukar kiran da nake mata bare kuma ta maidomin da duk sakonnin da nake aika mata..”

Tsaki Haj Husnah taja tana turo daurin d’ankwalin ta gaba,

“Eh kai ma ka fita harkar ta..”

“Ummah saboda me?”

“Saboda haka muka yanke hukunci da mahaifiyar ta.”

“Ummah gidan su kika je?”

Haysam ya tambayi mahaifiyar sa yana ware idanu hade da zubewa a kasa tamkar wani karamin yaro. Haj husnah tayi murmushin mugunta tana hura hanci,

“Eh gidan su naje..”

Salati Haysam ya fara jerawa yana kwararawa mahaifiyar sa magiyar ta janye furucinta. Haj Husnah ta karo sautin kallon da take tana gyada kai alamun film din na tafiya da ita. Tasa kafa ta shure hannuwan Haysam daya dora a kafafunta yana rok’on ta a gurfane.

“Ummah! Ummah dan Allah! Dan girman Allah umma...”

“Wallahi zan sharara maka mari. Dan bakin munafurci inajin ka da mahaifin ka kana gaya masa ya nemar maka auren ta. Toh indai na isa da kai a matsayi na na wadda ta dauki cikin ka na wasu watanni ta haife ka, Na shayar da kai har girman ka. Inde na isa ina kuma da kima da mutinci a idanun ka inason ka rabu da figalalliyar yarinyar can...”

‘Figalalliya? Yarinya dimir-mir da ita?’

Haysam ya furta ahnkali ashe Haj husnah ta jiyo shi ta saki murmushi mai sauti tana kada k’afafuwa,

“Inde irinsu kake so gasu nan a dangi birjik. Ga sadiyya yar aminiyata maimuna yarinyar nan kamar ita ta kera kanta kuma ubanta commissioner ne. Ga lulu yar Haj Bushra komai yarinyar nan ta hada ance bana zata zama likita, Ga asmau yar kawun ku.. Bama wannan ba da zaka kwantar da hankalin ka kabi zab’in da nake so wallahi daka warke. Domin yar gidan Amb Salees nakeson hada ka da ita. Sakarai..”

“Ummah banason su. Ni wallahi Batoul nake so ummah. Dan Allah kiy..”

“Billahil lazi zan kantsama maka mari, Kaga ja’irin yaro kafaffe. Wallahi zan daga maka su idan dai ba zaka bi magana ta ba. Ka tashi kaje babu ni babu kai.. Kaje gaka gata nan..”

Ta karasa fada tana mai nuni da k’irjin ta. Nanda nan hankalin Haysam sai ya sake dugunzuma, Ya rarrafa ya kifa kansa a kasan k’afafunta,

“Na tuba Ummah! Kiyi hak’uri ki gafarce ni dan Allah... Kiyi hak’uri ummah kinji?”

Wani shegen murmushi Haj husnah tayi tana shafa sumar kan Haysam,

“Ya wuce auta na.. Tashi ga magani can akan dinning table kasha sai ka kwanta. Kaji?”

Gyada kai Haysam yayi yana sharce hawayen dake kwarara a idanun sa. Maganin ya dauka ya shige dakin sa ya barke da wani sabon kukan mai tsuma zuciyar duk wanda ya saurara. Shin ya zeyi zai bijerewa mahaifiyar sa ne ya nemi soyayyar zuciar sa? Dafe kansa yai da hannuwa biyu yana zubar da hawaye da majina. Lamarin dai ba sauki.

•••X••O••X••O•••

GIDAN MATA TARA

Dawowata kenan daga Islamiyya naci karo da Mubeen a kofar gidan mu yana danna wayar sa. Yana hango ni ya kuramin idanu,

‘Dan iska..’

Na fada a hankali ina canza hanya. Ta can baya na biyo ina sake hade rai na amman hakan besa yaron nan ya dena kallo na ba. Ga wani munafukin murmushi da yake yi. Can na hango su Bintalo da Ruma suna tahowa suma zasu shiga gidah, Na shiga tafiya ahankali domin mu shige a tare dasu, Bintalo sai watsa hannu baya take tana dadawa takashin ta duka, Gaishe da Ruma nayi zan shige ciki na jiyo muryar Mubeen na magana,

“Ma..”

Gudun kar su Bintalo su gano wani abun yasa na tsaya ina murmushin yake. Bintalo ta zaro idanu tana kallon Mubeen,

“Dan bature sake dawowa kayi yau ma?”

Gyada kai Mubeen yai yana murmushi. Bintalo ta watsa hannu baya tana mai buga tsakiyar zanin ta,

“Tab sittin ta ubangiji kai kam angama wankewa an baka kasha. Wannan sururucewa har ina? Tun bikin Najeebu kake zuwa gidan nan. Kai bakada mafadi ne?”

Mubeen ya girgiza kansa yana murmushi. Ruma ta janye hannun Bintalo suka shige ciki. Mubeen ya marairace fuska zai yi magana na shiga karkada hannuwa cike da fada na dube shi,

“This should be the very last time da zaka kara tako kafar ka zuwa gidan nan, Sannan ko a makaranta kada ka kara zuwa wuri na kaji na gaya maka. Ka goge number dina kada ka sake kirana ko turomin sak’o.. Wallahi zan mugun sab’a maka. Kaje ka nemi dai-dai da kai mana sai ni? Ko an gaya maka mulki ko sarauta na siyan soyayyah? That aside! Ni ba sa’ar ka bace kana ji na? Na girmeka sannan kai dalibi na ne. Wannan wane irin reni ne fisabilillahi???”

Kallon sa nayi yadda ya tsaya yana kallo na ko motsi bayayi, Ya rame kome yasa oho? Ahankali cikin wata irin murya yace,

“Ma lefi ne? Shin lefi ne don dalibi yaso malamar sa? Kuma kinata zancen shekaru ni kinsan shekaru na ne? Bama wannan ba haram ne soyayya da wanda ka girmewa? Age da shirme ne figures ne fa Ma... Dan Allah ki tausayamin Ma.. Wallahil azim saboda soyayyar da nake miki yasa na kayar da kai na a courses dinki saboda banason na dena ganin ki.. Tun bansan ki ba zuciyata ta san dake. Aduk sanda naga gilmawar ki ko wajen daya shafe ki wallahi sai bugun zuciata ya canza... Ina sonki Ma..”

“Kanada hankali kuwa?”

“bani dashi inde akan soyayyar ki ne..”

Wai ni yaron nan ke gayawa wa’ennan kalaman? Billahil lazi ya gama renani. Naja ajiyar zuciya na sauke ina tunanin abinda zan gaya masa,

“Toh ka nemi sa’ar auren ka. Saboda nakusa aure..”

“Ai ba’a daura ba.. Har yanzu ba wanda yasan mijin ki.”

“Toh inaso ka sakko daga *IGIYAR ZATON* zaka mallake ni. Domin ni da kai ba tsaran aure bane. Ka cire *ZATON* samu na a zuciyar ka kana jina? Kai fatali da duk wasu waswasi da zuciar ka ke ‘kissima maka ni a ranka...”

“*IGIYAR ZATO*?????”

Ya tambaye ni yana murmushi, Na dage gira ina yamutsa fuska,

“Tabbas *IGIYAR ZATO* saboda ka hau *IGIYAR ZATON* abinda ba taba samu zakai ba kana jina? Domin ka hau doron wahala, Igiyar da ba matabbaciya bace. Ka hau *IGIYAR ZATO* toh kayi gaggawar sakkowa daga kai domin ni Batoul ko a mafarki bazan taba soyayya da irin ka ba..”

“idan kuwa hakane bazan taba sakkowa daga *IGIYAR ZATON* son ki dana hau ba. Kece first love dina. Da son ki nake kwana nake tashi, Akan ki gwara na rasa komai na dana rasa ki. Har na gwammace nayi nisa da gidah akan nayi nisa da ke.. Son ki ya rigada ya gama mamaye ilahirin jiki na da ruhi na,

“My love is forever yours. Come rain and sunshine, I will treat you like a diamond and will never let you stay a mile from me. Saboda haka ki sakko daga *IGIYAR ZATON* ba zaki mallakamin soyyayar ki ba. Even if you are far away from me, you will never leave my heart even for a second, My love for you will blossom until my dying days because I have felt purpose and I want to show you, love...”

Jiki na babu abunda yake idan banda rawa. Wannan wacce irin musiba ce? Gaba d’aya jijiyoyin kansa sun fito sunyi rud’u rudu. Zaure na shige ya biyo bayana yana janyo min kasan hijabi, Kasa kallon idanun sa nai. Saboda yanada wasu irin sihirtattun idanu masu wuyar fassarawa.

“Cikamin hijabi....”

“Ma.. Meyasa bakya sona uhm.?”

“Sakarmin hijabi kafin na sab’a maka Mubeen”

“Is it not okay to fall over heels with you ?Uhm?”

“Na shiga uku... Dan Allah ka ky’ale ni..”

“Dan Allah Batoul....Ki so ni ko dan kadanne. I promise to be an excellent lover..”

“Karka sake gayamin irin wadannan kalaman. Ka nemi sa’ar yin ka dai-dai kai kana jina? Kuyi duk abunda zaku yi. Idan kuma aure kakeso to ka gayawa iyayen ka su maka..”

“Hmm’ ma kenan! Ni dama ai da aure nake son ki.. Kuma nan kusa babu daukar lokaci. Babu wacce zuciya ta ta aminta da ita fyace ke.. Amman wait Can’t I date you? Am I that unlikable? Uhm? Ina son ki so mai tsanani.. Dan Allah ki karba kokon barar soyayyata..”

Dogon tsaki naja cike da takaici na dube shi,

“Ka gama?”

Daga kai yayi jiki a sanyaye. ‘Kofa na nuna masa da hannu ina sake hade rai,

“Fita toh! Karka kara tako kafar ka zauren gidan nan da sunan zuwa waje na kagane?”

Shiru yayi yana kallon kasa, Nai ‘kwafa ina shigewa cikin gidah gaba d’aya ya dagula min lissafi. Da yan iskan kalaman sa masu ratsa mutane. Na juya na kalli zauren ina hararar sa. Murmushi yai ya fice yana jefa muk’ullin motar sa sama yana cafewa. Sama na haye na shige daki raina a jagule. Zama nayi a kusa da Innar mu ina sakin ajiyar zuciya,

“Innar mu...”

“Na’amm me sunan uwa!”

Numfasawa nai na shiga raba idanuwa ina harhada hannuwa,

“Innar mu acikin...”

“Na’am acikin me?”

“Innar mu acikin dangin mu na Shema babu wanda za’a iya had’amu aure dashi...?”

Innar mu ta mike daga kishingid’en da take tana rage sautin rediyon ta,

“Meyasa kikace haka uhm?”

Hawayen danake makalewa ne suka shiga zubomin, Allah yasani na gaji wallahi. Abunda Haysam yamin yanacin rai na. Ga yadda yaron nan ke uzzuramin. Ga maganganun da yan gidan mu ke gasamin, Hakama yan unguwa na kirana da sunaye kala kala. Fisabilillahi ya zanyi da rai na??

“Innar mu bakomai kawai gani nake ta hakan ne zan samu mijin aure..”

“Bar kuka uwata, Share hawayen ki. IN SHA ALLAH! Mijin ki nanan tafe, zaki yi aure nan kusa keda duk wanda basu yi ba. Da aure da mutuwa da haihuwa dik lokaci d’aya ne uwata. Wallahi baka wuce lokacin ka, IN SHA ALLAHU! Allah zai zab’a miki mafificin alkairi. Mijin ki na zuwa nan kusa mai sunan uwa. Wani jinkirin alkhairi ne... Bar kuka kinji?”

Daga kai na nayi na shiga share hawaye na ahankali ina jin k’arfi acikin zuciya ta. Kalaman Innar mu sun tausasamin zuciya ta..

••

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: □□□□□□____□□□□□

44

Tunda wa’ennan abu suka faru ashe zukata da gangar jikin mutane uku ba acikin nutsuwa suke ba. Muhammad Mubeen yafi kowa jigata domin baida koshasshiyar lapiar da zuciyar sa zata jure rashin wani abu da yake so. Haka yaita watangaririn neman ganin Batoul amman hakan yaci tura. Shine a tafe kullum zuwa gidan su Batoul amma bata futowa. Gashi Bintalo ta sashi agaba. Muddin tagan shi haka zatai ta sukar Batoul awajen sa. Shi kuwa sai yai shiru har sai tagaji tatafi. A kofar gidan su yake kusan yini duk weekends idan zata islamiyya harta dawo yana hangen ta. Daya hanta hankalin sa zai dan kwanta sai ya tafi gidah. Gashi ko a makaranta bata bari su hadu. Kiran wayar duniya da tura mata sak’onni idan yayi bata dagawa. Ko ta whatsapp tayi blocking’ dinsa sam ya dena ganin statuses dinta da display pictures. Abun na damun sa kwarai matuka, Har ta kai ya fara rashin lapia a tsaitsaye...

Toh haka ma bangaren na Haysam lamarin ba sau’ki, Damuwa tai masa yawa tamkar zaucacce. Kodah mahaifin sa yai masa maganar gidan su yarinyar da yake so sai yace dashi an bada ita gudun karya tsallake maganar mahaifiyar sa. Mahaifin nasa bai kawo komai a ransa ba yai masa addu’ar Allah yabashi wata ta gari. Amman kullum Haysam sai yayi kukan bakin cikin rasa Batoul da yayi na har gaban abadan. Haj Husnah kuwa dadi kashe ta ganin zancen Batoul dai babu shi. Tuni ta

fara cuku-cukun yadda zata hadu da matar gwamna wato mahaifiyar Muhammad Mubeen.

Batoul kuwa gaba ki d’aya ma abubuwa ne suka taru su kai mata yawa musanman yanzu da babu wata kawarta da tayi ragowa wadda batai aure ba. Uwa uba ita kadai ce yanzu tarage ba tai aure ba dubada yammatan gidan mata taran kowanne da nasa a hannu yawancin su.. Gashi ‘yayan Gwaggo Aminatu mata biyun da suka rage bikin su za’ai a satin. Sati na zagayowa Gwaggo ta turo da buses guda biyu aka kwashe su sai kaduna. Anan sukai kwanaki har uku ana gwangwaje bikin yaran na Gwaggo Aminatu.

GIDAN MATA TARA

Tunda aka kammala bikin yayan Gwaggo Aminatu muka dawo gidah sai na kasance tamkar bani ba wallahi. Na rasa mai yakemin dadi? Zanje makaranta na dawo gidah, Asabar da lahadi kuma naje Islamiyya. Ko hira ban cika yi ba acikin su Innar mu. Nafi karatu ko na janyo wayata na shiga whatsapp na dan karanta littattafan da marubutan online keyi.

**** Ranar wata sanyayyar asubahin asabar an tafka ruwan marka-marka muka tashi da tashin hankula har biyu a gidan mu. Tashin hankali na farko shine an nemi Mari da Hinde an rasa. Kaf Zaria babu inda ba’a cigita ba basa nan. Anje gidan magajiyan tasu ma nanma basa nan. Tashin hankali na biyu kuma an sace asusun kudaden da Bintalo ke ajiyewa na mutane. Tun asubahi ta suma ake kwara mata ruwa taki farfadowa. Gaba ki dayan yan gidan mu mun taru akan Bintalo ana kwarara mata ruwa amman bata farfado ba. Cikin haka sai ga Kawu khamis da Dijangala wato shugabar matan gidan magajiya tare da wani ‘dan daudu yaci dauri sai kace mace. Kawu khamis ya zauna a bakin rijiya yana tsatstsafe gumi,

“Fada musu yadda ake ciki malam..”

Dan daudun yai fari yana cokalo daurin d’ankwalin sa gaba,

“Malam fa kace? Ka dube ni ka kira ni Malam? Ka dena ragemin matsayi. Sunana Sahura nice baby..”

Ya k’arashe maganar yana yamutsa fuska hade da watsa hannu tamkar mace. Dijagangala dake gefe ta dubi Bintalo dake sheme,

“Itace babar Hinde?”

“Itace...”

Kawu ila ya bata amsa yana sake kwararawa Bintalo gugar ruwa a fuska. Dijangala ta yamutsa fuska tana bin kowannen mu da kallo,

“Toh Mari fa?”

“Ya tace...”

“Toh abisa binciken da mu kai mungano Hinde, Mari da kuma wasu daga cikin yammatan mu sun tafi birnin ikko (lagos) domin samun manyan alhazawa.”

“Lagos?” Na maimata a hankali ina girgiza kai. Ashe Kawu Khamis ya jiyo ni.

“Kinsan da zuwan nasu ne..?”

Saurin girgiza kai nayi,

“A’ah Kawu.. Kawai dai kwanakin baya can zan tafi makaranta naga Hinde da Marin a zaure naji kuma sun ambaci lagos.”

Yan gidan mu suka shiga rafka salati da sallallami. Kawu Ishaq ya numfasa kafin yace,

“Toh aina suka samu kudin zuwa ikkon?”

“Gaskia ban sani ba. Amman dai kudade masu yawa suka nemo kila. Saboda sai sun kama daki acan ga kudin abinci.. A gaskia bamuji dad’in tafiyar su ba muma. Saboda suna d’aya daga cikin y’ammatan mu dake janyo mana manyan mutane.”

Dijangala ta fada tana mik’ewa tsaye. Kawu khamis ya k’ada kai yana cire aswakin bakin sa,

“Toh kinga mahaifiyar Hinde dake sheme dinnan?”

Dijangala ta daga kai tana bin Bintalo da kallo dake sheme a kasa,

“Toh wallahi uwar adashe ce itace ke ajiyar kudaden yan adashe na yankin yan kasuwa. Ta neme asusun ta rasa gaba d’aya an kwashe. Shine ta suma.”

“Toh fa! Allah ya sawwake. Sury nice tashi mu tafi..”

Dijangala ta fada tana duban dan daudun. Mikewa yai yana botsarewa kamar mace,

“Toh bayin Allah da alkhairi. Allah ya dawo mama dasu lapia. Yan uwana ina lalle da gyaran kai idan zaku yi..”

Cewar dan daudin da suke kira da sury nice. Ni kuwa sakin lebe nai da saleba ina kallon sa. Abun mamaki baya karewa a duniya. Gardeden namiji amman ya maida kansa mace. Ficewa su kai suna shewar su.

Bintalo kuwa tamkar babu rai a tattare da ita. Cikin ikon Allah Gwaggo aminatun da aka kira aka sanarwa halin da ake ciki ta iso hankalinta a tashe. Ba bata lokaci aka kinkimi Bintalo akai asibiti da ita. Alawiyyah da zabbau sai kuka suke yi suma. Likitoci sunyi mai yiwuwa ganin Bintalo ta farfado amman hakan yaci tura. Likitan ya cire safar hannun sa yana kallon mu,

“Wai shin meya faru da ita haka ne? Kawai yanke jiki tayi ta fadi?”

“Dakta tsaya kaji! Baiwar Allahn nan uwar dashi ce. Tana ajiyewa yan kasuwa kudaden adashin su. Wanda idan karshen shekara tayi duk suka dauka zasu babbata kaso mai tsoka. Toh wallahi sai aka dauke kudaden a ma’adanar su. Dama kafin nan an nemi yar ta anrasa. Toh asubahin yau kuma sai ta nemi kudaden bata gani ba. Shine muka jiyo karar ta ta yanke jikin ta ta fadi.. Alawiyyah haka ne ko?”

Kawu khamis ya tambayi Alawiyyah yana kallon likitan. Alawiyyah ta fyace majina da hawayen dake yar tsere a fuskar ta,

“Eh Kawu! Tana ta neman inda ta ajiye bata gani ba. Ta tattambaye mu muka ce wallahi bamu gansu ba. Ashe wai an dauke su ne aka musanya da wasu ba komai acikin su. Kawai muka ji ta saki Kara ta yanke jiki ta fadi..”

“Toh acikin dakin ku take ajiyar kenan?”

“Eh dakta..”

“Toh agaskia hakanne ya janyo mata da babban tashin hankalin da zuciyar ta ta kasa dauka. Yanzu dai sai ta farfado xamu san abinda zamu mata. Amman dai ga ruwa nan an sa mata mun kuma yi mata allurori. Allah ya bata lapia.”

Likitan na gama magana ya kade rigar sa ya fice. Sam Bintalo bata farfado ba sai wajajen yamma ta bude idanun ta ahankali amman ta kasa motsa kowanne sassa na jikin ta. Dakyar take iya nanata,

“Kudi na! Kudi na a asusu shud’i da ruwan toka da na ruwan zuma... Sittin ta ubangiji sai an fito dasu.”

“Kai wannan mata kina ji da kan ki kina maganar kudi kuma? Tab Allah ya kyauta..”

Cewar Baba Ummita. Ta ja majina tana karkada kai hade da sake cewa,

“Yarinyar nan Hinde ita ta ja Mari shiga bankadaddiyar hanyar nan...”

Baba Ummita ta karasa fada tana kwararawa Hinde kwandon tsinantaka. Likitan ne ya shigo d’akin da sauri yana wa Bintalo yan gwaje-gwajen. Bintalo ta sake sakin wata kara tana nanata,

“Kud’i na! Kud’i na a asusu shud’i da ruwan toka dana ruwan zuma.. Sittin ta ubangiji sai an fito dasu.”

Likitan ya tsaya yana kallon Bintalo kafin ya haska wani abu a idanun ta yana girgiza kai,

“Baiwar Allah daga hannun ki sama ko kafar ki..”

Bintalo tayi tayi ta kasa. Gaba d’aya ta kasa motsa wani sassa na jikin ta, Lamarin fa tamkar almara. Mu kai jungum jungum muna kallon ikon Allah.Ajiyar zuciya likitan ya sauke yana duban mu,

“Ina mijin ta?”

“Mijin ta ya rasu dr! Nan dik yan uwan sa ne da ‘yayan sa..”

Gwaggo Aminatu ta fada jikin ta a sanyaye. Likitan ya ka’da kai,

“Manya biyu daga cikin ku su biyo ni ofishi na..”

Yana gaba su Gwaggo Aminatu da Kawu Ishaq na biye dashi. Suka je office d’insa ya xauna yana zayyane musu abunda ya samu Bintalo ya karkare da,

“Toh kuyi hakuri! ta samu mutuwar ‘barin jiki a bisa muguwar faduwar da tayi kuma tanada ciwon sukari. Bayan nan jinin ta ya hau shima...Ta samu hauhawar jini.”

Salati suka fara yi gaba d’aya jikin su yayi sanyi. Sun jima kafin su dawo wajen mu. Inda Kawu Ishaq yace mu tafi gidah ai Bintalon ma sallar su xa’ai. Ai kuwa da yamma aka dawo da ita a nannade acikin tabarma tamkar kayan wanki, Sai surutu take ita kad’ai tana dadara hakoran ta..

“A hayye yau ga gaye ba makilis. Sittin ta ubangiji dole afito mun da yara na su uku, Shud’i da ruwan zuma da ruwan toka...”

Haka Bintalo tai ta surutai abun tausayi wallahi. Ni kam har a sujood sai dana mata adduar samun lapia da bayyanar ku’din nata. Haka muka kwana a gidan nan bacci barawo ne ya d’auke mu. Domin surutan da Bintalo ke zubawa dole su hana mutum runtsawa.

WASHE~GARI

Wajajen sha biyu da kwata saura Ruma tayi sallama tana kwalawa Bintalo kira da alamun batada masaniyar abunda ya faru,

“Bintalo sakko ki karb’i xubin su Shehi na gangaren kasuwa da Mati mai gidan biredi.. Har zan taho muka had’u da shegiyar nan. Nace ah ladiyo anyi abun kai. Wallahi nagaya miki sai ta shiga sunne kai tana sosa dudddugaggen kwakwidon kanta. Yanzu dai zo ki karbi kudaden mutanen nan. D’auka ya kusa zuwa kai na.. Nasan kina nan kina aikin susar takashi.. Bintalo!”

Na rike haba ina ayyana yadda Ruma zata yi idan taji babu kudaden nan. Gashi jia ake fad’ar Mari da Hinde ne suka sace su suka tafi dasu ikko suka musanya mata asusuwan. Baba Ummita dake shararar hawayen barin Mari ta sharce majina tana kallon Ruma,

“Ruma bakisan abunda ya faru bane?”

Ruma ta dora hannuwa a kirji tana ware idanu,

“Waye ya rasu?”

“Mari da Hinde sun gudu an neme su an rasa... Kuma”

“Kuma me?”

“Bintalo ba lapia tasamu mutuwar barin jiki.”

“Toh fa subhanAllah. Tana ina?”

“Tana dakin ta...”

Cewar Baba Ummita! Kowa yai shiru ya kasa gayawa Ruma gaskiar lamari. Ruma ta haye sama tana yan sallallami,

“Sannu Bintalo! Dankari Mak’ari! Sannu! Ina asusun suke na tafi dasu kawai tinda ke ba lapia.?”

Bintalo na hangen Ruma ta fashe da kuka tana kikkifta idanu. Ruma ta zauna a gefe tana rufe hancin ta. Ganin yadda Bintalo tayi face-face da katifar tayi fitsari akwance sai zarni kuma su Zabbau basu gyara ba. Ruma ta muskuta tana kallon Bintalo cike da tausayi,

“Garin yaya haka tafaru Bintalo? Ko akan tafiyar su Hinden ne...?”

Bintalo ta fashe da wani kukan tana k’ok’arin girgiza kai alamun a’a. Ruma taja ajiyar zucia ta sauke tana dudduba lungu da sakon da zata gano asusuwan.

“Sannu Bintalo! Allah ya sawwake. Dama akace idan baka mutu ba ba agama maka halitta ba. Ko a dad’a ko a rage ka... Ina asusun suke ne?”

Zabbau ta shiga harhada yatsu tana kallon Ruma ta gefen ido,

“Kiyi hak’uri baba Ruma..”

“Uhm babu komai zabbau! Allah zai tashi kafadunta ai ku za’a bawa hak’uri yanzu.”

“Ba wannan ba..”

Ruma ta kada kai alamun son jin bayanin gaba. Zabbau tasa hannunta akai ta shiga sosa wa tana in’ina..

“Baba Ruma walle talle bankin kudi dai an sace hi..”

Ruma ta mike tana sosa kunnenta,

“Kika ce me?”

“Ca nai an sace su. Walle babar mu batada masaniya akai. Mari da Hi...”

Ai bata karasa ba Ruma ta zube tana firfita fuskar ta da takalmi alamun ta shiga kololuwar balai. Gumi ne ya shiga tsattsaga a ilahirin jikin ta. A zuciye ta mike ta cakume wuyan Bintalo tana jijjigata gefe d’aya kuma ruwan balai da zagi take zuba mata,

“Kutmelesin kan babban bala’in bolar jakara. Billahil lazi ba yadda zamu yi ba. Kai idan gidan nan zaku siyar na rantse da Allah sai kin biya kudin mutane. Munafuka, Algunguma, Munasura, Yar bakin ciki da hassada. Har zaki kwanta cutar karya bayan kin cinye kudin mutane?...”

Bintalo ta shiga kakari saboda yadda Ruma ta shaketa tana jijjigata. Gaba d’aya yan gidan mu kowa ya fito yana kallo wasu suna leken dakin nasu. Alawiyyah ta fashe da kuka tana janye Ruma. Cikin zafin nama Ruma ta dauke ta da mari tana huci,

“Idan kika kara rik’e ni sai na hallaka ki wallahi. Kaga yan iskan mutane, Ayi muku dare kuyi ma mutim rana? Ringidi-ringidi gantalalliyar mahaifiyar ku tazo ta same ni na temaka mata. Na shiga na fita na samo mata ta zama uwar adashe. Sai data bari an tara himilin kudi za’azo min da maganar banza? Ni za’a damfara wai kudi an sace?..”

“Walle talle baba Mari da Hinde ne suka sace..”

Zabbau ta fada tana rausayar da kai. Ruma taja tsaki tana d’aure mayafin ta a kugu cike da balai ta watsa hannu baya tana buga zani,

“Kalar ku kalar mahaifiyar ku, Algungumai marasa amana. Ni zakuyi wa baraki? Wallahi sai anfito da kudaden mutane. Ba yadda zanyi ba. Ke Bintalo kinsan na dameki a rashin mutinci na shanye billahil lazi.”

Kawu ila ya jinjina kai yana bata hak’uri ta watsa masa kallo tana kada masa hannuwa,

“Da hak’uri yai gabas yamma nayi bakin munafiki. Munafukan banza da wofi. Wallahi sai kun biya ni kudaden mutane. Babu abunda ya dame ni. Kudaden mutane ba zasu ciwu ba. Yan iska marassa mutinci..”

“Ahayye kayya kai! Naci biredi na yage leda hehehe! Banci naninba nanin ba zata ci ni ba. Ilyasu da bintalon dai keda hakkin biyan ki tunda sune iyayen su..”

Baba usaiba ta karasa fada tana dukan cinyarta. Kawu ila ya dankara mata harara yana mai da kallon sa ga Ruma,

“Baiwar Allah babu ruwana wallahi! Bintalon dai itace zata biya ki ko kuma Ummitan mahaifiyar Marin.”

Baba Ummita ta buga tsallen albarka tana buga kirji,

“Da Mari aka kawo ni gidan nan? Ni kadai aka wanko daga wajen budar kai aka kawo ni, Billahil lazi sisi na ba zaiyi ciwo ba. Kai ne ubanta meyasa bakasa ido akanta ba? Kai zaka biya wallahi.”

Kawu ila ya shiga cire yar sharar rigar sa zai daka baba Ummita kenan Gwaggo Aminatu ta shigo cikin gidan mu tana tsawatar musu...

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😈□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: □□□□□□___□□□□□□□

45

“Kai Kai Kai! Haba ya isa. Wallahi tun daga bakin titi ake jiyo hayaniyar ku, Ku yanzu fisabilillahi ba zaku dena wannan abubuwan ba? Wannan wacce irin rayuwa ce kuka d’orawa kan ku? Allah ya sawwake..”

Haka taita nanatawa har ta hawo bene. Ta dubi Kawu ila dake kokarin mai da rigar jikin sa,

“Sannu ilyasu! Da wa zaku daku?”

“Da Ummita ne Yaya.. Ta renani. Agaban mutane take min rashin kunya.”

“Ba haka bane Yaya. Shine nan ike cewa wai da ni za’a biya Ruma kudin da aka sace.”

Baba Ummita ta fada tana dankarawa kawu ila harara. Gwaggo Aminatu ta jinjina kai tana kallon Bintalo,

“Tab sannu Bintalo. Allah ya baki lapia. Yanzu kudaden da kuke magana angano wanda ya sace su ne?”

“Eh Mari da Hinde ne Yaya..”

Kawu Ishaq yabata amsa yana cire tagumin daya zabga. Ruma taja tsaki tana jijjiga kafadu,

“Billahil lazi sai an biyani kudaden mutane. Babu abunda yasha min kwalar riga.”

“Baiwar Allah ke kuma wacece?”

“Ni ce wadda tai silar samawa bintalon zama uwar adashe. Kuma ina cikin masu zubin, Shine zaku zo da wata bazawarar magana wai kudade babu? Wallahi ba za’a damfare ni ba. Kudi yadda suke cis sai an fito dasu.”

Gwaggo Aminatu ta zabga tagumi tana kada kai,

“Innalillahi wa inna ilaihir raji’un! Wallahi sai dana bawa Bintalo shawarar tadena ajiye himilin kudaden nan agidah saboda tsautsayi. Kai ya SubhanAllah!”

“Oho dai! Can ta matse muku a matse matsin matsalolin ku. Ita tace zata iya ta dage sai da aka bata. Mu dari ne keyin adashin nan. Kinsan himilin kudaden da aka

tara kuwa? Na rantse da Allah ko mutuwa Bintalo zata yi sai an biya kudaden nan a yau.”

“A yau fa kika ce? Baiwar Allah duk cikin mu nan bamu da masaniyar sanda kuka gama maganar adashen ku. Da ita ku kai komai, Ko kotu akaje wallahi bamu da lefi.”

Gwaggo Aminatu ta bata amsa tana murmushi, Ruma ta sake jan wani tsakin a karo na ba adadi tana jijjiga kugu,

“Oho dai. Yanzu dai ya ake ciki. Yanzu zaku harhado ku bayar ko sai da yamma? Dan a yau za’a biya mu kudaden mu. Ko mu kai kara folisitehen..”

Gwaggo Aminatu tayi shiru kafin ta sauke nannauyar ajiyar zuciya,

“Idan nace miki zamu iya hada kudaden ku mu baki na miki k’arya wallahi, Saboda babu wanda zan tursasa ya biya abunda ba dolen sa bane kowa yana ji da kansa. Saboda haka zamu yi meeting da yan uwan mu gasu. Duk yadda ake ciki zamu kirawo ki kiji. Allah ya kyauta..”

Ruma ta kwararo rantsuwa ta dire tana karkada hannuwa,

“Wallahi kudade ba zasu sha ruwa ba. Yadda suke sai an biya su tas, Marasa mutunci..”

“Dakata baiwar Allah! Yanzu zamu iya nannade hannuwan mu mu barki ke da ita domin sanda kuke abinku ba masaniyar wani acikin mu. Zancen a had’a kudi a biya ma wallahi bai taso ba. Domin babu wanda zamu yiwa dole bama wannan ba bamu mai k’arfin iya biyan ku wannan kudaden. Kede yadda ake ciki kyaji kawai.”

Ruma ta buga zani tana dankarawa Bintalo harara ta karasa kusa da ita tana huci,

“Bara na miki yadda zaki fi ganewa bakar algunguma, Sittin ta ubangiji sai kin biya ni kudaden mutane. Shegiya maras mutunci wadda ba Allah a ranta. Muguwa uwar bakin hali, Kishiyar ki da yaranta kin sasu agaba kina musu mugunta da zagon kasa sai gashi a kanki komai yake k’arewa kinsamu mutuwar barin jiki. Wallahi inde kudi basu fito ba sai kin biya ni ko da tsiya-tsiya...”

Tana gama fa’da ta fice tana huci tana sake nanata,

“A kuma kirawo ni anjiman dan billahil lazi kudade ba zasu ciwu ba.”

Gwaggo Aminatu ta girgixa kai kawai tana kallon kowannen mu,

“Shi yasa ake cewa idan zaka gina ramin mugunta gina shi gajere saboda zata iya kasancewa kai zaka fada. Idan ka gina shi mai zurfi ma kai zaka fada, Ya kamata ace kuyiwa kanku karatun ta nutsu, Rayuwar nan ba matabbaciya bace wallahi kana zaune lokaci kankani zaka jika cikin rami ba ranka an shafe ka a rayuwar duniya. Akan me zaka tsaya kana jifan dan uwanka da sharri? Shi fa sharri wallahi dan aike ne duk inda zai je ya dawo sai ya koma kan ka ko wanin ka,

“Abinda kuke bakwa kyautawa musanman Bintalo da kai Ilyasu. Ku duba ku gani gaba d’aya acikin gidan nan rayuwar ku biyu dinnan tafi ta kowa watangariri. Ilyasu dubi kwana ki yadda shagunan ka suka kone gaba d’aya jarin ka da abunda ka mallaka ya lalace. Tun yaran nan na kaltume na kanana kake tsangwamar su da kyararsu, Ka kori Najibu ni banda masaniya ma sai daga baya. Wai zai afkawa kanwar Bintalo yanzu gashi Najibu ya zama wani abu a rayuwa yayi karatun sa ya samu aiki har yayi aure da gidan sa. Islahan da kuka ha’da baki da ita ina kwanakin baya akace tayi cikin shege an zubar har anzo daurin aurenta aka fasa?,

“Yanzu wa sharrin ya komawa? Bayan nan Ilyasu kaita had’uwa da masifu na rayuwa baka daddara ba ka sake matsawa Batoul ka hanata zama da samarin kwarai, Ka kore su tas. Kana jajibo mata wasu daban. Ta haka ka ha’du da gamon ka. Satin ka uku a chaji ofis ilyasu. Duka ba wanda ba’a maka ba. Da gande-gand’e aka samu aka futo da kai. Kasan ya akayi? Toh bari kaji dakunan ka guda biyu da

parlor an siyar, da su aka biya maka bashin kudaden da Alhajin ke binka.. Domin wanda muka harhada bai isa ba.”

Kawu ila ya dafe kirji yana ware idanu,

“Siyarwa fa kikace Yaya, uban uban waye ya siya?”

“Zage ni Ilyasu nagode.”

“Ba zagin ki nake ba Yaya. Meyasa za’a siyar min da hakk’i na ba tare da masaniya ta ba?”

“Amma bakada mutinci ko kad’an Ilyasu, Wa kake jira ya biya maka da? Banda ma zumunci da zuciyar musulunci ka isa mu biya maka? Toh a tak’aice dai da mu kai shawarwarin mu ba mafita yan kudaden da muka ha’da basu taka kara sun karya ba. Agaban shedu akai liman hamza da barrister kb. Muka roki Najeebu dan gidan Kaltume alfarma ya siye daki mai ciki da parlorn, wancan wanda babar su basmah ke ciki kuma shima muka mai kudi Najeebun ya siya muka biya maka bashin da marigayi salisu ke binka muka bawa iyalan sa gadon su...”

Kawu ila ya zube a kasa yana zunduma ihu,

“Inaaa ba zai yiwu ba wallahi..”

“Wallahi mai yiwuwa kuwa ta yiwu, Banda abinka da bamuyi maiyiwuwar ba mun ro’ki yaron ya siya kai ka isa ka fito daga chaji ofis d’inne? Wallahi akotu zasu maka ka. Yaro dan arziki dan kirki ma da yace shi kar ace ya siya saboda ya bar maka ka cigaba da zama har karshen rayuwar ka. Kawai dai daku na mallakin sa ne.”

Kawu ila ya shiga birgima yana koke koke. Ni abinma ya daure min kai? Don wallahi bansan da maganar nan ba kwata kwata banida masaniyar Yayan mu ne ya biya

kudin wajajen. Gwaggo Aminatu ta shiga fiffita da mayafinta. Saboda yadda aka taru aka rufar mata akai. Gashi dakin ba iska.

“Sannan kema Bintalo da sannu kike girbe abinda kika shuka, Duk kulle kullen da kike akan kaltume tun bata hayayyafa ba harta fara hayyayyafa yaran ta har suka girmaa suka mallaki hankalin kansu baki dena ba, Yanzu yau ina Najeebu shin meya zama a rayuwa? Kun kore shi yayi hak’uri yai karatu ya zama wani a rayuwa gashi har yayi aure. Batoul gatanan kaf gidan nan babu wanda ya kamo ko farcen ta ne a ilimin addini dana boko, Gashi nan aiki take da sannu gashi nan itama ta zama wani abun. Duk abunda kike kulla musu akan yayan ki yake karewa daga ke har ilyasun,

“Ba sharrin da baku yiwa Batoul ba akan ciki da sauran su, Sai gashi Hinde da Alawiyya su suka fara kwaso abin kunya, Alawiyyah ta samu cutar shan inna, Hinde kuma harda rabon ciki gashi nan ta haife shi. Zabbau ma gashi nan mijin ta ya saketa har saki uku yace yaran kuma ba nasa bane. Yanzu dubi abunda ya faru dake Bintalo duk fa Allah ne yake sakayyar sa tun anan duniya. Bama wannan ba daga ke har ilyasun gaba d’aya ‘yayan ku bame cikakkiyar tarbiyya. Ace wai har Mari da Hinde sun san zaman kansu agidan karuwai? Suna bada jikin su ana zina dasu? Kuma su kawo muku kudi ku amshe? Nan fa zan taho gidan nan kwana ki motar mu ta baci mun tsaya a gareji sai ga Mari a tsakiyar maza tana shewa suna babbaka daria,

“Nazo na maka magana Ilyasu kace min wai tana temaka muku ne shiysa. Yanzu ai ga irinta nan. Kwadayin ku ya kai ku ya baro ku. Sun kwashe kudaden Bintalo sun tafi lagos zaman karuwanci. Duk inda kuka fita dole a nuna ku ana zund’en ku. ‘Yayan ka tara Ilyasu kowanne da bakin ciki da yake cusa maka, Yazeedu da shafi’u sun zama barayi, Mariya ta zama karuwa ta shahara ma tabar garin, Narata yarinyar nan kunce bata dawowa gida sai dare itama. Walidi kuma ya gama renaku kana fada yana mayar maka ga shaye shaye, Basmah an mata fyade itama duk akan rashin basu ishashiyar tarbiyya ne. Kuna barin su suna fita ko’ina cikin dare, Ya kwakwume muku su ya musu fyade itada Fareeda danma Allah yasa anmata aure ita,

“Ga wasu yaran kanana kana dasu duk mata, Furera, Bushra, Mardiyya. Yayan ka mata shida rigis ga maza uku kowanne da bakin cikin da suke sanya maka, Haka kema Bintalo naki gaba d’aya ma mata ne. Amman dukkanin su bana kirki ciki harda Hauwa’u itama naga ta zama kamar Hinde. Gaba d’aya ku duba ku gani rayuwar ku data yayan ka dik abunda kuka shuka ne kuke girbar sa. Matan ka sun

guje ka kowacce zaman yayan ta take, Yaran ka suna ciyar da kansu. Yanzu ku dubi Bintalo ha’ula’i ne da ta samu kanta aciki duk kuwa da tata qaddarar kenan amman ai komai yana da sila. Toh haka rayuwar take wallahi kana ji da kanka ma yaka kare ballatana kana d’aukar hakkin wani, Haka abun yake wallahi inde zalunci kasa a gaba toda sannu zaka girbe shi tas. Saboda shi zalunci ko yaya mutum ya zubda hawaye ko ya kai karar ka wajen Allah to fa adduar nan batada hijabi ga mai sama sai yayi sakayya ko anan duniya ko a lahira,

“Yara goma sha tara ne agidan nan cif amman gaba d’aya yaran kaltume ne suka fita zakka kama daga tarbiyya, Ilimi da kuma sanin yakamata. Wallahil azim shiysa rayuwar su ke tafiya dai dai kullum ci gaba suke yi. Nasha kiran ku a’boye ku Ishaq da khamis da Dawood na muku magana akan ku tsawatar ku tsayar da lamarin nan duba da nidin ba anan nake ba amma kukai biris, Duk shiysa komai ya shafe ku tunda da sanin ku ake komai ku zauna yaro karami acikin mu yana juya ku saboda yana da dukiya ko? Yanzu ina dukiyar tasa! Kudin ma kun juya masa baya saboda yana cikin halin rashi yanzu, Shiysa ku kanku rayuwar taku data yayan naku gatanan itama sai a hankali ne. Ishaq yaran ka biyu mata Larai da Talatuwa suma har yanzu ba wanda yai aure acikin su, Ba karatun ba bokon sai neman magana a unguwa. Kai kanka baka da tsayayyen aikin yi sai jiran shago,

“Kai ma Dawood hakan take kai a komai ma ba abunda ya da meka ciki harda bawa yayanka tarbiyya kuwa. Tun sanda ka rasa aikin ka ka zama tamkar sullutu wai abincin cefane ma sai matar kace zata futa ta nemo. Yaran ku kunki tsayawa ku inganta rayuwar su, Fareedah da ita aka hada akai wa fyade donma Allah ya temaka kun aurar da ita, itanma dai ance ta kamu da ciwon yoyon fitsari. Fareed kuwa yana biyewa su yazeedu suna daukewa mutane kaya da kudade. Sam ba tsari a lamarin shin wannan ba hakkin wanda kuka sa agaba bane?,

“Khamis kai ma duk tare kuke har gwara ma Dawood shi bai cika magana ba, Amman shirun ma ai lefi ne. Yanzu dubi kwanaki nan akace Yusha’u ya sace kudin bintalon ashe shi da yaran Ilyasu ne. Bala ma ya zama dan chaburos? Kullum yana tafe yana tangalin maye.. Shin dan Allah ku gayamin rayuwar ‘yayan waye ke tafiya a mizanin gaskia? Me suka muku kuka tsane su haka? Shin wannan wacce irin tsantsar qiyayya ce? Gwara kowa ya sani. Tun da ran salis kuka tsani ya auri kaltume duk dan yafi samin alheri acikin ku, Kuma alokacin mahaifanta sune masu hali. Iyayen mutunci da karamci suka ri’ke ku a garin nan tamkar wanda suka haifa, Ya nemi auren yarsu suka bashi ba tare da sun hana ba saboda karamci irin nasu,

“Akai auren kuka tsawwala mata, Shekarar farko kuka fara yanyana maganganun juya ce bata haihuwa. Kuka sa ala dole ya auro Bintalo, Kuka uzzura kaltume ta tatafi gidan su ashe da shigar ciki ta dawo ta haife danta kukace ba dan Salisu bane na shege ne, Hakama haihuwar Batoul itama kuka shegenta ta, Me suna na ce kawai ta haife ta anan. Amman kowacce haihuwa sai taje gidan su saboda tsabar uzzurawa da mugunta irin taku. Sai ‘karairakin maganganu kuke yi wai ‘yayanta shegu ne. Wallahi tallahi kuji tsoron ALLAH musanman Bintalo da Ilyasu. Duk ku kuke fara haddasa komai,

“Bayan Bintalo ke kin manta halaccin da akai miki aka auro ki. Abun kunya fa kika aikata har an zauna daurin auren ki aka fasa. Aka dubi zumunci muka rufa miki asiri Salisu ya auro ki. Amman tunda kika shigo gidan nan kike neman raba shi da matar sa ta sunnah, Wai har kike shegen ta yaranta da neman fidda ta daga gidan ta na sunnah. Abar dai kaza cikin dakin ta domin tashin tashi na bata da dadi, Sai mu kwana mu wuni ana maida zantuka kuma dik marassa dadi. Duk dai gashi nan kowannen ku yana ganin sakayyar kaltume da yaranta akan sa. Kuyi gaggawar neman yafiyar su. Wata kila Allah ya dube ku da idon rahama idan suka yafe muku, Sannan maganar kudaden adashe kuma bansan yadda zamuyi ba dake ba Bintalo, Abunda nasan zamu iyayi shine kawai zamu sanarwa yan uwanki, Sannan zamu harhada kayan dakin nan yan gwangwan su siya, Zamu baki yan awanni keda ragowar yaran ki kuyi shawara dasu, Nan dakin da rabin na tumunin takarbi idan da akwai wanda zai siya a gidan nan toh sai mu siyar masa, Muma zamu harhada dan abunda aka samu sai abawa matar, Idan kinada wasu ajiyayyun kudaden ko kadarar suma ki kawo a biya su. Ke kika san yawan kudaden mu ba sani mukai ba, Bara mu baku wuri. Ke Zabbau da Alawiyyah ina Hauwa’u kuzo kuyi shawara da mahaifiyar ku. Sanda Allah yasa su Hinde suka shiryi suka dawo sai asan yadda za’ai.. Allah ya rufa asiri. Mu basu waje ko?”

Gwaggo Aminatu ta karasa fada tana mikewa tsaye. Na sharce hawaye na ina girgiza kai. Tabbas an jima ana zaluntar mu agidan mu. Sai gashi yanzun d’aya bayan dayan su suna gani akan su dakan yayan su. Lalle Allah buwayi ne gagara misali. K’asa Gwaggo Aminatu suka sauka ita dasu Kawu ila dake mitar yayan mu ya sai wajen sa. Ni kuwa d’aki na shige zucia ta cike take da maganganun gwaggo Aminatu.. Ba a wani d’auki lokaci sosai ba Zabbau ta sauka wajen su Gwaggo. Ina ga sun yadda da yadda gwaggon ta tsara, Domin tuni Alawiyyah ta zura mayafi ta kira yan gwangwan sukai wa kayan dakin Bintalo kudi suka dauke su duka suka biya kudin. Gwaggo ta kira Innar mu kasan mai suka tattauna oho naga dai Innar mu ta dauki kudaden ta na cikin kwalla ta koma. Daga nan kuma suka hawo saman inda gwaggon take sake cewa,

“Toh Alhamdulillah kamar yadda na fada d’axu mun gama magana, Dakin da Bintalo da Kaltume yake a matsayin tumunin takabar su yanzu na roki kaltume ta siye shi ya zama mallakin ta. Sannan ni na siya dakin nan na Bintalo agaban shedu ga kudi a account dina, Sannan zan kara wasu wanda nai niyya saboda zumunci. Ishaq da Khamis ma sun bada dubu biyu gasu. Ke Bintalo baki da wata kadarar a kasa?”

Bintalo ta barke da kuka tana jan majina,

“Ba ni dasu Yaya..”

“Toh fa! Ni dai nacewa Zabbau yanzu tazo tatafi kod’e ta sanarwa yan uwanki suma su dan tallafa a harhada a bada wani sashen dan wallahi bansan ya za’ai ba..”

Shiru tamkar ruwa ya cinye gidan mu haka akai dif na yan wasu mintina, Da alamun kowannen mu ya tafi tunani. Cikin haka zabbau ta shirya ta tafi kano kauyen lahadin makole can cikin rugar kod’e. An dau tsawon lokaci kafin ta dawo tun wajajen 11 saura kwata na safe ba ita ta dawo ba sai shida saura na yamma. Ta dawo hajaran majaran tana haki,

“Walle talle Gwaggo sunce babu ruwan su, Wai ai bata neman su duk tsawon hekarun nan sai yanzu? Dak’yar ma wallahi suka bani ruwa na hya. Dantakibiruwa ne kawai ya bani wannan..”

Zabbau ta karasa fada tana mikawa Gwaggo wasu kudi sun cuccure da juna, Yan ishirin da yan hamsin. Gwaggo ta kada kai ,

“Dantakabiruwa da suke uba d’aya dai?”

“Hi dai..”

“Sana’ar meya ke ma?”

“Rake ike siyarwa..”

“Allah sarki gashi ya bayar dari biyar cif. Angode Allah ya saka masa da alkhairi. Bintalo kinga irin ta, Yan uwan ki da kuke uwa d’aya uba d’aya ma sunki temakar ki saboda kin yanke zumunci dasu, Sai wanda kuke baba d’aya ne yaba ki. Bayan irin bak’ar muguntar da kika yiyyi masa, Har kaduna yaje yake gayamin. Allah dai ya kyauta kawai.”

Gwaggo ta fada tana d’aga kudin yan ashirin guda goma da yan hamsin guda shida. Direban ta ta kira awaya tabashi atm card dinta ya ciro mata kudi, Ta harhada dana wajen Innar mu da na kayan dakin Bintalo da aka siye, Sannan ta kira Ruma ta bata,

“Iya abunda Allah yasa muka hada kenan, Sauran abunda bai samu ba sai kuyi hakuri sai nan gaba idan Allah yabata lapia?”

Ruma taja tsaki tana watsa hannu baya,

“Sai na jira ta samu lapia? Wannan ai ba zata tab’a tashi ba. Ta rigada ta gama tashin aiki kuma. Kinga hajia ku biya ni kudade na kawai.. Babu wani xancen sai nan gaba. Babu wannan harkar a dishinari na ehe..”

Gwaggo Aminatu ta mike tsaye tana gyara zaman mayafin ta,

“Duk abunda kika ga zakiyi sai kiyi, Da kinsan ta yadda aka harhada wannan kudin na hannun ki da kin sha mamaki. Naga alamar jirgi d’aya ne ya debo ku keda ita. Toh mu dai munyi iya yin mu..”

“Toh billahil lazi na bada kwana ki uku rak dole abiya ni saurin kudade na.”

“Duk yadda zakiyi kiyi baiwar Allah!”

Gwaggo Aminatu tace da Ruma haka. Ruma taja tsaki ta figi mayafin ta ta fice tana masifa. Gwaggo ta tab’e baki tana jinjina kai,

“Allah yasa hakan ya zamto muku iznah agare ku. Sai ku gyara ku nemi yafiyar wanda kuka zalun ta. Ku kuma tuna zumunci ba abin yarwa bane. Allah ya kyauta ni zan koma. Bintalo Allah ya baki lapia..”

Gwaggo Aminatu na gama magana tai kasa tana rataya jakarta. Har waje muka rakata muka mata sallama ta tafi. Mata mai mutinci da karamci kenan. Duk duniya idan na cire iyaye na banida na biyu fyace ita. Bayan magriba yan gwangwan suka zo suka kwashe kayan dakin Bintalo duka ko tsinke babu abunda suka rage. Ina jiyo sautin kukan ta dana yaran ta, Cikin kuka take rokon su su temaka mata tai fitsari,

“Zabbau fitsari! Kinji Zabbau! Alawiyyah zanyi fitsari.”

“Walle nagaji bazan iya tahi ba. Sau hi kawai a haka.”

Zabbau ta bata amsa tana karkada kafafuwan ta. Alawiyyah kuwa cikan ki bata ce mata ba. Wohoho rayuwa, duniya kenan! Duk wanda ya d’aura da ita yai gaggawar kunce ta. Domin duniya tamkar rawar yammata ce na gaba ya koma baya duniya makaranta. Allah kasa mu dace.. Ni kuwa daren ranar gaba d’aya raya shi nai da sallolin nafilfili ina rokon Allah ya kara karemu daga sharrin masu sharri. Ya kuma biya mana bukatun mu na alkhairi..!

•••X•••O•••X••••O••••

“Mubeen! Mubeen! Mubeen!”

Haka Aunty Rahila kanwar Amb Salees ta shiga kwalawa Mubeen kira ganin yadda abincin da yace a zuba masa yake sandarewa, Shi kuwa Muhammad Mubeen alokacin yana dakin sa ya takure waje d’aya yana dafe da kirjin sa dake barazanar fadowa kasa. Sai wani wahalallen tari yake yi ahankali. Ganin bai fito ba yasa ta mike ta shiga dakin da yake. Tana shiga taja tayi turus tana dafe kirjin hade da callara karar neman kawo dauki,

“Wayyo Allah!! Gwaggo nashiga uku.”

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□[9/16, 11:29 AM] □: □□□□□□_____□□□□□

46

Mahaifiyar su Malama Adama Modu wacce suke kira da ‘’Ya” Itace ta shiga dakin hankalin ta a matuk’ar tashe.

“Meya faru dashi?”

“Ya wallahi bansani ba. Dazun nan fa na gama magana dashi akan abinci nace sai yaci dole. Yace a zuba mishi shine kuma shiru-shiru bai fito ba. Na shigo na ganshi haka..”

Aunty rahila na magana jikin ta na rawa, Yayyah Adama ta karasa wajen Mubeen tana tana taba goshin sa,

“Muhammadu! Kana jina?..”

Shiru Mubeen bai amsa ba. Gaba d’aya ya tukwikwiye jikin sa yayi zafi rad’au. Tashin duniyar nan anmasa ya’ki motsa jikin sa. Ganin haka yasa hankali tashe babban ‘dan aunty rahila ya sungume shi yasa a mota suka tafi asibiti. Temakon gaggawa aka fara bashi amman lamarin yaci tura. Likitan ya shiga office dinsa su Aunty Rahila na biye dashi. Ya shafe gumin goshin sa hade da bubbuga biro a teburin sa yana duban su Yayya Adama,

“Wacece mahaifiyar sa acikin ku?”

“Dr ni kanwar mahaifin sa ce, Wannan kuma mahaifiyar mu ce..”

“Toh Masha Allahu, Dama yana da dadaddiyar rashin lapia ne? Tun yaushe kuka same shi a wannan yanayin?”

“Gaskia Dr iya sani na dashi bayason abinci, Sannan da a Ethiopia suke, Toh akwai wata shekara da muka je kasar, Anan muka same shi bashida lapia Dr din yace a dena bata masa rai..”

“Okay... Shekarar sa nawa kenan yanzu? Yayi talatin?”

“A’a gaskia bai yi ba..”

“Toh a zahirin gaskia yaron ku yana fama da matsananciyar rashin lapia data yiwa gangar jikin sa da zuciyar sa mugun kamu. Gashi chronic ulcer taci karfin sa. Ya akai kuka bari matashin saurayi haka ya samu wa’innan mugayen cututtukan?”

Yayyah Adama da Aunty Rahila suka kalli juna kowannen su cike da mamakin kalaman likitan. Likitan ya kara numfasawa kafin ya cigaba,

“Inde har baku yi gaggawar bashi abinda zuciyar sa da gangar jikin sa ke muradi ba to akwai matsala gaskia..”

“Toh zan gayawa mahaifin sa yadda ake ciki..”

Likitan ya sake kallon su Yayya Adama yana kafa robar ruwa a bakin sa. Sai da yasha mai isar sa kafin ya cigaba da ce musu,

“Mahaifiyar sa da mahaifin sa sun rabu ne?..”

Aunty Rahila tai hanzarin kada kanta,

“Aa suna tare.. Shi karatu yake yi anan dinne a gidah na.”

Meyakwan yai shiru sai ya sake jeho waata tambayar. Kilan a tunanin sa riko a kewa Mubeen wanda ake takura masa dinnan da har hakan ke cin sa a ransa.

“Ya akai baya karatun awajen su..?”

Yayyah Adama ta cire tagumin data zabga,

“Kaga dakta! Mahaifin yaron nan shine gwamna mai ci na kaduna a yanzu, K...”

Bata karasa ba likitan yamik’e tsaye yana dafe da kirjin sa idanuwan sa duk sun furfuto,

“Gwa me?”

“Gwamnan kaduna..”

Rigar sa ya shiga kadawa yana jijjiga kai,

“Dankari! Billahil lazi sai da kika fada naga kamar sa da gwamnan mu tamkar an tsaga kara an karya. Allah ya bashi lapia, Ba.. Ba naje na kara dudduba shi.”

Sumsum ya fice yana sauri, Shegiya naira. Kankace me tuni ya fesawa sauran likitoci sun taru akan Mubeen suna sake dudduba shi. Aunty Rahila kuwa waya ta janyo ta kira Amb Salees da Haj Ahlaam inda ta sheda musu yadda ake ciki. Ba’a dau lokaci ba sai gasu sunyi ‘badda kama sunzo. Babu wanda zai dauka gwamna ne, A matuk’ar hargitse suke. Gwaggon ta kwakkwantar musu da hankali. Hankalin Amb ya kasa kwanciya da asibitin suka tattara suka koma kaduna.

KADUNA

GOVT HOUSE

Amb Sales ya kira private family doctors din su suka dauki Mubeen suka rankaya kaduna gaba d’aya. Manyan physicians ne suka taru akan Mubeen dake kwance bai san inda kansa yake ba. Gwaje gwaje suka yi tayi masa suna ganin results din. Haj Ahlam takasa zama sai zubar da hawaye take yi..

Tuni aka kira malamai suka shiga addu’oi suna ro’kon Allah. Cikin ikon sa da qudurar sa kuwa sai gashi Muhammad Mubeen ya farfado daga doguwar sumar da yayi. Amman bai motsa jikin sa ba. Numfashin sa dai na fita a hankali, Ya rame lokaci d’aya ya zabge. Karan hancin sa tamkar an sake jansa, Rubdugu suka shiga yi akan sa suyi wancen suyi wannan. Wani dogon numfashi yaja yana girgiza dan yatsan kafafun sa na kafar hagu,

“Muhammad Mubeen! Mubeen! Mubeen... Kana jina?”

Dr Affan (cardiologist) ya shiga tattaba kafafun Mubeen yana kokarin bud’e idanun sa. Amb Salees ya shiga zagaye dakin cikin tsantsar damuwa, Fita dr Affan yayi daga cikin dakin ya koma parlor wajen su Aunty Rahila. Suna ganin sa suka mimmike daga xaunen da suke,

“Hajia shin akwai wani abu daya faru dashi ne kafin zuwan ku wancen asibitin?”

“A’a likita, Kasan shi da ‘kin cin abinci. Na sashi a gaba kan ya temaka yaci ko kadanne. Sai ya tashi ya shiga dakin sa yace bari ya watsa ruwa ya fito yaci. Wallahi har na zuba masa abincin ma, Shiru shiru ganin bai fito ba abincin nasa na sanyi. Sai na tashi naje dakin nasa domin kiran sa. Shine fa na same shi cikin wannan yanayin. Ko Yayyah..?”

Ya Adama ta kada kai alamun Eh. Tana mai cigaba da jan carbin ta. Gaba d’aya itama hankalin ta a tashe yake. Dr Affan ya sauke gwauron numfashi yana kallon Amb Salees,

“Your excellency gaskia Muhammad Mubeen na cikin wani yanayi, Kasan daman shi ba ishasshiyar lapia ce dashi ba, Ga chronic ulcer data sake rarake jikin sa. Jinin sama yayi low wallahi. Meya taso da wannan ciwukan nasa lokaci d’aya haka?”

“Wallahi dr ni bansani ba. Iya bakin k’ok’ari dai muna yi masa. Akan abinci dama sai an ta fama dashi wallahi.”

Amb Salees ya bashi amsa yana dafe da goshin sa, Dr Affan ya sosa kunnen sa yana cije kasan leben sa,

“Wallahi kuwa taci karfin sa, Shiysa kullun zamu yi masa saline na tsawon sati uku da kuma alluran histidine monohydrochloride (Larostidin, Roche) Matsalan Muhammad Congenital heart disease dinsa yayi karfi da yawa, Abu ne da zamu kira shi da tun yana zanin haihuwa yake fuskan ta, Gashi bugun zuciyar sa ma ya canza (Arrhythmia). Kuma kaga it needs to be taken more seriously and treated. Ga Mitral regurgitation shi yasa yawanci yake jinsa a gajiye.

“Allah ya temaka ma bai shiga Myocardial infarction ba irin na shekarun baya. So dan ALLAH your excellency acigaba da kokarin tarairayar mUhammad wallahi yana shan wahala. Tun yana zanin goyo yake experiencing pains.“

“IN SHA ALLAHU! Allah dai ya tashi kafad’un sa.”

“Dr Affan ya tashi..”

Cewar Dr Uchenna daya le’ko da kansa ta k’ofa yana kiran sa. Da sauri Dr Affan ya koma ciki shida Amb Salees,

“Muhammad.. Mubeen ! Kana jina?”

“Son! Son son! Kana ji?”

Dr Affan da Amb Salees suka shiga kiran sunan Mubeen ganin yana kokarin bud’e idanun sa.

“Batoul...Ayana... Batoul!!!”

Sune sunayen da bakin Mubeen ya shiga nanatawa yana dafe da saitin zuciar sa. Likitocin suka shiga bashi temako. Shi kuwa Amb Salees sandarewa yayi a tsaye yana maimata sunan Batoul da Mubeen yake nema. Kowacece oho??

“Mubeen kana jina..? Dr Affan ne! Kana gani na?”

“Batoul..”

“Ba inda yake maka ciwo?kan ka, Cikin ka, kirjin ka inane yake maka ciwo?”

“Batoul.. Dan Allah ki saurare ni.. Ma plss!!”

Dr Affan yana kada kai yana kallon Amb Salees,

“Your excellency wacece Batoul? Tana ina Pls? Idan tana kusa sai komai yafi zuwa da sauki..”

“Wa..Wa..Wallahi bansan wacece Batoul ba.”

“Subahanallahi!..”

“Akwai matsala ne Dr?”

“Eh toh gaskia da son samu ne dai ace Batoul din na nan wajen.. Komai zai fi zuwa da sauki!”

Ficewa yai ya koma parlor wajen su Aunty Rahila,

“Ko kinsan wacece Batoul a zaman da ku kai da Mubeen?”

Amb Salees ya tambayi Aunty Rahila yana kallon agogon hannun sa,

“Gaskia a’a Yaya! Wallahi bansan ta ba..”

“Ko cikin yaran kuma?”

“Anya banaji gaskia, Amman bara na tambayi su Jawad.”

Daukar wayar ta tayi ta shiga kiran yaran ta maza ko sun san da masaniyar hakan? Duk cikin su babu wanda yasan komai. Ta katse kiran a sanyaye tana sanar dasu yadda akai. Amb Salees ya koma wajen Haj Ahlaam dake shararar hawaye,

“Ko kinsan wacece Batoul din Mubeen ke kira?”

Girgiza kai tayi tana fyace hancin ta,

“Bansan ta ba wallahi.. Pls a nemo masa ita.”

Mikewa yai bayan ya k’ada mata kai ya koma ciki wajen su Dr Affan,

“Dr bamusan wacece ita ba gaskia.”

“Toh Alhamdulillah mun masa allura ya koma bacci ma zuwa anjima zai tashi, Dan Allah adai cigito masa Batoul dinnan your excellency!”

“IN SHA ALLAHU! Mun gode sosai, Ga abinci can a site dina an ajiye muku.”

Ya karasa fada yana gaggaysawa da likitocin. Cike da girmamawa suka a’amsa kafin su fice don cin abinci, Amb Salees ma fita yayi ya koma wajen meeting da suke gabatarwa shi da sauran muqarraban sa akan matakin kwamishinas da zai nannad’a..

Muhammad Mubeen bai farka ba sai gab da sallar la’asar. A hankali yake bubbude idanuwan sa da su kayi masa nauyi saboda tsabar ciwo. Ya Adama da Aunty Rahila, Haj Ahlaam, Jannat da sauran yan uwa da aka taru akan sa. Wani likitan ya shiga dudduba shi yana tambayar sa,

“Mubeen kana gani na? Yatsu nawa ne na daga yanzu?”

Ya karasa fada yana hada hannayen sa guda shida. Mubeen ya kikkifta idanu yana taune leben sa na kasa ahankali cikin ciwo yace,

“Guda... 12 ne.”

“12????”

Likitan ya maimata yana dafe kansa, Mubeen ya kada kai alamun Eh. Amb Salees dake gefe ya shiga jujjuya kai cike da damuwa.

“Double vision... Ina Doctor Lyna??”

Cewar surgeon Isah! neuro-ophthalmologist Lyna ta matsa kusa da Mubeen tana dudduba idanun sa. Ta duba shi sosai sannan ta juya tana wa sauran doctors din bayani.. Haka dai su kayi ta gwagwarmaya akan sa. Amb Salees ya koma parlor ya zauna yana dafe kai. Daman Haj Ahlaam tana zaune tana kuka. Gaba d’aya sauran yan cikin dakin suka firfito ciki harda doctors din,

“Doctor ya..?”

“Ah bakomi! Mun mishi allura ne yana bukatar bed rest! Kakka dama your honor. “

“Ya batin double vision din?”

“Zai dawo normal nan da some hours daman transient ischemic attack ne...”

“Ya Subhan’Allah!!!”

“Kakka damu your honor! ISA zai wartsake dama ace ita Batoul din na kusa da tuni ma ya tashi..”

Fita Amb Salees yai ya kira direban dake kai Mubeen makarnta. Yan tambayoyi ya yiyyi masa anan ya gano cewar Mubeen din na kula wata malamar su dake zaria unguwar ‘limancin kona’. Mai suna ‘Batoul’ Waya ya zaro ya kira mijin Aunty Rahila inda yace ya gudanar masa da binciken Batoul din. Sannan ya sake kiran Alhaji Kabeer mai wafa a waya yace masa yayi bincike shima. Cike da karfin gwiwa ya koma parlorn da ahalin nasa suke. Yayi sa’a kuwa sai Ya Adama ta idar da sallar ta babu kowa sai Jannat a gefe tana danna waya. Yace ta basu wuri, Sannan ya shiga zayyane mata komai ya k’ark’are da,

“Toh kinji dai yadda ake ciki Yayya. Nama kira Alhaji Salim mijin rahila a

waya da wani yaro na Alh Kabeer mazaunin zarian ne. Ya kike gani Yayya? A nemo yarinyar tayi jinyar sa ko?”

“Toh agaskiya ‘dannan (Saboda shine dan fari) bazan bada goyon a dakko yarinyar mutane ta rika jinyar sa ba..”

“Toh Yayya ai shawarar ki nake nema.. Ya kika gani? Banda ma Mubeen da fitnar sa yarinyar ma fa malamar su ce wai..”

“Toh ai ba haramin bane ‘dannan. Ba kansa farau ba. Sai kaga idan Allah yasanya alkhairi a lamarin zaka sha mamaki. Wani hanzari ma ba gudu ba, Ita yarinyar babu maganar auren wani akanta ko? Saboda kaga babu kyau neman aure akan aure..”

“Hakane amman Yayyah hakan ba zai janyo surutai ba ganin ta fishi shekaru? Duk da dai shi din bai karatu da wuri ba ba kuma tabbatarwa mukayi da ta girmeshin ba...”

“Babu komai ‘dannan ni ina ganin zai samu ladan sunnoni biyu, Koda ta girmeshin. Wato sunnar aure da kuma ta koyi da fiyayyen halitta annabin mu (SAW)Tsira da amincin Allah su tabbata agare shi. Kuma kowanne dan adam yanada yadda Allah ya qaddarar masa rayuwa, Idan kayi hak’uri sai kaci ribar hakan agaba. Allah dai ya zabi abinda yafi alkhairi Ameen.”

“Ameen Ya... Duk yadda mu kayi dasu zan sanar miki”

“Allah yasa muji alkhairi..”

••X••O••X••O••

Alhaji Salim da Alhaji Kabeer duk sunyi bincike akan Batoul kuma Alhamdulillah babu wata suka da samu daga gare ta, Kuma babu neman auren wani akan ta. Uwa uba shekarun da ake kawo mata ba hakan bane. Nan da nan Amb Salees ya kira kanin sa awaya wato senator Bilalu da Alhaji Salim da Alhaji Kabeer kan suje su tambayo auren Batoul a gidan su...

Alhaji Kabeer daya gama kammala wayar da yake da Amb Salees ya dashare hak’ora yana murmushi. Haj Husnah ta kalle shi tana neman karin bayani,

“Alhaji samuwa ce ne?”

“Na’am Hajjaju.. Eh toh kusan hakane. Kinga neman aure aka samu ne, Munyi bincike akan wata yarinya dake nan kasan unguwar mu. Kinga har ana zancen nemo auren ta ma..”

“Wa kenan?? Alhaji har kai za’a sa binciken aure?”

“Eh gaba da gabanta ne hajjaju! Amb Salees ne ya samu.”

Hajia Husnah ta zaro idanu tana dafe kirji,

“Gwamna da kansa? Ya rasa inda Za’a nemo aure sai nan unguwar?Shine zai yi auren ko kuwa?”

“Toh menene aciki? Shi aure ai albarka ake nema ba kyale-kyalen duniya ba hajjaju.. A’a bashi zai yi ba”

“Wa..Yarinyar sa”

“A’a yaron sa ne..”

“Kuma Alhaji a kasan layin nan yake nema? Kaf unguwar nan akwai wanda ya kai gidan nan arziki?”

Dafe kansa Alhaji Kabeer yai yana sakin tsaki,

“Kina da matsala wallahi. Allah ya kyauta miki hajjaju, Sai yar me kudi zai aura? Ki canza dan Allah! Toh yarinyar ma marainiya ce mahaifin ta ya rasu. Inda Allah ya temaka ma tana aiki akace.. Ni kuwa yasunan gidan da muka jema?”

Alhaji Kabeer ya daga kansa yana tunani. Haj Husnah duk ta birki ce tana sosa kai. Alhaji Kabeer yai murmushi,

“Yauwa gidan mata tara.. Sunan ta Batoul! Ance yarinyar akwai nutsuwa da sanin yakamata.”

Wani gundumemen zagi Haj husnah ta saki tana zare idanu, Banzan kallo Alhaji Kabeer yayi mata yana girgiza kai.

“Alhaji da..Dan girman Allah dagaske?”

“Ga gaskiya ga rantsuwa..”

“Batoul dince zata auri dan gidan gwamna??? When! How? Why?”

Dai dai nan Haysam dake tahowa ya jiyosu. Dafe kansa yai da lokaci d’aya ya shiga juya masa. Hannu yasa ya rike bango yana rintse idanun sa. Alhaji Kabeer ya mike tsaye yana tattare rigar jikin sa,

“HasbunAllahu wa ni’imal wakil! Hajia kin fara bani tsoro gaskia. Ina ruwan ki da shiga harkar wanda ‘yayan su zasu aura? Taya akai ma kikasan yarinyar?”

Cikin rawar jiki da baki tamkar susucacciya Haj Husna ta sosa kanta tana yarfe hannuwa,

“Alhaji ina matar nan da tazo ta mana aikatau..? Shegiyar matar nan na tsane su itada ‘yarta.. Nan fa suka yiwa Haysam sihiri ya sururuce akan yarinyar. Batoul din ita ce dai wacce ka gama magana yanzu.”

Alhaji Kabeer yaja tsaki yana girgiza kai,

“Toh idanma kin tsane su ai Allah yana son su ko? Gashi yanzu cikin hikimar sa da zatin sa zai sanya yarinyar ta shiga gidan gwamnati.”

“Ba za’ai haka ba. Dan girman Allah kayi meyiwuwar hana auren nan.. Yarinyar nan fa itace wadda suka gama sihirce Haysam wai shi lallai sai ya aure ta.”

“Itace kwanaki yamin maganar ta ya dawo yace an bada ita ko? Kiji tsoron Allah husnah ki dena hada husuma. Sai yanzu na gano kece kika hanashi auren ta saboda ba masu kudi bane ko? Toh ai gashi nan ta xarce tunanin ki..”

Haysam ya shiga parlorn yana tangadi, Alhaji Kabeer ya kalle shi yana yamutsa fuska,

“Kai Haysam kasan Batoul?”

D’aga kai Haysam yayi jikin sa a matuk’ar sanyaye yana kallon idon mahaifiyar sa,

“Abba itace wadda nace ku nemar mun auren ta..”

“Kacemin aure za’a mata kuma? Meyasa?”

Saurin girgiza kai Haysam yayi yana mai da kallon sa ga Abban nasu, Saboda yadda Haj husnah ta tsare shi da idanu alamun karya kwafsa mata.

“Abba umma ce ta hanani neman ta.. Tace bata yafe min ba idan har na aure ta.”

Kada kai Alhaji Kabeer yai cike da takaici. Yana kallon Haj husnah dake raba idanu,

“Tsaya kaji Alhaji.. wa..”

“Inji me? Dakata tsaya Hajia. Kinsan na dade ina taraki daman ko? Toh a zahirin gaskia nagaji da ire-iren abubuwan da kike aikatawa a gidan nan. Kowa ya budi baki sai dai ya yabi abokiyar zaman ki? Sam baki da hali, Kowa yaita kawo korafi akan ki. ‘Yayan ki ma kin bata tarbiyyar su? Nagaji wallahi Asmau! Nagaji da halin ki..”

“Alhaji tsaya kaji”

“Kai Haysam kaga yanzu an riga da an fara nemawa yaron Amb Salees auren ta, Saboda shidin ba mai cikakkiyar lapia bane. Saboda haka kayi hak’uri, Allah yayi ba matar ka bace. Kaje ka nemo auren yar kanwata sahura d..”

Haj Husnah ta zunduma kara tana bubbuga k’afa,

“Alhaji auren yar sahura fa? Su da suke a can kauyen kura dake kano? Haba Alhaji”

Alhaji Kabeer ya jijjiga kai yana hade hannuwan sa,

“Yaje ya auri wadda kika zabar masa amman ba anan gidan ba. Kina jina? Ki tattara komai naki ki tafi gidah na sake ki saki d’aya, Idan naga kinyi hankali kya dawo, Idan kuma zaman mu ya kare ma shikenan..”

Haj Husna ta zube ak’asa tana kuka harda jefar da d’ankwalin kanta,

“Saki fa Alhaji? Alhaji me zanyi a kauye yanzu? Fisabilillahi na saba da miyar ja tasha nama anan na koma k’auye? Kuka ce fa akeyi shar da ita kullum, Ga ruwan kogi ne ake wanka. Ba wuta fa Alhaji.”

“Kinsan da hakan mahaifar ki take kike wulakanta mutane? Wallahi Allah sai kin tafi a yau ba sai gobe ba. Idan na dawo gidan nan na ganki ko naji labarin kina garin nan sai na mugun sab’a miki.. “

“Wayyo Alhaji ka temake ni..”

“Babu abinda zan iya miki. Ki tattara kayan ki ki koma inda kika fito. Alhamdulillah sahura jini na ce bazan taba iya rabuwa da ita ba ko na canza wata. Amman ke zan iya sauya ki na nemo wata. Tamkar hular sawa kike a wuri na kina ji? Ki koma can karkakar da kika fito. Allah ya kyauta.”

Yana gama magana yai hanyar kofa har yaje ya dawo yana duban Haysam dake tsiyayar da hawaye,

“Kai kuma ka tafi gidan Idris ka huta(kanin sa dake abuja) Ga habule direba can ya kai ka yanzu ba sai an dau lokaci ba. Allah ya kiyaye hanya kaji?”

D’aga kai Haysam yayi yabi bayan mahaifin sa. Ita kuma Haj husnah ta shiga birgima tana koke koke. Inna mai aiki na jin haka ta tattara komatsanta tayi gaba. Haysam ma mota ya shige direba yaja shi sai Abuja. Gaba d’aya ji yake komai na duniyar ya tsaya masa sak. Cikin addu’oin da yake kamowa yaji wani sanyi a ransa. Lambar Batoul ya lalubo ya goge yana tsiyayyar da hawaye hade da yi mata fatan alkhairi acikin rayuwar auren ta. Lokaci kankani bacci yai gaba dashi. Direban kuwa sai sharara gudu yake.

••*GIDAN MATA TARA••*

A bakin kofa Alhaji Salim da senator Bilal da Alhaji Kabeer mai wafa suka tsaya, Suna jiran a musu iso su shiga ciki. Kawu ila daya mula yasha iska ya mike daga kan bokitan sa yana botsarewa, hade da sakin wata shegiyar hamma yana sosa bayan sa.

“Ko su wanne natattunne oho? Haba tun d’axu sai faman doka sallama suke, Matsiyata.!”

Haka yai ta mitar sa ya fice wajen su dakyar yana kwakwular tasono.....

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] Ɨ GIYAR ___ZATO

47

Tsayawa Kawu ila yai yana kallon su. Shi dai yasan wa’innan mutanen ba kalar wanda sanayya za ta hada su bane.

“Bayin Allah ‘batan kai kukai ne..?”

Ya tambaye su yana sake bin kayan jikin su da kallo, Domin kallo d’aya zaka musu kasan manyan mutane ne. Kayan jikin su da yanayin fatar jikin su ma abar kallo ce. Ga wata arniyar mota da suka zo acikin ta.! Sosai ya mai dasu tv yana bin ilahirin jikin su da kallo, Senator bilal yai gyaren murya yana kallon agogon hannun sa,

“Dan Allah acikin gidan nan kake? Ma’ana kana da danganta da nan gidan..?”

Ya karasa fada yana mai nuni da karyaiyiyar kofar shiga gidan mata tara. Kawu ila ya ware idanu yana yarfe hannu,

“Bayin Allah wani ne ya janyo muku magana ko? Ai lamarin gidan nan sai a hankali, wane shegen ko shegiyar ce?”

“Subhan’Allah! Assha! Mu farin ciki ne ya kawo mu..”

“Farin ciki kuma?.....!”

Kawu ila ya maimata yana wulqita idanuwa,

“Eh! Ance duk tare kuke da sauran yan uwa ko?”

“Gashi kuma ka fada..”

Kawu ila yaba Alhaji Kabeer amsa yana yamutsa fuska. Suka kalli juna jin mamakin kalaman sa. Cikin ikon Allah sai ga Kawu Ishaq ya dawo dauke da leda fara da tumatir uku, Albasa d’aya da attarhu guda shida aciki. Da alamun cefane yayo. Yana ganin su ya tsaya yana mimmika musu hannu suka gaggaysa basu kyamace shi ba dubada yadda wasu masu kudin keyi.

“Bawan Allah kai ma acikin gidan nan kake.?”

Alh salim ya tambayi Kawu Ishaq ganin yadda Kawu ila ke raina musu hankali. Kawu Ishaq ya kada kai alamun ‘eh’ kafin yace,

“Eh anan nake ranka ya dad’e, Wani abunne?”

“Ko babu damuwa zamu iya samun waje mu tattaunawa? Ku biyu ne ko akwai sauran yan uwan ku?”

“Mu biyar ne ranka ya da’de. Maza hudu mace d’aya.”

“Masha Allah! Toh zamu dan yi magana ne daku idan babu damuwa cikon biyun naku ma zasu iya zuwa a tattauna dasu.”

“Toh babu damuwa ku shigo daga ciki ai suna nan suma.. Ilyasu muje parlorn ka ko?”

Kawu ila yaja tsaki yana sosa kwanyar kansa. Ya shiga mita agaban su bako yar kunyar bak’innan.

“Wai parlor na dan bakin munafunci. Ta ina ya zama parlor na? Ance ya zama na mallakin Najeebu! Hmm billa..”

Ashe dik sun shige bai sani ba shi kadai ne a soro ya daga hannu zai kwararo rantsuwa. Yaja tsaki yana hararar soron kai kace akwai mutum a tare dashi, Kawu Ishaq na shiga ya tura bala ya karb’o masa pure water masu sanyi a shagon Nata’ala. Ya kira Kawu Dawood da Khamis suka sakko ‘kasan suma. Sannan ya koma soro ya kira Gwaggo Aminatu ya sheda mata cewar ga wasu manyan attajirai nan sunzo gidan wai zasu yi magana dasu. Ai kuwa tace gata nan garzayowa itama. A parlorn Kawu ila suka zazzauna sai cika Kawu ila yake yana batsewa. Alhaji

Kabeer ya gyara murya yai sallama hade da fara gaya musu sunayen su da matsayin kowannen su,

“Da farko dai mu wakilai ne da aka turo don nemar wa dan mu auren ‘yar ku. Kuma Alhamdulillah kafin muzo nan din, Munyi bincike akan yarinyar kuma mun sameta da halin k’warai, Mun samu yabo sosai daga gare ta. Wani abun farin cikin ma babu auren wani akanta. Ni sunana Alhaji Kabeeru mazaunin nan garin na Zaria, Dan changi ne ni kuma inada iyali na dake nan garin na Zaria, Ga Alhaji Salim alkali ne shi anan customary court dake kaduna amman anan Zaria yake zaune da iyalin sa shima. Sai Senator bilal Senator ne shi yana Abuja! Duk kanin mu mun zone a bisa nemarwa dan mu auren yar ku.. Senator bilal ‘k’ani ne ga mahaifin yaron dake son yar ku uwar su d’aya uban su d’aya, Sai Alhaji Salim shi kuma siriki ne agare su, Domin mijin kanwar su ne. Ni kuma yaro ne awajen sa.”

Kawu ila ya saki baki yana tarin mamaki,

“Neman aure fa kuka ce? Kuma nan gidan ne kuwa? Anya ba ‘batan kai kukai ba?”

Alhaji Salim ya girgiza kai,

“Banan ne gidansu Batoul ba?”

Kawu Ishaq da Kawu Dawood suka kada kai alamun Eh! Kawu ila kuwa baki ya sake hangamewa cike da mamaki,

“Ba... me?”

Su kayi shiru basu amsa shi ba kuwa, Kawu Ishaq ya dungure shi da kafar sa alamun yai shiru. Ai kuwa Kawu ila ya shiga magana ‘kasa k’asa kamar zaucacce. Kawu khamis ya numfasa kafin ya fara magana a nutse,

“Masha Allahu! Munyi farin cikin kasancewar ku a tare damu, ALLAH ya saka da alkhairi Ameen! Toh nan gidan duk yan uwa ne wanda ke zaune a inuwa d’aya. Dukkanin mu iyaye ne da ‘yayayenmu da kuma jikoki. Mu shida ne awajen mahaifan mu Allah ya jikan su da rahama. Sunana Khamis, A tare dani akwai yan uwa na kuma kanne na wato, Ishaq, Dawood sai autan mu Ilyasu gashi. Sai mace guda d’aya tak dake aure a Kaduna. Muma usulin mu yan kadunan ne. Neman abinci ne ya maido mu nan Zaria inda muka kafa ahali, Toh Alhamdulillah munji dadin yadda kuka samu yabo na kwarai akan ‘yar mu Batoul,

“Batoul ‘ya ce awajen mu. Domin mahaifin ta marigayi malam Salisu shine babban wa agare mu baki d’aya. Kuma uwar mu d’aya uban mu d’aya dashi. Ya rasu shekarun baya. Duk muna tare dasu da mahaifiyar su anan gidan dama abokiyar zaman ta itama da nata yaran...”

“Allah sarki! Allah ya jikan sa da rahama da sauran musulmai baki d’aya!”

Senator bilal ya fada yana girgiza kai cike da tausayi, Sauran suka amsa baki d’aya da,

“Ameen!”

Kawu khamis ya shafa hannuwan sa a fuska sannan ya cigaba da cewa,

“Itace ta biyu awajen mahaifiyar su, Sai yar kanwar ta Aminatu. Alhamdulillah tayi karatun boko da arabi sosai. Domin tayi saukar alqur’ani mai girma, Tana kuma da matakin digiri na biyu. Alhamdulillah tana koyarwa yanzu a jami’ar Amadu bello dake nan Zaria tana kuma zuwa tahfiz asabar da lahadi. Kamar yadda kuka ce din gaskia ne batada wani tsayayye na aure amman dai akwai maneman da yawa.”

“Masha Allahu! Lalle mahaddaciyar alqur’ani ce. Abu yayi kyau tanada kwazo gaskia. Allah ya temaka Ameen.”

Cewar Alhaji Salim. Ya cigaba da cewa,

“Toh neman alfarma muka zo, Munzo nemawa dan mu auren yar ku ne..”

“Ai tanada masaniyar zuwan ku daman ko? Ma’ana akwai maganar sa akasa.”

“A’ah gaskia! Domin banajin suna da wata alaqa dashi yaron namu fyace ta malama da dalibin ta..”

“Toh.....”

Cewar Khamis yana kallon idanun su Kawu Ishaq. Senator bilal ya cire hularsa yana gyara karin ta kafin yace,

“Muhammad Mubeen shine sunan yaron namu, Kuma dalibi ne ga ita Batoul din. Kuma banajin ta san yana son ta ma.”

“Allah sarki! Ya za’ai kenan?”

Kawu Ishaq ya tambaye su da tsantsar gaskiyar sa domin bai san ya za’ai ba. Alhaji Kabeer ya dan sake muskutawa kafin ya karbi zancen,

“Yauwa kamar yadda muka fada da farko, neman alfarma muka zo kuyi mana. Yaron mu yanzu haka yana kwance babu lapia. Kuma Allah ne mai bada lapia amman Batoul itace zata zamto silar farfadowar sa. Yana kaunar ta kauna mai tsanani wadda ta kwantar dashi ciwo. Bamusan ko tasan yana dauke da tarin kaunar ta ba gaskia. Domin bai fada a gidah ba. Ya dai suma yanzu haka likitoci na kansa. Amman Allah yana temakawa yana farfado wa da sunan ta ya tashi a bakin sa. ‘Batoul’ Toh anan aka danyi yan bincike aka gano wacece ita, Domin shi yana daga cikin miskilan mutanen nan masu b’oye abunda ya shafe su. Rashin bayyanarwar tasa shine ya haddasa masa kwanciya ciwo. Dama kuma yana dauke da ciwo wanda bayason damuwa.

“Tun yana zanin goyo yake dauke da ciwon, Domin dashi aka haife shi ma. Abune daya shafi zuciyar sa. Kusan shine ya hanashi karatu ma tun yana ‘karami, Abu kalilin ne zai sa ya tashi yaita wahalar dashi. Dan da kila ba shida wata matsala ta iya yiwuwa shima ya kammala matakin karatun da ta yiyyi..”

“Allah sarki Allah ya bashi lapia mai dorewa...Yasa kaffarane Allah ya tashi kafad’un sa. Ameen”

Cewar Kawu Ishaq. Saura suka amsa da Ameen. Akai shiru na yan wasu sakanni. Bala ya kawo musu pure water din ya ajiye a sabon tiren Hajara matar Kawu ila. Kawu ila ya hararo tiren yana kauda fuska, Kafin cikin tsukewar fuska yace,

“Yanzu ku ‘danku zaku aurawa malamar sa? Inada tabbacin ta ninka shekarun sa.”

Suka kalli juna. Su Kawu Ishaq kuwa kunya ce ta kusa cinye su tamkar wajen ya bude su fada suke ji. Senator bilal yai murmushi kawai domin ya gano hassada ce ke damun ilyasun da alamun akwai wani abu a kasan zuciar sa,

“Kada ka damu babu komai, Munji mun kuma gani muna so a hakan, Koma ace ta nunka shekarun nasa babu komai, Ai ba kansa farau ba ba kuma za’a dena a kansa ba. Kaga zai yi koyi da sunnar ma’aiki. Allah yasa mu dace Allahumma Ameen! Mu dai yanzu a shirye muke domin da kudin sadakin mu muke tafe..”

“Toh ku kuka sani domin mah...”

Kawu Ilyasu bai karasa ba Kawu Ishaq ya janye shi suka tashi. Soro suka koma ya shiga lurar da shi abunda yai bai dace ba. Kallo d’aya zaka yiwa Kawu Ilyasu ka gano bakin ciki ne zalla a tattare dashi. Ai kuwa sai ga Gwaggo Aminatu ta shigo soron sai murmushi take, Tana ganin su tasha jinin jikin ta,

“Ilyasu ne yai katobara ko??”

Kawu Ishaq ya zayyane mata komai tana jinjina kai tana dankarawa Kawu ila harara,

“Kaga Ishaq kaje ku cigaba da tattaunawa ni bari na samu kaltume da maganar, Me za’a jira ne? Ai gwara tayi auren ta. Kai kuma Ilyasu jeka ka dawo anjima dan Allah..”

“Amma Yaya..”

“Jeka dai dan Allah”

Ficewa yayi yana mita ita kuma ta haye sama. Kai tsaye ta fara duba Bintalo dake kwance kudaje sai binta suke su Zabbau na gefen kofa suna hirar su sun barta aciki basu tsaftace wajen ba. Wajen kaltume ta shiga bakin ta dauke da sallama, Batoul bata nan tana makaranta hakama Aminatu. Ai kuwa Gwaggo ta shedawa kaltume yadda ake ciki, Kaltumen ta kasa boye farin cikin ta. Abunda ake nema shekara da shekaru yazo me za’a jira?

“Duk yadda kuka tsara Yaya hakan za’ai, Amman kamar yadda kika tambaya din nagane yaron domin yasha zuwa gidan nan gaishe ta. Har kayan dadi ya kawo wa Auta. Kuma bakiga ba hidimar bikin nan duk da shi aka yiyyi. Ban dai tab’a ganin saba amman wannan yaron ma (Najeebu) yace yanada kirki wallahi..”

“Masha Allahu! Abu yayi wallahi mu dai munyi na’am. Ance wai dalibinta ne nace toh ita soyayya ina ruwanta?”

“Wallahi kuwa! Nan take fada ma ya faffadi a jarabawoyin ta kuma yanada k’ok’ari fa tace. Nace tasa kaddarar kenan. Amman dai yaya ba matsala?”

“Ta me fa??”

Innar mu tai ajiyar zuciya tana harhada hannuwa,

“Wai duba da shidin dan gidan gwamna ne mai ci na yanzu..”

Baki galala Gwaggo Aminatu ta bu’de, Can ta dubi gabas tayi sujjada tana matsawa kusa da Innar mu,

“Alhamdulillah kaltume. Ai abunda muke so kenan. Alhamdulillah! Alhamdulillah! Alhamdulillah! Dan gidan Amb Salees kenan. Idan kuwa haka ne yaron ruwa biyu ne domin mahaifiyar su ance yar Ethiopia ce. Kai amma nawa Batoul murna wallahi. Mahakurci mawadaci. An ce ma wai zata girme shi, Kanin uban yace sun ji sun gani suna so a haka, Ai zai yi koyi da sunnar ma’aikin manzo SAW! Wallahi Ishaq duk ya mayar mun. Yaron nacan rai a hannun Allah wai sunan Batoul kawai yake kira, Shine suka zo neman alfarma. Ni naga dankareriyar mota mai numfashi ashe tasu ce,

“Ishaq yace min harda Senator acikin su, da alkali da wani babban Alhaji. Yace kuma fuskar su a sake daga gani suna goyon baya. Ai kudi ba karya bane kaltume, kowa yanason inda zai huta nasa su huta. Ya kika gani? Don da sadakin su wai suka zo...”

Innar mu tayi shiru tana jinjina kai, Ita dai batada matsala a daura ko yaushe domin zancen yayi na’am a zuciar ta, Sai dai kowa na duniya nada magabata, Dole ta nemi manyan ta suyi magana dasu.

“Hakane Yaya! Amman idan babu damuwa gobe da safe ISA zan tafi shema na shedawa su Baffa Ardo kar suji daga baya babu dadi..”

“Hakan yayi kaltume.. Wallahi yayi! Allah yasanya albarka da alkhairi. Ni zan tafi da Batoul din akwai yan maiduguri dake gyaran jiki a kusa damu sai a shisshiryata, Amman ba zamu sanar mata wanda zata aura ba ko?”

“Eh Yaya...”

Innar mu ta fada tana sadda kanta kasa saboda macece mai kunya. Gwaggo ta mike da kanta tasa aka kirawo Kawu Ishaq ta sheda masa da yagayawa bakin cewa daurin auren ayi shi jibi ranar jumu’ah ko da daddare ne sai ayi domin za’a shaidawa su Baffa Ardo. Hakan kuwa akayi ya koma ya fada musu sun amince amman daurin aure sai zuwa jibi wato ranar jumu’ah. Suka musu sallama, Senator bilal ya ajiye musu rafar dubu d’aya. Bakin su Kawu har kunne suka rakasu waje. Sai ga Batoul ta dawo daga makaranta sanye cikin abaya baka tayi masifar yin kyau tamkar ka saceta ka gudu. Gaishe su tayi zata shige Kawu Ishaq ya kira wota yana nuna musu ita,

“Itace Batoul din ranka ya dade..”

Senator bilal ya fadada murmushin sa yana kallon Batoul,

“TubarkAllah! Lalle son yayi sa’a. Allah ya miki albarka kinji?”

Gyad’a kai nayi domin bansan me zance ba ko suwaye hakan? Na shige ciki kai na a kasa. Da’ki na shige abuna, Gwaggo da Innar mu a daki suna ta hira nayi sallama, Gwaggo Aminatu ta rungume ni tana rawa. Nan ta shiga shedamin neman aure na akazo kuma jibi za’a daura. Bata dai gayamin waye ba tace wani ne mazaunin kaduna yana canma ba lapia zanyi jinyar sa bayan an d’aura. Haka kawai naji zucia ta ta aminta da zancen. Aure ai ibada ne, Inata kokarin hada idanu da Innar mu taki yarda nasan kunya take ji. Ni kuwa bokiti na saba na sauka kasa nai wanka na. Su Kawu Ishaq sai nannan suke danni. Na tab’e baki ina mamakin wannan sabon salon. Nai sallah bayan naci abinci. Ina yiwa Allah godia hade da neman alkhairin sa. Gwaggo Aminatu ta sauka kasa wajen su Kawu Ishaq. Ta karbi kudin hannun sa ta raba shi kashi uku, kashi d’aya ta sa aka kira masu gini ta nunna musu inda zasu dan gyaggyara a gidan mu. Kashi na biyun kuma ta aiko aka bawa Innar mu kan tayi kudin mota. Dayan kuma tace su Kawu su raba. Ni kam kallon abubuwan nake tamkar a mafarki shin wane late comer ne wannan? Lalle Allah qadirun ne ala manyasha’u. Kaya na na shiga hadawa a dan akwati domin Gwaggo tace ita zanbi mu tafi kaduna. Sai yamma lis muka tafi kaduna..

WASHE_GARI

Da sassafe innar mu da autar mu suka tafi Shema, Dama tuni ta sanarwa Najibu yadda ake ciki shima yace yananan tafe. Koda Innar mu ta samu su Baffa Ardo da zancen sun bada goyon baya dari bisa dari, Har ma sun harhada gudunmawar su mai tsoka sun bata don gudanar da biki.

KADUNA

Tunda muka tafi muna zuwa Gwaggo ta cicciro wasu magunguna a roba ta shiga dirka min, Ga gyaran jiki da wasu yan maiduguri suka fara min. Lamarin dai ba sauki, ciki da waje gyaran sa kawai akeyi min. Fata ta sai sheki da santsi take kamar tarwad'a.

GOVT HOUSE

Senator bilal ya sake karkarcewa a kujera yana duban Amb Salees,

"Wallahi yaya yarinyar tayi, Da ladabi ta gaishe mu bayan batamasan suwaye mudin ba, Kuma she's young ma. Allah dai ya sanya albarka. Ya tashi kuwa Mubeen din?"

Amb Salees dadi ya cika shi sai murmushi yake,

"Masha Allah haka ake so, Yana ciki bamu ma gaya masa ba tukun so nake sai an daura..."

"Woah! Hakan yayi! Allah yasanya alkhairi shi kuma Allah ya bashi lapia."

"Sun gama hada kayan lefen?"

“Eh sun gama, Naji suna set 4 inaga akwatunan ne. Kasan wata mata aka bawa kwangilar yi..”

“Hakan yayi. Allah ya temaka.”

“Ameen”

Hirar su suka shiga yi, Daga bisa ni kuma suka koma wajen Mubeen. Yana zaune akan gadon sa anjigi na masa pillow, Hannun sa d’aya ana masa karin ruwa ya sake yin haske da kyau. Senator bilal ya zauna akusa dashi yana murmushi,

“Son na Batoul... Wai wacece Batoul dinnan ne? Uhm?”

Mubeen yai murmushi kawai yana sunkuyar da kansa kasa. Senator bilal ya sake cewa,

“Ai naje na fara bincike ashe ma malamar ku ce..”

Mubeen yai saurin daga kai yana kallon kawun nasa. Senator bilal ya kada kai yana dan duba yatsun hannun sa,

“Wallahi kuwa har na ganta ma fa.. Mekyau da ita kamar kai. Ashe saboda ita ka dage sai ka koma Zaria?”

Amb Salees yai murmushi kawai ya fice ya basu waje, Ai kuwa Senator bilal ya shiga tsokanar Mubeen. Kuma yaki ya gaya masa yadda ake ciki,

“Kana sonta son?”

Mubeen ya daga kai a hankali yana kallon gefe.

“Yanzu ya zakai ance aure zata yi.”

Mubeen ya shiga kikkifta idanu ahankali ya cije yana magana ahankali,

“Uncle pls.. Wallahi inason Batoul!”

“Zan duba nagani, Idan akwai yadda za’ai. But kar kasa hope akai..kai ta addu’a.”

Daga kai Mubeen yai hawaye na zirara a idanun sa. Senator bilal ya fice yana daria kasa-kasa, Shi dama akwai shi da tsokana musanman da Mubeen don yaga shi miskili ne.

*****Ranar jumu’ah da rana aka kai lefen Batoul akwatuna set hud’u guda ashirin da 24. Komai yaji babu ce kawai babu. Zo kuga kallon kaya awajen ahalin gidan mata tara da matan unguwar. Gaba d’aya yankin ya dauka da zancen kayan da aka kawowa Batoul. Fadilah ma ya Najibu ya gaya mata wanda Batoul din zata aura amman bata nunawa Batoul din tasan waye ba. Da ita akai komai domin dama ita Mubeen din ya mata wallahi tana son sa da Batoul tun ma hakan bata kasance ba. Kawai dai tasan kawar tata tafison manyan mutane masu shekaru. Duk wasu wahalhalun kayan daki da gara Amb Salees yace su barshi dan Allah. Su kawai Batoul suke so ba komai ba.

Daren ranar kuma bayan sallar ishai aka daura auren Muhammad Mubeen Salees Muhammad da amaryar sa Zahrau-Batoul Salisu Idris Najibullah. Abisa sadaki mai tsoka, Sai a sannan mutane suka sheda dan gwamna Batoul zata aura ganin harda shi akazo daurin auren. Gaba d’aya kaduna da Zaria ta dauka da maganar. Ana dank'awa Kawu Ishaq sadakin Batoul kawu ila ya karb'e yana danna su a kasan cinyar sa. Sai huci yake kamar bijimin sa, Bayan an daura suna ta yan gaishe gaishe, Kawu ila ya sulale ya fito soro da sadakin Batoul a hannun sa yana jujjuya su, Can ya shiga duddubawa ganin babu kowa a inda yake. Yana tafe yana magana shi kadai, Ya tare mashin ya hau ko ina zashi da kudin oho? Can gidah kuwa sai neman sa ake an rasa shi gashi bai bada kudin sadakin ba.

“Wallahi saro kaya zanyi dasu, Sai nayi kudi na dawo. ‘Yayan iska kawai mutanen banza...”

Dan mashin din ya dan kalli gefe yana rage gudun da yake shararawa,

“Me kace Alhaji?”

“A’ah bada kai nake ba, Da wasu mutanen banza nake masu son ganin baya na. ‘Kara gudu mu tafi dan Allah.”

Kawu ila ya gaya masa yana hararar keyar sa. Me mashin din ya kara gudu gashi ba fitila ajikin mashin din kuma dare ne. Ga kuma babban titi ne, Ai kuwa wata mota kirar ‘daf’ ta kunno kai, Mai mashin din yayi tangal tangal zai koma gefe kawai mai motar ya danna kai ya shallara dasu gefe suka bigi wata jibgegiyar bishiya. Mutane aka taru akan su, Shi mai mashin din dai ya jijji ciwo a gwiwa da kansa, Kawu ila kuwa bai masan inda kansa yake ba, Domin kafar sa d’aya ta rabu da gangar jikin sa, Gashi ya samu raunuka a sakamakon buguwar da yai ta kai sai jini ne ke fita, fatar sa duk ta daddaudauje. Aka rankaya dasu asibiti mai mashin din sai kuka yake domin mashin din nashi ya tashi daga aiki. Shi aka tambaya inda ya dakko Kawu ila? ta haka aka gano daga gidan mata tara ilan yake. Ai kuwa babu b’ata lokaci aka je aka shedawa ahalin gidan. Hakan ne yasanya Batoul bata ji sunan wanda aka aura mata ba domin hankulan kowa ya tashi aka shiga sallallami.

Alokacin na goge numbers din su Mubeen dama sauran wanda bani da alaqa dasu. Duk lamarin nan bansan waye mijin ba, Domin ca akai ta min wanda na aura yana asibiti a kwance don babu ango aka daura auren.. Sanye nake cikin atamfa mai ratsin blue da fari na yafa mayafi fari, Nayi kyau sosai abuna. Addua naita kwararawa akan sabuwar rayuwar da zan shiga tare da wanda bansan shi ba bai sanni ba.. Duk yan gidan mu suka shirya zasu tafi dubo Kawu ila asibiti nima na mike ina gyara mayafi na Gwaggo Aminatu ta murmusa tana kallo na,

“Ina zaki ke kuma?”

“Dubo Kawu.”

“Hak’uri zakiyi Batoul, Yanzu ai ba zaki fita koina ba fyace sai da izinin mijin ki. Kiyi hak’uri kinji? zamu ce kina duba shi.”

Gyada kai nayi na koma bakin katifa ina hawaye, Yanzu shikenan kuma dik inda zani sai na tambaya? Wayyo Allah na! Gaba na ya shiga faduwa. Yanzu kenan yar koyarwar da nake yi denata zanyi? Toh ai dama haka auren yake komai dan hak’uri ne, Wata zuciar ta bani amsa. Ya Subhan’Allah! Na furta ina cije lebe na. Koda su Gwaggo Aminatu suka je asibitin suka tarar da halin da Kawu ila yake ciki abun ya basu matukar mamaki, Toh ina zashi oho? Suka tambayi mai mashin din dake gefe ana nada masa fulasta ya sheda musu yadda sukai dashi har maganganun da yai. Suka cika da mamaki, ana duba aljihun wandon sa guda biyu kuwa sai ga sadakin Batoul. Nan suka gano guduwa zai yi dasu, Sai gashi Allah ya nuna ishara akan sa. Gwaggo Aminatu ta cije yatsa tana kallon Kawu ila da wani irin kallo mai tarin ma’anoni, Dan takaici kasa tsayawa tayi ta wuto gida da kudin sadakin, Tana zuwa ta mikomin sadaki na naki karba ina jijjiga kai,

“Me zanyi dasu Gwaggo?”

“Rik’e banason taurin kai, Ai hakkin ki ne ko jari kyaja dasu.. Ilyasu ya gudu dasu sai gashi beje ko’ina ba tsautsayi ya fada akan sa. Duk nasihar da nake yiwa yaron nan baya ji ai ga irin ta nan. Babu kafa d’aya ta balle kamar ta yartsana. Bai masan wanda ke kansa ba, Duk wani abunda likitoci zasu yi sunyi yaci tura, Mutu kwakwai rai kwakwai. Ya shiga koma wai, Allah kadai Yasan ranar farfadowar sa. (coma: A period of prolonged unconsciousness brought on by illness or injury. It can be caused by a variety of problems — traumatic head injury, stroke, brain tumor, drug or alcohol intoxication, or even an underlying illness, such as diabetes or an infection. A coma is a medical emergency.)”

“Subhan’Allah buguwar da yai kenan ce ta haddasa masa shiga coma din?”

Na tambayi Gwaggo Aminatu cike da tausayi. Gwaggon ta gyada kai tana goge hawayen dake tsiyaya a fuskarta,

“Eh! Duk alhaki ne ke binsa Batoul! Nayi nayi nayi da Ilyasu ya dena abubuwan da yake yaki ji, Bansan meyasa yake haka ba. Wallahi shi kadai ya fita zakka acikin mu. Allah ya bashi lapia ya kuma ganar dashi gaskia Ameen.”

“Ameen Ya Hayyu Ya Qayyum!”

“Yauwa bude kunnuwon ki na miki nasiha Batoul... Ina fatan zaki amfani dasu”

“IN SHA ALLAHU Gwaggo!”

Kai na a k’asa. Ina jina tamkar mafarkai wai ni ce yau za’aiwa jan kunne na raruwar aure? Wainan daura aure na? Wallahi tamkar mafarki haka nake ji. Gwaggo ta fyace hancin ta fara magana cikin hankali da nutsuwa....

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali😊😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: _*ETERNAL LOVE□_*

*EPI: 4/8*

••

“Toh!..Zan d'anja hankalin ki akan yadda ya kamata ki dinga tarairayar mijin ki ta siga daban-daban kamar; kissa, jan hankali da kuma ladabi da biyayya kowanne

xan daukeshi d’aya bayan d’aya na miki bayani akansa, ki sani dukkan xamantakewar rayuwar aure ba xata yiwu ba saida kissa, idan akace kissa ta kunshi abubuwa da yawa, kissa ta kasu kashi biyu akwai kissa marar kyau akwai kuma kissa me kyau, Mara kyau itace ta shirye tuggu da makirci da sihiri, Za ki ga kishiya ta kullawa kishiyarta sharri ko idan ta daidaici ta gama girki taje ta tsuga mata gishiri ko yaji ko kananzir ko kuma tai k’ok’arin fitar da ita daga gidan ma gaba d’aya, zaki ga mace ta shiga tsakanin d’an mijinta da mijin,

“Ta cikin dabara ko mace tashiga tsakanin mijinta da iyayensa da makamantansu wannan kissa mara kyau sede muce tur da ita. Allah ka ganar da masu irin wannan kissa, Amma kissa mai kyau itace kulawa da mai gidah da tarairayarsa kamar kwai wanda daga ciki akwai, Kissar magana, kissar tafiya, kissar kwalliya, kissar abinci, kissar tsafta, kissar kallo mind you ba kallon film ba to kallon miji nake nupi, yawwa se kissar shagwaba da kissar kwanciya se kissar kula da jikin mai gidah suma xan d’auki kowanne nai miki bayani akansa Ina fatan kina ganewa?!''

Cikin k’asa da kai da murya na amsa ma ta da,

“Eh Gwaggo..”

“Kissar magana: Cikin nutsuwa da tauna magana xaki gaya masa kafin ki fadeta don gudun gaya masa maganar da baxai ji dadinta ba ko bata masa rai, Ki dinga magana cikin sigar hankali karki dinga bud’e masa muryarki kala-kala wani lokacin ki maketa wani lokacin ki dan budeta wani lokacin ki dinga yi a hankali kamar bakyason magana, wataran kuma idan kinason gaya masa magana mai dadi ko ta soyayya kice saiya baki kunnensa xaki rada masa. Sai kissar mu ta gaba,

“Kissar tafiya; idan xakiyi tafiya kuma kin tabbatar yana gurin ko yana kallonki daga inda yake ki dinga tafiyar da xata dauke masa hankalinki xuwa gareki misali ki dinga tafiya a hankali kamar bakyason taka k’asa wani lokacin ki dinga tafiya kina karairaya kina dan jujjuya jikinki wani lokacin kuma sauri-sauri xaki dingayi kina juya maxaunanki idan ta gaba yake kallon ki kisan yadda xaki dan dinga girgiza kirjinki cikin hikima bata sigar da xai gane ba, amma fa Batoul mijinki kad’ai xaki dinga yiwa wannan kala kalar tafiyar cux kikaiwa wani xaki dau zunubi ne,”

Cigaba da koya mata kissoshi tadingayi kama daga kissar kwalliya, da kissar abinci kissar tsafta, da kuma kissar kallo ciki harda kissar shagwab'a data kwanciya, wanda sosai Gwaggo taja kunnen taakan kissar kwanciya ta k'ar-k'are mata da yadda zatai kissar kula da jikin mijin ta,

“Kin gane?!”

“Nagane Gwaggo”

Cewar Batoul datai wiki-wiki da idanuwa wai yau Gwaggo ce take mata irin wannan zancen, Maganar ma ta manya duk kunya ta dabaibaye ta.

“Yawwa to sai dan karin jan hankali daxan miki wanda idan kika durfafi yinsa tabbas Zaki xamo shalele awurin mijin ki. yaxamto ba wacce yake so da gani sai ke. hanyoyin jan hankalin sune,

“Kula da duk wani abu da mijin ki yafi so, kula sosai da duk wani abun da baya so, ki lura da abinda yake damun shi da hanyar da zaki kula da iyayen shi da dangin su da yadda zaki xauna lafiya da kowa babu ruwan ki da wani kishi na banxa da wofi wanda zai kaiki ga samun hypertension, kishi dole ne ba ace karki yi ba amma akwai irin kishin da akeyi bana yanxu da yaxama na hauka ba, Kede babu ruwanki, domin kin taso Kinga yadda ake zaman chakewa a gidan nan ko?”

Kad’a kai Batoul tai tana wasa da yatsun hannunta d’aya , Dayan kuma tana goge hawaye, cike da nutsuwa.Gwaggo ta cigaba da yi mata jan hankali akan rayuwar gidan miji ta k’ark’are da,

“Abu na k’arshe shine ladabi da biyayya, babbar magana kenan domin duk abubuwan dana fada abaya idan ba ladabi da biyayya yaxama na banxa don duk iya tafiyar ki ko iya farinki idan bakya yiwa miji biyayya meye amfaninsa?! Misali kinyi kwalliyar jan hankali kinyi masa kalar girkin dayake so jira kike ya dawo yaga kwalliya, Yaci abincin da kika tanadar masa amma yashigo ba sannu da xuwa ba karb'ar kayan hannunsa sai dai ki bishi ki dire masa abincin da kika yi masa tana iya

yiwuwa ma alokacin ki fara masa k’arar ko kudi da makamantansu toh tell me tayaya zaiga kyan kwalliyar sannan kuma yaji dadin abincin?!,

“Ko kiga wasu matan miji na magana suna yi suna fada sosai fad’i in fada bai dace ba sam, kamata yai idan mai gidah yana fadansa ki masa shiru idan yagama sai ki bashi hak’uri idan kuma ke aka batawa baxaki iya bada hak’urin ba tunda ranki yakai kololuwa a baci to kiyi shiru kawai kuma ko menene yace kiyi masa koda kuwa ran naki a bace yake don kansa shima xe sakko ku shrya, Wasu kuma matan xaki ga suna yawan korafi akan maxajen su don abinda ba abin fada ba sai su rufe su da fada wasu ma kawai xakiga sun fice daga harkar matan kwata kwata inkinga sun kusancesu to sede idan rabo ya tsinke yawanci kuma xakiga akan maganar da mukai d’axu ne akan rashin gamsuwa damu da maxajen mu ba sayi xakiga mace har mace, Kamar ita tai kanta don kyau sai kiga sun had’a kishi da wadda bata kaitan ba harma xata xamto itace mai fada aji gurin mijin xakiga yana Allah Allah girki ya xagayo kanta don yafi gamsuwa da ita xakiga wasu matan suna yawan tambaya to meyasa wata macen ake gamsuwa da ita wata ba’ayi?!,

“Ba komai bane yake kawo haka kisani sai kowa da irin ni’imar da Allah yai masa misali kowanne jinsin halitta akwai maza akwai mata kuma both ana samun farare da bak’ake dogaye da gajeru mai kib’a da siriri ke kowanne abu dake jinsin bil adama xaki ga nawani yafi nawani to haka ma ni’ima take ajikin mata da maxan wata macen tanada ni’ima sosai bata buk’atar kari wata kuma tsaka tsaki ce wata ma bata da ita se d’an abunda ba’a rasa ba,

“Don haka Batoul, ki sani kamar masu bukatar karin jini da ake cewa ga abubuwan daya kamata suci haka ma matan masu neman k’arin ni’ima ajikin su akwai abinda yakamata suci domin ance idan kanada kyau to kadad’a da wanka,sai dai wasu matan suna amfani da magunguna barkatai wanda wasu ma basusan komeye ba sudai suci susha buk’atar su ta biya kawai shikenan, Wanda zaki ga yin hakan yana haifar da cututtuka barkatai ga mata,shawara ta dake karki xamto cikin irin wa’innan matan masu bankawa cikinsu kowane magani suka ji ance yanayi aa sam karki soma kowaye yakawo ko yaxo maki dashi karki soma amfani dashi kinji dai na gargadeki domin hakan yana haifar da toshewar mahaifa, hana haihuwa ko canxawa yaro kamanni kamar wata k’awata sumayya matar ma’aruf wallahi abinda yafaru da ita kenan, Tahaifo yaro marar cikar halitta abun tausayi saboda ita komai cusawa take ta bankashi a baki duk bamu sani ba se bayan da xata haihu a asibiti dr tace har cancer magungunan suke sawa dakyar aka mata cs don kasa haihuwan tayi abu nabiyu ga kaikayin gaba wato infection,Da kurajen gaba plus ciwon ciki ke da abubuwa da dama de, ki lazimci shan fruits kamar yadda kikaga ana saki sha a kaduna,

“Kankana, gwanda, ayaba, guava, lemo, tumatir, rake, aya, kwakwa, dafaffiyar gyada, xuma, nono, madara, madaran shanu, gurji, cukwi, zogale da ruman da inibi sai tuffa da kuma xaitun kina ganewa kuwa?!”

Nodding kai kawai nayi, gaba d’aya jiki na yayi sanyi sai yanzu nasan tabbas aure aka min, batare da Gwaggo ta damu da damuwar da na shiga ba tacigaba da maganar ta,

“Se abu na k’arshe naga lokaci na ja, Addu'a wato ki rik’e addu'a, wallahi addu'a makarin mumini ce ke duk wanda ya lazimci addu'a wallahi baxai tab'a tab'ewa ba azkhr dinnan ki dinga yawaita yinsu nataho miki ma da wasu littafin du’as din suma ki rik’esu gidanku kullum yaxamto cikin karatun qur’ani musanman suratul baqra domin duk gidan da ba’ayinta ance kamar kango yake, Ki yawaita yin addu’oi na neman tsari ga korar shaid’an ya kuntata masu ya karyasu dama mutane ma sharranta masu nufarku da sharri, addu’a tana jawo yardar allah ta’ala, suna gusar da bakin ciki da bacin rai a zuciya,suna janyowa zuciya farin ciki da nishadi,suna karfafa zuciya da jiki,suna jawo arziki suna kara imani da tawakkul da sabr, kai sunasa komai na mutum ya daidata ya samu peace of mind! Ki kama Allah ,ki rik’e addua da qur’ani Insha Allah rabbi zaki bani labari,anan xan tsaya seki fad’i tambayoyin ki karkiji kunya ta ko tsoro, ki saki jikin ki, ki fad’amun abinda baki gane ba.,”

Shiru Batoul tayi, tana k’as k’as da yatsun hannunta, kanta a ‘kasa kunya dukta isheta jin shirun yayi yawa ne yasa Gwaggo sake tambayar ta,

“Uhum ina jin ki”

Nanma tayi shiru! Gwaggo ta cigaba da cewa,

“Yawwa sai magana ko ince jan hankali da zan miki akan WAYAR MIJI! Kinga wayar miji wallahi tallahi daukar ta masifa ce, Kai idan ba dole bama Karki bari kisan kalar yanayin wayar mijin ki! Domin saninta hypertension ne, daukar ta kuma tamkar shigar ciwo ce, lalubar cikin ta kuma Wlh ciwon zucia ne. Domin ganowa kan ka abinda yafi karfin ranka zakai, tamkar albasa ce idan baki bareta ba babu ruwan ki

da yajin ta ko zubar hawaye, kina fara barewa kuwa idanuwan ki zasu fara rena kansu, Daga nan sai ambaliyar hawaye. So dan ALLAH Batoul babu ruwan ki da wayar sa, Kiyi harkar ki da taki yayi harkar sa da tasa. Shikenan a zauna Lapia. Kina koyarwar ki, Idan ya barki fine ki cigaba ki had’a da business non stop, keep ur self busy, engage in activities by one way or the other. Ki karfafa fara business dinki, income ya dinga shigo miki, wani abun ba sai kin tambayi miji ba kiyi da kan ki, Bani bani idan tai yawa sai miji ya fara kosawa. Akwai wata friend dita *Haj Hafsat Rano* Matar nan tana karatu kuma tana business daban-daban, wallahi baki gaba yadda take maida biyar goma ba, hustler ce. So haka rayuwar ta canza yanzu, keep doing you, find a job ko business of your own, ki kare martabar ki data iyayen ki, stand on your own feet... Ba sai da namiji ake neman kudi ba, kowacce irin sana'a indai ba haramiya bace ki yita ki samarwa kanki sauki dama mijin ki baki d'aya.. lastly inaso kiyi hak'uri , ki kuma yiwa iyayen ki halacci! Ki rike rayuwar auren ki cikin lumana da 'kaunar juna! Haka ALLAH yayi wannan mutumi da yazo d’aga baya shine mijin ki, Saboda haka ruguntsumin rayuwar baya ta wuce Pls! Yanzu kin shiga sahun matan aure, sabon foundation ne zaki gina na zaman gidan miji, wata sabuwar rayuwa ce ta daban, wanda Alhamdulillah kece first wife din mijin ki, turbar da kika dora shi akai haka zai tashi wallahi, Dan kuwa mijin 'kazama, 'kazami ne..hhhh! Toh anan zan dira aya, May your matrimonial home be forever blessed❤”

(Wannan shawarwari kowanne book dina sai kun gansu😂Nasha wahalar hadata shiysa zatai ta circulating♀ Allah ya samu mu amfana da dan abunda ta kunsa Allahumma Ameen!!)

Kuka na barke dashi wanda har sai da kai na ya fara ciwo, Cikin dashasshiyar murya na cewa Gwaggo Aminatu,

“Gwaggo nagode. Allah ya saka da alkhairi.. Ameen!”

“Ameen Batoul din mu, Share hawayen ki kinji? Allah ya baku zaman lapia ya kauda fitna Ameen.”

Tana gama fada ta fice tana nanatawa su Zabbau dasu tsaftace wajen da Bintalo ke kwance, Ni kuwa kifa kai na nayi akan katifa na shiga rera kuka ahankali, Gaba ki d’aya daren ranar ni de bacci kadan nayi domin kuka yafi yawa..

WASHE-GARI

Da sassafe Gwaggo ta tashe ni, Sai kara gyaran jiki ake min, Na tsugunno ne, na wanka na sha da naci, Gaba d'aya nagaji wallahi, Kamshin dake tashi a fatar jiki na ma ta ishe ni. Wani dandatsetsiyar laffaya lace wanda Gwaggo Aminatu ta hado a gudunmawar ta aka nad'amin. Maroon color ne da dishi-d'ishin black. Kai na yasha gyara da sheki, Sosai aka nad'a min ita ta zauna daram. Wani dogon takalmi mai tsini da tsada na sanya shima baki, wallahi nayi kyau domin ni kai na na sheda hakan.

Wajajen sha biyu da rabi motar daukar amarya suka zo guda biyu rak, Domin Gwaggo ta hana kai amarya saboda halin da Kawu ila ya shiga na rai a hannun Allah.. Batoul kuwa tunda aka fa'di sanarwar zuwan su take kuka. Kawunnin ta sun sata a tsakiya da Gwaggo Aminatu sun mata nasiha mai ratsa jiki sosai, Wadda ta sanya Batoul yin hawaye. Daga nan kuma aka hau da ita wajen Innar mu inda Batoul tun ta rungume ta tana kuka,

"Innar mu zan tafi.. Zan tafi.. Innar mu zan tafi.."

Batoul ta shiga maimatawa tana kuka shab'e shabe. Duk dakiyar Innar mu sai da tayi hawayen itama. Tai saurin goge wa tana kallon gefe,

"Allah yasanya alkhairi agidan auren naki, Allah ya kade fitnah. Allah ya azurta ku da yara masu albarka. Allah ya bashi lapia ya baku zaman lapia. Tashi ku tafi."

Innar mu ta karasa fada tana janye ni daga jikin ta. Kuka na fashe dashi sosai ina goge majinar hanci na. Lokaci d'aya mura ta kama ni, Kai na ya shiga sarawa sosai. Dak'yar aka bambare ni daga jikin Innar mu,

"Wayyo Allah na Innar mu! Wayyo Allah na!"

Autar mu ta rirrike ni itama tana hawaye, Muka kankame juna muna sakin ajiyar zucia, Gwaggo Aminatu ta janye ni suka shigar dani wata zungureriyar mota itada

wasu mata biyu dangin mijin dana aura, Sai hak’uri suke bani suna kwantar min da hankali. Tunda muka shiga motar na kifa kai na ina rera kuka a hankali....

KADUNA

Tunda muka shiga kaduna gaba na yake fad’uwa, Banmasan mun isa ba sai da na jiyo hirar su gwaggon kancewar mun isa. Gaba na sosai ya shiga fa’duwa tamkar zai fadi. Na rintse idanu ina lumshe jikakkun idanu na da suka jike saboda hawaye, Bamuyi wata tafiya mai nisa ba naji alamun tsayuwar motar mu, Ahankali matan suka kamo ni suna maimata,

“Yauwa futo amaryar mu munzo...”

Ahankali na fito suna rike dani kai na a kasa, Wani sashe aka shiga dani mai dauke da mutane, amman ba masu yawa ba, Muna shiga suka yo kai na suka rungume ni, Tamkar zasu cinye ni don murna, Lalle sunason dan uwannan nasu domin da alamun soyayyar da suke masa ce ta shafeni.

“Mamma Ahlaam gata..”

Aka kaini gaban wata farar mata kamar ita tayi kanta dan kyau, Rungume ni naga tayi tana sumbatar goshi na. Na sunkuyar da kai na kasa ina sake jan laffayar ta rufemin fuska, Ina jiyo wasu agefe suna zuzuta kyau na. Haka dai akaita adduoi sosai. Aka kai mu wani babban parlor ni dasu Gwaggo Aminatu. Abinci ne kala kala a bubbude wanda kowa zai je ya diba da kansa, Ahankali sauti ke tashi acikin babban parlorn. Sanyin na’urar ac dik ta ishe ni abunka da basabun ba, Na kudundune jiki na ina karkarwa, Sunci abinci sosai ni kuwa na kasacin komai su Innar mu kawai nake tunawa, Dak’yar fadila ta tursasamin na tsakuri wanda take ci naci na kora da ruwa, Bayan sallar la’asar suka dau hanyar komawa Zaria, Naci kuka da zasu tafi harda majina wallahi, Na rungume Fadilah da Gwaggo suna hawaye ina yi, Haka aka janye ni su kuma suka tafi cike da abubuwan arziki da aka babbasu. Bayan sallar ishai wata yar budurwa ta shigo kira na tana murmushi,

“Aunty wai ga kaya kisa zan raka ki wajen Ya MM..”

D’aga kai na nayi ina bin kayan hannun ta da kallo,

“Tohm. Nagode”

Kada kai tayi tana nuna min takalma a gefe kalar rigar,

“Ga shoes din. Ina jiran ki a parlor.”

Murmushi kawai na mata ta fice tana janyomin kofar. Mikewa nai dak’yar na cire laffayar jiki na. Wani band’aki na hango acikin dakin na shige ciki na rage fitsarin da nake ji. Kayan na cire na wanko fuska ta. Rigar na daga ina binta da kallo, Irin arabian dogayen rigunannanne masu duwatsu ajikin su. Tasha ado orange and black. Na yane kai na da mayafin ina zura covered shoe din da ta nunamin. Na kalli kai na ta mudubi ina cije lebe, Ya Mm na maimaita, it sounds familiar ko a film ne oho? Na fice ina lek’a parlorn. A karshen parlorn na ganota tana danna waya, Tana gani na ta mike ta rungume ni tana murmushi,

“Kinyi kyau Aunty Batoul..”

“Nagode sis...?”

“Jannat!”

Ta maimata tana murmushi, Nima nayi murmushin ina riko hannunta yadda ta rike nawa. Inata maimata sunan nata na yan gayu a zucia ta. Ta corridors muka shiga wani babban sashe, Daga kofar da zata sadaka da shiga sashen ta tsaya tana murmushi, Tanada fara’a gaskia,

“Anan zan tsaya Aunty! Ki shiga yana ciki..”

Kada kai nayi gaba na na matukar faduwa. Adduoi na shiga kamowa ina maimatawa har na shiga ciki, Na wuce wani babban parlor na kutsa cikin wani daki, Can na hango mutumi a lullube acikin bargo ga ‘karin ruwa anayi masa a hannu d’aya,

“Assalamu Alaikum!”

Na fada gabana na matukar faduwa kamar zai fad’o. Tamkar a mafarki muryar Batoul ta shiga yin karakaina a kunnuwan Mubeen, Mikewa yai daga kwanciyar da yake yana kokarin bu’de idanun sa, A hankali ya shiga bude su ya sauke su akanta. Tana Juyawa suka hada idanu, Su kayi wani kallon kallo marar fasaltuwa. Mubeen ya mike zumbur yana goge idanun sa,

“Ma..!”

Ya furta a hankali yana kokarin takowa inda nake, Bansan sanda na saki waya ta a ‘kasa ta fadi ba ji kake ‘tartsisss’, Duk na dubibice na shiga dudduba lungu da sako ko zan hango wani daban bashi ba,

“Me…Me kakeyi anan Mubeen?”

Kansa ya dafe yana cije lebe saboda jirin dake dibar sa, Shi duk a zaton sa ma mafarki yake. Tangadi ya shiga yi zai fadi dakyar ya koma baya ya zube akan gado, Dai-dai lokacin su dr Affan suka shiga suna bashi temakon gaggawa, Ni kuwa sandarewa nayi a tsaye domin mamaki, Al’ajabi da tsoro sun gama cika ni. Likitoci ne suka taru akan sa suna bashi temakon gaggawa, Kenan shine marar lapian da aka auramin zanyi jinyar sa? Kenan boyemin akai kowa ya sani? Ina tsaye ina zancen zuci jannat ta shigo ciki ta kirawo ni kan mahaifin su na kira na. Lalle man kai na ya malale da daxu bangane Ya Mm na nufin Muhammadu Mubeen da Jannat ta fadaba. Wurin mahaifin su ta kai ni yana zaune shida wa’enda na gaisar a kofar gidan mu rannan. Duk sai yanzu abubuwa suke ta dawomin da can bangane ba. Kasa jure kallon su nayi na sunkuyar da kai na ina gaishe su. Kowanne ya amsa fuskar sa a sake wasun su nata tsokana ta. Amb Salees wanda shine mahaifin mubeen kuma gwamna na kaduna yai gyaran murya ya shiga yi min nasiha mai ratsa jiki ya kar’kare da,

“Kiyi hak’uri ‘yata. Nasan an tauye miki hakki na aura miki wanda bakyaso kuma dalibi a karkashin ki. Kiyi hak’uri dan Allah! Ga amanar Mubeen nan mun danka mki, Mubeen miskilin matashi ne da baya iya boye abunda zuciar sa ke so ba kuma zai bayyana a tallafa masa ba, Yana dauke da ciwo a zuciar sa wanda kusan haihuwar sa akai dashi, Ciwon nasa shi ya hanashi karatu. Kullum ba lapia dakyar ya fara samun sauki inda muka dawo nan nayi masa sha’awar fara karatu anan jami’ar da kike koyarwa, Ashe Allah zai sa ya hadu dake har ta kaiga aure duk kuwa da ba lallai idan kinsan yana kaunar ki ba.. Munyi mamakin mai ya mayarda Mubeen ya zamto kullum fuskar sa a sake yana wasa da dariya ba kamar shekarun baya ba? Changes de kala kala aka samu daga gare shi, Sai da muka yi zuzzurfan bincike muka gano kece sila.. Batoul! Kiyi hak’uri ki karbi Mubeen a matsayin mijin ki kinji? Dan Allah na roke ki, Ko dan rashin lapiar da yake ciki ahalin yanzu dai kece zaki zamto silar wartsakewar sa ganin ki kawai a tare dashi ya wadatar.

“Da sunan ki ya farfado a bakin sa daga doguwar sumar da yayi, Ta haka muka gano ki muka fara bincike akan ki, Ni da anawa shirmen rokon ki zanyi kizo ki jinyar sa, Sai mahaifiya ta tace a’a ba za’ai haka ba, Gwara ya aure ki tinda dama akwai k’auna a tsakani. Hakan kuwa akayi gashi har an daura, inaso ki dau hakan ki ajiye a matsayin taki kaddarar kenan, Kuma babu wanda ya isa ya wuce kaddarar sa.Kinji ko ‘yata..?”

Tunda ya fara magana kai na a kasa yake, hawaye sai zirara suke. Tabbas na gama hawa *IGIYAR ZATON* ba zan mallakawa Mubeen soyayyata ba da gangar jiki na, Sai gashi Allah ya sanya hakan a matsayin tawa qaddarar. Duk tarun shekarun nan daman shine mijin da zan aura? Hawaye na na sharce ina kara sunkuyar da kai na kasa,

“Babu komai Insha Allahu ranka ya dade..”

Amb Salees yai murmushi yana kada kansa,

“Masha Allah daughter! Ki kira ni da papa kamar yadda mijin ki yake fada kinji? Kinason wani abun?”

Na girgiza kai na,

“A’a Papa..”

“Toh Allah ya miki albarka.. Inde kinason wani abun ki gayamin ko ki aiko a fad’amin kinji?”

Kada kai nayi ina yaba kambawa da dattako irin na ahalin gidan. Mikewa nayi Jannat taja hannu na muka koma sashen da Mubeen yake. Har yanzu likitoci na kansa suna gwagwarmaya. Wani daga cikin likitocin ya leko yana dagomin hannu,

“Yauwa Mrs Mubeen.. Zo Pls”

“Mrs Mubeen?”

Na maimaita ina yamutsa fuska. Dakin na shiga ina sunne kai,

“Zo ki dan kira mana sunan sa kinji..”

Likitan ya sake fada yana nunamin saitin Mubeen.. ‘dankari mak’ari’ ‘Na furta Ina k’arasawa wajen jiki na sai rawar tsoro yake.

“Mu..be en...”

Na fada a rarrabe kamar maijin tsoro, sannan kuma a ahankali ina dafe kirji na dake barazanar fad’owa, wallahi a tsorace nake. Likitan ya sake cemin na nanata sau uku ko zai farfado,

Shiru na d'anyi kamar bazance komaiba, Doctor yace,

“Sau uku pls, Saboda ke kadai ce muke da hope akai. Ko mu baku waje?”.

Kai na d'aga a hankali, alamar "eh", dan hakan kamar zaifin sauk'i.

Babu musu duk suka fice aka barmu mu biyu kawai.

Hakan yasa naji d'an sakewa, na juya idanu tamkar mai hararsa, Mai kuma na tuna sai na sauke ajiyar zuya kad'an ina ciza leb'ena tare da sake matsawa jikin gadon sosai yanda zai iya jina, mayataccen k'amshin turarensa na sake shigemin k'ofofin hanci.....

“Mrs Mubeen! An dace ne?”.

Muryar Doctor ta katseni daga waje. Da sauri nace, “Gashi dai inayi”.

Likitan baice komaiba. dan haka nima na maida hankalina ga Mubeen dake kwance tamkar wani gawa, cikin wani irin yanayi nace,

“Mubeen, Mubeen ka tashi gani nazo, ga Batoul d'in...”

Na kare maganar da wani irin karsashi.

Gani nai hannunsa yad'an motsa, na waro idanuna waje da fad'in “Doctor gashi ya motsa.....”

Da sauri su Doctor suka shigo cikin sassarfa, dai-dai Mubeen na fadin,

“Batoul...Batoul... Ki saurare ni pls.”

Dr Affan yai murmushi yana dudduba kwayar idanun Mubeen,

“Mubeen kana jin mu? Ka farka ga Batoul din a kusa da kai..”

A d'arare Nace, “Ya tashi d’axu fa.. “

Na basu amsa ina ja da baya. Duk kallona sukai da mamaki,

“Mubeen din? Ya tashi mikewa sosai kuma?”

Nace, “Eh, amma kuma sai ya koma ya kwanta.”

Gyada kai yayi ya cigaba da dudduba shi, Ni kuma ina gefe lokaci zuwa lokaci nakan kira sunan sa kamar yadda suka umarce ni. Cikin ikon Allah kuwa ya shiga bude idanun sa yana sauke su akanmu mu duka, yanda yake kyakykyaftasu zai baka tabbacin dishi-dishi yake kallonmu, a bazata mukaji yace,

“Ma..! Kece dagaske?”

Baya naja a tsorace, su Doctor kuwa sai suka sanya dariyar farin ciki.

Ya yunkura yana sake maimaita sunana da kokarin son mikamin hannunsa da kyar. Kasa motsawa nayi, amma ya d'an bani tausayi, dan haka na kada kai, ina juyarwa gefe kadan, ‘Wai Mubeen ne mijina?’ ni jin lamarin nake tamkar a mafarki. Gaba d’aya ya maida ni kamar mudubi, kallo na kawai yake ko kifta idanu bayayi. Cikin haka mahaifin sa ya shigo shida sauran mutanen d’axun. Sunji dadin yadda suka same shi ya farfado, daxuma har ya mike kamar yadda dr Affan ya sheda musu.

Yanda yaketa kokarin son naje garesane ya saka Dr Affan fadin, “Mrs Mubeen zauna kusa dashi Please”.

Tamkar zan fasa kuka haka naji, ga kunya kamar na nutse cikin kasa saboda mahaifinsa da gayyar mutanen da suke tare, amma a mamakina sai naga su ko'a jikinsu.....

“Daughter zauna kinji, karkiji komai”. Maganar papa ta katse shakkuna.

Zama nai gefensa tamkar mai jin tsoro, kamar jira yake kuwa ya sakala hannunsa cikin nawa carab, duk da babu wani karfi tattare dashi. wani iri naji a raina, wai nice yau hannun Mubeen da nawa cikin na juna?, jin abin nake tamkar a mafarki....

Yanda yake ta kokarin son dora kansa saman cinyatane ya saka dr Affan fad'in na taimaka masa ya dora din, nikam lamarin Mubeen ya fara girmar wayona, banida zabin daya wuce bin umarni kodan kunyar idon mahaifinsa, haka na taimaka masa kansa ya dawo saman cinyata, ya sauke wata nannauyar ajiyar zuciya yana lumshe idanu, murya a sanyaye ya furta,

“Thanks Ma..!”.

Ban iya koda kallonsaba balle na motsa, sai ajiyar zuciyar da Papa ya sauke shima ta sakani jin tausayinsu, lallai suna k'aunar Mubeen sosai.

Karin ruwa aka sanya masa hade da wasu allurorin a jijiyoyin sa. Har aka kammala komai kamar yanda dr Affan ya sanar sai kuma gobe idan Allah ya kaimu, yace,

“Mrs Mubeen kiyi hakuri har barcinsa yadanyi nisa, dan yanzu kina zame jikinki zai iya farkawa”.

Kaina na jinjina masa a kunyace.

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER*

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IGIYAR ZATO.....

(Eternal_love)

50

KADUNA

Haka rayuwarmu ta cigaba da tafiya a wannan gida, ina kokarin danne zuciyata wajen jinyar Mubeen da basa dukkan kulawa, hakan nama ahalinsa dadi sosai, Shi yasa suma suke bani dikkan kulawa.

Rashin kunyar Mubeen itace kawai ke batan rai, zuwa yanzu duk yanda zan canjama yaron nan fuska kona d'aure akan karya tab’ani baya jina sai yayi, musamman ma idan zan bashi abinci yafi min duk iya shegen daya gadama. Sai dai ina kokarin dannewa saboda rashin lafiyarsa, ga Doctors dinsa sun shinfidamin dokoki akan yanda zan bashi kulawa kodan dai-daitar komai.

Alhamdullahi yanda nake kokarin bin dokar tasu kuma ana dacewa, dan akwanaki goman nan dana dauka tare dashi jikinsa yayi kyau sosai, zuwa yanzu har dan fita yakanyi harabar gidan yasha iska.

Duk yanda naso sabawa da bakin al'amuransa nakasa hakan, sai dai nasihar Gwaggona tana dakatar da dukkan yunkurina akan komai.

Tunda na tashi a safiyar yau da tunanin maganar komawata makaranta na tashi, dan hutuna ya kare. Abin mamaki sai juya zancen nake a raina da tunanin yanda zan tinkari Mubeen dashi. Cikin kullawa da kwancewa na gama kimtsawa daga shirin da nakeyi, dan wanka na fito, ina cikin fesa turare ya shigo dakin da sallama.

Amsawa nai, sai dai ban juyaba dan ina kallonsa ta cikin mirror. Yanda na hango idanunsa na yawo a jikina duk sai naji na takura, nadan hade fuska dan banason raininsa, sai dai dana tuna kuma maganar komawata majaranta saina dan sake kadan...

Ajiyar zuciya na sauke a hankali jin ya rungumeni ta baya, tunanin dana tafi baisa naji sanda ya iso gareniba, ya dora kansa saman kafadata yana gogamin gashin sajensa a wajen. Take tsigar jikina ta hau tashi, nai kokarin ture hannunsa dake kan cikina amma na kasa hakan.

Ta cikin mirror muka hada ido, nadan hararesa shi kuma yay min murmushi mai cike da ma'anoni da yawa, cikin sanyaya murya yace,

“Tsaurin idonki yayi yawa Fateemah, bantaba ganin matar dake harar mijintaba sai ke”.

Shiru nai ina maimaita sunan Fateemah daya kirani dashi, sai naji kamar ba sunanaba, dan tunda nake a duniya zan iya cewa babu wanda ya taba ambatar sunan da hakan..

Sake katsemin tunani yay da cewar,

“Kinason kiji labarina Mah!?”.

Samun kaina nai da daga masa kai alamun amsawa. Yay murmushi tare da sumbatar wuyana, sannan yace,

“I love you”.

Ban tanka masaba, danshi wannan kalmar ya maidata tamkar me a harshensa, a yini yakan fadamin ita sama da sau goma, duk da ni banajin son nasa amma inajin dadi, sai dai nakan kanne bana nuna masa naji dadin dan karya samu lagona.

Hannuna yaja zuwa bakin gadon, ya zauna sannan ya dorani saman cinyarsa. Da sauri na kalle shi inason sauka amma sai ya rikeni da kyau yana girgiza kansa.

“Dan Allah karkice zaki tashi kinji My Fikre”.

Ban tankashiba, na dauke kaina ina mamakin solon fitina kala-kala na Mubeen.

Hannuna daya kama cikin nasa ya murza yace,

“Mah! Kin zama tawa ni kadai, sai nake ganin Kamar mafarki... Ina kaunar ki fikre!”

“Meye fikre?” ‘Na fada inadan juyowa na kallesa.

Sai da ya dagan gira daya da wani salo sannan yace,

“My love.... Ko bakyaso?”.

Shiru nai ban tanka masaba, saima dauke kaina daga sashensa da nayi. Yace,

“Toh ki zaba d’aya: Babe, Love, Beautiful, Princess, Buttercup, Cutie pie, Dreamgirl, Lovebug, Sunshine, sweetheart, Precious..”

“Banason ko d’aya.. Bani labarin da kace.”

Ajiyar zuciya ya sauke yana sake narkar da idanun sa akai na, Hannun sa d’aya na aikin murza hannu na.

“Kiyi hak’uri da neman aure na da ya zamto tilashe akan ki, Da farko dai ina dauke da ciwo ne wanda dashi aka haife ni, Tun ina zanin goyo nake shan wahala. Wanda na samu hakane alokacin da Mamma zata haife ni shekarun baya, (Preeclampsia is a condition during pregnancy where there is a sudden rise in blood pressure and swelling, mostly in the face, hands, and feet. ||If the preeclampsia remains untreated, it can develop to eclampsia, in which the mother can experience convulsions, coma, and can even die. However, complications from preeclampsia are extremely rare if the mother attends her prenatal appointments.),

“An haife ni da ciwon zucia, Ga ciwu ka kala kala, Ko yaushe muna hanyan asibiti tun ina kankani dan dai Allah yayi da sauran kwanaki na agaba, Ga chronic ulcer da nake da ita, Fikre idan zan lissafo maki ciwukan dake damu na zamu kwana mu wuni anan, Yawan ciwukan dake damu na yasa banyi karatu da wuri ba, Dana fara karatu ciwo zai hanani na dena karatun, Ya zamto kawai anamin home school har na girma nazo na fara online university Manchester na dena, Daga nan na fara AIU (Atlantic international university) shima months nayi na dena, Daga baya dai nayi Boston University Online shima na dena ciwo ya tashi, dana warke na fara Drexel University Online shima ciwo na worsen, Daga karshe kuma nayi Arizona State University Online shima ciwo ya tashi kawai na dena gaba d’aya ma. Nayi shekaru bana fita koina, Sai daga baya nake bin driver mu dakko kanne na a German embassy school wato mashkur da Aeedah. Jannat kuma tana high school duk aciki.,

“Ina ta shan magani a hankali har ciwukan ya lafa muka dawo nigeria. Papa yace na fara nan Ahmadu Bello a time din ma na nuna banaso nafison home school ko na kara applying online. Papa yace A’a! Ashe Allah yayi zan hadu da ke. Ina son ki fikre, Ina kaunar ki wanda kalamai sunyi kadan wajen nuna soyayya ta agare ki, Kin daukeni a matsayin ‘kankanin yaro saboda kinga ina karkashin ajin da kike koyarwa ko? Toh ba komai bane yasa hakan face wannan lalurorin na rashin lapia. Su suke maidani baya a komai na rayuwa, Kiyi hak’uri da auren ‘kanin ki kamar yadda kikace din bayan dai baki girme min ba...” ‘Ya kare maganar da kumshe dariyar shak’iyanci ’.

Na zabga masa harara ina yatsina fuska,

“Harara ta kike? Ai shi namiji baya kadan.. Allah Fikre kibar cika baki hmm!”

Kwatsam haysam ya fadomin a rai na, Domin shine ke gayamin kalmar haka a shekarun baya. Mubeen ya sake yin rau-rau da idanu kafin ya cigaba da cewa,

“Fikre! No matter how many challenges come in my life, I will face them without difficulty if I have your support.I am taken by the most beautiful woman in my life. I Love you!..”

Shiru nayi ina sauraransa har sai da ya gama magana sannan na sauke numfashi, naji tausayinsa kwarai amman ban nuna ba a fuskata. Shikam idanu ya tsuramin tamkar yaune ya fara ganina, da alama dai yanason jin wani abu daga bakinane, amma saina dauke kai abuna naki cewar.

Ya langabe kai kadan yana sake kafeni da wadannan idanun nasa masu saka dukkan gashina mikewa batare dana shiryaba, can kuma ya dafe tsakiyar kirjinsa yana faman rintsa ido. Yadda naga yana janyo numfashi da kyar ne yasa ni saurin matsawa kusa dashi hankali na a matukar tashe, jan numfashin ne ya tsananta tsoro ya kama ni ban san lokacin dana sauka a jikinsaba na zauna a bakin gadon tare da sanya hannuna na dora a inda yasa nashi din.

“Sannu Mubeen, zuciyar ka ce ko kirjinka?”

Na tambayesa cikin sanyin murya mai tattare da jin tausayin halin da naga ya shiga tamkar zan fashe da kuka.

Kasa magana ya yi, sai hannunsa da ya dago da kyar ya kwantar min da kaina a saitin kirjin nashi inda yake masa zufin. Ya na iya, dole nayi luf saboda ina tsoran kar wani sabon abin ya faru akansa bayan ana ganin nice maganin warakarsa, kar naje kuma na zama sanadin mutuwarsa gabaki daya.

Jinai ya saki wata sassanyar dariya cikin kunnena, nai saurin dagowa na kallesa da mamaki. Gwalo yaymin tare kashe ido daya ya nuna kasa da babban danyatsansa.

Fahimtar shakiyancine ya sakashi yin hakan saina hararesa na yunkura zan tashi. Saurin kamo hannuna yayi ya maidoni muka fada a gadon tare yana dariya. Kokari kwacewa nake amma na kasa, gashi yasa kafa ya danne tawa,

“My fikre wallahi zuciyarki gulmammiyace, anason dan yaron nan ana kaiwa kasuwa”.

Ture shi nake sonyi amma na kasa, ya kuma matseni yana dariyarsa, cikin kunnena yace,

“Fadamin tun yaushe kika kamu?”.

“Ban saniba, ni wallahi bammasan ya akai ka rainaniba har haka Mubeen?”.

Dariya ya sake kwashewa da ita fiyema data farko, wadda nikuma ta sakani kuluwa da sabon haushi. Juyowa nai sosai garesa zanyi magana cikin masifar da ni kaina ina mamakin yanda na iyata a yanzu kawai bawan Allahn nan ya hade mabinmu waje daya. Duk yanda naso kwatar kaina na gaza, dan Mubeen duk yanda na rainashi yafi karfina, tunma ina gwada dan karfin nawa harna koma nai luf ina karbar sakwanninsa.

Tafiya tayi nisan da gaba dayanmu munfita hayyacinmu, ban tashi fargaba saida naji yana neman wuce gona da iri. Dan karfina na tattara na turashi, kasancewar shi yayi laushi saina samu nasara. Nai azamar juya masa baya wasu hawayen takaici na gangaromin a fuska.

Ina jiyosa yana sauke numfashi da sauri-sauri mai alamun murmushi, ban sake gigin juyawaba na cigaba da hawayena a haka.

“I love you my Fikre”.

Na jiyo muryarsa yana fada a hankali.

Banko motsaba, sai sauran hawayena dana goge, ‘gaskiya Mubeen ya bala'in rainani’ na faɗa a zuciyata batare dana san maganar ta fito filiba.

Jinsa kawai nai ya kwantomin a baya yana fadin,

“Ni na isa raina malamata, kawai dai kinsan nima a gida nine malamin”.

Hannunsa naso turewa amma saina gagara, maganar malanta da yayi kuma ya tunamin abinda ke raina. Shiru mukai na tsahon lokaci, kowannema a ransa yana daukar dan uwansa ko yayi barcine. Babu zato mukaji kiran sallar karfe biyu.

“Mah kin makarar dani banyi sallah da wuri ba”

Mubeen yayimaganar cikin kunnena’. Janye jikina nai daga nasa, bai hananiba kuwa. Sai da na sakko daga gadon na kalle shi ina daga girata cikin dauriya da danne kunyarsa da nakeji ta cikamin kirji.

“Kafin nazo gidan waye yake sawa kayi salla? Ko kuwa dan ni yau kaga mun kwanta gado daya a tare shine zaka ce min haka?”.

Sai kawai naga ya saki murmushi yana lumshe idonsa, na harareshi ina nufa cikin toilet.

Ina shiga na maida kofar na rufe sai na jingina, kaina na dafe tare da kirjina, ina jiyo dariyarsa daga nan, wani haushi ya sake kamani, nai kwafa ina nufar yin fitsari nai alwala.

Idanu na zaro tare da jin wani takaici, sai kawai naji hawaye na zubomin, wai yanzu nan nice dan yaron can zai saka yin wanka? ‘Na shiga uku ni Batoul’ kawai sainaji kukan dayafi na farko karfi ya zomin.

Babu yanda na iya, dole na cire kayan jikina nai wankan tsarki, rufe kofa da naji tun dazunne ya sakani ji a jikina yabar dakin, dan haka na fito kaina tsaye.

Ajiyar zuciya na sauke ganin bayanan, na zauna ina goge gashina a gaggauce danna samu nai salla.

“Mah! Kema sai da kikai wankan kenan”.

Wani masifaffen faduwa gabana yayi, zuciyata kamar zatai zallo ta fado kasa saboda kunya da takaicin Mubeen , bangama dawowa hayyacinaba na ji ya zare karamin towel din hannuna ya dora saman kaina yana cigaba da tsane ruwa, sai faman jiyo sautin murmushinsa nakeyi. Bakina kam yagama mutuwa rumus yau, ko kallonsa naki yarda nayi harya kammala ya sakamin doguwar riga.

“Tashi muyi salla, mun makara da yawa”.

Yanzunma ban taka masaba, bankuma kalleshi ba amma na mike dan muyi sallan. Bayan mun idar ya juyo yana kallona da wani murmushin, tamkar na nutse a wajen haka nakeji...

“Wai ‘dan yaron nan ya zama surikine yau Fateemah?”.

Maganar Mubeen ta daki kunnuwana, Harara na dago na dalla masa ina yunkurin mikewa daga wajen. Saurin kai hannunsa yay ya jawota ta dawo ta fada jikinsa.....

Muryata na rawa nace,

“Mubeen banason abinda kakemin, sakemin hannu”.

Kin saki yayi. saima sumbatar goshina da yayi, yace,

“Allah idan kika cigaba da cikamin baki mai gaba dayama zanyi ki tabbatar na girma niba yaro bane”.

“Innalillahi” na shiga ambata da sumbin al'ajabin Mubeen da tsagwaron tsaurin idonsa na rashin kunya.

“Sorry Mah! nayi shiru”.

Ya fada a hankali cikin kunnena.

Shiru nai masa ban tankaba, shima sai bai sake maganaba yadai zubamin idanu kawai kamar wata tv.

*_Washe gari_*

Tun a jiya dana samu Mubeen yabar dakin muka koma yar wasan buya, naki yarda mu hadu, nama kulle dakina nakuma bar key a ciki yanda bazai iya budewaba, yamin kiran duniya da knocking naki na bude, daga karshe dole ya hakura ya kyaleni, Amman dan naci sai da ya dawo washegari ala dole na bude.

Kamar kullum ina tashi nayo wanka nabi lungu da sako na shafa turarukha, Wata bou-bou rigar lace na saka. Na dan tsaya ina shafa hoda kadan gudun maik’o. Ta mudubi na hango Mubeen yana kallona tashin sa kenan daga baccima daga gani. Na turo baki gaba ina yatsina fuska dan na manta na bude dakin da asuba na fita dakko ruwa kitchen.

“Ina kwana....?” na fada cikin dauke kaina

Lumshe idanu yayi ya bude yana taune lebe hade da sakin murmushi,

“Fikre! Barkan mu da safiya.. Meyasa bakya tashi na kullum sai ki ta tashi kina riga ni yin wanka?”

Ya karasa fada yana langab’ar da kai da karasowa inda nake. Na tabe baki ina cigaba da zizara kwalli acikin idanu na,

“Idan zaka shigo dakin mutane ka dinga neman izini dai”

Dariya yayi data bayyana hakoransa sosai yana fadin,

“Saikace wani kwarto , nida dakin matata kuma”.

Ban tanka masaba, saima saurin barin wajen da nayi, nama fita a dakin.

Tana fita Mubeen yayi murmushi yana nufar bandaki. Na dawo dauke da shayi naji motsin ruwa a bandaki, ban kawo wanka yakeba nadai zauna kawai ina shan tea din, dan da yunwa na kwanta yaron nan jiya yajamin kin cin abinci. Yadan jima sannan ya fito daure da bathrobe.

Saurin dauke kaina nayi tamkar ban ganshiba, yace,

“Kinyi kyau..”

“Nagode..” na fada batare dana kalle shi ba dai.

Tsulum sai gashi a gaba na yana shafa kwantaccen gashin kai na dana hade shi wuri d’aya da ribbon. Na lura yanason gashi, Bayan idan santsi ne dakyau nasa yafi nawa. D’ankwali na dauka zan daura ya rike yana zama a saiti na,

“Ki bar kan ki a haka... Kinji?”

Kasa masa musu nayi na kad’a kai kawai ina cigaba dashan tea dina. Mik’ewa yai yana murmushi ya jima yana taje sumar kansa, Kafin ya zauna a kasan carpet yana tankwashe kafafu bayan ya zira jallabiya a jikinsa.

“Fikre.. bani abinci yunwa nakeji”

Ka’da kai nayi na kakkai masa abincin dana shigo dashi a tire gaban sa,

“Toh a bani”

Yana iya haka na zage Ina bashi domin in dai shine zai ci to ba zai shi da yawa ba barin shi zai yi. Amman inde nice zan bashi to zai ci sosai wani lokacin harda ‘kari. Tas ya cinye na hada masa tea yasha.

“Mubeen..”

Saurin dagowa yai ya kalle ni. Na dan kalli gefe ina jujjuya maganar a zucia ta,

“Dan Allah inason komawa school.”

Ware idanu yai sai kuma ya hade rai yana turo baki ni abinma daria yaso bani na danne nima,

“Kaji? Dan Allah.”

“Meyasa kikeson komawa Zaria kingaji da ni ne?”

Girgiza kai nayi,

“A’a! Kawai inason na cigaba ne.”

“Hankali na ba zai kwanta ba Fikre! Ace ina kaduna matata kuma tana Zaria, Amma zan gayawa su papa”

“A’a kabarshi kawai.”

Na fada jiki na a sanyaye. Taune k’asan leben sa yai yana sanya hannu na acikin nasa, Yana son yimin wasu salo masu birkitamin lissafi a wasu lokutan,

“Fikre ina sonki, So mai tsanani. Banason kiyi nisa da ni, Nasha wahala kafin na mallake ki. Banason kiyi nisa da ni ko yaya wallahi.. Idan su Innar mu ki kai missing sai muje mu gayda su, Sai muje kuma school din ko?”

Kada kai nayi kawai jiki na yai sanyi.

Sai da yaci abincin sosai sannan yacemin ya koshi, tashi nai na tattare kwanikan na fita dasu, ina dawowa na iske baya dakin.

Zama nai abuna ina kokarin kunna wayata, sai gashi ya shigo cikin kananun kaya, yayi kyau sosai, amma saina dauke kaina tamkarma ban ganshi ba.

Wayar ya zare daga hannuna, sannan ya kama hannun ya mikar dani tsaye, ya dakko wayar sa akan gado hade da bude drawer ya dakko min hijabi,

“Saka muje wajen su papa..”

“Ga mayafin kaya na nan agefe sai hijabi.”

Nabi zungureran hijabin daya bani da kallo,

“Eh a haka zaki sa Allah! Duk sun tashi sun sa miki mayafai shara shara. Ni wallahi bana son su.”

“Toh ni inason kaya na ahaka.”

“Toh ni banaso, Ai dai ni zakiwa kwalliyar ko? Toh inde ni da ke ne ko dankwali ba sai kin saba amman inde zaki fita daga kofar nan to hijab zaki sa. Zan karo miki wasu.”

Na kalle shi cike da karfin halin jin kalaman sa. Karbar hijabin nai na zura. Na isa gaban mudubi na dakko maroon Jambaki zan saka kenan Mubeen ya karb’e yana ajiye shi,

“Meye hakan? Bani kaya na.”

“Fikre bar jambakin nan ba sai kin saba.”

“Mubeen meyasa kake haka ne? Fisabilillahi ya za’ai na tafi haka kamar wadda aka tono a rami ba dan jambaki. Dan Allah bani.”

“Ga Vaseline nan ki shafa ya wadatar.”

Banbi takan sa ba nai ficewa ta na barshi a tsaye yana daria. Da sauri ya karaso ni yana rikemin hannu, Na hadu da gamo na haka naita kiciniyar kwacewa amman yak’i saki na. Saboda rashin ta ido har parlorn Mamma Ahlaam muka k’arasa a haka hannun mu saqale dana juna. Na zare nawa dakyar ina matsawa can gefe bayan mun gaysa dasu.

“Ga abinci can a dinning.”

“Tab mun koshi, wallahi Fikre ta bani dankali da kwai da kunu ga tea harda soup na hanta kinji ciki na kuwa..”

Mamma Ahlaam tai murmushin jin dad’i, Ni kuwa gaba d’aya kunya ta ishe ni.

“Ai kuwa kayi kiba ba laipi. Alhamdulillah! Gwara kai ta ci ai ka samu ka maida jikin ka.”

“Ki mata magana ma wallahi sani fa take a gaba sai na cinye da yawa Mamma.”

Haj Ahlaam tayi murmushi kawai tana cigaba da danna wayar ta, Mubeen yai ta neman maganar sa har papa ya dawo muka gaysa nide duk kunya ta kamani. Anan muka wuni har dare muka koma sashen mu. Wanka nayo na haye kan gado can karshe ina dudduba waya ta. Daga nan bacci mai nauyi ya d’auke ni. Mubeen na ganin tayi bacci ya lallaba ya shige jikin ta yana sinsinar wuyan ta da k’irjin ta, Ga hannun sa d’aya na karakaina a ilahirin jikin ta. Ita kuwa Batoul ji take tamkar ana mata tafiyar susa sai kara bankaro jiki take tana susa, ta nan Mubeen ya samu ya rage zafi yana murmushi..

WASHE—GARI

Da safe muka shirya driver yaja mu zuwa Zaria, Sanye nake cikin doguwar rigar atamfa da hijabi blue kalar kayan. Gaba d’aya rai na a bace yake akan takurawar da Mubeen yake min tasa hijabi da sauran su. Dan sai da muka kwashi fad’a ma kafin mu taho, Tunda muka taho yake neman magana ban kula shi ba. Naci jambaki ja ya gauraye labbana, Haka muka karasa kofar gidan mu, direban ya sauka a hanya Mubeen ya karasa damu. Yana gama parking nasa hannu zan bude najita gam,

“Bude min na fita..”

“Idan naki fa?”

“Dan Allah fa nace..”

“Goge jambakin ki tukun..”

Hawaye ne ya tahomin na shanye ina dudduba tissue babu, Kasan atamfar jiki na na dago zan goge ya dakatar dani,

“Ungo nan goge..”

Juyawa nai da nufin kallon sa kawai ya hade bakin mu waje d’aya.. Wata irin sweet and passionate sumba mai zagaye jini da bargo ya shiga min, Cikin wani salo na daban yana yi yana dakatawa yaja numfashi ya cigaba, Daga goge jambaki sai abu yaso ya faskara, Inata janye jiki na ya rike ni gam yana cigaba da budurinsa. Wasa wasa tun ina irgen sakanni har na fara na mintina. Tun ina mamaki har lamarin ya fara bani tsoro ganin ya danna wani madanni kujerar da nake tayi baya ya rankwafo sosai yana kallon fuska ta, Nai saurin rufe idanu na ina rufe bakina,

“Wayyo dan Allah! Kabari..”

Murmushi yai ya koma ya zauna yana kifa kansa a sitiyari fuskar sa na kallo na. A hankali cikin lumshe idanu yace dani,

“Zan shigo daga baya...Kije”

Saurin kada kai nayi ina gyara zaman hijabi na na shige da sauri ko takan wayata ban bi ba.....

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□

[9/16, 11:29 AM] □: *_EPI: 4/9*

Karon farko a rayuwata dana samu kaina da karema Mubeen kallo, tabbas shid'in k'yak'yk'yawane, abinso ga kowacce mace, sai dai ni bansan meyasa banajin komai a kansaba, har cikin raina jinsa nake yamin ƙanƙanta, duk da kuwa ingarman namijine mai cikar zati, ta ko ina ya tseremin, banda ya kasance ɗalibina babu yanda za'aima na hura hanci wajen tunanin na girmesa. Na d'an sauke numfashi ina kai hannuna kam sumarsa da tun d'azun take d'aukar hankalina, haka kawai na samu kaina da tura yatsuna cikinta, sai dai tamkar ina a tsorace da hakan, zuciyata sai fat-fat takeyi, na lumshe idanu na ina shaƙar daddad'an kamshinsa tare da jin laushin sumar na ratsa fatar hannuna.

Gani nai ya motsa kad'an, tare da sake matse hannuna, na bude idanu da sauri na kalli fuskarsa, sai dai kuma barci yake, yana fidda numfashi a yanayin da yake tabbatar da baida lafiya sosai.....

Mamma Ahlaam dake tsaye a bakin k'ofa tun kusan mintuna uku tai murmushin jin dad'i, cikin takun k'asaitarta na manyan mata da keji da mulki ta k'arasa shigowa da sallama a bakinta....

Kaina na d'aga da sauri dan a bazata naji sallamar tata, nai saurin janye hannuna dake cikin sumarsa ina 'yan kame-kame, jinai tamkar na ture kan Mubeen dake a cinyata.

Ta dafa kafad'a da murmushin dahar nake iya jiyo sautinsa,

“Daughter karmuyi haka dake, ni mamace ba suruka ba kinji”.

Kaina na d'aga mata ina murmushi, ta cire hannunta daga jikina ta zauna a bakin gadon kusa dani, hannu takai bisa fuskar Mubeen ta d'an shafa tana fad'in,

“Su Mage sarakan san laushi dama haka akeso, anbi an hayema yarinta cinya daga zuwanta ko hutawa bataiba”.

K'asa na sakeyi saboda kunya, ad'an awoyin dana d'auka a cikinsu, na fahimci tsantsar k'aunar da sukema juna, musamman ma Mubeen, kowa kaffa-kaffa yake dashi tamkar shine autan gidan.....

Maganar Mamma ta katsemin tunanina,

“Daughter bara na taimaka miki mugyara masa kwanciya kema ki kwanta ki huta”.

Ba tare dana kalleta ba nace, “Ai Doctor yace a barsa barcin yay nisa sosai dan karya farka”.

Murmushi tai na jin dad'i, wani sanyi na ratsa mata zuciya, har ranta tanajin Batoul zata kawoma rayuwar Mubeen sauyi mai tsafta, ta sauke numfashi da mik'ewa.

“Mungode sosai Batoul, mun gode da shigowarki rayuwar yaronmu, duk da munyi abinda koba'a fad'a manaba muma munsan son kaine, dan d'aura muku aure a lokacin da bai dace muyi hakanba, ki yafe mana, wannan ita kad'aice mafitarmu.....”

Cikin son katse hak'urin da take bani nai saurin cewa, “Kibar bani hak'uri Mamma dan Allah, ni bakumin komai mara kyauba".

Yanzunma Murmushi ta saki tana shafa kafad'ata, ta juya ta nufi k'ofa ba tare data sake min maganaba, haka kawai naji a raina kukane ya taho mata, sai tausayinsu ya sake kamani.

Cak ta tsaya a bakin k'ofa, amma bata juyiba, sai da ta share kananun kwallar da suka zubo mata sannan ta juya ga Batoul tana murmushi,

“Mungode sosai Daughter, Allah yay miki albarka, nasan tunda sukai masa allurarnan da wahala ya sake farkawa sai kuma safiya, nanda mintuna goma ki tashi kema ki kwanta ki huta kinji, sai da safe”.

Kaina na d'aga mata, amma na kasa magana saboda tausayinta dake sukar raina, uwa kenan.

Bayan fitarta ajiyar zuciya na sauke ina maida idona kan Mubeen dana lura barcin Nasa ya fara nisa sosai, hannuna na maida saman sumarsa na dora, sai dai yanzu kam ban saka yatsuna a cikiba. A take kewar tawa uwar da auta ya dawoma zuciyata sabo, sai kawai naji hawaye nabin kumatuna.

Nayi nisa sosai a tunani har ban ankaraba dare nata sake zurfi, sai da gidan ya k'ara daukar shirune na dawo hayyacina saboda motsawar da Mubeen yayi harya raba hannuna da nasa, kallonsa nayi ina mai matsa hannuna saboda sanyi da yaymin,

yanda yake dan mutsu-mutsu ne ya fahimtar dani gyara kwanciya yake sonyi, taimaka masa nai na maida kansa saman filon mai azabar taushi, a take ya sake gyara kwanciyar, na sauke numfashi tare kokarin cire masa ruwan dan ya karema.

Sai da na shiga toilet din dake dakin nayo fitsari sannan na fito, anannefa naita raba idanu da tunanin inda zan kwanta, dan nikam bazan yarda mu kwana gado daya da wannan yaronba, gashi inason canja kayana zuwa na barci, sai dai kuma bansan inda zan samuba. Ganin banida wannan mafitar sai kawai na nufi kujerar dake dakin mai kyar nai kwanciyata, da gyalen jikina na lulluba, dukda banji nayi yanda nakesoba haka na hakura dan hakan yafi sauki a gareni.

*_Washe gari_*

Abin mamaki da asuba Mubeen sai ya riga Batoul farkawa, tunkanma kiran sallar farko ya tashi shi, dan allurar ta sakeshi, sai dai bai sakkoba yana a gadon kwance.

Yana bude idanu da fuskar Batoul dake kwance a sofa ya fara cin karo, dan kamar an dai-daita kwanciyar tasu suna fuskantar junane.

A zabure yay yunkurin tashi saboda mamaki, dan a daren jiya duk zatonsa a mafarkine yake ganinta, amma yau kam ya gasgata lallai a zahirinefa.

Kansa yay saurin dafewa yana cije baki saboda jikinsa babu kwari, gashi yayi yunkurin tashi da hanzari. Shiru yay a zaunen amma idonsa na kanta kyam, ji yake kamar idan ya matsar zaik'i ganintane. Sai da ya samu hutu na mintuna kusan biyu kafin ya iya zura kafafunsa kasa ya sauka, har lokacin hannunsa dake da kansa.

Dakyar ya mike, yana layi ya nufi inda Batoul ke kwance, zubewa yay gaban sofa din yana sauke numfarfashi, amma yayin daya kai hannunsa kanta ya tabbatar itadince dai ba mafarkiba sai ya saki wani murmushi yana dora kansa a jikinta tare da ajiyar zuciya mai karfi,

“Ma! Da gaske kece tare dani? Da gaske ba mafarki nakeba? Da gaske kece muke kwance a daki daya? Da gaske kece kikazo dubani?”.

Dagajin yanda yake jero tambayoyin kasan na sambatune kawai.

Jin nauyin abu a jikina ya sakani bude idanuna da sukaimin nauyi, gabana ya fad'i ganin Mubeen a jikina dukda dai a zaune yake a k'asa, kansane a jikin nawa zuwa kafad'unsa.

Yunk'urin tashi nai amma sai ya sake sakemin nauyinsa,

“Mubeen lafiya dai?”.

‘Nai maganar ba tare da sanin ta subuce minba ba’.

Idanunsa kafe a kaina ko kyaftawa bayayi ya motsa labbansa da kyar,

“Wallahi da gaske kece Ma.. Dama zakizo dubani da gaske?”.

Harga Allah sai nadanji tausayinsa, amma na kanne ban nunaba, yunkurawa nai na tashi ina zame kansa daga jikina, ina gama dai-daita zama yana sake doramin kansa bisa cinya tamkar mai tsoron na gudu.

‘Yau naga abinda ya girmeni’ na fada a zuciyata da wannan lamari na Mubeen.

Kafin waninmu ya sake magana aka kwala kiran sallar asubahi a masallacin dake cikin gidan na gwamnati. Kallonsa nayi ina bata fuska dan banason yace zai kawomin rainima,

“Ka dagani salla kaga ake kira”.

Shiru bai mitsaba, sai murza hannuna dake cikin nasa kawai yakeyi a hankali, yayinda idanunsa keta kallona tadan hasken fitilar dake kunne a dakin, gaba daya kallon ya gundureni nikam, shiyyasa naketa kauda fuskata gefe, amma bawan Allan nan yaki janye idonsa kona sakan guda.

Maganar da nayice ta sakashi motsa baki dakyar yana dafe kai, yace,

“To zanyi wanka”.

“Wanka kuma?”

‘Na maimaita ina kallonsa’.

Kai ya dagamin yana yamutse fuska alamar dai bayajin dadin jikinsa,

“Ki hadamin ruwan da zafi sosai dan jikina ciwo yakemin”.

Ban tankashiba, sai dai nayi yunkurin son tashi, hakan yasakashi janye kansa nikuma na mike zuwa bayin ina wani kumbura baki da ni kaina bansan na minene ba.

Duk da ban ganiba, naji a jikina kallona yakeyi, haka na shige bayin tare da kunna fitila mai haske sabanin wadda na tarar a kunne kalar blue.

Tsaf bandakin yake babu wani datti, amma saina tsinci kaina dason sake tsaftacesa, na wanke sama-sama kafin na hada masa ruwan wankan mai dan zafi tankar yanda

ya bukata, nai yunkurin yin alwala sai naga ma ashe babu damar hakan, abin takaici sai naga jini yazomin, dafe goshi nayi na rasa ya zanyi, saboda ko pad banzo da ita gidan ba, gashi da kunya na tambay, nace a bani. Fitowa nayi bayan na gama wanke fuskata da hannu da kafa, na dawo cikin dakin. Inda na barsa anan na dawo na iskesa zaune kansa kwance a kujerar dana tashi.

Shiru nai ina kallonsa, dan bansan ma mizance masaba, ganin lokaci na tafiya na daure nace,

”Ga ruwan wankan can ka tashi kayo”.

Idanunsa ya dago ya kalleni da kyar, sai kuma ya lumshesu tare da mikamin hannunsa, kin rikewa nayi, saima baya dana danja kadan ina hararsa.

Yay guntun murmushi yana buso iska kadan a bakinsa, murya a raunane yace, “Bazan iya tashiba sai da taimakonki Mah, kiyi hakuri”.

Kamar bazan kulashiba, sai kuma na kama hannun ina kauda fuska. Duk zatona zan iya tadashi a haka, dan ganinsa nake ba wani jikiba, ashe karyata tasha karya, dukda yana a halin ciwon jikin yan mazan na nan, jinfa bazan iyaba yasani kallonsa, shima kallona yakeyi.

Yay guntun murmushin karfin hali da cewa,

“Dan yaron nan baida nauyi ko?”.

Kauda kaina nai daga sashensa ina sake hade fuska, na mika dayan hannuna ya kama yana karfafa jikinsa dan yasan bazata iya dagashiba da gaske, a ransa sai fadi yake, ‘Amma itanan jinta take yayata’.

Bansan yanaiba nikam, dan ina tadashi hannuna na zare na matsa baya.

Baice min komaiba ya nufi bayin cikin bin bango, ina tsaye ina kallonsa harya shige, na sauke ajiyar zuciya a hankali ina komawa saman kujerar na zauna.

Tagumi na zabga ina tunane-tunane, har yanzu jina nake wata banbarakwai matsayin matar Mubeen, nice ɗan yaron nan wai ya aure?

Naja guntun tsaki ba tare dana saniba, kasan zuciyata inajin wani takaicin wannan auren. Tsahon lokaci bai fitoba, harma na fara tunanin wani abune ya faru dashi a bayin sai kuma naji motsin za'a fito.

Tashi nayi da sauri na fita, ina zuwa babban parlour na fara dube-duben ta inda zanga hanyar dakina da aka fara kaini, sai naji murya Jannat tana gaida ni.

“Aunty Bee an tashi lafiya.?”

Juyowa nai da sauri sashen da take, nayi murmushi nima ina amsawa.

Ta tambayeni jikin yayanta na amsa mata da cewar, “Da sauƙi, yana wankane”.

Yʻar dariya tayi da fadin, “Tunda kina gefensa ai dole ya warke”.

Bance mata komaiba sai murmushi dana danyi, kasan raina ina tunanin kona tambayeta pad d'in, dan tabbas za'a iya samun matsala daga nan zuwa wani lokaci....

Katsemin tunani tayi da cewa, “Aunty Bee mekike nema ne?”.

Saida na danyi jim kafin Nace, “Ammm ina ne zan samu audugar mata?”.

Jannat ta girgiza kai cikin rashin fahimta tace, “Me kenan Aunty?”

“Sanitary Pad nake nufi.”

Sai a sannan tace,

“Okay bari na dakko miki a daki na.”

Ta juya zata tafi nayi saurin kiranta ta tsaya nace.

“Wane daki ne kayana suke ciki?”

Jannat ta kuma yin murmushi tare da nuna min kofar da yatsanta. Godiya nayi mata sannan nayi saurin zuwa na shige harda sanya mukulli.Toilet nashiga dan nai wanka kafin ta dawo.

Koda Jannat ta dawo ta murda taji kofar a rufe, sai kawai ta juya ta nufi dakin Mubeen, duk a zaton ta na koma can.

Mubeen koda ya fito yaga Batoul bata nan sai baice komaiba, yaji dadin jikinsa sosai yau, ballema yanzu da yay wankan nan, ruwan jikinsa ya karasa tsanewa, sai faman sauke ajiyar zuciya yake, a gaggauce ya ciri jallabiya ya saka a jikinsa, dai-dai nan kuma Jannat tai sallama a kofar dakin nasa. Daga ciki Mubeen dake kokarin tada salla ya amsa tare da bata izinin shigowa.

Harta shigo idonsa a kanta, fuska babu walwala yace, “Lafiya dai?”.

Murmushi ta masa da fadin, “Lafiya lau Yaya, nazo ganin ko kun tashine dama, Sai yanzu ka tashi?”

Kada mata kai kawai ya yi tare da kallan hannunta.

“Aunty ba ta shigo nan ba?”

“Ya akai?”

Sai kawai ta daga masa pad din tana cewa.

“Tacene naje na kawo mata pad, kuma na duba dakin ta naji a kulle sai na taho nan, bari naje nayi knocking.”

“Kawo nan kawai idan tazo sai ta dauka.”

Yayi maganar yana mika hannu alamun ta bashi. Mika masa tayi kuwa cikin girmamawa, ya saka cikin aljihu kafin ya juya yana kokarin tada sallah, sai kuma ya juyo yana kallon Jannat daya bari a tsaye.

Yace, “Yaushe tazo nan?”.

Jannat data fahimci wadda yake nufi tai murmushi tana juya idanu, “Yaya idan na fada minene goron albishir dina”.

Wajen zama ya nuna mata kafin ya juya ya tada sallarsa. Bata musaba ta zauna tana murmushi, tana nan zaune harya idar da sallar yay addu'a kafin ya juyo gareta, batare da yayi maganaba yay mata nuni data fada.

Cike da doki ta taso ta dawo kusa dashi, “Humm yaya fara fadamin tukuycina to”.

Kamar bazai tankaba sai kuma cayay, “me kike so?”.

Cike da zumud'i tace, “Yah sabuwar Tab”.

Murmushi yay mata kawai ya dauke kansa, hakanne ya sakata fahimtar ya amince, ta sake matsowa kusa dashi tamkar mai rada tace, “Yaya jiya aka kawota bayan an kulla muku igiya uku cif”.

A matukar razane ya kalli Jannat, bakinsa har rawa yake amma ya kasa cewa komai. Ta tuntsure da dariya kuwa, cikin tsokana ta kuma fadin, “Yah MM yau kai ai sabon angone na Aunty Bee”.

Yanzunma kasa magana yayi, harta fice bai iya motsawaba, koda wasa bai kawo hakan a ransaba, kawai sai jin hawaye yay na gangaro masa a kumatu, yayinda yakejin gabadayan nauyin kirjinsa na sauka wani sanyi da nutsuwa na mamayeshi.

Nikam sai bayan ta fitane na fito daga bandaki, jinta shiru da nayine ya sakani tunanin koma ta manta, harna hakura na gama shirina na fito da tunanin zuwa dakin Mubeen ko tissue na samu sai muka hadu, nan take shaida min cewar wai ta kaimin dakin Mubeen, dan karta yi tunanin wani abu yasa na saki murmushin yake nayi godiya tare da wucewa. ita kuma ta nufi kitchen din sashen da muke tana yiwa mai girkinsa magana.

Da sallama ciki-ciki na shigo dakin ina sake tamke fuska dan bana bukatar raini, sai dai muna hada ido dashi gabana ya fadi ganin hawaye nabin kumatunsa.

Cikin tsantsar firgici na karasa garesa har ina neman hardewa na fadi, ni zatona ko jikin nasane, hannu nakai jikinsa ina fadin, “Mubeen jikinne? Komu kira Doc.....”

Hannu kawai yasa ya fisgoni na fada jikinsa dukda bayajin kwarin jikin, gabana yay masifar faduwa, na shiga mutsu-mutsun son kwace jikina da son yin magana amma ya hanani kowacce irin dama. Mamakin karfinsa nayi, yanda nake ganinsa hakannan ban taba zaton zai iya min wannan rikonba, “Mubeen meye hakane wai? Me kake son.....”

Nanma ya dakatar dani ta hanyar sake kankameni yana jan wata nannauyan ajiyar zuciya da taso wuntsulo tawa kasa. Na gagara fahimtar matsalarsa, gashi yaki min magana kuma.

Nai saurin ture fuskarsa daga jikin wuyana saboda yanda yaketa tura kansa yana shinshinata, ga hawaye yanata digamin.

“Mubeen banason wannan abun Please ka bari”.

Cikin rawar murya ya shiga fadin, “Yanzu da gaske ke matatace? Halalina Batoul!? Dan Allah kin amince dani matsayin miji? Kina sona? Zaki rayu dani? Zaki kasance dan.....”

Saurin dakatar da sambatunsa nayi ta hanyar turasa da karfi, na janye jikina daga garesa gudun karna batashi saboda jin zubar abu, a dayan bangaren kuma na kula neman haukatamin tunani yakeyi, tsigar jikina dukta mike saboda sabon al'amarin da yazomin dashi.

Matsowa yay kusa dani, nai saurin matsawa baya ina hararsa, yay wani murmushi yana cije lebensa na kasa da lumshe ido.

Tashina ina kuma zabga masa harara da kokarin son dai-daita kaina, yayinda idanuna ke dube-duben ta inda zan gano pad din amman wayaam babu shi.

fahimtar da Mubeen yayi ne ya sakashi mikewa dad'an karfin daya samu yanzu ya ciro ta a aljihu, kallansa nayi da mamaki har ya bude ya d'akko guda d'aya yana

barewa, ga baki daya kunya ta mamaye ni, amma gudun karyaga lagona saina hade fuska tamau ina dauke kaina daga kallonsa.

“Mah gashi.” ya fada da alamun shakiyanci.

Na maka masa harara tare da zuwa na warce duka ina hade rai na.

“Sorry Mah rage miki aiki nayi.”

Cewar Mubeen cike da shakiyanci. Nayi masa banza cikin fushi na shiga toilet nasa, da kofar bayin na jingina tare da rumtse idanuna na dafe kirji, sai kuma nai kwafa kawai.

Koda na kammala na jima ban fitoba, sai da na dai-daita kaina sosai sannan na fito, sai faman cin ‘daci nake ni a dole anyi min abinda bansoba.

“Good morning Mah my Fikre..”

Na tabe baki ina kawar da kai, ya taso ya nufi inda nake tsaye, yasa tattausan hannayensa yana kokarin riko ni duk da cewar a rankwafe yake tafiya saboda ulcer din sa har baya ta rike mishi baya iya mikewa sosai.

“Ina gaishe dake fa baki amsa ba.”

“Ka tashi lafiya.?”

“No Mah na tashi da tsantsar ciwon baya, ko zaki matsa min shi?”

Na kada kai cewar ba zan yi ba tun da tambaya ta ya yi ba wai umarni ya bani ba, sai Jina yi kawai yace.

“Okay to bari na kira Papa daman shine yake min kafin zuwan ki.”

Ina jin haka na san kuma zai iya sai na ce dashi.

“Muje nayi maka karka fara kai karata wajan iyayen ka”

Murmushi yayi tare da jan hannuna muka nufi kan gado. Kwanciya yayi ni kuma na sunkuya ina matsa masa a hankali, cikin rashin sani naji ya janyo ni na fada kanshi, murya kasa kasa yake cewa,

“Na fi san nauyinki ni wannan tausar bana jin komai.”

Ai kuwa na fara kokarin kwatar kai na amman yaron nan ya hanani, har sai da ya jiyo muryar su Dr Affan sannan ya sakar min jiki na tashi na tsaya ina karanta wasu takardu kamar gaske. Murmushi Mubeen yai yana kallo na ta kasan idanu, na balla masa harara kafin na amsa sallamarsu da basu izinin shigowa kamar yanda suka bukata.

Saurin gyara mayafina nai ganin harda Papa, na koma gefe tare da durkusawa har kasa ina gaisheshi. Cikin fara'a ya amsamin, ya kai dubansa ga Mubeen dake zaune yana kallonmu.

“My Daughter lallai na shaida ke farin cikinmuce, a kwana guda kacal munga haske tattare da Mubeen”.

Murmushi nai ina sake dukar da kaina kasa, ya taka zuwa ga Mubeen ya zauna gefensa, ina jiyosa yana gaishesa, shi kuma yana amsawa cikin tsantsar kulawa mai nuni da jin dadin ganinsa hakan.

Suma su Dr Affan sunji dadin canjin da aka dan samu, nan suka duddubashi tare da sake bada shawarwarin yanda zai samu kulawa.

A haka Mamma da Jannat suka shigo suka samemu, sai mai aiki dake biye dasu d'auke da wani kwando mai azabar kyau da aka rufo da farin kyalle.

Itama cikin kunya da girmamawa na gaisheta, ta amsamin da kulawa hannunta cikin nawa, mai aikin ma rissinawa tai ta gaisheni, sannan ta gaida Mubeen da masa yaya jiki.

Dakin yayi shiru na wasu mintuna da Doctor Affan ya kammala magana da Mubeen.

Muryar Papa na tsinkayo yana tambayar Dr Affan d'in ko sun kammala?.

“Yes na gama your excellency! Sai zuwa da yamma. Allah ya kara sauki yasa kaffarane..”

“Ameen..”

Muka amsa baki d’aya, Gaba d’aya duk suka fice banda mahaifin su da Jannat da Mamma. Suna ta maganganun su da Mubeen dake kallo na yana basu amsa, Sam bashi da kunya wallahi. Ni duk na dubibice ma gaba d’aya, amma shi ko a jikin sa, Wai an tsikari kakkausa. Amb salees yai gyaran murya yana kallon Mubeen.

“Toh Mubeen ga amanar daughter nan. Mun nema maka auren ta, Za tai jinyar ka, Idan ta kawomin karar ka ko sau d’aya ne sai na saba maka wallahi.”

Mubeen ya saki baki galala yana ware idanu cike da mamaki, duk da dai dama Jannat ta sanar masa d'azun.

“Papa da..Dagaske?”

“Zan maka karya ne?”

Kasa boye farin cikin sa yai ya kalle ni na zabga masa harara ina mai da kai na kasa, Amb Salees ya kalli Mamma suna daria.

Mik'ewa sukai duk suka fice da sanar mana suna zuwa.

Jannat ma ta gama tsokanar sa tukun ta rik’o hannu na tana masa wasa,

“Aunty Batoul muje bacci ko? Dan ya kamata ki kara hutawa k..?”

Wata harara ya wurga mata yana nuna mata kofa,

“Fita kafin na tashi na karairaya ki.. idiot.”

Daria Jannat ta shiga kyalkyalewa tana rufe fuska,

“Ya mm meyai zafi? Ni wasa nake. Aunty Bee sai anjima zan dawo na tayaki hira”

Ficewa tai da sauri tana daria, Na juya ina hararar sa.

“Meye hakan?”

Lumshe idanu yai yana karkatar da pillow dinsa saiti na.

“Mah dagaske ne?”

Harara na kuma zabga masa ina yamutsa fuska,

“Nima bansan kai bane da bazan taba yadda ba, yaro dakai, tsaurin idonka yayi yawa wlhy..”

Kasaitaccen murmushi ya saki yana shafa kansa, yad'an tabe baki da dage kafadarsa, “Karfa ki cika baki da yawa love, amma da kanki zaki tantance koni yaronne”.

N

Shiru na masa ina mai da kai na gefe, ya kawo Hannunsa yana ri’ko nawa, cikin wani salo ya d'an murza.

Idanu na na rumtse saboda wani abu daya tsargamin, “Cikamin hannu kafin na sab’a maka”.

Murmushi yai yana cije lebe,

“Idan naki fa? Uhm!, yanzufa ked'in tawace Fikre!”.

“Banason iskanci cika ni dan Allah” ‘Nai maganar muryata na rawa da sake yin sanyi’.

Wata y'ar dariyar mugunta yayi da cewa, “Iskanci? Mutum da matarsa sai ace yayi iskanci? Wallahi Kamar a mafarki haka nake gani Mah. Ina kaunar ki fikre! Ina kaunar ki..”

Jan hannuna nai yanda dole ya sakarmin, domin ya fara cazamin kai,

“Zan sha tea..”

“Tea kuma?”

Na bashi amsa ina kallon dakin, Komai akwai harda kayan shayin. Mikewa nai na shiga hada masa, inaji a jikina kallona yake. hakan yasani jin sake takura ina jinjina rashin kunyar yaron nan, na dawo na mika masa. Girgiza kai yayi yana langabar da kai...

“Ki bani da kan ki..”

Kamar na sharara masa mari haka naji, na dire kifin ina fad'in, “Zaka yini da yunwa kuw.....”

Sallamar Jannat ta hanani karasawa, dole na amsa mata tare da bata izinin shigowa. Ta ajiye karamin kofin data shigo dashi tana zama gefena, “Aunty Bee ga addu'oin Yah MM inji Mamma, tace daya kammala cin abinci a bashi yasha”.

Kaina na d'aga mata ina satar kallon Mubeen, ya dagan gira daya, na kauda kaina, cikin hanzari yacema Jannat data mike wai ta dawo ta zauna.

Hakan da yayine ya sakani fahimtar da biyu yayi, naji kamar na kwad'a masa mari yasin.

Cikin danne dariyarsa yace, “Bani tea d'in karya huce Mah”.

Danne zuciya ta nai na zauna gefensa, dan banason k'anwarsa tai tunanin wani abu daban.

kofin na saka masa a baki ina murmushin yake, shiko idonsa a kaina yana sha a hankali yana wani murmushi mai ma'anoni da yawa, ‘Ni kam na shiga uku da kallo’. Nai maganar a zuciyata.

“Ina sonki Batoul..” ya faɗa yana kashemin ido daya.

Da sauri nakai dubana inda Jannat take zaune, sai naga ma sam bamu take kalloba, hankalinta nakan wayarta, na cije lebe ina danna masa kofin a baki,

“Ouchhh da zafi fa”.

Harara na zabga masa tare da masa gargad'i da ido, Jannat ta mike tana dariya ta fice abinta.

Tana fita na ajiye kofin ina sake zabga masa harar, shikuma yay min gwalo da d'age kafad'a alamar ko'a jikinsa.

Kamar zan fasa kuka haka naji, na dauke kaina kawai batare dana tanka masaba.

ZAFAFA BIYAR

KAUNAR MU: MAMUH GEE

ALKAWARIN ALLAH; HUGUMA

GUDU DA WAIWAYE: BILLYN ABDUL

DAURIN GORO:HAFSAT RANO.

IGIYAR ZATO: MISS XOXO

LITTAFI DAYA 200

BIYU 300

UKU 400

HUDU 450

BIYAR 500

ZAKU BIYA KUDI TA BANKI TA WANNAN ACCOUNT DIN□□

2260792279

MARYAM SANI

ZENITHBANK

saiku tura shaidar biyanku ta maana screenshot ta wannan layin□□

07067124863

*_GA MASU TURA KATIN MTN SAISU TURA KATINSU ZUWA GA WANNAN NUMBER TAREDA TURA MATA SHAIDA_*□□

09032345899

Sayen nagari, maida kuɗi gida masoyan asali☺😻□□😍😍😘😘□□□□□□[9/16, 11:29 AM] □: _Could this actually turned into something real? Shin ya zata kaya ne da zukatan masoya biyu wanda suke da banbance-banbance a tsakanin su? The class of the have and the have not??? Suraidah 'yar gidan wani babban oil tycoon ce.

Muhammad Mahboub kuma d'an gidan talakawan talak ne. Shin ya zata kaya ne da qulluwar zuciyoyin wanda ba tsaran rayuwa bane ballanatana aure😮? Tab Shin ya kuke ganin wannan ruguntsumin zai kaya? Dr Falal Rabiu mai Mai wani sanannen billionaire ne wanda keda rijiyoyin mai a fad'in Najeriya, yana taimakon talakawa amma shi kam baya son talaka ya rab’e shi. Taya za’ai Muhammad Mahboub ya zamto siriki agare shi? Kai abin da kamar wuya. Mahboub *ANNURIN ZUCIYAR* Suraidah ne. Da sonshi ta rayu ya rene ta ya girmama a zuciar ta. Shin ko Suraidah zata iya bijerewa mahaifin nata? Tab! dankari Makari. Akwai cakwakiya fa, kun ta6a ganin talaka mai tsattsauran ra'ayi? Ku biyoni muje dan kuji me za'a kulla a tafiyar. Wannan labarin yasha banban da sauran rabarai na, zai ta6a zuciyoyin masu karatu, sannan zai fad'akar daku masu karatu, insha Allahu zai sanyaku nishad'i. Akwai zazzafar soyayya da kuma zazzafar kiyayya, akwai jarumtaka, sadaukarwa ta fannoni da dama, *ANNURIN ZUCIYA* daban yake a cikin sauran labarai. Na marubuciya (HAJJAH CE)akan nera dari biyu□□ (+234 706 528 3730)

IGIYAR ZATO.....□

(Eternal_love)

Wattpadd:missxoxo00

51

Mubeen ya bi wayar tata da kallo, Can ya dauka yana kallon yadda ta farfashe. Number sa ya gwada dialing yaga ba tada number sa. Cije lebe ya janyo wayar sa ya saka layin ta aciki. Ya sanya mata number sa yai saving da ‘Hubby.’

Murmushi yayi kafin ya zura ta aljihu ya shiga cikin gidan bakin sa dauke da sallama, Yan gidan suka amsa suna binsa da kallo tamkar zasu cinye shi. Sama ya haye dakin su Batoul kansa tsaye kamar yadda autar mu ta masa iso. Gaisawa sukai da Innar mu kowanne yana jin kunyar kowa. Ni daria ma abin ya bani wallahi. Can Mubeen ya mike zai tafi gidan su Aunty Rahila ni kuwa kemadagas nayi na juye kai na gefe ina kafa kofin kunu a baki. Yana wa Innar mu sallama yana kallo na ni

kuwa na kauda fuska don banason kallon sa. Ficewa yai bayan ya ajiyewa autar mu kudi fal wai ta sai sweet.

“Tashi ki masa rakiya mana..”

Cewar Innar mu dake jefamin kallon ban kyauta ba. Tashi nayi ina cuno baki na sauka kasan. Yana cikin mota ya bararraje kamar ba tafiya zai ba.

“Toh ka gayshe su.. “

“Zo kiji....”

Ya fad’a yana janyo ni cikin motar hade da rufe ta da lock,

“Zazza’bi nake ji..”

“Sannu Allah ya sauwake..”

“Ki rungume ni na minti uku kawai.. Dan Allah karki ce a’ah!”

Ajiyar zuciya na sauke ganin yadda yake narkar da idanu ya dafe goshi, kada kai nayi ban ko amsa ba kawai naji ya bani wata kyakkyawar runguma yana sauke ajiyar zucia. Na shiga raba idanu ina kiciniyar kwace kai na amman ya hana sai sunbatar gefen kunne na yake,

“Ina kaunar ki fikre..”

Kwace kai na nayi na matsa ina gyara zaman hijabi na.

“Sai yaushe zan zo na dauke ki?”

“Sati d’aya kacal..”

Ware idanu yai yana in’ina,

“Sassa sati kuma?”

Na daga kai ina hada hannuwa,

“Kaji pls!”

“A’a! Ni fa yau zamu koma.. Kema kinsan ba zan iya rashin ki a kusa da ni ba ko da kuwa na yan awanni ne.”

“Fisabilillahi yaushe muka zo da har zamu koma? Ko fa kawu ila bamu je mun gano ba..”

“Na yadda zamu kwana d’aya! Amman ba zaki kwana agidah ba gaskia, Ban fa warke ba.”

Ya k’arashe maganar yana langabar da kai, Na kauda kai na gefe ina yamutsa fuska,

“Kuma kawai sai na bika mu tafi ina to?”

“Muje hotel..”

“Ho me?”

“Hotel..”

Ya bani amsa yana kwantar da kujerar sa. Na kalle shi ina jinjina kai,

“Yau naga abunda yafi zare tsawo.. Ai sai ayi damu.”

“Mace da mjjin ta? Wa zeyi magana? Ni dai zan dawo na dauke ki anjima bayan isha’i.”

“Bude min na fita..”

“Fikre pls..”

“Budemin na futa Mubeen.”

“Allah ya huci zuciyar ki..”

Bude min yai na fita zucia ta na kuna, Iko da takurar da yake nunamin ta isa. Gidah na shige raina a b’ace, Bintalo na shiga na duba tana kwance tamkar kayan wanki sai dai a kwantar a tayar. Sai surutai take tana babbaka daria,

“Sittin ta ubangiji sai an fito dasu, Su uku ne, Na ajiye su a kwallar da Ruma ta aikon. Amman aka sace! A hayye yau ga gaye ba makilis...”

“Sannu Baba..”

“Sannu ladiyo kudin kika kawo? Kawo su nan naji danshin su.”

Ganin yadda kanta ya birkice yasa na fito ina jinjina kai cike da tausayi. Daki ne shiga muka shiga hira da Innar mu, Wadda na lura tana kunyata yanzu domin rabin hirar da autar mu muke yi. Bayan sallar ishai har na bararraje akan katifar Innar mu, Na cire kayana daga ni sai vest da zani na fara gyangyadi autar mu ta tashe ni,

“Yayya ki tashi uncle Mubeen yaxo daukar ki..”

“Yazo ina?”

“Yana ‘kasa.. Innar mu tace ki fito ku tafi.”

Hawaye ne suka shiga reto a fuska ta bansan yanayin bakin cikin dana shiga ba. Hijabina na zara na zura kawai na fita ban wa kowa sallama ba. Baya na bude na shiga ya tayar da motar muka tafi wani hotel. Sai wani ciccijewa yake yana rage murya,

“Fito mu shiga Fikre..”

Yana gaba ina biye dashi a baya muka shiga cikin hotel din, Wani babban parlor mai dauke da daki aciki muka shiga. Na zauna akan kujera ina dafe kai na,

“Fikre...”

“Fikre! Talk to me pls.. “

Banza na masa na cire hijabi na ina yamutsa kai na. Shaf na manta vest ce ajiki na da zani ba bra. Kallon da Mubeen yake bina dashi ne yasa na farga, Dai dai lokacin room service ya turo k’ofar,

“Soooo pestiferous! Meye haka malam?”

Ya karasa fada yana hade jiki na da nashi, mutumin ya bamu hakuri yai saurin ficewa , Kirji na ya manne da nasa gashi vest din ta kwanta. Naita kiciniyar kwace kai na Mubeen ya hana ya matse ni ga gam..

“Fikre yi hakuri.. Bar ni naji dumin jikin ki zucia ta zafi take.”

Bazan iya ba gaskia, Kiciniyar k’wace kai na nashiga yi Mubeen ya rike ni gam. Dak’yar na mike na shige bandaki da sauri, Alwala na dauro na fito banbi takan kallon da yake bina dashi ba, Sallah na tayar ta nafila na shiga sallamewa ina yin wata har Mubeen ya mike ya kwanta dakyar yana dafe da ciki. Ina idarwa na karasa nesa dashi ina sake jan hijabi na,

“Zaka ci abinci?”

Girgiza kai yayi yana rintse idanu. Can karshen gadon na kwanta ina kudundunewa da bargo. Ahankali na jiyo hannun Mubeen akan hijabi na,

“Meye haka?”

Nace dashi ina juyawa, Kallo na yai idanun sa duk sun kankance,

“Minti uku kawai..”

Rungume ni yai sosai ya kashe bedside lamp ‘yau naga abunda yafi zare tsawo’ Na fada a zucia ta ina raba idanu. A hankali naji ya zare hijabin jiki na yana yawo da hannayen sa acikin rigata,

“Mu..”

Ban karasa ba ya hade bakin mu yana tsotsa ahankali, Ga hannun sa na yawo ajiki na. Wai ni ce a gado d’aya da Mubeen hannun sa na yawo a jiki na? Kuka na fashe dashi jin abubuwan da yake yimin a jiki na, Hak’uri ya bani dakyar ya zare bakin sa ya maidamin hijabi na sannan ya rungume ni, Yana ta bani hak’uri a haka bacci ya dauke mu..

Da safe wanka nayo na maida hijabi na, Na kasa hada idanu dashi domin dana kalle shi daren jia nake tunawa duk kuwa da ba’abinda ya shiga tsakanin mu. Ai kuwa sai neman magana yake naki biye masa. Gida ya sauke ni na canza kaya da hijabi gaba d’aya na zama matar malam dai. Wajen su Aunty Rahila muka fara biyawa sannan muka dubo Kawu ila da har yanzu bai farfado ba, Daga nan muka wuce kaduna...

Har muka isa garin Kaduna babu wanda ya sake magana, sai dai hannuna yana cikin nasa yana matsawa. Muna shiga gida na wuce daki na saboda na kagu na cire hijabin jikina da duk ya gama takura min, na cire ina ninkewa sai gashi ya shigo naki juyawa na kalleshi dan karma ya yi magana naji tausayin shi.

"Fikre zan yi wanka please, sannan kice zaki tayani yi a bisa umarni na na mijin ki. Idan kuma kince ba zaki tayani ba fine, zan samu yadda zan yi."

Mubeen na gama gaya min haka yasa kai ya fice ba tare da yaji me zance ba. Mamaki ya kamani cikin raina ina hango abubuwa da yawa wanda banyi tsammanin Mubeen zai dinga furta min su ba duk da cewar shi din miji na ne a yanzu. Hararar kofar nayi sannan na karasa toilet nayi abunda zanyi na fito. Hijabin na sake dauka nasa ina tunanin ta yadda zan gujewa wannan katuwar bukatar ta Mubeen domin har ga Allah ba zan iya yin abinda yake so ba. Ina shiga dakinsa na tarar dashi zaune akan stool daga shi sai boxer yana faman kallona da alama ya shirya ni yake jira. 'Lallai yaron nan daman haka yake? Shi yasa ita a tsarin ta taso ta auri wanda

zai ji kunyarta ba wanda itace zata ji kunyar shi ba, yanzu dubi Mubeen wai ni yake jira.

"Fikre are you ready.?

"Na me fa?"

"Har kin manta da maganar mijin ki ko?"

'Ikon Allah, wallahi magana yake min tamkar wani babba kuma a bisa nuna gargadi yake min. Jiki a sanyaye na karasa wajan toilet d'in kamar na fashe da kuka, na kunna heater na tari ruwa nasa turarukan wanka a cikin ruwan sannan na juya ina kallon kofar. Tsayawa nayi ina tunanin ta yadda za'a yi nace dashi taho nayi maka, gashi na kasa zuwa na lallaba shi saboda karma ya kawo min wani wargin. Dana rasa abin yi sai kawai na fito kaina a kasa dan ba zan iya sake kallonsa a yanayin da yake ciki ba.

"Fikre ya aka yi."

"Kayi min afuwa kayi hakuri ka daure kaje kayi wankan can kai daya, wallahi ba zan iya yi maka ba harga Allah."

Nayi maganar kamar zan hadiyi zuciya dan haushi, ya kuwa fara takowa a hankali zuwa inda nake tsaye. Na kasa koda motsi bare na matsa masa har sai da ya karaso kusa dani yasa hannayensa ya dafo kafaduna yana kokarin shigar da idanunsa a nawa amman na ki yadda hakan ta faru. A hankali ya jani zuwa jikinsa ya kwantar da kaina a saitin kirjinsa wanda yake tsananin bugawa har yafi nawa tsananta, muryarsa a sarke cikin kalamai masu karya jini da tsokar jikin dan adam yace min.

"Fikre kinji ko? Kinji yadda kike a cikin zuciya ta ko? Fikre zuciya ta kaunarki take yi a koda yaushe, soyayyarki ta zame min kamar zuciya a cikin jikina wanda idan ta bugu zan iya rasa rai na, shin kina son kiyi kisan kai?"

Ban san lokacin da na dinga girgiza masa kai ba, saboda jin yadda bugun zuciyar tashi ke daga min kai na da ya kwantar a gurin. Yasa hannun sa a bayana yana shafawa yayin da kansa yake saman nawa. Duk sai naji nima na fara karaya, meye aibun Mubeen a tare da ni? Matashi kyakkyawa dan asali dan gwamna mai hankali da nutsuwa. Wacece ni da har nake neman cutar da kai na ta hanyar haramtawa zuciyata abin da Allah ya mallaka mata. Ni yar talaka, marainiya, yar gidan mata tara gidan daya tara duk wani tarkacen duniya, sai kawai nayi luf a jikinsa ina lumshe ido.

"Na yafe miki kije zanyi wankan ni kadai, nasan tabbas yanzu ba zaki iya ba sai nan gaba lokacin da kika amince na zama miji a gareki."

Sai ya dago ni yaja hannuna ya zaunar dani a bakin gado shi kuma ya juya ya shiga toilet yana jan kafa. Langab'e kai nayi ina jin wani abu yana tasowa tun daga tsakiyar kaina har zuwa babban yatsan kafa ta, na lumshe ido tare da fadawa kan gadon ina tunani. Kafin ya fito nabar dakin naje kitchen inda na tarar da ma'aikata suna ta aiki, gaida su nayi sannan na fara wurga idanuwa ina son na hango koda akwai abinda zan kama musu. Muryar Haj Ahlaam na jiyo tana kira na, na juya tare da zuwa inda take na durkusa har kasa ina gaisheta.

"Me kike yi kuma a kitchen.?"

"Babu koma Mammah kawai zuwa nayi ko zan samu abinda zan taya su dashi."

"A'a ba zai yiwu ba, ki tashi yanzu kije ki dakko jakarki zamu je dubiya yanzu."

Ban Musa mata ba naje na dakko wayata da jakata naje muka tafi, sam banyi tunanin sanarwa da Mubeen ba ganin mahaifiyarsa ce ta bani umarnin bin nata. Sai da muka je muka dawo naje dan na kwanta na tarar dashi kwance yana kallan saman p.O.p nayi sallama yaki amsawa sai wani kallo da ya jefeni dashi.

"Daga ina kike?"

"Dubiya muka je da Mammah dasu Jannat."

"Kin tambaye ni?"

"No da naga Mammah ce ta sani shi yasa na manta ban gaya maka ba."

Sai kawai ya sako daga kan gadon, yanzu ma daga shi sai boxer amman ba na dazu bane wani ne ya kuma sakawa. Dauke kai na nayi ya matso kusa dani.

"Fikre har yanzu baki dauke ni a matsayin mijin ki ba ko?"

Na girgiza kai alamun a'a ya sake matsowa ya kamo ni tare da zare hijabin jikina yana cewa.

"Gashi kuwa kin fita baki sanar dani ba."

Nayi shiru domin ni kai na nasan mai laifi ce.

"Idan har kika tafi kika barni, zuciyata batada sukuni har sai kin dawo gare ni Fikre ina sonki."

Yana fadar haka naji ya zuge min zip din riga, nayi sauri zan rike masa hannu ya kamoni gabaki daya ya matse a jikinsa tare da dora bakin sa akan kunnena ya zura harshensa yana jujjuya min shi a ciki. Nan da nan na rikice masa kafafuwa na suka soma rawa kawai sai ji nayi ya dauke ni gaba daya ya kwantar akan gado.

Nasan tunda ya yi min wannan kwanciyar dole sai ya kamo min baki, dan haka nayi saurin rufeshi ya yi yayi ya sanya nashi ya kasa dan haka sai ya koma wani gurin

wanda yasa ni saurin yin magana ba tare da na shirya ba na fara yi masa magiya ina rokansa.

"Mubeen please, dan Allah Mubeen karka yi min komai ina ganin mutuncin ka."

"Shhhiiiii Fikre, idan har muna gida nine malaminki dole duk abinda nace ko nayi to ke naki kawai ki aikata. Idan muka koma school kema ai kece malamar tawa? So ba'a hana malami isar da darasin da yake son isarwa ga wanda yake neman karin matsayi."

Sai duk ya kashe baki na, tsabar mamakin kalamansa yasa na kasa kuma yin magana, sai da naji ya zare rigar jikina nace.

"Please Mubeen dan..."

"Karki hanani, idan har kin san ke bakya bukata to nikam zamana tare da ke yasa duk wata jijiya dake jikina bukatar ki, na baki dama ki toshe kunnuwanki ki rufe idanunki dan karma kisan ke nai wa hakan."

"How Mubeen?"

"Nima how kike son na yi wa haura?"

Yaron ba zai gane irin tashin hankalin da nake ciki ba, shi yasa duk yadda zan rokeshi ba zai haura ba. Kwanciya ya yi tare da sanyani cikin jikinsa yana shafar bayana bakinsa a kan wuyana yana min yawo da sajen sa, tsigar jikina sai tashi take yi yarrrr yace dadi.

"Fikre kece burin rayuwa ta, kece alfaharin rayuwata, I am proud of you because you are intelligent and beautiful, You are everything I admire, aminci ya tabbata a gareki ya Annurin zuciya ta..."

Yana gama fadar haka ya karasa zare kayan jikina ya rufe mu da bargo ruf.

Duk yanda nai tunanin Mubeen ya wuce hakan, tsoro sosai ya riskeni da yanda gaba daya ya birkicemin ya koma wani bahagon zaki.

Duk yanda kuke tunani na mance da zancen wai nama fishi watannin da nake cika baki na girme masa, saiga Batoul na kuka da rokon Mubeen yayi hakuri, shiko sam bama yajina balle nai tunanin samun sassauci.

Inaji ina gani Mubeen ya mallaki abinda yakeji a ransa da tinkahon mallakinsane, na jigatu, sannan na magantu, kuka kam har hawayena na neman karewa, daga karshe ya rungumeni a jikinsa shima yana hawayen da bansan na menene ba.

Mundauki tsahon lokaci a haka yana zubamin sambatu da kalamai masu matsukar tsada daban mamaki, yaukam na sake tabbatarwa Mubeen na tsananin kaunata da sona, sai nima na samu zuciyata dajin wani yanayi akansa.

Bayan munci kukanmu mun koshi ya taimakamin zuwa toilet, yau ko musu gaza yimasa nayi, da taimakonsa na gyara jikina, ya kuma taimakamin muka fito, wasu kayan barcin ya sakamin masu dan kauri saboda sanyin da nakeji, ya kaini na kwanta, zaune yayi a gefena yana shafa bayana alamar lallashi har barci yayi gaba dani, daga lokacin ban sake sanin meke faruwaba sai da asuba daya tasheni salla.

Duk yanda yaso mu hada ido naki, sai fitar sautin murmushinsa kawai nake jiyowa nidai, hakan yasakani jin wani haushinsa, nai kamar zan harare shi sai kuma na fasa.

Dariya Mubeen yayi yana kallonta, yace,

“Meyasa kika fasa to?Harare ni mana”.

Ban kulashiba na tada sallata kawai.

•••

Could this actually turned into something real? Shin ya zata kaya ne da zukatan masoya biyu wanda suke da banbance-banbance a tsakanin su? The class of the have and the have not??? Suraidah 'yar gidan wani babban oil tycoon ce. Muhammad Mahboub kuma d'an gidan talakawan talak ne. Shin ya zata kaya ne da qulluwar zuciyoyin wanda ba tsaran rayuwa bane ballanatana aure😮? Tab Shin ya kuke ganin wannan ruguntsumin zai kaya? Dr Falal Rabiu mai Mai wani sanannen billionaire ne wanda keda rijiyoyin mai a fad'in Najeriya, yana taimakon talakawa amma shi kam baya son talaka ya rab’e shi. Taya za’ai Muhammad Mahboub ya zamto siriki agare shi? Kai abin da kamar wuya. Mahboub *ANNURIN ZUCIYAR* Suraidah ne. Da sonshi ta rayu ya rene ta ya girmama a zuciar ta. Shin ko Suraidah zata iya bijerewa mahaifin nata? Tab! dankari Makari. Akwai cakwakiya fa, kun ta6a ganin talaka mai tsattsauran ra'ayi? Ku biyoni muje dan kuji me za'a kulla a tafiyar. Wannan labarin yasha banban da sauran rabarai na, zai ta6a zuciyoyin masu karatu, sannan zai fad'akar daku masu karatu, insha Allahu zai sanyaku nishad'i. Akwai zazzafar soyayya da kuma zazzafar kiyayya, akwai jarumtaka, sadaukarwa ta fannoni da dama, *ANNURIN ZUCIYA* daban yake a cikin sauran labarai. Domin mallakar ANNURIN ZUCIYA na marubuciyar MUSAYAR ZUCIYA (HAJJAH CE) ku tuntubi lamba kamar haka akan nera dari biyu kacal: +234 706 528 3730

Masu neman books dina su duba wattpad na dora wa'ensu:: missxoxo00

[9/16, 11:29 AM] □: _Could this actually turned into something real? Shin ya zata kaya ne da zukatan masoya biyu wanda suke da banbance-banbance a tsakanin su? The class of the have and the have not??? Suraidah 'yar gidan wani babban oil tycoon ce. Muhammad Mahboub kuma d'an gidan talakawan talak ne. Shin ya zata kaya ne da qulluwar zuciyoyin wanda ba tsaran rayuwa bane ballanatana aure😮? Tab Shin ya kuke ganin wannan ruguntsumin zai kaya? Dr Falal Rabiu mai Mai wani sanannen billionaire ne wanda keda rijiyoyin mai a fad'in Najeriya, yana taimakon talakawa amma shi kam baya son talaka ya rab’e shi. Taya za’ai Muhammad Mahboub ya zamto siriki agare shi? Kai abin da kamar wuya. Mahboub *ANNURIN ZUCIYAR* Suraidah ne. Da sonshi ta rayu ya rene ta ya girmama a zuciar ta. Shin ko Suraidah zata iya bijerewa mahaifin nata? Tab! dankari Makari. Akwai cakwakiya fa, kun ta6a ganin talaka mai tsattsauran ra'ayi? Ku biyoni muje dan kuji me za'a kulla a tafiyar. Wannan labarin yasha banban da sauran rabarai na, zai ta6a zuciyoyin

masu karatu, sannan zai fad'akar daku masu karatu, insha Allahu zai sanyaku nishad'i. Akwai zazzafar soyayya da kuma zazzafar kiyayya, akwai jarumtaka, sadaukarwa ta fannoni da dama, *ANNURIN ZUCIYA* daban yake a cikin sauran labarai. Domin mallakar ANNURIN ZUCIYA na marubuciyar MUSAYAR ZUCIYA (HAJJAH CE) ku tuntubi lamba kamar haka akan nera dari biyu kacal:
+234 706 528 3730_

*ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

_07067124863_

*_Ko kuma*_

_09032345899_

BAMUB

_52_

Inayi jiki na na amsa min, Gaba d’aya ciwo yake kota ina, Ina kallon yadda shima ya kudundune a bargo yana rawar sanyi. Can ya d’au waya ya daddana da alamun sak’o ya tura. Ni dai ina zube akan sallaya ina sakin numfarfashin ciwo Jannat tai knocking, Mik’ewa yai ya karbo wasu kwalayen magani ya ajiye a bedside drawer,

“Taso musha magani Fateemah!”

Ba musu na mike dakyar domin Ina buk’atar maganin ina cije lebe na karasa na zauna akan gadon can nesa dashi ina rike hijabin jiki na, Matsowa yai kusa da ni na shiga ja da baya, Da karfin tsiya ya janyo ni ya sanya ni a kirjin sa. Cikin kunne na ya shiga radamin,

“Hak’ik’a nayi dace da samun kyakkyawar mace abar kwatance. Zan kasance tare dake a duk inda kike, cikin mafarkinki, cikin tunaninki, cikin farinciki da bak’in ciki. Zan kasance mai share maki hawayen ki, ya ma za’ai in bar idanuwanki su zubar da hawaye ? sam sam!.

“Zan kasance mai tarairayar ki tamkar kwai a tafin hannu. Fata na ki kasance cikin farin ciki da annashuwa, fata na ki zamto tauraruwar dake haske duniyar masoya. Ke ce tawa har abada Fateemah, Kin zarce sauran mata Ina neman wata kalma wadda babu wanda ya santa. Ina neman wata kalma da zan furta miki cewa…..ke ta daban ce, ke kyakkyawa ce, kin zarce sauran mata. Zuciya ta da taki ba za su ta6a rabuwa ba har abada. Ina son ki….”

Gaba d’aya jikin sa rawa yake, Ni kuma zazza’bi ne yake neman kwantar dani, Amman saboda tsabar mugunta bawan Allahn nan sai ya shiga ko’karin zare hijabin jiki na,

“Ya haka.. Dan Allah kayi hak’uri.”

Na fada hawaye d’aya nabin d’aya. Mubeen ya girgiza kai kawai ya cire hijabin ya cillar,

“Ba nace miki idan mu kadai bane basai kin saba?”

Ya rad’a min a kunne na, Hannun sa d’aya kuma yana karakaina a jiki na. Ina ji ina gani ya ragemin sauran kayan jiki na daga ni sai zani ya lullube mu da bargo, Daga nan salo ya canza. Bidirin sa yake sosai yana hawaye ina hawaye. Ni hawayen ciwo nake wallahi na bakar zalunta irin tasa, Shi kuma bansan hawayen me yake ba. Tun ina bashi hak’uri har na dena baki na ya mutu numfashi kawai nake fitarwa. Gaba

d’aya sarrafa ni yake tamkar wata kayan wanki. Naci azaba iya abaza. Da kansa ya tsaftace mana jikin mu, Sannan ya barni a bandakin na kara yo wani wankan.

“Allah ya isa wallahi..”

Na fada a hankali ina goge hawaye. Murmushi naga yayi yana yafito ni da hannu,

“Zo kiji..”

“Wayyo Allah na! Dan Allah kayi hak’uri.”

“Matsoraciya! Ni ba abinda zan miki.”

Rungume ni yayi bayan munsha magani. Duk minti sai ya sumbaci goshi na, Baki na, da gefen kumatu na. Ni kam na shiga uku! Hawaye ne naga sun shiga yar tsere a fuskar sa. Kankame ni yayi ahankali cikin wata irin murya ya fara cewa,

“SO shi ne abun da ya dun’kule zuciyoyinmu waje guda har muka tsinci kanmu a cikin soyayya, Duk kuwa da dai ni kadai ne ke wahala akan kaunar ki. ina fatan ba za ki bari wani d’an ‘karamin abu ya zo ya raba tsakaninmu ba? Ina son ki. Ke tamkar gishiri ce a cikin rayuwa ta, idan na rasa ki zan yi rayuwa ne da babu armashi a cikinta,

“Fikre! Da akwai wasu lokuta da nake zubar da hawaye saboda ke, na san za ki ce saboda me?…..Da akwai wani lokaci da yake zuwa na ji tamkar na yi fikafikai na tashi sama…..Kin kuwa san duk saboda mene ne? Saboda motsawar sonki a cikin zuciya ta da tsintar kaina a cikin matsanancin shau’ki a dukkan lokacin da na ji muryarki ko na tina da ke…..Ina fatan za ki amince mu rayu a tare har abada. Ina son ki fikre,

“Bazan iya rayuwa babu ke ba, A mafarki da kuma a cikin soyayya babu abun da ba zai iya faruwa ba. Ina son ki sosai hakan ya sa nake ji tamkar ba zan iya rayuwa idan ba tare da ke ba. Ba na fatan rasa ki a rayuwa ta, domin kuwa a dukkan lokacin da na rasa ki, na tabbatar da rayuwa ta za ta shiga garari. Ina Son Ki kuma ba zan taba denawa ba.

“Hakika kin shayar dani zumar da ban taba sha ba, Kin kai ni garin dadin da ban taba mafarkin zuwa ba. Na kuma same ki cikakkiyar yar mutinci, Lallai agaida Innar mu da dawainiya. Kalmomi sunyi Kadan wajen kwararo godia ta agare ki.... Kina jina kuwa?”

Sake kasa nai da idanu na ina cije lebe, Hannun sa yasa ya dago hab’a ta yana kallon cikin idanu na, Ai kuwa da sauri na rufe su ruf, Sumbatar idanun yai daga nan ya koma kan baki na, Dakyar na kauda fuska ta,

“Ya kamata ace kin fara daukar darasi awajen dan karamin Malamin nan naki, Jia munyi darasin...”

Saurin rufe masa baki nai da tafin hannu na,

“Ya isa haka dan Allah! Kaji?”

Mirgino ni yayi, Ina ‘kasan sa yana sama. Ya sake narke min idanun sa masu rikitar wa,

“Mah!!!! Our marriage is our sacred bond–one that symbolizes love, hope, and the strength to overcome any obstacles. My unending love for you is my vision, my hope, my goal, and my soul. You’re my Goddess, my hope, my joy, and my life. Please be with me forever, my love. I love you more than life itself Fateemah na!”

Bawan Allah ya bani tausayi matuka ganin yadda yake ta zayyana min can cikin zuciyarsa. Na kuma gyara kaina a jikin sa sai dai fadin rai ya hana na nuna masa komai sai lumshe ido dana sake yi. Hannunsa yana saman kai na sai faman zuzzura

yatsunsa yake yi a cikin, ba karamin dadi nake ji ba hakan ne kuma yasa na koma bacci ba tare da na sani ba.

Saukar numfashi na da yaji ne ya tabbatar masa da cewar nayi bacci, ya tashi ya koma saitin fuskata yana kare min kallo tamkar wanda yaga wata sabuwar halitta. Yatsunsa guda biyu yasa yana jan hancina tare da shafar gashin girata, duk da yana cikin halin zazzabi hakan bai hanashi janyoni zuwa kirjinsa ba, ya makale min tamkar wanda ya samu sakon cewa idan ya barni za'a sace ni. Lebansa yasa a saman nawa ya sumbata tare da lumshe idanu shima bacci ya dauke shi.

Mutanen gidan kuwa tunda suka ji mu shiru babu wanda yaje yaga halin da muke ci, daman Jannat ta sanarwa da Mammah cewar Yaya Mubeen yasa ta kaimasa magani bata sani ba ko jinsa ne kona matarsa. Jin haka ne kuma yasa Mammah Ahlaam hana kowa zuwa dakin dan dama taga take-taken Mubeen akan Batoul d'in tun kwanaki biyu yana ta karakaina a kanta.

Bamu muka farka ba sai wajan karfe goma na safe shima nice fitsari ya dameni shine na tashi da ban san lokacin da zamu tashi ba. Kasa hada ido nayi dashi ya kamo yatsuna yana matsawa tare da sanya tafukan hannunsa a wuya na, jin babu zafi yasa ya min magana a hankali kamar baya so.

"Fikre kin warke? Yanzu ina ne yake miki ciwo?"

Ban kalleshi ba na dai kawai girgiza kai na sannan na yi kokarin kwatar hannuna zan tashi, ya yi azamar rigani yana yaye min bargon da muka lulluba.

"Ina kuma zaki je?" Murya a dashe nace.

"Sauka zanyi.." Ya janyo ni na kwace saboda ya matse ni idan ya rike ni ji nake kamar zai zubo.

"Zaki je toilet ne?" Kai na kawai na mirgina ba tare da na ce komai ba.

"Okay tashi na kai ki." Na kasa yi masa musu haka na mika mishi hannu ya tasar dani saboda har lokacin jikina a tsamama yake.

Muna zuwa bakin band’aki na cije alamun ya barni daga nan, sai naji ya yi murmushi tare da sake damke min hannu tare da murda kofar ya bude. Ciki ya jani muka shiga tare, ya nuna min inda ake fitsari da kuma inda ake tutu na kalleshi cikin son jin karin bayani dan ban bahimce shi ba, ya daga min girarsa tare da makalo ni ta baya yace.

"Wanne zaki amfani dashi?" Na yi saurin kwace jikina na juya muka hada ido, harara na watsa mishi ina turo baki tare da hade rai nace.

"Ina ruwan ka da ni, ka tafi mana." Wajan sink ya nufa tare da daukar brush ya waigo ya kalli ne, nima a lokacin shi nake kallo.

"Guri daya zaki bari nima zanyi amfani dashi dan duk abinda kike ji nima shi nake ji. Yo banda abinki my Fikre jiya meye ban jinba bare gani? Kefa matata ce duk abinda muka yi tare lada za'a baki, idan na kalli wani abu a tattare dake naji dadi za'a rubuta miki lada ko so kike na kalli na wasu a rubuta miki alhaki saboda kin hanani yin wasu abubuwan da Allah ya halatta min.?"

Jikina ya yi sanyi, ni kaina na rasa me yasa nake masa hakan, amman dai nasan ina jin kunya gaskiya sannan ba wani sabawa nayi da yin hakan bare yace dama na kware. Babu yadda zanyi gashi kiris ya rage nayi a tsaye sai kawai na nufi gurin da aka tanada dan yin fitsari na tsugunna bayan duk na jajjanyo zanin jikina na bazashi daga baya. Shi kansa yasan cewar ya takura min hakan yasa shin murmushi yaje ya ajiye brush d'in ya fita, ina jin ya fice na sauke ajiyar zuciya fitsarin da ya makale shima ya karasa yowa waje.

Sai da na gama abinda zanyi sannan na fito, baya cikin dakin hakan ya bani damar cire zanina da ruwa ya jika shi na canza kaya zuwa wani hadaddan material orange color riga ne da skirt wadanda suka yi min das a jikina. Ina cikin daurin dankwali ya shigo hannunsa dauke da tray nayi saurin barin daurin na nufi wajan shi da nufin karba sai ya tsaya yana kallo na tamkar yaga sabuwar halitta.

“Wow wow wow my Fikre, iyeeee kullum sararin samaniya cike take da kyawawan taurari masu haske ta cikin hasken farin wata, amma kuma haske mafi kyawu da gani yana cikin idanuwanki my Fikre zo na sake ganinki.”

Ya karasa maganar yana karasawa wajan gado ya dire tray din. Kafin ya juyo tuni na karasa wajan madubi ina gyara daurin da nake yi, ya zo bayana tare da sanya hannayensa ya riko min kuguna yana kallo na sosai.

“Kinyi kyau my beloved wife.”

Nayi murmushi ina lumshe ido dan yanzu naji wani shauki akan yadda yake min magana, na samu kai na da cewa.

“Na gode.”

Ya jani jikinsa sosai, naga alama yana matukar jin dad'i idan ya rungume ni.

“Zo muje kiyi feeding d'in mu ina jin yunwa sosai, duk kuma kece silar ta.”

Tsabar mamaki ban san lokacin da ce.

“Ni kuma?”

“Kwarai da gaske kin san wannan abun idan aka yi shi yunwa yake karawa.”

Shiru nayi dana gano abin da yake nufi, wallahi bansan gayen nan haka yake ba, yaro a fuska sai kace idan kasa masa yatsa a baki ba zai ciza ba, ashe shima lamba

d'aya ne. Yana rike dani har muka karasa ya zaunar dani wajan bedside carpet ya koma ya dakko tray din ya ajiye a gabana yana so mu hada ido naki.

“Bari naje na dawo.”

Yayi maganar yana riko hab'ata nayi saurin rintsa idanuwansa. Ina jin shi yana murmushi har ya fita, ni kuma na bude kwanukan ina ganin ko menene a ciki. Mayarwa nayi na rufe sai gashi ya kuma shigowa hannunsa rike da kwando mai dauke da tea flask da kayan shayi yazo ya dire tare da zama a kusa dani.

Kansa ya kwantar a kafada ta yana bude baki, na fahimce shi so yake na hada komai na bashi a baki, wannan gayen tabararsa tayi yawa na ayyana hakan a cikin zuciyarta tare da mika hannu na ciro flask d'in. Hadawa nayi shi kuma yana faman shafar bayana, har sai da na kammala hada mana sannan na ce dashi.

“Bismillah.”

“Hahh.”

Ya bude min bakin sa alamun na bashi, samun kaina nayi da sunkuyawa na leka fuskar shi tamkar ya san zanyi kafin nayi magana naji ya sakar min wani zazzafan kiss a saman lips dina. Nayi saurin kawar da kai ina dan murmushi zuwa lokacin Mubeen ya dena bani mamaki dan naga shi din mutum ne mai san soyayya yana kaunar pure love wato irin wanda yake min har cikin zuciyarsa.

Sannu a hankali na dinga gutsuro funkason da hannuna bawai cokali nasa ba, ina hadowa da yan cikin da aka yi miyar dasu ina bashi a baki yana ci, sai da naga yaci da yawa har ya fara kawar da kai tamkar ana bawa yaron goye sannan ne nima na fara cin nawa. Kansa ya dora akan cinya ta ya kura min ido yana kallon yanayin yadda nake ci yana murmushi.

“Fikre komai naki daban yake, ban san menene yasa nake ganin kin banbanta da duk sauran mata ba. Na godewa Allah alhamdulillahi da ya bani ke a matsayin matata wacce nake saka ran wata rana zata haifa min quadruplets”

Ban san lokacin da na kalleshi na zabga masa wata uwar harara ba, cikin subutar baki nace dashi.

“Waye yace maka zan haihu bare har nayi biyu-biyu sau hudu sai kace kaza?”

Hannunsa yasa a saman cikina yana shafawa, ya dago narkakkun idanunsa tare da daga min gira.

“Yarinya mun yi magana da Mammah tace honeymoon zamu tafi, wace kasar kike so muje my love.?”

“Wace yarinyar.?”Na tambaya cikin mamaki.

“Oh sorry Mrs Mubeen.”

Yatsina fuska nayi ina dauka kofin shayi na shiga girgiza masa kai.

“Ni babu wani honeymoon da zanje saboda Fadeelan Yaya Najeeb ta kusa haihuwa”

“Karki saka ran za'a yi a gabanki, kema shiryawa zaki muje yawan bude idanu idan mun dawo sai muje barka, haka ake cewa ko? Barka.”

Na zabga masa harara ya kai hannu zai ja min hanci naki yadda.

“Fishi kike yi? Yarinya na cewa Papa Paris zamu je garin masoya garin da suke tsaga soyayya su baje ta a fili, ina son ki tanadar min kalolin love, romantic

abubuwa dan idan mukaje baki min ba ba zamu dawo ba kuma babu ke babu lecturing."

A zabure na janye kafafuwa na ban sani ba wallahi na manta jin ya ambaci komawa gurin aiki yasa murna ta rude ni, kanshi ne ya bada wani irin k'um.... ! Duk da naji bugun amman ban kula ba, baki na yana rawa fuskata cike da fara'a nace dashi.

“Da gaske kake zan koma gurin aiki na?!”

Yatsan sa da naga yasa a baki yana cizawa gashi sai wani irin kallo yake min ashe wai harara ce shine yasa na ankara da abinda nayi masa, yace dani.

“Ban miki alkawari ba, kina ganin ma yadda kika fasa min kai. Zoki duba min ki gani ko yayi jini.”

Harara na zabga masa ba tare da ya kalleni ba, kan nasa ya zuro min har sai da ya mai da shi yadda yake sannan ya juyo min da keyarsa ya takura min sai na duba mishi gurin.

Hannu nasa tare da fara bubude kanannad'add'an gashin kan nasa, babu komai ko alamar kumburi amman dana tabo fatar kanshi zai fara cewa.

“Ashh... ! Ahhhh.. Ohhh..! Zafi my Fikre.”

“Wai kai dan Allah baka jin kunya ne, kayi ta abu irin na babies?”

Na fada ina murgud'a baki ba tare da yasan nayi ba. Tashi ya yi daga kan kafar tawa ya janyo ni gabaki daya zuwa jikin sa, wuyan sa ya zuro a nawa yana fadin.

“Baki sani ba? Ke tunda kika zo gidan nan kinga su Mammah sun min abun da zai nuna miki cewar ni gardi ne?”

“Sau nawa ina gani.” Nayi magana ina kawar da kai.

“Okay haka ma zaki ce ko, muje zuwa ke da kanki zaki kuma maida ni baby boy yarinya. Taso muje mu kwanta.”

“Ni bana jin baccin kaje kayi kawai.”

“Haba my Fikre da ne ai nake kwana ni kadai, amman banda yanzu, zo muje kan gadon kisani nayi bacci idan ke bakya ji.”

“Ohh Mubeen.”

“Ahhhh Fikre please mana.”

Yayi hakan yana sake narkewa a jiki na, ya zanyi haka aure yake dole nabi umarninsa muka hau gado, gashin kansa na dinga yamutsawa a hankali wai dan ya yi baccin amman gayen nan yaki yi, sai ma ni da ya juyo yana jijjagawa tamkar wata baby girl, ai kuwa tuni nayi bacci shi kuwa bansan lokacin da ya yi nasa ba, kawai dai na bude ido nagan shi sakale dani baccinsa abin sha'awa har wani murmushi yake kona Meye oho.

***Ganin yana bacci yasa na zare jiki na na shirya cikin wata atamfa ruwan hoda da zani tasha aikin stones, Na yafa mayafi na na nufi sashen su mamma Ahlaam. Ina tafiya ina gyara tafiya ta azato na zasu gano wani abun. Ina shiga kuwa suka fara nannan dani tamkar zasu hadiye ni dan so. Ni dai kai na a kasa na zauna ina wasa da wayar hannu na. Ashe Mubeen canxa min waya tayi. Tayi kyau sosai da tsada kuma.

“Kawo mata abinci Jannat..”

A koshe nake amman ba zan iya musa mata ba. Gaba na aka cika da cima kala kala. Sai ga Mubeen ya shigo a hargitse, Idanun sa akai na.

“Ashe nan kika taho..? Mamma barka da safiya ..”

Yana kallo na yana gayda mahaifiyar sa. Wallahi bashida ta ido. Kada kai nayi kawai na cigaba da shan juice dina. Gaba na ya zauna yana cin chips din da nake ci,

“Shine baki tashe ni ba..”

Ya nai min wani kallo na cikin idanu, Kasa amsa masa nai, Matsowa ya kara yi yana janye warmers din gaba na. Ai kuwa na mike da sauri na nufi wajen wanke hannu. Mamma Ahlaam ta tashi tana waya Jannat na biye da ita. Nasan kuma bamu waje su kai,

“Meye haka Mubeen?”

“Tashi fa kikai ki kai tahowar ki, Kinsan neman da na miki kuwa? Ko wanka banyi ba. Amma ke kinyi.”

“Toh kayi hak’uri..”

Na fada ina rintse idanu na saboda yadda kai na yafara ciwo lokaci d’aya. Cikin rawar jiki da baki ya shiga tambaya ta,

“Menene? Ina ne yake miki ciwo? Ko wajen ne? Zo muje na duba..”

Wata uwar harara na dankara masa ina janye hannun sa dake kan goshina,

“Ka duba ina? Matsa dan Allah”

“Wajen mana…. Wuri ne mai matukar martaba da mutinci. Ko muje asibiti uhm?”

“Wai bakajin kunyar su Mamma ne?”

“Kunyar me? Matata ce kefa ta sunnah! Halaliyata kuma. Tukunna ma mena ce miki akan mayafi da jambaki?”

Ya fada yana tsare ni da kallo, Ban bashi amsa ba na cigaba da yatsina fuska. Mik’ewa yai ya janyo hannu na. Ina tirjewa ina komai haka ya daga ni,

“Mamma mun tafi..”

Ya dan d’aga murya da karfi yana gayawa mahaifiyar sa,

“Tsaya na mata sallama..”

“Babu inda zaki muje ki karba hukuncin ki.”

Yana gaba yana janye da hannu na haka muka koma sashen mu ina kukan zuci. Naki shiga ina tirjewa a bakin kofa. Jina nai a sama ya dago ni ya ajiye ni akan gado yamin rumfa,

“Mena ce miki akan sa hijabi da jambaki?”

Ckkin rawar murya na shiga in’ina,

“Kayi hak’uri na rigada na saba ko agidah ne, dole sena sa jambaki. Hijab kuma ban cika amfani dashi ba, Kuma naga duk gidah ne ko?”

Birkito ni yai muna kallon juna,

“Ya zanyi da son ki uhm? Abinda kake so shi kake wa kishi. Zawjati ina sonki so mai tsanani. Amma ya zama dole ki karb’a hukunci.”

Ni dai rufe idanu na nai ina jin saukar numfashin sa akan fuska ta mai dauke da flavor din mint. Lebe na ya kamo cikin wata siga ya shiga lashe jambakin kai daga nan wasa ya canza. Sai ga hannun mutumi acikin rigata. Yanason tab’o inda nake ganin girman sa ajiki na. Ya gama kashe ni da wani irin salo na tafiyar tsutsa. Ji nai kawai kofofin jiki na na maraba da amsar sak’on sa. Fashewa nai da kuka alokacin da naji sabon abinda yake min tamkar karamin yaro da ake shayar dashi. Ina kasa ta tsage haka naji. Hawayen takaici kawai nake, Ina jinsa ya zare sauran kayana ya shiga babban aiki ko gajia bayayi. Wallahi nagaji matuka. Kuka sosai nake ya hanani ta hanyar rufe bakin mu.

“Ina kaunar ki Fateemah na! Dan Allah ki so ni ko kadan ne, Ki karb’e ni a matsayin mijin ki, Ki dena kallo na amatsayin karamin yaro da kike koyarwa, Kinji dai yadda tawa qaddarar tayi da ni da tuni na zamto wani abu a rayuwa nima.. Ki saki jikin ki dani na miki alk’awarin shayar dake zuma mai dadin gaske... Ina kaunar ki Zawjati Fateemah”

Haka yai ta sumbatun sa yana aikin gaban sa. Ni kuwa banda zirarar da hawaye babu abunda nake, Ina jiyo sautin radar da yake min a kunne,

“Ni fa malamin ki ne, Ki saki jikin ki sosai domin naga alamun kofofin jikin ki na kar’bar sak’o na. Amman saboda kafiya irin taki kin ki bani hadin kai! Ni fa mubakaci ne. Kiyi hak’uri dani kinji? Ki tallafamin muyi ta raya sunnar ma’aiki..”

“Ciwo.. Dan Allah ka bari..”

Be amsa ni ba ya cigaba da harkar gaban sa, Ranar nasha azaba da radadi ga ciwon kai. Wallahi dakyar nake daga yatsa na, Bandaki ya kai ni ya tara ruwan zafi, ‘sit bath’! Inayi yana hucewa yana canza wani. A ranar dai bayan mun sha fada sai da yamin wanka tatas ya cude ni da soso da sabulu,

“Dama kinada tawadar Allah akan nan?”

Ya fada yana mai nuni da kirji na na hagu. Na dankara masa harara ina cije lebe,

“Ka fita zanyi wankan tsarki...”

Sumba ya sakarmin a goshi na yana murmushi,

“Wane dare ne jemage bai gani ba? Uhm? Komai fa nagani Fateemah na..”

Ya sakarmin gwalo ya fice da sauri, Wankan tsarki na shiga yi ina zubar da hawaye, Sekace inji ko gajiya bayayi akan abu d’aya. Gaba d’aya naji na takure bazan iya ba wallahi.

Muhammad Mubeen kuwa na komawa daki ya tsaya a gaba drawer Batoul yana karewa kayanta kallo. Wasu shegun kaya ya ciro gaba d’aya bana mutunci. Yai murmushi yana hango yadda zasu kwashe da Batoul. Ajiye su yayi akan gado ya koma wajen pantries da bras yana kallan su idanun sa awaje. Ina fitowa na hango shi ya ciro brazier ya kura mata idanu,

“Ya haka...?”

Juyowa yai yana murmushi yana kallon beriziyar yana nuna ta,

“Gani nai ta miki kadan fa, kalla fa.”

Na kauda fuska ina jinjina kokari irin nasa,

“To ajiyemin kaya na..”

Mayawa yai ya kamo ni a hankali muka zauna akan gado,

“Ga kaya nan kisa..”

Nabi shegiyar rigar da take a ajiye gaban ta shara shara kamar abun tatar koko da kallo. Ita yake nufi nasa? Tab lalle ma.

“Banason wannan zan sauya wata.”

“Toh ni inaso.. Ki saamin naga yadda zata miki. Itama fa kamar zata kamaki da alamu.”

Gaba d’aya dai halittar jiki na yake nazarta kome? Na danne bacin raina Ina zura rigar hade da dora zani akai. Gefen drawer na janyo na dakko hair dryer na jona a socket,

“Kawo na taya ki..”

“A’a..”

“Wallahi sai na yi, Ai dole na busar miki dashi ni ne sila.”

Da k’arfi ya janyo ni ya dora akan cinyar sa, Kaman kujera. Haka ya shiga busar min da kai yana huramin iskar kunnen sa a kunne na,

“Sannu.. A hankali nake miki..”

Tsigar jiki na sai tashi take tana kokarin amsar sakon sa,

“Inason ki Fateemah na..! Bansan irin son da nake miki ba. Gashin ki, leben ki, kunnen ki.. idanun ki, Da nan da nan! Kai komai naki ma.”

Ya fada yana mai nuni da kirji na. Banza nai masa, Tsaf ya gama busarwa,

“Bara na miki oiling..”

Sai na samu kai na da tambayar sa,

“A’ina duk ka iya haka?”

“Sanda Jannat na karama ina taya mamma yi mata aiyuka. Kinsan akwai shekaru a tsakanin mu da ita. Har kalba na iya fa..”

“Uhm..!”

“Meyasa kike min kallon karamin yaro ne wai? Bayan na gaya miki komai nawa? Daga karshe fa nina maida ke cikakkiyar mace...”

Toshe kunnuwa na nai sai daya gama surutun sa sannan na bude, Ya gama shafe min kai na da mai ya daure da ribbon. Can karshen gado na koma na kwanta ina janyo littafin adduoi na,

“Ka koma dakin ka.... Zan kulle nan.”

“Babu inda zani! Bazan iya kwana ni d’aya ba Mah! Kin sangarta ni.”

Shigewa bandaki yai yana daria, Ni mamakin sa nake yi wallahi, sunaye kala kala abakin sa ko gajia baya yi yace Mah, Fikre, Ayana, Fateemah, Zawjati.. Duk ni kadai? Na yamutsa fuska bayan na gama karanto addu’oin kwanciya na kakkabe wajen da basmah na kwanta ina lumshe idanuna, bacci sosai nake ji wallahi. Ina jiyo sanda yafito yana shafe shafen mayika da turaruka. A hankali ya salallabo yana rungumo ni ta baya, Na shiga zame hannun sa ina jan bargo,

“Dan Allah ka ky’ale ni wallahi jiki na ciwo yake.”

“Ki tausaya min kinji? Ki rungume ni to.. “

“Kamar wani baby? Dan Allah matsa.”

“Ai babyn ki ne wallahi, babyn baby ba. Ina kaunar ki Fikre!”

Banbi takansa ba na sake jan bargo ina rufe jiki na, Janye bargon yai ya shige min jiki, Kyakkyawar runguma ya bani yana sakin ajiyar zuciya,

“Ina kaunar ki... sonki yayi mini da baibiya yabi jini, tsoka, zuwa bargon kashi na. Domin zuciyata ita ce ma’adanin surrikan tinaninki..”

“A’ina ka iya hausa haka ne uhm?”

“Yare na ne fa! Embassy din da muke kamar nigeria haka yake. And agidah ma hausa muke. Mamma ma bata cika yi mana Amharic ba. And sanda ina karami muna zuwa Nigeria sosai da papa. Sanda nake 18 ma munzo mun dade sosai. Kuma ina koya online.”

Kada kai kawai nayi domin bacci fusgata yake. Na kyale Mubeen yana ta bidirin sa akaina domin bacci nake ji. Ina jin hannun sa na karakaina na cije lebe kawai daddadn bacci yai awun gaba dani kafin shima daga baya yayi baccin. Munyi bacci sosai domin yan kwanakin nan baya bari muyi bacci saboda fitinar sa, Shiysa da asubah har makarar sallah muka yi.

Da safe

Da wuri na zare jiki na daya kanannade tamkar zan gudu, na shiga bandaki nayo wanka. Wani dandatsetsen lace pusher pink na dauka nasa mai ratsin blue. Na saka dan kunne da sarka na da Gwaggo Aminatu ta siyamin da yan kudaden dana tara. Light makeup nai na cokala daurin ture kaga tsiya. Alokacin Mubeen ya mike yana mik’a da salati,

“Kinyi kyau Fateemah na...”

“Ina kwana?”

Na gaishe shi ina goga turare a gefen kunne na. Kayana sai tashin kamshin turaren kaya suke. Na bulbula khumra ina goga jambaki a lebe na.

“Kinyi kyau..”

“Nagode! Za Kai wanka ne na hada ruwan?”

Wata shegiyar mikar ya kuma yi yana girgiza kai,

“Tab! Ai kuwa da rabon zaki sake wani wankan.. Zan yi abuna kawai.”

Ya fada yana kashemin ido d’aya, shigewa bandakin yayi yayo wankan, Ya shirya cikin wasu manyan kaya, Shadda blue kalar kwalliyar lesi na, Ya faffesa turaruka yana taje kansa a mudubi,

“Me zaka ci...?”

“Dik abunda zaki ci. “

“Ni fa nakoshi..”

“Nima na koshi”

“Ka...kaga..”

Dawowa yai kusa dani yana kallon idanu na hade da kamo hannu na ya sanya cikin nasa,

“Menene uhm... Fateemah na! Kiyi magana! Ni nai lefin uhm?”

Salon sa na kashe ni, Na girgiza kai ina kallon gefe,

“Abincin su ne nagaji dashi Mubeen! Wainar fulawa nake sha’awa.”

“Anything for you Fateemah na! Muje su dafa..”

“Soyawa ake.. Amman ni zanyi da kai na.”

Gyada kai yayi, Ya kamo hannu na muka shiga kitchen din. Ma’aikatan sai xubewa suke suna gaishe mu,

“Zamuyi waina ne..”

Yace dasu yana karewa kitchen din kallo, Wata daga cikin ma’aikatan ta kara kasa da kai cikin ladabi take tambayar sa,

“Yallabai wainar gero ko ta masara ko ta shinkafa?”

“Ta flour!”

“Akwai fulawa yallabai komai akwai..”

“Toh ku bamu waje..”

Ficewa su kai d’aya bayan d’aya. Suna fita ya murza key a kofar yana nannade hannun rigar sa,

“Madam da me zamu fara.”

“Babu komai.”

“Kinma isa? Tare zamuyi komai.”

“Toh yanka albasan can. Bara nayi sauran aikin.”

Rigar girki muka sassanya, Na shiga harhada komai ina murmushin yadda yake mici mici da idanu suna hawayen yajin albasa, Gashi ko d’aya bai gama yankawa ba. Na matsa kusa dashi ina mika masa hannu na,

“Basshi! Kawo na karasa..”

“Uhm’ uhm banyadda ba gaskia gaskia ni ban yadda ba.”

Girgiza kai nayi na dauke albasar kawai, Ina cikin yankawa naji ya rungume ni, Ya sakalo hannun sa ta ciki na kansa akan kafada ta,

“Sannu da aiki Zawjati...”

Duk inda nayi yana nanike dani yana aikin magana, Haka na gama soyawa fal kula. Na mika masa,

“A kaiwa su Mamma wannan ga tamu can.”

Gyada Kai yayi ya sumbace ni a gefen kumatu. Daki na koma da tray din wainar tamu. Banko jira shi ba na shiga nannadata a yaji ina dannawa a baki na. Ni kam nagaji da irin cimar su, Ga nama kamar ka zubar, su Innar mu kawai nake tunawa. Ina cikin ci ya dawo,

“Laaa cinyewa zaki? Baki jira ni ba fa.”

“Ai baka iya ci ba...”

A gabana ya zauna yana daukar Wainar , Ya jima yana binta da kallo kafin ya doni yaji yasa a bakin sa,

“Kai! Dadi wallahi.!”

Kafin kace me? Bawan Allah ya tashi da wainar nan yana sude hannu,

“Tayi dadi..”

Gyada masa kai nayi kawai na dauke tray din na kai kitchen,

“Yauwa mamma tace nace miki Aunty rahila zata zo da yaranta da yaran uncle bilal.”

“Tohm..”

Nace dashi kawai, Bandaki ya fada yin wanka, Wasu kayan na ciro na dora akan kabbasa na shiga turara su. Yana fitowa na shige nima nayi wankan. Gani nai ya sake sa wasu kayan kalar wanda nake turarawa. Akan kabbasar ya dora shima yana gyara bathrobe din jikin sa. Mai na shafa na shiga tsantsara kwalliya, Na shafe baki na da jambaki ina bin lungu da sako na jiki na da turare, Mubeen yai murmushi yana taune leben sa,

“Ina zaki da jambaki uhm? Gwara ma ki goge shi kafin ki k’arba hukunci..”

“Fisabilillahi Mubeen ni fa macece, Ya za’ai ka hanani saka jambaki dan Allah?”

“Abinda kake so shi kakewa kishi... Kuma acikin ba’kin da zasu so harda maza, Nasan bakin ki zasu yi takalla. Shiysa fa nacewa Mamma ta kyale ki..”

Bai rufe baki ba Jannat tai knocking kofar,

“Assalamu Alaikum! Na shigo!”

“Shigo Jannat..”

Na karasa fada ina zura hijabi na. Shigowa tai kanta a kasa tana murmushi,

“Aunty bee! Mungode da waina yayi dadi. Bakiga santi ba. And mamma tace ace miki su Auntyn sunzo..”

“Fita to...”

“Kai Yaya...”

Harara ya dankara mata ta fice sum sum, Na kalle shi ina yamutsa fuska

“Meyasa kake mata hakane? Baza ta zo muyi hira ba kenan?”

“Matata ai ba sa’ar hirar ta bace.. Na miki lefi ne Fatimah na..? Kiyi hak’uri to!bazan kara ba.. Pls ki bari nacewa Mamma bakida lapia basai kinje ba.. Kinji! Na fada? Uhm? Kinji?”

“Aa zanje.”

Mik’ewa nai na zame hannun sa, Kayana na cire na koma can gefen closet dina nasa kaya na. Dauri na nayi na yafa mayafi a kafad’a.

“Bari naje..”

“Tsaya ni..”

Mik’ewa yai yana mita shi kadai,

“Mutum da matar sa, Gaskia sai munbar gidan nan.”

“Ni babu inda zani..”

“Wallahi sai mun bari. Duk sun takura mana.”

Na girgiza kai kawai ina kallon agogon hannu na. Takowa yai daidai kunne na ya radamin,

“Kinyi kyau! Sai dai ki yafa mayafin ki akan ki ba a kafada ba. Bara kuma na rage yawan jambakin nan..”

Kafin nayi magana ya hade ni da kofa ya jima yana kallon fuska ta kafin ya sauke idanun sa akan lebe na. Cikin wani salo ya lashe jambakin a hankali. Ya kuma dora min mayafin akai na,

“Yauwa haka yafi.. Muje to!”

Bance masa komai ba nai gaba yana biye dani a baya, Nayi mamakin rashin jerawar mu. Ashe Mubeen yana ta bayanta ya saita waya yana video din mazaunanta, Hotuna kawai yake mata ba adadi.

A babban parlorn sashen aka hallara, Yan uwan su Mubeen fal. Na gaggayshe su na koma gefe na zauna. Yammata kala kala sai binsa suke da kallo suna masa magana, Shi kuwa idanun sa na kai na. Ni har kunya ta ishe nima. Motsi kadan ya dago min hannu alamun ba matsala. Nama dena kallon gefen sa gaba d'aya. Lokacin sallah nayi na mike na shige dakin Jannat. Nayi sallah ta, Na jima ina adduoi kafin na koma parlor. Ina shiga idanuwana suka gane min Mubeen shi da wata yar uwar su a kujera d'aya tana nuna masa wani abu a waya yana murmushi, Muna hada idanu ta gallamin harara, Yadda suke a zaune sun dace sosai yasa gaba na faduwa. Na shiga dedeta nutsuwa ta ina jujjuya xoben hannu na. Mubeen ya dago ya dube ni da alamun bai masan na dawo ba. Zabga masa harara nai, Can na mike na koma sashen mu zuciata na kuna. Ina shigewa daki na fashe da kuka wanda banmasan na meye ba, Mubeen kuwa hankalin sa atashe ya shigo dakin yana kwalawa sunana kira,

"Fikre! Fikre! F..."

Da sauri ya k'araso inda nake ya juyo da fuska ta,

"Ya salaaam! Fateemah na! Kukan me kike uhm? Ni na miki wani abun?"

Cikin kuka bansan ya akai ba na daga kai ina nanata,

"Kai ne mana.. Sai dariya kuke kai da yar uwar ka.."

Cikin gigita ya cire hularsa ya wullar yana sharce gumi,

"Ni kuma? Plsssss! Kiyi hak'uri! Wallahi hotunan convocation d'in su take nuna min. Haba me zanyi da Sajjeedah? Wallahi Allah bana sonta! Fateemah na! Ki saurare ni! Wallahi Allah babu macen da nake so bayan ke sai yar da zaki haifa mana nan

gaba. Narantse da Allah bansan so ba sai akan ki, Ya Salam bansan ya zanyi ba dan Allah kiyi hak’uri! Me zanyi ki hak’ura uhm! Ina sonki Fikre! Ina kaunar ki. Ina miki tacacciyar soyayya marar gauraye..”

Hawaye na na goge da tafun hannu na ina ajiyar zuciya.

“Zan nuna miki kalar kaunar da nake miki..”

Mik’ewa yai ya kulle kofar dakin da makulli, Ya rufe labulayen dakin. Ya dauki wayata ya kashe da tasa sannan ya kashe fitilar dakin ya kunna dimlight, kayan jikin sa ya cire, A hankali ya dawo kusa dani ya janyo ni yana ragemin nawa, Na shiga kokarin hanashi,

“Ki bari Fateemah na! Kinji?”

Kyaleshi nai ya cire ya rufe mu da bargo, wata iriyar soyayyah ya shiga nunamin yana hawaye. Bansan Meyasa ba amman na amsa gayyatar sa’kon sa. Tuni na bada kai bori ya hau, Ruwa aka shiga tsugawa tamkar da bakin kwarya, Hakan ya sake dilmiyamu cikin wani yanayi da nakasa fasalta annashuwar da nasamu Kai na. Gaba d’aya babu inda Mubeen bai lashe ba ajiki na. Wata irin kalar soyayya yake yimin wadda na samu kai na da fashewa da kuka, harshen sa ya zura a kunne na yana tafiyar tsutsa dashi,

“Kin zarce sauran mata Fateemah na! Kece Sinadarin rayuwa ta! Ina son ki, kece murmushi na, Son ki na matsowa acikin zuciya ta... Ki yarda dani, inason kasancewa tare dake na har gaban abadan. Acikin idanun ki Akwai wani sirri me bani armashi Fateemah na! Kece harshen zucia ta.. Ina sonki fiye da kalmomi..”

Ya karasa fada hade da zare ribbon din kai na ya cillar yana wasa da gashin kai na da dayan hannun sa. Cikin kunne na ya shiga radamin,

“Dalibata...!Ina fatan kina daukar darussan malamin naki? Ina fatan wunin yau Malam ya jefa kwallon sa a raga Ameen... Ina kaunar ki fadimah na! Fikre na! Ayana na! Batoul dina... My one and only beautiful wife.”

Luf nai a kirjin sa ina karb’ar sakon da yake aikamin. Banida bakin magana wallahi, Gaba d’aya ya gama dani a fagen soyayyar sa! Haka bacci ya d’auke ni baki na dauke da adduar Allah yasa mu shiga shekarar 2019 zata shigo washe gari a sa’a, Allah ya kade fitnar ciki ya samu amfana da albarkar cikin ta...

_

MX□□

ZAFAFA BIYAR NA KUDINE,IDAN KIKA GANI (DON GIRMAN ALLAH) KARKI SHARING,IDAN KINA BUQATAR SIYA ZAKI TUNTUBI WANNAN NUMBER

07067124863

Ko kuma

09032345899

ku ziyarci tasharmu ta youtube don ganin shirye shiryenmu da sauraron litattafanmu tsofaffi da sababbi,karku manta ku dannan SUBSCRIBE kuyi LIKE sannan kuyi SHARING□□

https://youtu.be/LxY42ErBf_8

IGIYAR ZATO.....

(Eternal_love)

INAH ZAKI DAMU!!! daga jin sunan labarin ba saikun tambaya ba kunsan labarine daya kunshi al'amuran da suke faruwa a cikin duniyar nan tamu wanda tunani ko zato bai taba kawowa ba, ban tausayi al'ajabi soyayya fad'akarwa da ilimantar wa duk zaku samu a cikin littafin nan da naira 200 kacal littafin marubuciyar nan da kuke nishad'antuwa da rubutun ta *SISIN MAMA* marubuciyar labarin nan naku mai farin jini *GOYON KAKA* kada ku bari a baku labari sark'ak'iyar dake k'ulle cikin littafin *INAH ZAKI DAMU* labarin SU'AD yarinyar data taci cikin tsanani da wahalar rashin sanin asalin ita d'in wacece kada in cika ku da surutu dan samun mallakar littafin ku nemeta a wannan number d'in 08107499249

53

GIDAN MATA TARA

Shema’ulle kanwar Bintalo ce da tazo daga kauyen su na ko’de dake lahdin makole ta kano. Ta bararraje akan turmi tana ratattaka magana. Kamar su d’aya da Bintalo tamkar an tsaga kara an karya. Sai kakazar magana take ko gajia bata yi. Ita da yaranta su hudu, Mata biyu maza biyu. Ta sosa kanta tana mai cigaba da bawa Bintalo labari dake numfarfashin ciwo akan shamilalliyar tabarmar ta, Yaji tayo shine tazo wajen bintalon, Kwanan ta uku anan kullum cikin cigaba da bada labarin abunda ya hada su da mijin da kishiryar ta take, Cikin hausar ta ta karkarar karshe,

“Makaryacin asara! Rabu da hegu Bintalo. Ai nakance ni ka fara aure sallau kafin adama, Hmm hegen ya kance ai adama ta fiki cikar komai, Hege dan bankadaddiya, Ranar da zan taho, Sai ga dan ‘kaddarar ya siyo awara ta wazobiya yabai dan adama ya kai mata.. hege dan gantalalliya,

“Walle na kama mihi wuyan riga nakance dahi zab’i d’aya sallau ko ni ko adama? Yakance adaman dai! Hmm me akai da maza inji karya? Wai adama sallau ike so? Yakance yar duma-duma ce. Makaryacin asara! Ai kuwa da zan taho nabi randunan mu na farfahe hegun, Na kuma dakko takaumin sa (takalmi)wari biyun na jefe hegu a kwatar gidan haladu..”

Bintalo na kwance ta sheke da dariya,

“Shegiya shema’ulle! Sittin ta ubangiji gwara kici uwar sabada. Dan kundin uba da bajajjen hanci tamkar uban sa na gangare.”

Shema’ulle ta kece da dariya tana sosa hanci,

“Rabu da hegen, ai nakance mihi munin ka irin na ubanka na gangare mai kayan miya.. Ya kance gara hi akan namu uban mai yasar kahi.. ranar muka higa dambe da juna. Na mar duka hegen.”

Yinin ranar su Bintalo na hirar su, Baba usaiba da Ummita kuma na zazzaga fada ma’kota na faman rabiya,

“Cika ni furera! Ni kam naci biredi na yage leda, a hayye kayya kai! Ku rabu dani na karairaya matar can.”

Baba usaiba ta karasa fada tana cakumo baba Ummita suka shiga haurawar fada. Lamarin dai sai a slow. Gashi shirin yin biki ake a gidan. Amma kullum da fada suke tashi su kwanta, washegari tayi su dora akan na jiya..

Baba kaltume kuma sun tafi Shema Itada Aminatu autar mu, Tunda akai wa su autar mu hutun zangon karatu na biyu suka tattara suka tafi Shema yin hutu da kuma zagaye dangi..

KADUNA

Da sauri na shiga shiryawa saboda tafiyar mu washegari ne, Na roke shi ya kai ni wajen Gwaggo Aminatu na mata sallama tunda shekaran jia waccen munyi sallama da su Innar mu ta waya tace suna shema sun hutasshe mu. Naso ganin Innar mu da autar mu amman haka na hakura, Da nace muje sheman mu mata sallama tace aa Allah ya dawo damu lapia. Innar mu kenan gaba d'aya kunyata take ji yanzu kamar wata yar fari. Doguwar rigar abaya na zura maroon color, Nasha kwalliya sama sama abuna sai tashin kamshi nake,

"Anya ba zaki sa hijabi ba kuwa?"

Nayi rau rau da idanu ina cuno baki gaba,

"Dan Allah Kayi hak'uri gidan Gwaggo ne fa.."

"Eh gidan gwaggon! Haka kawai a dinga kallemin mata."

Kowa yana harkar gaban sa wa zai tsaya kallo na kamar wadda nafi kowa kyau? Saurin yin gaba nayi ina rataya jaka ta a kafad'a. Motar sa muka shiga yaja mu muka dau hanyar gidan Gwaggo Aminatu, Wak'a ya saka ahankali yake bi yana matsa dayan hannu na,

"It's a beautiful feeling! What we got deep inside! We got a flame that will last forever! Together, you and I! Such a rush of emotions! There's no way we can push it away! Cause they'll never tear our love apart! Our bond will never break!Do you believe in the power Of everlasting love?□□,

"We can make it if we stay together!Our love is just enough!Promise me this forever!We'll always stay this way

We can start at the end of time!!And do it all again! Oh, my love...I'm all yours...□□

“And there will never be another one

'Cause I'm eternally yours! My heart's a flame! And it's burning in your name

Even through the sands of time

My love will always grow□

“And I won't let go! It's a beautiful feeling! We've got deep inside

And there will never be another one

'Cause I'm eternally yours! My heart's a flame! Such a rush of emotions

Burning in your name! We can't push it away! Even through the sands of time

My love will always grow! My eternal love.. Fateemah na I’m all yours till eternity do us apart...□□”

Murmushi kawai nayi masa na cigaba da danna carbin hannu na,

“Ina kaunar ki fikre! Da kaunar ki aka halicce ni a zucia ta. Fikre ba so nake miki ba. Kaunar ki nake! Kauna tamkar SO take, sai dai kauna tafi aminci. Domin ita kauna bata canzawa, har agaban abadan. So tsuntsu ne yana tashi , soyayyah ruwan zuma ce mai ‘karewa. kauna kuwa bata ‘karewa a kullum kamar kara mata wutar ruruwa take yi. Za’a iya shiga tsakanin so ya zamto anasamin matsaloli har zucia tafara waswasin canzawa, Kauna kuwa a kullum dad’uwa take yi makauniya ce akan abunda ake muradin so. Fateemah na! Shi so sau da dama idan zucia bata samu abunda take so ba, sai kiga wannan soyayyar ta koma ‘kiyayya har wasu nayiwa abun son nasu fatan shiga uku. Ita kuma ‘kauna bata canzawa, so tsakani da ALLAH shi ake kira da ‘kauna, Fikre akan ki nasan SO, nasan menene SO? Akan ki nasan ‘kauna. Ina miki Son so, Ina miki son ‘kauna, Ina miki taccaciyar ‘kauna marar gauraye..”

Haka yaita zubamin kalamai har muka k’arasa gidan Gwaggo Aminatu mai gadi ya wangale gate muka shiga ciki,

“Zo kiji..”

Na kauda kai, Domin zo kijin sa na nufin abubuwa kala kala na mugunta,

“Ba sai nazo ba, Bari naje ciki.”

“Haka zan kawo ki ba godia babu komai sai juya keya..To jeki!”

Ashe gatse yamin, Inasa Hannu najita a rufe,

“Kayi hak’uri. Dan Allah!”

“Toh xoki ji..”

Matsawa nai ya kamo ni ya rungume yana sauke ajiyar zuciya,

“Ki kular min da kan ki Fikre! Zan dawo nan da minti goma na dauke ki.”

“Minti goma kuma? Haba Mubeen! Kenan ba zaka shiga ku gaysa bama?”

“Ai idan muka shiga bazan iya fitowa na bar ki ba wallahi, Sai dai idan na dawo daukar ki. Yanzu fa zan dawo dan bama zanbar area dinba.”

Don ya barni yasa nai k’ok’arin kamo hannun sa nasa acikin nawa ina kallon idanun sa,

“Dan Allah... Ka bari sai bayan magrib kaji? Ka yadda? Uhm?”

“Ya Salam! Kina birki tamin lissafi Fateemah na! Toh sai dai da sharadin xaki min wanka.”

Na ware idanu ina ture hannun sa.

“Aa gaskia.”

“Toh saura mintina nazo d’aukar ki..”

“Na yadda...”

Murmushin mugunta yayi yana taune lebe, sumbatar hannu na yayi

“Ina son ki fikre! Ki gayda gwaggon zan dawo da an Idar da sallah Insha Allah!”

“Allah ya kaymu..”

Na bashi amsa ina daga masa hannu, Ciki na shige. Sai data shjga sannan Mubeen yaja ajiyar zuciya ya sauke ya tashi motar ya fita. Can wani gefen masallaci ya zauna ya zaro wayar sa yana chatting da abokansa na Ethiopia.

Cike da farin ciki na karasa cikin parlorn gwaggo. Tayi murnar ganina ta rungume ni. Cikin nutsuwa na gayda ta muka shiga hirar yaushe gamo? Ai kuwa ina idar da sallah ya kira ni yace gashi nan a kofar gidah, Na masa izinin shigowa suka gaysa da Gwaggo. Ya mata sallama ya Fita bayan ya ajiye mata ledoji biyu agaban ta. Wata leda ta d’akko dauke da robobi aciki da magunguna fal na mata.

“Ungo nasha dana tsugunno ne. Allah ya kai ku a sa’a Batoul..”

“Amin Gwaggo. Nagode Allah ya saka da alkhairi”

“Amin! Ni ce da godia! Dan Allah kibi mijin ki sau da kafa Batoul. Duk abinda yace ki masa inde ba haramin bane. Idan kun samu sabani ki bashi hak’uri. Ki zamto kece a kasa a kullum shine a sama..”

“Toh Gwaggo.”

“Yauwa Allah ya miki Albarka! Allah ya kare ku ya tsare ku daga sharrin masu sharri..”

Har kofar gidah ta rako ni tana daagamin hannu. Na shiga mota Mubeen ya ja mu muka d’auki hanyar gidah,

“Me muka samu...”

“Maganin typhoid ne.”

Daria yayi yana haska ledar da fitilar mota.

“Mungode sosai Gwaggo... Da magani.”

Tsuke fuska nayi nia kyale shi Har muka karasa gidah. Ciki muka shige muka fara gayda su Mamma kafin mu wuce sashen mu. Wanka nayo na zura rigar bacci mai kauri saboda sanyin garin. Daukar gorar maganin nai na fara sha. Domin zuma ce da wani hadi na T-chad.

“Sanmin nasha.”

Cewar mubeen yana miko min hannun sa,

“Bazan bayar ba maganin typhoid ne fa.”

“Ai inada ita..”

Mika masa nai ya shiga daddaka yana murmushi,

“Babu wani maganin typhoid. Gwaggon mu ta mutinci Allah ya saka da alkhairi. Duk ‘karuwar mu ce.”

“Kaji dashi..”

“Gaskia maganin nan akwai dadi wallahi! Dan karamin wata robar.”

“Kwata kwata fa guda biyu ce...”

“Toh ki shanye dayar mana..”

Mikewa nai na dauki na tsugunon na shige d’aki na dashi, Garwashi na kunna na zauna akan steaming chair na fara yin na tsugunon. Gaba d’aya jiki na naji yana neman canzawa. Na lumshe idanu hade da mikewa na sa turaren wuta akan garwashin. Nai kwanciyata akan gado ina taune lebe. Sai ga Mubeen ya shigo,

“Muje kimin wankan..”

“Wayyo kayi hak’uri dan Allah.. kai nane yake ciwo!”

“Tab wallahi bazan ha’kura ba. Ni dai ki yimin kawai.”

Dagowa nai na kalle shi dakyar ina rintse idanu na. Tashi nai ina ha’da hanya na shiga band’akin ya biyo bayana cikin rawar jiki. Kayan sa ya rage ya cika bahon da ruwa, Ya diddiga abubuwan kamshi aciki,

“Na shiga ki min?”

D’aga kai nayi kawai ina kokarin danne marata dake tsinkuli na. Idanuwana har dishi dishi suke, Bahon ya shiga yana wasa da kumfar ciki. Rintse idanu nai na shiga goga sosan ajikin sa. Mubeen na ganin yana yinta ya janyota cikin ruwan,

“Fateemah na! Meya faru?”

“Ba... bakomi bacci nake ji.”

Kwantar da ni yai akan k’irjin sa yana sabule rigar baccin ya jefar. Daga karshe dai mutumin ku ne yai wa malamar sa wankan. Ya kuma shiga wani sabon lamarin. Sam ban hanashi ba saboda jiki na babu karfi. Haka Mubeen yai ta bidirin sa da ni. Kamar wasa yajiyo ina bashi gudunmawa. Daren ranar dai Mubeen ya kwashi ganima awajen Batoul.. Haka yaita sa mata albarka. Muna fitowa ya dauroni a towel ya kaini kan gado. Ya tsotsi nan ya taba can yana min sumbatin soyayyah a haka daren ranar muka tsinci kansu..

Tsaye nayi ina yane kai na da d'an garamin hijab sannan na dakko mayafi na dora a kafadata ni kaina nasan nayi masifar yin kyau. Juyawa nayi da nufin karasawa na dakko takalmin da zan sa kawai sai na ganshi a tsaye ya hard'e hannayensa a kirji yana bina da kallo. Murmushi nayi a cikin zuciya ta ba tare da na kuma mai da idona gareshi ba duk kuwa da zuciya ta tana son kuma kallon shi saboda ya yi kyau ba karya. Dukawa nayi ina shirin janyo takalmin kawai naga ya tako har kusa dani ya dago ni yana kare min kallo.

"Proposing u was my desire, having u is my jackpot, loving u is my attitude, pleasing u is my duty, missing u is my habit, kissing u is my wish 2gether 4eva my Fikre."

Yana gama fada ya sumbaci saman lips dina da na gogawa lipstick mai dank'o.

"Kai dai baka gajiya wallahi."

"Akanki ne bana gajiya my Fikre."

"Thank you, mu wuce ko?"

Nayi maganar cikin basarwa dan naga yana wani kifkif da idanuwansa. Murmushi ya yi ganin ina saurin fita daga ɗakin sai ya yi saurin zuwa ya riko min hannu.

"Oya muje mu yiwa Papa sallama naga yana sauri zai je wajan wani taro."

Kai tsaye sashen mahaifinsa muka nufa, ganin yana shirin shigar dani hannun mu saƙale da juna yasa ni tirjewa, ya kada ya raya mu shiga a haka naki sai dai ya yi gaba. Murmushi ya kuma yi tare da cizon lips ya shiga nabi bayan sa bakin mu dauke da sallama.

"Papa zamu wuce."

"To MM yau sai kasar Faransa kenan?"

"Yeah Papa jirgin eight zamu bi gashi yanzu seven thirty karmu makara."

"Toh Allah ya kaimun ku lafiya ya dawo daku lafiya. Fatima sai kin dad'a hakuri da mai gidan naki saboda akwai raki, Allah ya kiyaye muku hanya kun ji?"

"Amin Papa mun gode Allah ya kara girma."

Nayi maganar kai na a duke kafin daga bisani yace mu tashi muje. Ina mikewa Mubeen ya kamo min hannu Papa yana kallan mu ya yi dariya yana kada kai da alama farin ciki ne tsanka a cikin ransa. Muna fito zamu wuce gurin Mammah Ahlaam na fizge hannuna ina turo baki fuskata a haɗe nace.

"Kai ko kunyar su Papa baka ji, a gaban su kake riko mace." Sai da ya matso kusa dani sosai yace.

"Toh wace macen? Ina cewa mata ta ce ba? Karki ja idan muka shiga gurin Mammah na tsotse miki lipstick d'in lips naki Kinga sai ki ji kunyar da hujja."

Nayi masa banza ban tanka ba dan nasan tsab Mubeen zai yi wannan katobarar. A parlour muka tarar dasu Jannat duk sun shirya zasu yi mana rakiya zuwa airport. Na durkusa na gaida Mammah sannan ta yi mana fatan alkairi, har muka fito ta raka mu har parking lot muka shiga mota drive yaja muka tafi. Su jannat sai labarai suke yi daman ba wani bamu lokaci yake yi ba, kullum shi dai na zauna tare dashi kamar kamar wasu mararsa 'yan uwa.

Muna isa airport muka firfito, driver da wasu escorts da his excellency ya bamu suka yo mana rakiya, sune suka fito da trolley d'in kayan mu gabaki d'aya muka rankaya wajan screening. Bayan mun gama komai kasan cewar jirgi ne na gwamnati akawai wasu manyan kusoshe da zamu tafi da su wadanda gwamna ya tura zasu yi wani aiki a can, muka nufi filin jirgin su Jannat suna makale dani.

“Ku ya kamata kuzo ku koma gida, ko bin mu zaku yi ne?”

Dariya duk suka saki ganin yadda yake bude idanuwa.

“Ya MM iyakar mu nan ko da baka yi magana ba, Aunty Bee Allah ya tsare hanya ya dawo daku lafiya Allah yasa daga can ku samo mana b...”

“Jannat ya isa haka sarkin magana.”

Mubeen ya katse ta yana yatsina fuska.

Hannu na yaja muka nufi matakalar jirgin, duk da cewar wannan shine karo na farko da na taba zuwa zan hau jirgi hakan be sanya nayi kauyanci ba, idan kuka ganni sai kuyi zaton daman can na saba shiga. Guri na musamman aka bamu daga ni sai shi, na yatsina fuskata saboda nasan wannan lokacin ma Mubeen ba saurara min zai yi ba.

Zama muka yi ina kusa da shi ya janyo ni jikinsa na kuwa lafe saboda nasan ko ban yarda da yi ba dole ya samu abin da zai sanya mu rungume junan mu. Wayarsa ya janyo ya dinga daukar mu hotuna, lokacin da jirgin zai tashi sama ne luuuu d'in da naji yasa ni makalkale shi ina sake riko shi kamar wacce za'a gudu a bari. Murmushi naji ya yi hakan ne ya ankarar dani kwafsin da nayi, sai na sassauta rikon na gyara zama na.

Drink ya zuba mana ni dai ban wani sha da yawa ba dan bana son naji fitsari, shi kuwa ya dinga kurba ina jikinsa yana rungume dani hannunsa d'aya yana danna waya dayan kuma yana shan lemo. Bacci ne ya dauke ni a jikin nashi, bai motsa ba saboda kada na tashi, ai kuwa har muka kusa isa sannan na bude ido, jikinsa duk ya yi tsami saboda rashin motsi amman bai nuna min ba sai tambaya ta da ya yi me nake so, na kada kai alamar babu komai sannan naga yana faman cije baki. Ganowa nayi ganin baya iya motsi da hannunsa, sai na zare jikina na fara jajja masa yana faman raki.

“Ahh! Wayyo my Fikre da zafi fa! Ahhhh Mammah!”

“Wai menene haka dan Allah, sai abokan Papa sun yi tunanin wani abu ake a nan?”

“And so? Ke ba matata bace”

“Mubeen...!”

“Na'am my Fikre.”

Ganin ni kawai nake jin kunyar ihun nashi yasa na kyale shi dan shi ko a jikinsa. A hankali naji ya dagoni tare da gyara min zama ya janyo ni yana nuna min tagar jirgin. Ya Subahanallahi idanuwa na suka fara dishi-dishi lokacin da suka fara cin karo manya manyan tsaunikan gidaje, tabbas daga kauye muka zo domin Najeriya irin kauyen kyayayau d'in nan ne a kasar France. (Batoul ta saki murmushi tare da kallo na ni Miss xoxo dana dukufa ina ta rubuta labarin, sannan ta maida idanunta kan tawan wato Billyn Abdul wacce ta zabga tagumi tana kallon Mrs Mubeen da take cikin shiga ta kece rai ni, sai Ya Hajja ce da ta saki baki da alama labarin da takeji jin ta take tamkar itace Batoul d'in 😂Sai madam rano dake afkin lodawa cikin ta rice tana lumshe idanu. Kasan cewar su na dauka rakiya muka je government house dakko labarin). Mikewa tsaye tayi tana kallon mu tace.

“Bari a kawo muku abinci sannan kuyi sallah ku huta sai na dawo naci gaba da baku tarihin rayuwata, da abubuwan da suka faru a can kasar Faransa.”

Tana gama magana ta juya ta shige cikin wani ɗaki. Tawan (Billyn Abdul) ta sauke wata katuwar ajiyar zuciya ta kalle ni tace.

“Wai dan Allah matar nan da gaske take ba zata nuna mana koda hoton mijin nata mu gani ba?”

Yaya Hajja ce ta saki dariya tana daukar kwalin lemo ba tare da tace komai ba. Ni ce na ajiye biron tare da rungume littafin da nake daukar story d'in ina lumshe ido nace.

“Tawan barta ta boye abin ta, dan wallahi tunda ta fara bamu labarin nan naji gayen ya min, hmmm idan har na ganshi mukai ido da ido dashi yau ba zan iya bacci ba.”

Suka yi dariya dai dai sannan hadimai suka dinga shigo mana da abinci dana sha dama na kwalam da makulashe, muka baje muka ci daga nan sallah mukai sannan duk muka baje akan carpet sai gata ta shigo cikin wata sabuwar shigar. Gaskiya dole ne ma Mubeen ya dinga mannewa matar nan saboda akwai daukar wanka da kamshi. Zama tayi tare da kallo na tace.

“Kin shirya muci gaba miss xoxolious, madam ceo yerwa. Kinga wannan turaren wutar da na siya a wajanki? Hmmm duk lokacin da na turara kaya na tun daga kofar parlor yake fara zame takalminsa da safa, da ya karaso inda nake...hmmm.”

Nidai nai dariya kawai ban ma so tace hmmm d'in ba naso ta yi min dallah dallah amman matar nan ta gumtse.

“Ai Mrs Mubeen duk turaren yerwa babu mai kauri, wallahi koni ina san su har ma bana son su kare min. Wai kuwa hajjaju kin taba karbar turaran wanka dana wanke pants? Au harda na mopping , wallahi haj...”

“Ya isa Hajja ce kike ko wa? Ina amfani da kayan yerwa gabaki d'ayan su hafsat rano tasani, kuma ko yanzu haka turaran khumran da kika ji a jiki na, miss xoxolious ai na ki ne ko?" Ni dai nayi murmushi kawai nayi na kagu ma taci gaba da bamu labari, aikuwa sai ji nayi tace.

Paris....The city of love

(16th arrondissement)

Tun a cikin jirgin na hango symbol d'in Eiffel tower, sai kawai naji bakinsa a cikin kunne na yana cewa.

“Wannan symbol d'in da kike gani na soyayya ne, dan haka na zabar mana d'aya daga cikin hotel din da yake kusa dashi wato Global blue, dan haka ki shirya shayar da babyn ki madarar zallar kauna, idan ba haka ba kuma..”

Ya yi shiru tare da sanya hakoransa ya ciji fatar kunnena.

“Ashhh.!”

Na furta alamun naji zafi kuma babu abinda naji kawai so nake na firgita shi. Ai kuwa ya rude ya janyo ni jikin sa ya shiga hura min wajan yana bani hakuri, ni kuma sai faman rintsa ido nake yi. Fuskata ya juyo tare da kallo na nayi saurin dauke idona akan nasa, bakin sa ya zura cikin nawa ya shiga murza harshensa a ciki, tuni na yafe masa na manta ma da cewar lallashi na fa ake yi, sai da mukaji saukar jirgin a ƙasa sannan ya ciro bakin sa yana kokarin sai mun hada ido naki yadda.

“Kina bani kunya Fikre, wallahi sai ayi abu yanzu-yanzu amman kiyi fuska tamkar ba dake akai ba.”

“To ni kuma me nayi yanzun?”

“Gashi nan kuwa, da kika kama baki na kin saki kikai, please me kika ji da kina kissing d'in?”

“Kaga ni ban san abinda kake nufi ba, ka tashi ka gyara gashi nan ana cewa mu shirya.”

“Uhmm ke dai akwai maziya.”

Na tabe baki ba tare da nace masa komai ba, can kuma shima ya fara gyara nutsuwarsa ya riko hannuna kamar wanda aka ce masa zan gudu. Bayan jirgin ya gama tsayawa akai announcing cewar passengers zasu fito. Hannuna cikin nashi

haka muka fito daga cikin vvip suite d'in da aka ware mana a jirgin, ana gama sauke mana talattakalar muka sauka daya sauke kafarsa d'aya zan dora tawa a haka muka diro.

“The city of love.”

Na fada a hankali lokacin da idanuna suka shiga karakaina akan mutanen dake shawagi a wajan, duk mutanan indai mace da namiji ne to tabbas rungume zaka gansu da juna, baka taba gane yaya da kanwa ko saurayi da budurwa bare kuma ace maka mata da miji saboda yadda ake makalewa da juna.

“Me kika ce my Fikre?”

Mubeen ya tambaye ni ashe a fili nayi maganar, amman sai na yi fuska nace.

“Ba magana nayi ba.”

“Okay tsaya a nan bari naje muyi sallama da MD sai nazo muje masaukin mu ko?”

Kai kawai na daga masa sannan ya sakar min hannu ya tafi yana waiwaye na, ni kam sai kalle-kalle nake ina kuma karewa Eiffel tower kallo ganin yadda gadar take da tsawo sosai ga mutane nan sai daukar hotuna suke abin sai wanda ya gani.

Babu jimawa sai gashi ya dawo ya riko ni daya hannun kuma trolley d'in kayan mune yana janta, ga mamaki na ina jiran mu tari taxi sai naga mun isa wajan ruwa yaje yana magana da wani mai jirgin ruwa (yacht) irin me fukafukan nan. Naga mai jirgin ya gyada kai tare da tayarwa, Mubeen ya kamo hannuna, da sauri na cuke a wajan ina zaro ido.

“Ina zamu?” Na tambaya a razane.

“Hotel mana ko anan zamu zauna?”

“Amman a jirgin ruwa?”

“Yes menene? Kinga hotel d'in can fa gashi can a tsakiya babu abinda zai faru dake my Fikre insha Allahu, karfa ki manta daga sama kika sakko meye na tsoran ruwa?”

Ganin duk na tsorata yasa shi janyo ni jikinsa tare da sanya tafin hannunsa ya rufe min ido, bakin sa a saitin kunne na yake fadin.

“Karki ji tsoro ki dauka cewa daki zaki shiga. Yauwa baby na nasan zaki iya jaruma ta, kinsan akan ce, Behind every successful man is a woman–whoever said this is 100 percent right. You're the secret behind my success, my dear wife. I love you...”

Kunsan Allah tsabar jin dad'ad'an kalamansa yasa ban san mun shiga cikin jirgin ba sai kawai gani nayi ya bude min ido muna cikin jirgin ruwan d'are-da’re. Ai kuwa ana fara tafiya nayi saurin fadawa jikinsa tare da kankame shi, ko minti goma bamuyi ba sai gamu a bakin hotel d'in.

Muka sauka mai jirgin ya fito da trolley d'in kayan mu ya ajiye mana bayan mun fito daga ciki muka nufi cikin hotel d'in kai tsaye. Lift muka shiga yana ta faman kallo na wanda na rasa kona menene har muka karasa cikin dakin da zamu zauna.

“Wai banga ka tsaya a reception ka karbi daki ba ya haka?”

“Yeah komai ta online akai aka gama shi yasa kika ga ina zuwa mun taho dakin mu.”

“Uhmm ya yi kyau hakan ma ana ta ci gaba a duniya..”

Bayan mun shiga mun zauna ya kwanta a jikina kamar wani wanda ya yi tafiyar kafa sai faman mika yake yi.

“Mu fara yin wanka ko?”

“Eh amman ka fara yi kafin sannan na gama shirya mana kayan mu..”

Yayi dariya yana kallon fuska ta yasan cewar wayo nake son yi masa, har lokacin na kasa sabawa dashi ina jin nauyin yin wasu abubuwan a gabanshi. Ya tashi ya bude bathroom d'in da kanshi ya hada ruwan wankan sannan ya dawo inda nake fito da kayan mu ina ware nashi ina sakawa a wardrobe. Jan hannuna kawai ya yi muka shiga tare babu yadda na iya dole muka yi tare muka fito lokacin har an kawo mana abinci an zuro mana shi ta cikin wani guri mai kama da window.

“Zo mu fara cin abinci sannan sai mu shirya.” Na daga kafada alamar ban yadda ba ina cewa.

“Wai kai yanzu acici ka zama ne?”

Ya janyo ni muka je muka dakko abincin ya dire a kan wani table dake ajiye a bakin gado ya zaunar dani kusa dashi yana cewa.

“Nima na gani wallahi my Fikre, but kin san menene sirrin?” Na girgiza kai alamar a'a.

“Saboda ke kike bani shi yasa.”

“Yayi kyau acici bismillahi to.”

Nayi maganar ina saka cokali a cikin abincin wanda sam beyi min ba, hasalima amai naji yana niyar taso min. Da kyar na samu na bashi yaci, yana ta cewa naci amman nace so nake sai ya gama sai naci nawa. Bayan na gama bashi sai na tashi zan bar gurin yasa hannu ya janyo ni na koma jikin sa. Kallo na yayi saboda towel d'in jikina da ya dan zame kasa nayi saurin taro shi, sai ya yi tamkar be ganni ba yace.

“Ina kuma zaki je?”

“Zan sa kaya ne wallahi banjin dadin zama a haka.”

“Zo ki fara cin abinci tukunna.”

Naji tamkar ma yasa min shi a baki na nayi saurin kawar da kai na ina kada kai.

“Na koshi wallahi” Ya zaro idanunsa.

“Mekika ci.?”

“Na dai koshi ba zan iya ci ba.”

“Ba zai yiwu ba Fikre ko kalar abin cin ne beyi miki ba?”

Kafin na bashi amsa ya kuma magana.

“A kawo miki shawarma ko pizza or kina da abinda kike so a ranki.?”

Na dinga girgiza kai dan bana bukatar komai, ya kuma jana jikinsa bayan ya gyara zamansa, ya dakko ya fara bani abincin cikin lallashi, ganin ya dage yasa na fara ci

ina yatsina fuska. Bai fi spoon uku ba da nayi wani yunkurin amai ya taso min, kafin na kwaci jikina tuni na fara yi na kwaraye tray d'in abincin da amai.

“Meke damunki ne? Me kike ji?”

“Zuciya ta ke tashi, ban san wannan kamshin abincin.”

“Okay.. Okay bari na dauke miki shi sorry please.”

Yana magana yana tayar dani, muka shiga bathroom ya hada ruwa ya wanke mu tas sannan ya nado mu a towel guda d'aya saboda na bata na jikina dana shi da amai. Sai da ya fara ciro min riga nasa ya kwantar dani akan sofa tare da lullube ni da blanket sannan yace ya gyara wajan tas sannan ya dawo kusa dani ya zauna. A ranar dai ya shiga damuwa saboda yanayin da na shiga. Babu inda ya fita a haka muka kwana tare dashi a jikina kamar wani yaron goye.

Sai da na dauki kusan kwanaki uku bana jin dadi har yana tunanin ko dan ban saba da yanayin kasar bane. Sai a kwanaki na hudu ne naji na koma dai dai sannan shi ma yakan fita ya dan siyasa mana wasu abubuwan bukatar a cewar shi idan na warke zamu fita yin abin da ya kawo mu kasar wato shakatawa..

****

A hankali nake jiyo tafiyar harshen sa acikin kunne na. Sake kudundinewa nai ina jan bargo kai na domin baccin be sake ni ba.

“Bacci nake ji...”

Na bashi amsa ina matsar da hannun sa daga kan baya na. Shigewa yai cikin bargon ya janyo ta jikin sa sosai tamkar za’a kwace masa ita,

“Baccin ki yayi yawa yanzu fateemah! Ko dai baki da lapia ne?.”

Bacci na nacigaba da yi harda munshari, A hankali Mubeen ya cigaba da shafa sumar kanta yana sumbatar saman goshin ta. Sai da tai bacci ishasshe kafin ta farka dakyar tana adduar tashi daga bacci.

Mikewa nai na janye hannayen Mubeen daga kai na, Ban’daki na shige na yo wanka hade da alwala. Ina fitowa naga ya mike daga kan gadon sanye cikin kananun kaya har ya tashi tun d’axu kome?

“Ina kwana..?”

Agogo Mubeen ya duba yana murmushi, kusa da ita ya matsa yana kamo kafadunta yana hura mata iska a idanu, a hankali ya rankwafo da fuskar sa dai dai fuskar ta yana bin idanun ta da kallo,

“Kwana fa kika ce Fikre? Sha biyu da kwata yanzu..”

“Dan Allah?”

“Allah kuwa! Tun d’axu na shirya nake ta tashin ki kika ki.. Daman inaso muje wani wuri ne. Bara nayo wanka.”

“Baka yi ba?”

“Ai kin warware shi tas.”

Ya karasa fada yana kanne idanu. Na cuno baki gaba ina tsane kai na da tawul,

“Ni da nake bacci? Wlh babu ruwana..”

“Dande bakisan me nayi miki bane da kina baccin..”

Na shiga dudduba jiki na ina ware idanu, Na bude baki kenan zanyi magana Mubeen yai daria,

“Wasa fa nake! Kawai wanka zanyi da ruwan zafi. An fara snow..”

Gyada kai nayi ina maimata ‘snow’ din daya fada. Nide inde ba a film ba ko a kalmance bantaba ganin ta a Zahiri fa sai yau. Ta balcony na leka. Sharr sai zuba kankarar take yi gwanin sha’awa. Lalle Allah gwanin hikima ne! Shigar wata baturiya na kalla tamin kyau. Daki na koma na ciro riga da wando nima da jacket. Harda sabon booth da Mubeen ya siyo mana jia a blue water mall. Kafin ya fito tuni na gama shiryawa cikin kayan. Na yane kai na da mayafi. Yana fitowa ya tsaya yana bina da kallo kamar wacce ya fara sani a lokacin,

“Ina zaki a haka?”

“Ba kace fita zamu yi ba..?”

Yamutsa fuska yai yana shafa kwantaccen gemun sa.

“Anga zamu fita dinnan kuwa.”

Kasa amsa masa nayi. Haka kawai na tsinci kai na da binsa da kallo. Dogo ne sosai, Yanayin mazantakar kirar jikin sa ta dace dashi, Bashida kiba, Amma ba za’a sashi a jerin masu rama ba. Six packs dinsa sun dace da faffadan kirjin sa TubarkAllah! Yana da kanannadden gashin kai baki wuluk dashi a kwance. kallo d’aya zaka masa kasan ruwa biyu ne shi. Fuskar sa doguwa ce mai dauke da siririn hanci tamkar shiya zana kayan sa. Idanuwan sa dara dara ne mai dauke da kwayar ciki coffee brown! Ga gashin ido dana gira daya kusa hadewa. Labban sa jajaye ne kamar wanda ya shafa Jambaki. Ga sajen daya zagaye fuskar sa ya sake kayata shi.

Hakoran sa farare tas a jere suke dauke da hushirya a tsakiya. Ga side dimples dake lobawa a gefen kumatun sa. Cikin shagalar dana tafi a kallon sa na jiyo takun tafiyar sa ya tsaya a gaba na. Ba zato ya sakar min kiss a gefen kumatu na,

“Day dreaming?!!”

“Kind of. Ina tunanin su Innar mu.”

Kada kai yayi yana murmushi, Ya janyo hannu na muka koma bakin gado. Sanye yake cikin wasu kananun kaya samfarin Italy yayi kyau ba karya. Nail cutter naga ya dakko a gefen gado yana mikomin hannu,

“Mu yanke farcen mu ko?”

Na kalli farce na tas dashi ko dan yaji jia ina zan rage? Girgiza kai nayi ina murmushi,

“Aa zanyi da kai na..”

“No! Ai nagaya miki wanke kai, kafa da cire nails duk zan dinga yi miki..”

“Ai kakka zaftare min farata na ni dai..”

“Worry not sweethrt!”

‘Sweetheart?’ Na maimata a zuci ina lumshe idanu. Ba musu na mika masa hannu na ya shiga cirewa a hankali cikin nutsuwa.

“Nagode Mubeen..”

“Anytime my love.. I love you soo much Fateemah na. Ki adding nails dnki acikin abubuwan da nake so a tattare dake. Ina sonki da yawa fateemah na!.”

“Nagode Mubeen!”

“Nifa gaskia sai kindena cemin wani Mubeen. Haba! Babu kyau fadar sunan miji gatsal..”

Murmushi kawai nayi ni dai namike ina gyara mayafi na. Kafadata ya kamo cikin tasa muka sauka ta lift. Wannan karon ma yacht muka hau muka karasa wani tower da ake kira da,

‘Eiffel tower’

(Symbol of love)

“My love welcome to Paris the city of love.. Ga Eiffel Tower symbol of love! Ga mu masoya! Duk wanda kika gani awajen nan masoya ne. Fikre dan Allah ki karbi soyayyah ta! Yaushe zuciar ki zata amince dani a matsayin masoyi! Uhm?..”

Gaba d’aya na shagala da kallon tower din! Banda a movies ko a bayan littafin A’b’c’d bantab’a sheda ta ba sai yau. Idanuwa na na sake mitssikewa ko mafarki nake? Masoya sai wargajamin su suke. Mubeen ya sake janyo ni jikin sa yana nunnuna min ko’ina. Wurin cin abinci muka je agefen wajen muka ci, Sannan muka futo! Photographer Mubeen ya kirawo ya shiga daukar mu a hotuna, Sai matse ni yake a jikin sa mai hoton na bamu styles din yadda zamuyi.

“Ki saki jikin ki.. Nan fa Paris ne! Kowa harkar sa yake Fikre! Basu papa a kusa.”

Yana min maganar mai hotan na dauka a haka, Sai muka bada wani style lokacin yana magana na daga kai na kalle shi. Gurin wani mai sai da kwado (padlocks) yaje

ya siyo mana guda biyu, yafuto ni da hannu yayi, Na karasa kusa dashi. Ya mikomin yana nunamin yadda zanyi,

“Yauwa ki zana zanen zuciya anan sai kisa sunana da naki daga kasa ki rubuta forever ko dai wani abun..”

“Saboda me?”

“Saboda haka akeyi anan! Tradition ne. Idan mun gama sai mu sakale su anan, mu jefa keys din acikin seine din”

Banason yi Amman gudun kar na gwale shi yaji ba dadi yasa na karba kwadon na shiga zana karamar zuciya na rubuta sunayen mu ni dashi aciki,

Mubeen & Batoul..(Forever)❤

Murmushi yai lokacin daya karanta, Ya gyara zama sosai yana tsantsara nasa,

Fateemah na (Batoul) & Muhammad Mubeen 2019! Paris #Eternal love! Two hearts, locked in love. Love is all we need. Happiness is not perfect, until it is shared. You make my heart happy Fateemah.. Love you eternally□□

Murmushi nai lokacin dana karanta abinda ya rubuta,

“Ina keys din naki...?”

Nuna masa nayi, Ya Kada kai hade da jan hannu na muka koma koma inda ake jefa keys din a seine! Nan muka wuwwula muda sauran masoya da suka zazzo wajen. Mubeen ya rungume ni yana murmushi,

“Fateemah na! Wannan tradition ne na Paris daya samo asali a 20th centuries, Saboda Paris birnin masoya ne. Haka ma Eiffel Tower dinnan wurin zuwan masoya ne.Abunda mu kayi yanzu shi yan faransa suke cewa Padlock marked with the railings and throwing the keys in to the river seine . Wai shine Locking thier love forever in the Most romantic city of the world... Abun ya burge ki???”

D’aga kai nayi a hankali ina kokarin zare jiki na daga nasa,

“Ssssh! je t'aime tellement Fateemah na!”

“Na’am?”

Murmushi Mubeen yayi wanda kyakkyawar hushiryar sa ta bayyana,

“Nace I love you soo much! Wai Yaushe xakice kina sona uhm?”

Shiru nayi ina bin mutanen wajen da kallo. Mubeen ya gyara hular kansa yana sake kamo hannun ta cikin nasa,

“Bara na kuma nuna miki yadda dayan tradition din yake. Matsawa na cigaba dayi muka kai har karshen karshen karfen tower din,

“Kin kalla titanic??”

Na daga kai na ahnkali ina hadiye wani yawu. Yai murmushi yana yamutsa fuska,

“Toh haka zaki yi..”

Hannuwan sa yasa ya d’aga nata sama, Shima ahankali cikin tafiyar tsutsa daga cikin ta zuwa can saman kirjin ta ya daga nasa saman. Su kai tamkar fuka-fukai,

“Ki saki jikin ki kiji iskar masoya mai kad’awa Fateemah na! Kina ji?”

Ya fada a kunne na yana cizan sa hankali..Juyowa yai dani ya bani wata kyakkyawar runguma, Daga nan ya hade bakin mu waje d’aya yana gaya min wasu kalamai,

“A yayin bayyana miki adadin yadda nake jin son ki a zuciyata Fateemah na! zan iya yin amfani da kalmomi irin su…….hmm ko dan ina ganin cewa babu wata kalma da za ta iya wakiltar matsayinki a gare ni. Sai dai a yau a kuma yanzu ina mai ƙara sanar da ke cewa, ina son ki Fateemah na.. you’ve slipped under my skin, invaded my blood and seized my heart...”

Kokarin kwace kai na nake Mubeen ya sakamin karfi ta hanyar hade hannuwa na biyu ta bayan karfen. Dayan hannun sa kuma ya shjga gyaramin gashin kai na daya zubo gefe. Wasu Shegun kisses ya shiga bata a ko’ina wanda yasa Batoul hawaye. Abun mamaki sai ga Mubeen yasa harshen sa yana lashe hawayen cikin wata irin siga ta soyayyah,

“I love you babe, and every time I see you I just want to hold you in my arms and never let go because you’re the girl that fills all the little dark places in my heart, Fateemah na! Darasin mu na yanzu zamu yi shine akan french kiss’ dama gamu a french country ko? Wato Paris! Ga kuma Eiffel Tower!...”

Kafin nayi magana ya rankwafo dani yana kallon fuska ta. Wata irin sumba ya shiga yi min wanda duk ilahirin jiki na sai da ya amsa sakon sa cikin girmamawa.

“I am addicted to your love! I am crazy about you Fateemah na! Komai nake is just! Ya salam! Fateemah na! I get lost in ecstasy when you make love to me. Allah ya biya miki bukatun ki na alkhairi.”

‘Gaba d’aya na rai na ajina, Tunani na, Shekaru na kai dama karatu na. Gaba d’aya muhammad Mubeen ya gama birkitamin lissafi. Wallahi tamkar a film haka nake ji. Danshin hawayen sa ne ya shiga diga a fuska ta, Ko na meye oho!

“I will travel a thousand miles to be with you. If I could I would make love to you a thousand times..”

“Dan Allah ka sakarmin baki na! Wallahi ciwo yake! Baka ji baya na ba...”

•

Could this actually turned into something real? Shin ya zata kaya ne da zukatan masoya biyu wanda suke da banbance-banbance a tsakanin su? The class of the have and the have not??? Suraidah 'yar gidan wani babban oil tycoon ce. Muhammad Mahboub kuma d'an gidan talakawan talak ne. Shin ya zata kaya ne da qulluwar zuciyoyin wanda ba tsaran rayuwa bane ballanatana aure😮? Tab Shin ya kuke ganin wannan ruguntsumin zai kaya? Dr Falal Rabiu mai Mai wani sanannen billionaire ne wanda keda rijiyoyin mai a fad'in Najeriya, yana taimakon talakawa amma shi kam baya son talaka ya rab’e shi. Taya za’ai Muhammad Mahboub ya zamto siriki agare shi? Kai abin da kamar wuya. Mahboub *ANNURIN ZUCIYAR* Suraidah ne. Da sonshi ta rayu ya rene ta ya girmama a zuciar ta. Shin ko Suraidah zata iya bijerewa mahaifin nata? Tab! dankari Makari. Akwai cakwakiya fa, kun ta6a ganin talaka mai tsattsauran ra'ayi? Ku biyoni muje dan kuji me za'a kulla a tafiyar. Wannan labarin yasha banban da sauran rabarai na, zai ta6a zuciyoyin masu karatu, sannan zai fad'akar daku masu karatu, insha Allahu zai sanyaku nishad'i. Akwai zazzafar soyayya da kuma zazzafar kiyayya, akwai jarumtaka, sadaukarwa ta fannoni da dama, *ANNURIN ZUCIYA* daban yake a cikin sauran labarai. Domin mallakar ANNURIN ZUCIYA na marubuciyar MUSAYAR ZUCIYA (HAJJAH CE) ku tuntubi lamba kamar haka akan nera dari biyu kacal: +234 706 528 3730